Ouummey 001  [ 6/12/2024 1:42 PM ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)
✍️ Ouummey
Free book!!!

page1️⃣

____________________Da ƙarfi aka buga ƙofar ɗakin tare da shigowa, a dan firgice na dago kai na daga sunkuyar da shi ɗin da nayi, sedai Kafin nayi wani yunkuri tuni naji an rufe ni da duka

"A'a a'a, kai Safiyya, me yasa bakya jin magana ne".

Fadin yaya tana kokarin hana  Mama dake amsa sunan Safiyya dukana.

"Ki bar ni yaya, ki bar ni in sabauta yarinyar nan ko zan ji sanyi a raina, wannan wace irin ƙaddara ce, ka haifi da a cikin ka ya zame maka musiba, wallahi ina nadamar haihuwar yarinyar nan, da na sani da tun a ciki na zubar da ita na huta da bakin ciki".

Yayah  ta janye Mama tana fita da ita daga ɗakin

"Ki dena fadin irin wannan mugayen kalaman kan yar da kika haifa da cikin ki dan kin san bakin uwa, ki kuma yi hakuri ki daina wannan kukan dan ba abinda ze kara face musiba ga rayuwar ta yau ace mahaifiyar ta na zubda hawaye akan ta".

"Banni Yayah, banni nayi kuka, tun fara girman NU'AIMAH take kunsa min takaici kala kala, ban da bakin ciki babu abinda na amfana da shi a rayuwar yarinyar nan, wace irin soyayya ce ban nuna mata ba, wane irin kauna ne ban gwada mata ba, a duk cikin ya'yan da na haifa wa na so na kauna kamar ta, wa nai wa gatan da nayi wa AIMAH?, amma kaf cikin su ita ce kadai me bakan ta min rai, ki fa duba irin tashin hankali da gwagwarmayar da ta saka ni shekara biyar zuwa uku baya, shine kuma duk be ishe ta ba se ta sake wani yanzu? Kashe ni take son yi ko me, wai Allah ni Safiyya na shiga uku".

Ta kai karshe tana sake rushewa da kuka,

"Koma dai ya faru a baya fa har da laifin ki Safiyya, ko da laifin AIMAH amma zan iya cewa naku ya fi yawa dan kuka bata dama ku ka sakar mata kuka kuma sangarta ta shiyasa ta taso a haka, se kuma daga baya kuce zaku gyara ta, bayan shi ice tun yana danye ake tankwara shi, in kuwa ya girma aka ce za'a tankwara sedai ya balle".

Ajiyar zuciya Yayah tayi tare da riko hannun Mama

"Kiyi hakuri da yanayin ƙaddarar ta Safiyyah, ki kuma koyi yin kyakkyawan kalami a kan ta, ina ji a jikina komai yazo karshe a wannan lokacin Insha Allah".

Zare hannun ta tayi daga na Yayahn

"Na dade da zare Aimah daga cikin addu'a ta dan ba lafiyar ƙwaƙwalwa ce bata da ita ba balle ace ai bata san daidai ba, haka kuma ba aljanu gare ta balle ace she's possessed, kawai tsabar iskanci da jin ita ta tsaga ne dan haka na bar bata lokaci na wajen mata addu'a tunda Allah ai ya azurta ni da wasu ya'yan bayan ita, taje tayi rayuwar ta duk yadda taga zata iya sedai ɓacin ran da take sani da damuwa da sannu itama zata haifa kuma zata gani, Abu daya na sani shine wallahi se na raba wannan kaddararren auren tsakanin ta da MASDOOQ, dan shi ɗin ya fi karfin ta, ba sa'an auren ta bane dan haka se ya sake ta taje ta naimo daidai ita".

"Ashe baki da hankali Safiyya, auren da aka ɗaura ɗazu ɗazu kike maganar rabawa?".

"Shi dai Yayah, ashe ma in na bar auren taci riba kenan, bayan duk abinda tayi a baya kina tunanin ta dace da samun irin wannan damar ne?, Sam wallahi dan haka kar ki ma fara ce min in dakata Yayah dan a wannan karon ba zan ji ki ba".

"Nima kuma ba zan saurari haukan ki ba dan haka auren Aimah da Masdooq ban ga wanda ze raba shi ba ko da kuwa shi ɗin da kan shi ne".

A mamakan ce Safiyya ta kalli yayar tata

"Kar ki yi haka Yayah, kar ki fara fadar haka, kar ki sa zuciya ta ta fara saka min tunanin dan Masdooq yana dan ki ne yasa kika fadi haka Yayah".

"In har haka zuciyar ta ki ta saka miki to ki dauke shi as hakan, dan na gama magana, Aimah ta zama matar Masdooq and ba zan yadda da duk wani matsala da zata shigo tsakani ba".

Yayah na fadar haka ta tashi ta fita daga ɗakin leaving Safiyya wadda ake kira da MAMA na rushewa da kukan karin takaicin kalaman dake fitowa daga bakin yayar ta ta da bata da wadda ta fita, wadda take ganin ko kowa yaki goyan bayan ta ita zata yi sedai gashi tun kan aje ko ina ita ta fara kwaye mata baya, sedai wallahi baza ta bari ba, aure ne se ta raba shi sedai duk abinda ze faru ya faru, ai itama NU'AIMAH yar ta ce, itace ta haifi abar ta dan haka zata yi iko da ita.

*********

A can ɗakin kuwa ni Aimah ce zaune na hade kai da gwiwa cikin wani irin tashin hankali , a kallon farko me kallo na ze shaida n din amarya ce dan kuwa kayan jiki na masu matukar kyau

da tsada dake ta daukar ido sun fallasa hakan, ban da kuma tsararren kunshin dake kan kyakkyawar fair chocolate skin dina.

Shigowar da naji anyi dakin yasa na ɗago a firgice dan nayi tunanin Ummi ce ta dawo, a boye na sauke ajiyar zuciya tare da lumshe idanuna da suka yi jajajaja na tashin hankalin da nake ciki.

"Aunty Aimah an daura auren tun dazu, guess what, da yayanmu aka daura fa, bari kiji recording din da Walid ya turo min".

Bata tsaya kallo na ba balle ta kalli reaction di na ta shiga danna wayar hannun ta cikin rawar jikin farin ciki, recording din ta kunna tare da matsowa dab da ni

"An daura auren NU'AIMAH BASHIR da angon ta MASDOOQ MUHAMMAD kan sadaki dubu ɗari biyar lakadan ba ajalan ba".

Kalaman suka shiga kutsawa cikin kunnuwa na tare da kurdawa cikin kwakwalwa ta suna ratsa dukkan wata jijiya ta jikin na, a sannu na fara jin wani irin sanyi na ratsa gabban jiki na, jijiyoyi na na sakewa haka kuma wani yanayi na ratsa zuciya ta.

Ban san lokacin da ba dauka a haka ba se buɗe ido nayi naga babu sumaiyya, cousin di ta ta bangaren baban mu da ta kawo min labarin.

Sake maida idanuna nayi na kulle cikin zurfin tunani, gaba daya kwakwalwa ta ta cushe, tunani na ya gushe kamar yadda lissafi na ya ba ce, se yanzu na gane dalilin dukan da Mama ta rufe ni dashi dazu, se yanzu na gano kukan da Mama ke yi dazu.

Mahaifiya ta ce da zan iya dafa Kur'ani na rantse cewa ita ta dauki ciki na tsawon watanni tara, tayi nakuda ta ta haife ni, ta kuma raine ni cikin tsananin soyayya da gata amma tashi daya yanzu bata da makiyya kama ta, ta tsane ni kamar ta manta ita ta haife ni, ban taɓa ganin tsana daga wajen wani mahaluki ba kamar wadda Mama ke gwada min yanzu.

Na sani na cancanci hakan, na kuma kama ci hakan daga kowa amma ban da Mama da duk wani ahalin gidan nan domin kuwa ko me na zama yanzu SU NE SANADI, ko me nayi a baya SU NE SUKA JA MIN, amma kuma yanzu se suce zasu juya min baya?.

Yayye na daidai har biyar duka maza, acikin su ba wanda be gwada min kauna da gata mara algus ba, amma yanzu ba wadda suka tsani su buda ido su gani kamar ni, shin laifi na har ya kai su min haka? Ko kuwa dama ba su taba kauna ta bane, ko kuwa.......!.

Tunanina ya katse sanadin bude kofar da aka kuma yi, wannan karan ban iya nako ɗago kai ba balle na kalli me shigowar dan zuciya ta tayi wani irin rauni, tarin damuwoyin da nake dannewa wata da watanni sune suka bijiro min tare da rauna ta duk wani kuzari na.

Daga bakin kofar itama ta tsaya cikin hade rai dan karfin hali ne kawai take yi dan hakan ne ya kamata,

"Ki tashi ki yafa mayafin ki muje na kai ki gidan mijin ki".

Bam san a ina na samo karfin da na ɗago a zabure ba jin kalaman Hajiya Yayah kamar yadda mu yara ke kiran ta

"Eh haka nace, ba dai mamaki kike ba ko, ke da me kike zato, a tara mutane a tafi kai ki gidan aure kwana kadan ki ɓallo ki dawo da abin kunyar da ze sake barar mana da dan ragowar mutuncin da ya rage mana? To in haka kike tunanin maza ki aje shi gefe ki mike, kafin kuwa Uwar ki ta zo nan dan ban da na janye ta a kan ki kin san se ta kusa kashe ki, ja'ira mara jin magana".

Cikin wani irin kunar zuciya na mike dan kuwa kalaman Hajiya Yayah gare ni jin su nayi kamar rushin wuta a rai na, amma kuma ai kome suka fada ni na jawa kai na, komai aka ce a kai na na cancanta ne, da na kasance yarinya ta gari da duk ba za'a fada min ba, da naji maganar iyaye na a lokacin da suke fada min da duk komai be faru ba, da tuni na ina cigaba da rayuwa da kaunar ahali na gare ni, amma a lokacin se na kasa yi musu biyayya, na kasa duban darajar su, na zabi farin ciki na saman na su, na zabi saɓa musu dan wani cikar buri na da Allah ya jarabce ni da shi, dan haka dole nayi hakuri na shanye koma me za'a ce ko za'a yi mon, watarana se labari.

A hankali nake takawa zuwa wajen motar Hajiya Yayah da take Parke a compound din gidan, duk inda na wuce haka jama'a ke bi na da kallo suna kus kus abinka da gidan biki.

Har wata ajiyar zuciya ce ta kwace min lokacin da na zauna a seat din gaba da Hajiya Yayah ta buɗe mim dan idanun jama'a da suka min yawa kamar sa kada ni.

Tada mota Hajiya Yayah tayi tare da ficewa daga gidan bayan me gadi ya buɗe mata gate, wani irin yanayi na rashin jin dadi ya darsu a zuciya ta ni Aimah, gidan aure ne fa na tafi batare da sa albarkar iyaye na ba, se ma tarin bakin ciki da ɓacin rai tare da fushi me tsanani da mahaifiya ta ke yi da ni, anya kuwa zan ga daidai a rayuwa ta?, Anya zan ga alkhairi a gidan aure na, anya kuwa aminci, salama tare da kwanciyar hankali zasu ziyarci rayuwa ta?!.

Bana tunanin hakan, dan ko ba wannan situation din daga iyaye na shi mijin fa?, Shine dai Masdooq da na ki shekarun baya, shine dai Masdooq da ma guda a baya, shine dai na zaga, na wulakanta na kuma guda a baya, anya ze yafe min kuwa?, Anya ze dube ni da idanun rahma balle har ya karbe ni a matar aure?, Anya ze iya sake dubana kuwa?, To in ma ya dube nin shin ni da wane idon zan daga ta kalle shi?, Lallai akwai sauran rina a kaba.

Kallo na Hajiya Yayah tayi ganin yadda na rakube kan seat kamar wata marainiya, kallo daya

za'a min a ga tashin hankali da damuwar dake shimfide kan kyakkyawar fuska ta wadda a baya walwala da farin ciki ne mamaye da wannan fuskar.

Mai da kan ta tayi kan titi tare da cigaba da tukin ta,

"Duk wanda yace ze yi wa rayuwa garaje tabbas yana tare da nadama da dana sani. A baya ke din halitta ce mafi soyuwa gamu iyayen ki, yan uwan ki har ma da abokan arzika, a cikin ya'ya ba kowane ya samu gatan da kika samu ba, ba kowane ya samu soyayya da kaunar da aka gwada miki ba, amma duk kika sa hannu kika tankwabar da wannan, kika sa kafa kika shure, kika zabi namiji kan mu, kika fifita damuwar ki kan mutuncin iyayen ki, kika daukaki san zuciyar ki kan umarnin ubangiji, taya ya?, Nace taya ya zaki ga daidai Aimah?.

Su iyaye daraja ne da su, iya haifar ki kawai da aka yi an gama da ke ko da kuwa ace ba ayi kowace wahala dake ba bayan haka, amma ke se kika nuna naki iyayen ba wasu bane, banza ma tafi su daraja a wajen ki, Manzon Allah ya jaddada mana darajar iyaye gare mu musamman kuma uwa mace da seda ya ambace ta matsayin wacce za'a a kyautatawa har so uku kafin ya ambaci mahaifi, Aimah ka bauta wa Allah ka kiyaye dokokin sa ka bi uwa ka bi uba a wannan duniyar ya ake karewa balle ke da kika zabi tozarta su madadin biyayya?.

Hmmm, bana miki baki, bana kuma yi miki fatan wahala amma kina da sauran aiki a gaban ki, kin ga wannan auren kan sa gare ki sabon kalubale ne, haka kuma dalilin da yasa zan tsaya kai da fata wajen ganin ba'a kashe shi ba shine dan ki samu experience na rayuwa, dan ki kara hankali a rayuwa, dan kuma ki fahimci ba koyaushe kake rasa abu ka kuma samun damar sake mallakar sa ba, haka ko ka samu damar akwai tarin kalubale, Masdooq da kika sani a baya bana tunanin shi zaki tadda a yanzu, haka kuma rayuwar sa ba irin ta baya bace dan kuwa yanzu shi ɗin magidanci ne me mata da ƴa daya, wani karin kalubalen gare ki kenan wato matar sa.

Na sani, kin sani, kowa ya shaida SA'ADAH ba fitinanniya bace, yarinyar kirki ce me hakuri da biyayya, wannan halayen su suka siya mata soyayya wajen mijin ta kuma mijin ki a yanzu, dan haka bana tunanin samun gurbi a wajen shi gare ki yanzu abu ne me sauki domin ya saba da bari na bari, yi nayi da dukkan nau'i na biyayya da girmamawa, kar kiga a baya yayi tolerating tsayayyar ki yanzu ma kiyi tsammanin haka ne, sam sam dan haka se ki shirya tunkarar sabuwar jarabawar ki.

Abu daya nake so ki sani, shi hakuri magani ne na dukkan kowace matsala, addu'a makami ce na yakar kowace damuwa, kamar yadda ba zan iya bayyana miki tasirin biyayya ba, dole kuma se kin koyi kau da kai.

Sedai fa kar in ji kuma kar in gani, na san SA'ADAH kamar yadda na san ki, duk naji fitina da wata matsala na san daga gare ki ne, ba kuma ina fadin hakan dan wai Na tsane ki ko na fi son ta ba, a'a sedan dukkan ku na san ku, haka kuma kauna ce tasa nake miki wannan karatun.

Eh ina jin haushin ki me girma Aimah, amma iyaye basu taba kin dan su ba sedai kokarin yi masa gyara, in kika dage kika jure da sannu komai ze wuce rayuwar ki ta dawo kamar da ke har ma ta iya fin da wajen daidaito, farin ciki da kuma kwanciyar hankali".

Hajiya Yayah na rufe bakin ta ta shiga yin horn gaban madaidaicin gate din gidan, haka kuma na kwashe komai a kai na na daga nasihar ta ina yi wa kowace kalma fashin baki da har ban san mun shiga compound din ba.

"Fito ko".

Ɗagowa nayi na kalli Hajiya Yayah da fuskar ta take nan ba yabo ba fallasa kana na fito da kyar kamar wadda bata da laka a jiki, ko kafin na karasa fitowa tuni Hajiya yaya tayi gaba abinta.

Da sallama na shiga cikin falon a rai na kai na na sarawa, rayuwa ta ta baya a gidan na dawo min daki daki

"Wai wane irin shashanci ne wannan ina miki magana kina ji na, ko kin fara kurman cewa ne ban sani ba".

Da sauri nayi gaba jin fadan Hajiya Yayahn da ta ja tsaki tana min pointing wani daki

"Gashi nan ki shiga nan ki zauna kafin ya zo ya san yadda ze yi dake wajen gurin zama, in kuma duk a nan din zaku zauna se kuyi magana, me gidan bata nan dan haka ni ba ni da abin yanke wa, dakin baki ne kuma ciki da falo ne".

Ta faɗa bayan mun shiga cikin falon da me aiki ta buɗe mana, ba musu murya can ƙasa kamar ba Aimah ba nace

"Angode Allah ya saka da alkhairi".

Batare da ta amsa mim ba ta juya ta fita dan sauri take taje ta sami SA'ADAH ta taushe ta sanin sam ba'a kyauta mata ba, sedai ya zata yi WATA KUSAN TAFI WATA.................✍️.

Assalamu alaikum jama'a, barkan mu dai, fatan duk muna lafiya, kamar yadda Allah ya tsara gamu mun sake hadewa cikin wata sabuwar tafiyar da ku, fatan zamu ilmantu, mu nishadantu mu kuma wa'azantu, kuma ku kwantar da hankalin ku, BA KOWANE SO BANE..free book ne domin jin dadin masoya na.

Fatan kawai ku faranta min ta hanyar sambado like, Comment tare da taya ni sharing, yawan comments din ku ne ze yi determining wether to proceed or to stop!!!.

Ga masu neman litattafai na na baya, su tuntubi wannan number 👇
09013101854, heart you all ❤️.

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 002  [ 6/13/2024 8:59 PM ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)
✍️ Oummey
Free book!!!

Ouummey 002

Page2️⃣

________________ Kallan dakin nake yi fuskata dauke da wani yanayi mara fassaruwa, dakin baki ne me ɗauke da ciki da falo, falon karami ne sosai dan one and two sitters kawai ya dauka, se karamin fridge dake gefe.

A hankali na taka na zauna kan kujerun, wanda alamu ya nuna ana gyara dakin koyaushe dan a tsaftace yake babu ƙazanta.

Na dade zaune a wajen kafin nan tashi zuwa bedroom din, nan din ma karami ne dan kuwa gadon kwanciyar mutum daya ne baze ci mutum biyu ba, shima nan din a gyare yake sedai babu bedsheet a kai, na wuce toilet shima na duba, shima dai ba laifi duk da be min yadda nake so ba amma dai ba ƙazanta.

Ban fara karambanin wankewa ba na koma falo na zauna tun da ban san matsayi na ba a gidan, nan din kamar wajen zaman wucin gadi ne kafin me gidan ya dawo ya san yadda zeyi da ni kamar yadda Hajiya Yayah tace.

Zama nayi na zuba tagumi ina tunanin rayuwa, a yadda na budi ido na taso ban taba tunanin rayuwa ta zata juye irin haka ba, ban taba tunanin akwai wata ƙaddara da zata ratso tayi tafiyar yaji da gata na da jin dadi na ba, se gashi tashi daya komai da kowa ya watse, abin da na fi karfi a baya yanzu ya fi karfi na, rayuwar da nake ganin wasu a ciki na tausaya musu se ga shi nima na tsinci kaina a ciki dumu dumu.

Ban san kuka nake ba se da na ji digar sassanyan ruwan hawaye na kan hannu na dake aje kan cinya ta, ban iya na daga hannu na share ba saboda hayaniyar da naji na tashi a compound.

Kamar munafuka haka na tashi na daga curtains din dakin ta bangaren compound, a lokacin ne na fahimci me ke faruwa dan kuwa SA'ADAH ce wasu mata biyu dan ban gama shedawa ba suka riko, irin kukan da take yi seda ya sa naji wani dam a raina, haka kumq kirji na ya shiga dukan uku uku.

A falo suka zaunar da ita kan sofa suka zagaye ta suna bata hakuri ita kuma se kuka kawai take yi, da kyar ta iya bude bakin ta ta fara magana muryar ta na fitar da sautin kuka haka kuma tana rawa

"Me yasa sai ni? Me nayi wa Hajiya Yayah me zafi da ta yanke min wannan zazzafan hukuncin? Aunty A'i me yasa duk kusancin ka da mutum da kaunar da ze nuna maka wataran se ya fifita nasa a kan ka duk min girman zunubin nasan?, Ina nan nan gidan yarinyar nan ta tozarta Ya Masdooq, a gaban kowa ta zabi wani ta bar shi, a kan ta wane irin wulakancin da tozarci ne ban fuskan ta ba Aunty, na sha wahala matuka da Masdooq kafin ya manta da ita, na yi kuka har idanuna suna neman samun matsala kafin na samu Masdooq ya dube ni, iya iyawa ta kuma faranta ran Hajiya Yayah nake, da dukkan zuciya ta nake kaunar ta kamar uwa ba wai uwar miji ba, saboda ta nuna min gata, ta tsaya min a lokacin da ba wanda ze iya, amma me yasa yau kuma take neman rusa fadin ciki na, shin me na mata na ba daidai ba, a ina na kuskure, dan Allah Aunty ku tambayar min ita zan gyara wallahi, zan kuma kiyaye maimaita hakan amma dan Allah su rufa min asiri su raba auren nan, wallahi ba zan iya jurewa ba, ban da karfin zuciyar da zan ga Masdooq na juya baya gare Ni, zuciya ta bugawa zata yi, innalillahi wa inna ilaihi rajiun".

Sa'adah ta shiga jujjuya kai tana kuka me cin rai, ni dai ina daga daki ina saurarensu, kirji na yayi min nauyi haka kuma ina jin kunyar daga ko curtains ne na kalle su, a lokacin ne naji Muryar ta me sanyin nan ma'abociyar nutsuwa da kamala, muryar ƴar uwa daya tilo da na dauka jigo ga rayuwa ta, yar uwar dake iya hana cikin ta abu ta bani, yar uwar da ta tsani ganin damuwa a kan fuska ta balle aje ga hawaye, se dai a yau ba'a gare ni ne ta kasance me share hawayen ba, ga KISHIYA TA ne ta zamo me lallashin, tausasawa tare da shawarwarin ta masu dimbin fa'ida da a baya na kasa bude ido na kalle su balle nayi tunani har na gano girman fa'idar su har se da na kai kaina na baro.

"Dago nan ki dube ni SA'ADAH, kar na kuma jin ko da wasa kin ce Hajiya Yayah bata ɗauke ki

ƴa ba, kar na kuma jin ko da kuskure kin ce wai Hajiya Yayah na kokarin rusa fadin cikin ki, da dukkan zuciya ta nake sanar da ke Hajiya Yayah ta dauke ki fiye da ƴa, tana kuma kallon ki da dukkan so da kaunar da uwa zata yiwa ƴar ta, sedai a rayuwa kowane bawa da irin tasa ƙaddarar, haka kumq jarrabawar mu baze taba zama daya ba kamar yadda muka banbanta ta fuskar halaye da ra'ayoyi, ina so ki sa a ranki ba Hajiya Yayah bace ta nemawa mijin ki aure, Allah ne ya ƙaddara ƙaddarar su a sarke take da ta juna, bana kuma son ki saka hakan a ranki balle ya dame ki, ke din macece me daraja me kuma kima, ba'a iya idanun mu mu yan uwan ki ba har da idanun mijin ki, mijin ki na son ki soyayya me tsafta, hakan kuma ya samo asali ne daga kyawawan halayen ki da ya fuskan ta, tarbiyyar ki da nutsuwar ki tare da biyayya sun sama miki gurbi me matukar girma da zurfi a rayuwar Masdooq, ba zan so kiyi sakarci ko sakacin da zaki rasa su ba. Bari in fada Miki, duk yadda kika dauki rayuwa haka zata zo miki Sa'adah, dan haka ina so ki sa a ran ki karin auren mijin ki ba komai bane ba, ba kuma dan baya san ki bane, haka kuma ba dan kin gaza ba, sedan ƙaddarar shi kenan haka kema taki kenan, ki kuma sa a ran ki karin auren shi baze taba rayuwar ki da shi ba ta kowace fuska, ki cigaba da kyautata masa, ki cigaba da faranta masa da dukkan iyawar ki, kar ki sake Kice zaki tashi hankalin sa saboda haka, abinda mu mata mu ka kasa fahimta shine, daga lokacin da kika rika bori da tashin hankali kan namiji ya kara aure, daga lokacin kika fara zubar da damar ki, dan tun yana lallashin ki yana ta taki har se ya gundura ya fita harkar ki, amma in kika nuna baki damu ba, kika danne kika shanye wannan dacin wallahi shi kan sa namijin shakkar ki ze dinga yi, dan be san me kika boye a ran ki ba, kullum tunani da zullumin sa shine me zaki yi ko me zaki ce, hakan kuma ƙarin kima ze jawo Miki, dan duk yadda yake son amaryar ko yake dokin ya zaki ba za bata damar taka ki ko raina ki ba.

A karshe ina me baki hakuri Sa'adah, tabbas an Miki laifi mafi muni a wajen ya mace, sedai babu yadda muka iya, ba mu muke halittar kan mu ba balle mu tsarawa kan mu rayuwa, dan Allah dan Annabi kuyi hakuri on behalf of Hajiya Yayah da ni kaina, muna baki hakuri sosai, kamar yadda Aimah take tamu, ke ma tamu ce dan haka ba zamu dau daya mu bar daya ba, haka ma mijin ku, kamar yadda na fada a yanzu kin fi kowa sanin sa dan kin fi kowa kusanci da shi, kin san me yake so kin san me ye baya so, dan haka fiye da rabin ragamar rayuwar sa da zuciyar sa na hannun ki, se kin yi wasa ko sake ne za'a kwace miki, amma in kika zage dantse Ina tabbatar miki you'll forever be the favorite of your husband, at long last kuma ina so dan Allah ki zauna da Aimah lafiya, na san ki na san halayen ki haka ma mijin ki, dan Allah ki cigaba da kasancewa cikin kyawawan halayen ki kamar yadda ake miki shaida, kar ki bada dukkan wata dama da rigima zata fara bullowa tsakanin ku, hakan shi ze samar wa mijin ku kwanciyar hankali, prioritize your husband and his peace above komai, Insha Allah baza ki tabe ba a rayuwa".

AUNTY LUBAH, yar uwar da a gare ni ba ni da sama da ita, yar uwar da na so na kuma kauna fiye da kowa a cikin yan uwa na, yau itace zaune da kishiya ta tana bata shawarwari da zuciya daya wanda in hara tayi amfani da shi zata kai ga gaci, batare da ni ta ko tambayi inda nake ba, take kokarin daga jakarta ta bar gidan, dan na jiyo ta tana yi wa Aimah da dangin baban ta sallama, kasa daurewa nayi se da na daga curtain na shiga bin ta da kallo har sanda ta fita zuwa compound, gate man ya bude mata karamar kofa ta fice daga gidan.

A hankali na koma zaune dabar, raina na kuna zuciya ta na zafi, shin har illar da nayi wa rayuwa ta ta kai haka? Har ya zama Aunty luba ta shigo gidan da nake zaune ta fita bata tambaye ni ba, bata damu da ta ganni ba, se ma neman zama yar uwar kishiya ta datake yi.

"Kin manta dama can yar uwar Tata ce?".

Wata zuciyar ta tuna min, eh Aunty Luba yar uwar Sa'adah ce dan ba ciki daya muka fito ba.

Ita din shakikiyar Masdooq ce, wanda da mahaifiya ta Mama Safiyyah da mahaifiyar su Hajiya Yayah uwar su daya uban su daya.

Aunty Luba ita ke bin ya Masdooq, wanda tsakanin su shekaru biyar ne, ni kuma ta bani itama shekaru biyar, tun yaye ta dawo hannun Mama wadda duka ƴaƴan ta maza ne kafin Allah ya bata ni, shiyasa muka taso tare yaya da kanwa, masu tsananin so da kaunar junan su, a duk girman Aunty Luba bata da kawa da abokiyar shawarar da ta wuce ni haka ni ma a waje na bani da sama da ita, ina jin ta a raina fiye da shakikan yayye na da muka fito ciki daya, ina mata kaunar da bana yi wa yayyena na ciki daya, haka kuma ina sirrin da bana yi da mahaifiya ta da ita.

Ta bangaren Sa'adah kuma, da baban su Aunty Luba da mahaifiyar Sa'adah suma uwar su daya uban su daya, wannan yasa Aunty ta zama yar uwar mu duk mu biyun, sedai a yanzu ina ji a raina dole zan sallama ta ga Sa'adah, ba zan iya sharing ba musamman ga ita da nake kwayewa sirri na.

Na sani na yi laifin da na cancanci hukunci, na yi laifin da ba lallai a kusa kusa ba na samu yafiya, amma ai in bera da sata to daddawa ma da wari, in na dauki kaso saba'in na laifin to kuwa Lallai su suna da talatin, amma me yasa suke tattara komai gare ni ni kadai? Me yasa ni kadai nake daukan nauyin zunubin duka, anya an min adalci  kuwa?.

Abinda Aunty Luba tayi yau ya taba raina matuka gaya, ko da na cancanci hukunci amma ba irin wannan ba, daukan side din kishiya ta da tayi ya taba raina sosai.

"KISHIYA". Na fada a hankali da wani irin daci a kan harshe na, na sani tun a baya wasu Shekaru da suka wuce Sa'adah na nuna ra'ayi kan mijina, sedai a lokacin babu kowa gaban shi da cikin ran sa in bani ba, wannan yasa ban damu ba sosai, amma tun da na gane bana yarda na sakar mata fuska in tazo gida na, har ya kai itama bata san zuwa din, tun tana ɓacin kira da turo masa sako har ta hakura ta daina, dan lokacin idanun sa sun rufe ruf akan so da kauna ta, wanda ni da kai na na sa kafa na hambarar, ban tsaya iya nan ba se da na gasa masa maganganun da na san zasu tunzura shi ya bar ni in tafi zuwa ga muradi na, cikar buri na, wanda na san har duniya ta naɗe ya Masdooq baze taba manta wa ba, kai in nace ya manta ma ai na so kaina dan ban fadi iya abinda ya kamata a manta din ba.

Sedai duk a cikin shikashikan rashin mutuncin da na shuka, a cikin rashin albarkar da na watsa masa, akwai wani abu guda daya da ya tsaya min a rai, wanda duk yadda na so na yakice shi na kasa, nake kuma nadamar yi har kawo yau shekara biyar da aikatawa, lamarin da ya sabbaba zubar hawaye a idanun gwarzon namijin da ban taba ganin ɓacin ran sa ba balle nuna damuwa ga rashin hankali na, wannan dai aikin da yaja za min mumman tsana a idanun yar uwa daya tilo da zan iya bugar kirji in nuna matsayin tawa, ya zama na ta yanke alaka dani kwata kwata, ta kuma nuna bata kaunar sake hada inuwa da ni.

"Ya Allah na tuba, Allah na tuba ka yafe min, ya Rabb ka dube ni kamin afuwa ko na samu sassaaucin wannan jarrabawa da nake ciki".

Na fada idanuna kwararar da tawayen nadama da kaico, da basa fasa fita a duk sanda na tuna da wannan mummunan aikin nawa.

Kiran sallar magrib yasa na mike jiki ba kwari na shige bedroom tare da kunna ruwa a toilet nayi alwala, da lafayar jiki na na gabatar da Sallah bayan na shimfida dankwalin tsadaddiyar atamfa ta, ko da na idar ban tashi ba, addu'o'i na cigaba da yi tare da istigfar cikin neman gafarar ubangiji, daga inda nake kuma inq jiyo kara kainar matar gidan ta shige da ficen ta, har zuwa sanda kamshin daddadan girki ya kawo min ziyara, se kuma a lokacin da ciki na yayi kuka na tuna rabo na da abinci tun jiya da daddare, dan da safe tea kawai na iya sha, da rana kuwa kasa kai komai baki na nayi saboda zulumi.

A hankali na gicciye na kishingida kan dankwalin daidai da fara vibrating din waya ta, da kyar na lalubo ta saboda duhun da dakin yayi, seda gaba na ya yanke ya fadi ganin sunan babban yaya na kan screen din.

Ban da kuzarin dagawa dan haka har ta yanke wani kiran ya kuma shigowa ina kallo, shima ya yanke wani ya biyo baya sannan na iya karfin halin dauka gabana na faduwa murya na rawa nayi sallama sedai tuni ya tare ni cike da hayagaga da fada.........................✍️.

Vote
Comment
Share fisabilillah

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 003 [ 19/6/2024 9:21pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)
✍️ Oummey
Free book!!!

Ouummey 003

Page 3️⃣

___________________"Dalla rufe min baki ki saurare ni dan ba gaisuwar ki na kira in ji ba, yanzu haka Mama na kwance a gadon asibiti saboda bakin ciki da takaicin ki, wallahi duk kika sake wani abu ya samu mahaifiyar mu saboda ke ki kuka da kan ki dan se na tabbatar na wulakanta ki, shegiyar yarinya me zubin mayu, kuma wallahi ko da wasa na samu labarin kin zo gidan ko kuma kin kira ta a waya se na kusa kashe ki, tun da kin ce ke bakya jin magana kuma ba'a isa a saki ba to ki nemi wasu yan uwan, dan ko da wasa kada ki sake ki kuma kina da wani dan uwa me sunana, bani wayar nan Yaya Salman".

Naji Muryar Ya Najeeb bayan yaya Salman ya gama nasa, be jira komai ba kuma ya mika masa shima ya dora nasa, daya bayan daya haka yayye na uku suka tabbatar min da babu su babu ni, tare da kashedi me tsauri kan mahaifiyar mu da kuma zuwa gidan mu, Yaya Ahmad ne kadai ne be sanar da ni ya yafe ni ba, ya dai min fada cikin nutsuwar sa kamar yadda ya saba, ya kuma min nasiha a karshe, kafin Ya Salman ya karba ya sake zage ni tas.

Ban ma san ya kashe wayar ba tsabar nisa da nayi cikin tunanin irin rayuwar tashin hankalin da nake ciki, babban abinda yafi damuna a lokacin shine jin Mama na kwance a gadon asibiti hawan jinin ta ya tashi, hawan jinin da ta same shi a dalilina yanzu gashi ya kuma tashi a dalili na.

Anya kuwa akwai mara Sa'a a rayuwa kamar ni? Anya kuwa akwai wadda rayuwar ta bata da wani amfani da ma'ana irin tawa?.

Kuka nake, kukan fili da na boye, zuciya ta na zafi raina na kuna, ina tur da Allah wadai da halaye na na baya, ina kuma kukan rashin samun dama ta biyu wajen iyaye na da yan uwa na, rashin bani damar bayyana musu canji na, rashin bani damar bayyana musu nadama ta, kukan da ban san yaushe zan daina ba.

Ban ankara ba se kiran Sallar Isha na ji, sedai yadda jiri ke kwasa ta kaina na juyawa yasa na kasa tashi balle na gabatar da sallar, har wajejen karfe goma ina nan wajen a yashe, tun ina jin motsin kai kawon Sa'adah har na ji shiru, har kuma lokacin ruwan hawaye sun kasa kafewa daga idanu na, wanda na san da suna karewa da tuni nawa sun jima da karewa dan irin kukan

da nayi shekaru biyar baya zuwa wanda nake yi yanzu Allah ne kadai ya san shi.

A hankali na kokarta na tashi zaune tare da gyara zaman lafayar kaina na tada sallah daga zaunen, a haka na gabatar da Isha dan in nace zan mike bana tantamar irin kayin da juwa zata min.

Waya ta da ta fadi gefe na tun sa'ilin da ya Salman ke min zagin karshe na jawo na duba lokaci, karfe goma da hamsin da biyar agogon wayar ya nuna, idanun na kuma suka sauka kan power bank din wayar da ya bayyana saura 2% kawai da nasan ko yaushe zata iya mutuwa.

Da taimakon Allah na mike zuwa bedroom din na bude toilet tare da wanke fuska ta na kuma tara hannu na shiga shan ruwa ba kakkautawa dan irin yunwar da nake ji jikina har wani kakkarwa yake, yana daya daga cikin abinda duk wani makusanci na ya sani rashin jure yunwa ta, sam bani da sauki ta bangaren abinci, ina da saurin jin yunwa kamar kuma yadda bana iya jure ta, yanzun nan se in fita a hayyaci na, akan haka mun yi yawon asibiti sosai da Mama da Abba sedai amsar daya ce, lafiya ta lau kawai halitta tace a haka.

Seda na cika cikina da ruwa sannan na fita, se kuma nayi tsaye ina karewa gadon kallo, tashi daya idanuna suka kuma cika da hawaye, wani shuɗaɗɗan al'amari na dawowa cikin kwakwalwa ta da idanuna.

Ban manta ba, kamar dai war haka dan lokacin ze kai sha daya ko ya haura kadan, na fito daga wanka daure da karamin towel din da be gama ratsa ni ba, kasancewar ina da matukar jin zafi yasa ban yi tunanin saka kaya ba, na fada kan sabon bed dina dake amsa sunan na aure ba daure da towel dina zuciya ta na fada min ai baze yi gangancin shigo min daki ba dan be taba kwatantawa ba, lokacin satin mu biyu da aure, sedai cikin bacci na da a lokacin yayi min mugun dadi dan ta ko ina iska ratsa ni take yi kawai na fara jin wanzuwar wasu sababbin al'amura cikin jiki na, tsananin firgitar da nayi ya sani kasa shaida shine muka shiga dambe, duk yadda yake fada min shi ne ban fasa kokawa da shi ba dan a lokacin na tashin hankali na nunkuwa yayi dan babu abinda ya fado raina face alkawarin da na daukawa muradi na na kin mallaka wa kowa kaina face shi, wannan yasa na kasa fahimta da jin lallashin sa gare ni har ta kai ga yasa min karfi ya karbi abinda yake hakkin sa kuma mallakin sa, wadda se da yayi nadamar da baki baze iya misalta ta ba dan kuwa komai ya sake rincabewa ne bayan faruwar wannan babban al'amari.

Wani busasshen murmushi ne yayi escaping lips Dina da na tuna irin yadda ya rikice da lallashi na da ban baki saboda yadda nake wani irin kuka kamar zan mutu, kai kace ba miji na ne ya same ni ba wani katon dan ta'adda ne.

Duk kuma irin kulawa da kauna tare da tarairayar da yayi min be sa na fasa ja masa Allah ya isa da musibu ba wanda be damu ba, bukatar sa kawai shi in yi hakuri in daina kuka.

Tsananin ja da idanun sa suka yi lokacin da na ambata masa sunan muradi na ina kiran da na

san haka zata faru da shi na mallakawa kaina ko da kuwa babu aure be sa ya dage ni ba ko duka ko da kuwa mari ne, se dai yayi fushi da ni ta yadda be kuma lallashi na ba, be kuma ban hakuri ba amma fa be fasa kulawa da ni ba har na warke kamar yadda fushin sa be sa na fasa duk rashin mutuncin da na san ze bakanta masa ba, dan ni a waje na ɓacin ran sa shine buri da farin ciki na.

A yanzu haka da na tuno irin kulawa da tarairayar da na samu se na ke jin ina ma ana dawo da da, ina ma ban kasance me taurin kai ba, ina ma ban bari zuciya ta tafi karfi na ba, sedai akace danasani keya ce, musamman irin tawa da ba zata taba amfanar da ni ba.

A sanyaye na warware lafayar jiki na na shimfida kan gadon tare da zama a gefe, kananan kitson kaina da aka min na aure suka zubo a gadon baya na da gaban fuska ta, da kyar na iya daga hannu na maida su baya Kafin nayi addu'a cikin nauyin baki na shafa sannan na gicciye kwance, ba wai dan ina tunanin zan iya bacci ba, sedan sanin zata bani kariya daga dukkan wani abin ki na fili da na boye.

*******SA'ADAH******

Duk yadda take cikin damuwar mummunar ƙaddarar ta be hana hankalin ta tashi ba tare da duba agogo duk bayan wasu mintuna, jinin ta a tsinke yake na damuwar inda yake a wannan tsohon daren.

It's very unusual of him staying late a waje, shi ba hira yake fita ba wajen abokai dan da ya dawo daga aiki baya kuma fita se sallah, in kuwa ya shiga gida after Isha to se kuma gobe in Allah ya kai mu indai kuma ba wani abu ne ya faru ba na daban, kuma ko an samu akasin da ze kai ko da karfe tara ko goma ne a waje se ya kira ya sanar da ita, amma dubi lokaci fa yau, its to twelve amma shiru, ta kikkira numbers din sa duka ukun basa tafiya, karin tashin hankalin ta ma switch off da service ke sanar da ita.

A hankali ta samu hannun kujera ta zauna tana dafe kan ta da taji ya sara mata da wani tunani da ya shige ta mara kan gado, sedai da sauri ta kawar da shi tare da fara karanto duk wata addu'a da ta zo bakin ta kan Allah ya kare mata shi a duk inda ya ke ya dawo mata da shi Lafiya.

Wata kakkarfar ajiyar zuciya ce ta kwace mata lokacin da ta ji karar bude gate, jiki na rawa ta daga curtains din ta idanun ta suka sauka kan gaban motar sa dake shigowa compound din.

Se da ya gama shigowa gaba daya gate man ya maida gate ya rufe sannan ta saki curtains din tare da neman kujera ta zauna jiran shi ya shigo.

A sannu ya bude kofar motar ya fito hannun sa dauke da suitcase din sa, ya maida kofar ya rufe

tare da locking motar sannan ya yi wa gateman se da safe ya nufi ƙofar falon gaban sa na faduwa da irin abinda ka iya zuwa ya dawo, wannan shine dalilin sa na kasa dawowa gida a lokacin da ya saba.

Tun da Hajiya Yayah ta kira shi gida ta masa bayanin abinda ke faruwa yake cikin tashin hankali, da ace ra'ayin sa ta nema baze bata lokaci ba ze hanata aikatawa dan baya bukata kuma baya so, rayuwar da yake gudanarwa yanzu cike take da dimbin farin ciki, jin dadi hadi da kwanciyar hankali dan haka baya buƙatar duk wani abu da ze kawo masa tsaiko ko nakasu a cikin ta, shigowar ta rayuwar sa kuwa ze iya rantsuwa babu abinda zata kawo masa face rikici, rashin kwanciyar hankali, fargaba da damuwa, shikuma be shirya wa duk hakan ba.

Above all shine ya riga ya rufe babin ta a rayuwar sa, hatta zumunci da ita ya yafe baya bukata, sedai Hajiya Yayah iko tayi a kan sa sannan take sanar da shi, tare da kanagarkin ban hakuri da kalamai irin na uwa, da rarraahi irin na mahaifiya haka kuma da umarni irin na isa, ta ya ze iya duban ta yace baya san jinin ta? Taya ze kalle ta yace base yi mata biyayya ba?.

Wannan yasa ya amsa wadda dacin hakan har yanzu be bar kan harshen sa ba, zafin lamarin be bar zuciyar sa ba.

Karin tashin hankali da fargaban sa shine Sa'adah, be san da wane idon ze dube ta ba, be san da wane yare ze mata bayani ta fahimce shi ba, duk da ta kasance me hakuri da biyayya, duk da ta kasance me hangen nesa da iya danne zuciyar ta, duk da ta kasance me fahimtar sa cikin kowane yanayi baya jin a wannan lokacin zata masa uzuri, baya jin zata saurare shi balle har ta fahimce shi, ita din wani babban jigo ce a rayuwar sa da baya san duk abinda ze kawo girgiza gare shi, ta tsaya masa a lokacin da ya kasa, ta tallafe shi a lokacin da yake neman durkushewa, ta so shi amidst zallar kiyayyar da aka nuna masa, ta yi hakuri da shi lokacin rashin dadin sa haka ta jure zama da shi a lokacin da yaki kallon ta har yazo ya fahimci amfanin ta ya karve ta hannu bibbiyu, bata taɓa korafi ko mita gare shi ba, kome yace bi take yi ba ja in ja, taya ze mata wannan sakayyar, sam bata cancanci haka daga gare shi ba, amma yaze yi? Wadda ta isa da shi take kuma kaunar shi fiye da kowa ce ta aikata, ba shi da abin yi shima face biyayya.

A hankali ya tura kofar falon cikin sanda kamar mara gaskiya zuciyar sa na bugawa da sauri da sauri, se da ya dan bada kafa sannan ya shiga yana tafiya a sanda bayan ya zare takalman kafar sa, baze so ya tashe ta ba dan ya san yanzu tayi bacci, duk da bata bacci bata jira shi ba yasan yau kam tayi dan yana da tabbacin fuskar sa ce karshen abinda zata so gani a yau.

Sa'adah na da kishi yafi kowa sanin haka, dan tun kan su kai inda suke a yanzu ta roke shi da Allah kan kar ko da wasa ya dinga kawo mata batun tsohuwar matar sa bata so, dake lokacin shima baya buƙatar hakan se kawai ya amsa mata, kuma be taba kawo ko da sunan Aimah gare ta ba tun lokacin, ya sani da ace Aimah na son sa baya tunanin kishin ta ze kai na Sa'adah, sedai ba ze shedi hakan ba tun da bata so shi ba ma balle ta gwada kishi a kan sa ko yaya.

Hasken daya mamaye falon ya sa ya dago a razane, idanun sa kuma suka fada cikin nata tana tsaye tana kallon sa, da sauri ya sukunyar da kai yana runtse ido tare da rashin jin dadin kama shi da tayi.

Sa'adah da tun shigowar shi take kallon sa abin ya bata mamaki ganin yadda yake sanda kamar sabon barawo ba wai me gidan da ya shigo gidan sa ba, mamaki ya hana ta masa magana sedai ganin ya nufi dakin yar su Safiyya da taci sunan Mama ake kiran ta da Noor yasa ta kasa daurewa ta kunna fitilar falon wadda ta kashe tun wajen tara na dare.

A hankali ta taka gaban sa ta tsaya tana kallon sa ganin yadda ya sunkuyar da kai, ita gaba daya se ta ga ya canja mata, ba haka suka saba ba dan duk ya dawo ko bata falo se ya bita daki, kai ko toilet take ciki se ya nata knocking ya fada mata, in kuma wanka take ma direct yake joining din ta.

"Lafiya kuwa Hubby? Me ya faru haka ka kai this late a waje, duk kasa hankali na ya tashi da tunanin wani abu mara kyau ne ya same ka?".

Ajiyar zuciya ce ta kwace masa da har se da ta ji ta sake zuba masa ido, se kuma taja hannun sa kawai zuwa dakin su..................✍️.

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 004  [ 20/6/2024 10:01 pm ]
BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)
✍️ Oummey
Free book!!!

Ouummey 004

__________________Bata kuma ce masa komai ba ta haɗa masa ruwan wanka kana ta dawo bakin gado in da ta zaunar da shi ta shiga cire masa kayan jikin sa, da undies ta bar shi tare da tura shi cikin toilet ta rufe kofar.

Kayan bacci ta fitar masa tare da feshe su da turare ta aje masa kan bed din tare da fita ta shigo masa da abinci.

Ko da ya fito kayan ya saka tare da zaman cin abinci yana yi yana satar kallon sa da ta zuba masa ido har ya gama.

Tana dawowa daga kai kayan kitchen ta kamo hannun sa daga zaunen da yake kan carpet ta kai shi kan bed tare da fadin

"Muyi bacci, Allah ya tashe mu lafiya".

Kwanciya itama tayi tare da jan duvet sedai inaaa, baze iya ba, baze iya wannan wasan nata ba, shi ba haka yayi tunani ba, ba kuma haka ya zata ba, ba kuma ze yarda da silent punishment din nan ba, kawai Gara ta tashi ayi ta ta kare dan haka ya yaye duvet din

"Tashi muyi magana Aadah".

Ɗan bude ido tayi daga kwancen

"Ka gaji kana bukatar Hutu, mu bari zuwa gobe ko?".

Hannu kawai ya sa ya dago ta ya zaunar tare da kamo hannayen ta duka biyun ya rike cikin nasa, sedai ya rasa ma me zece, ta ina ze fara ko taya ze fara, hakan yasa yayi shiru tsayin mintuna.

Sa'adah dake kallon sa cikin tausayawa dan kam ta san mijin ta, ta kuma fahimci situation din sa se ta zame hannun ta daya ta maida kan nasa, cikin sooting voice tace

"Ba se kace min komai ba Hubby, na sani na kuma fahimce ka, na sani ba zaka yi duk abinda ka san ze sani cikin damuwa ko tashin hankali ba, ba zan rufe ka ba at first hankali na ya tashi, na rude na kuma firgice dan ban haɗaka da komai, dole in shiga damuwa jin na gaza maka har ka kawo min wata ka haɗa mu tare, sedai da Aunty Luba ta zauna ta fahimtar da ni se na gane baka da laifi, iko da isar hajiya Yayah ne yasa ta kawo wata tsakanin mu saboda ganin dacewar hakan, mu kuma a matsayin mu na ya'ya masu biyayya ne ga iko da umarnin su dan haka ina me farin cikin sanar da kai yanzu babu digo na jin haushi ko fushi da kai a raina, haka ma Hajiya Yayah dan mahaifiya ce gare ni, yadda ba zan yi fushi da ikon Ummu a kaina ba haka itama.

Nidai bukatata daya ce a wajen ka, ko kuma ma ince alfarma daya nake nema daga gare ka, na

sani kaso Aimah ta yarda har ka samu ciwon zuciya akan ta, na sani itace farin cikin ka kuma kwanciyar hankalin ka kuma zaka iya komai a kan ta ciki har da bayar da rayuwar ka domin tata, Ina so dan Allah ka dinga tunawa cewa na so ka kuma ina son ka da dukkan rayuwa ta, kaina farin ciki na kuma kwanciyar hankali na, kamar yadda zaka iya mutuwa domin ta ka dinga tuna ni zan yi abinda yafi mutuwa a kan ka in har akwai shi, ina rokon alfarmar dan Allah kayi adalci tsakanin mu, ban ce dole ka so ni yadda kake son ta ba dan na san ita din rayuwar ka ce, sedai ko yaya ne kar ka gwada min bana da gurbi ko muhimmanci ga rayuwa da zuciyar ka , in har hakan ya faru ban san ya rayuwa ta zata kasance ba, ban san me ze faru da Ni ba, na dai san zan iya hadiyar zuciya na mutu wallahi Hubby.
Ka sani ina da kishi a kan ka, ina da matukar kishi musamman kuma akan AIMAH, ban zauna da ita da kai ba amma ina kishin ta fiye da duk wata mace da zata rabe ka a duniya, dan Allah kar kayi abinda ze sa kishi na akan ta ya halakar da ni, ina son ka Masdooq, tsananin son da ban san iyakar sa da iyakar abinda zan iya yi domin ka ba, dan Allah ka taimaka ka min wannan alfarmar dan.....".

Da sauri yasa hannu ya rufe mata baki zuciyar sa na karyewa da wani irin rauni da tausayin ta, ya sani Sa'adah na son shi, son da wata ya mace baya taɓa gwada masa ba, shi waye a cikin butulu da ze fifita wace mace a kan ta?, Macen ma kuma AIMAH for Allah's sake!!!.

Ya sani ya so Aimah da dukkan rayuwar sa, ya kaunace ta da dukkan zuciyar sa, ya sadaukar da farin cikin sa wa so da kaunar ta, ya yi tolerating din ta fiye da duk yadda yake tunani, haka kuma yaso rayuwa da ita har a aljanna, sedai bayan duk yadda abubuwa suka kasance baya jin yanzu akwai wadda ya tsana ko da ganin inuwar ta kamar ta, tuni ya ƙera wata iriyar akwata da karfen kwangir wanda hausawa suka ce yanke shi se makerin asali ya zuba duk wani so da kauna da yake zuciyar sa a kan ta, ya sa mukulli ya rufe tare da jefar da key din cikin kogin da dadai duniya babu ke iya samo shi balle har a bude, dan haka so da kaunar Aimah a ran sa shuɗaɗɗan al'amari ne haka kuma dawowar shi mafarki ne da baze taba tabbata ba.

"Bayan mahaifiya ta Hajiya Yayah da Mama na ina me miki rantsuwa da Allah babu wata ya mace da ta kai ki matsayi da girma a raina Sa'adah, ke din wata ginshiki ce tawa wadda faduwar ta yake nufin faduwar rayuwa ta, kina da fili me girma a zuciya ta da kika sanarwar kan ki bisa jajircewa da kokarin ka wanda bana tunanin ba Aimah ba akwai wata macen ma da zata iya samun ko da kwatankwacin sa, dan Allah dan Annabi kar ki kuma downgrading matsayin ki a zuciya ta, yin hakan na sa na ji kamar na gaza Miki ne da har yasa kike ganin akwai gurbin da baki cike ba, farin cikin ki nawa ne Sa'adah kamar yadda walwalár ki ce Mabudin tawa, za kuma ki tabbatar da hakan cikin zaman mu dake yin da har a da baki lura da hakan ba".

Sassanyan ajiyar zuciya ta shiga saukewa a hankali zuciyar ta na sake mata sanyi hankalin ta na sake kwanciya,

"Aunty Luba ta tafi da Noor, tace zata dawo da ita next week".

Gyada mata kai yayi kawai tare da hade bakin su ya shiga wanke mata duk wani ɓacin rai da ta

wuni da shi, salo salo na soyayya me tsayawa a rai ba wanda be gwada mata ba, duk da cewa kalaman sa sun zaftare fiye da rabi na tashin hankalin ta amma aikin sa ya sake tafiyar da komai, be bar ta ba se da ya tabbatar da ya goge duk wani bakin ciki dake ran sa ya kuma dasa mata bishiyar farin ciki da walwala a ran ta.

Daren ranar ya zama one of the most memorable darare na rayuwar auren su, suka yi bacci cikin farin ciki da kwanciyar hankali tare da so da kaunar juna.

*****Washegari****

Tun karfe uku na dare na farka saboda wata azababbiyar yunwa da ta addabe ni, ban kuma komawa bacci ba har aka kira sallar asuba na tashi nayi alwala a daddafe na zauna lazimi, ana kiran biyu kuma na gabatar da Sallah ta da lafaya ta da na yaye daga kan gado.

Ko da na idar kasa cigaba da azkhar nayi na cigaba da zama a wajen da tagumi hannu bibbiyu na, a haka har bakwai tayi na ji dawowar megidan daga masallaci, daya daga cikin dubban kyawawan halayen Ya Masdooq da na shaida tun kafin auren mu kenan wato tsaida sallah kuma cikin jam'i.

Bayan shigewar sa kuma na fara jin karakainar matar gidan, na sani tana kokarin dora karin safe ne dan gyaran gida kam tana da yar aiki dake yi.

Nunfashi na sauke sanin na kusa samun abinda zan ci tun da har ta fito girki, ina zaune nan wajen jiran gawon shanun a gama abinci in ci sedai shiru har karfe tara saura, lokacin kuwa hatta idanuna launin su ya canja sosai, rawar da hannu da jiki na ke yi kuwa bata buya ba.

Se karfe goma da minti biyar aka kwankwasa min kofar daki, bani da karfin tashi na bude se kawai shigo da na fada da kyar.

Yar aikin jiya ce ta shigo hannun ta rike da bowl karami ta aje min a gabana se kuma ta fita ta dawo rike da cup shima ya aje min, se kuma lokacin tace

"Ina kwana, ga abinci in ji Aunty".

Gyada mata kai nayi dan ban da karfin bude baki, tun bare da idanuna suka sauka kan abinda ke cikin bowl din wanda chips ne da aka soya da kwai, zubin sa kuwa kamar za'a bawa yar shekara bakwai ba ni Aimah da maganar cin abinci na ya zaga dangi ba se bread yanka hudu, cup din kuwa Black tea ne a ciki tsura, girgiza kai kawai nayi na ja bowl din na shiga ci ina haɗawa da Black tea din duk da na san Ya Masdooq baya taɓa batik gidan sa ba madara, madarar ma kuma be aje kadan tun ma a lokacin da budin sa be kai haka ba kenan.

Ko da na cinye ban ji ko rabin alamar koshi ba, sedai rawar da jiki na ke yi ya ragu, na tashi zuwa toilet na sha ruwa dan ko da na bude fridge din dakin babu komai a ciki.

Waya ta na janyo sedai ta riga ta mutu, gashi babu caja a tare da ni balle na saka se kawai na bude bedside drawer na jefa ta a ciki na rufe, na tashi na shiga gyaran dakin dan a kwai kayan broom da su basket a ciki.

Ina gamawa na shiga toilet na wanke da ragowar detergent din da na samu a ciki, ina gamawa na watsa ruwa na fito dan babu komai na daga kayan sawa ko na wani amfani na a tare da ni.

Kayan da na cire wanda atamfa ce ɗinkin riga da skirt da suka kama ni tsam ne a jiki na se na dora lafaya.

Gefen bed na samu na zauna ina bin fatar jiki na da kallo wadda ke sheki da ɗaukar ido dan glass skin gare ni da baya rike ruwa, in ruwa ya hau fatata haka yake gangarewa tas.

A sannu na dago na zubawa mirror din dake fuskan ta ta ido, ina da kyau ni Aimah, kyau kuma me daukar hankali da ke fizgar idanu, a kallo na awa daya ma ba zaka iya nuna wani abu me muni a fuska ta ba balle jiki na, fata ta ba fara bace sedai ba baka bace dan kuwa zam skin din iyayen mu mata na yan Ethiopia na gado har ma kuma nafi su dan duk wani hanya ko abu me gyara fata bana wasa da shi.

Idanuna masu shape din kwai masu girma da haske ga sheki da ɗaukan idanu ne, hasken su kan sa mutum kau da ido daga kallo na a duk sanda na ware girman su baki daya a kan su, hakan kuma na faruwa ne duk sanda nake jin tsiwa da rashin kunya ta.

Baki na akwai kaifi wanda na daya daga cikin abinda suka jawo kin shiga halin da nake ciki yanzu, siraran lips ne da ni so pinkish tun bare da nake lips therapy se suka sake laushi da taushi tare da ɗaukan ido musamman in yawu ya sauka a kan su ko lipgloss.

Hakwara na yaryaryar ne kananu masu dan tsayi wanda duk sanda na ware su dan yin dariya ko murmushi me kallo na yake kasa janye ido daga kan su a lokaci daya, se kuma dogon hanci na da ya sauka kan saman lips dina kadan, haka kuma be da wani fadi haka be yi tsirr din siranta da yawa ba.

In general, fuska ta na da tsayi ba sosai ba, haka kuma tana da cika duk da bata yi lukuta ba, sedai fa tana da ɗaukar hankali matuƙa wanda tana daga cikin abinda ta jawo min irin rayuwar da nake yi yanzu.

Jiki na kuwa jiki ne irin na models, shape dina is way close to perfect tun da ance babu wanda yake perfect, amma a tsarin zubin mace ina da komai da ake bukata cikin tsari, ba yawa ba kadan, wannan yasa nake amsa sunan MATAR MANYA a bakin yan uwa da kawaye na, musamman kawayen dan har yanzu sunan be canja ba.

Kyau na da kyan fasali na yasa na zama wata cele a social media, haka kuma ya kara min

wayewa kan yadda zan kula da jiki na da kai na, da kuma irin tsarin sutturar da ta dace da jikina cikin different occasions.

A sannu na sauke nunfashi na lumshe ido, tunanin irin rayuwar da zan gudanar na kawo min cafka.......................✍️.

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 005  [ 20/6/2024 10:02 pm  ]
BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)
✍️ Oummey
Free book!!!

Ouummey 005

Page5️⃣

______________________Ina nan zaune cikin rashin sanin abin yi har na ji fitar me gidan, ko da na duba time it's to eleven, ban yi mamaki ba sanin dama baya fita da wuri duk weekend, yanzu haka fitar da yayi ba office za shi ba gidan Hajiya Yayah ne za shi gaida su kamar yadda ya saba.

A baya dai na san bayan azahar yake dawowa gida, daga nan kuma baya sake fita se yin sallah kadai, duk da irin wulakanci da nuna masa ban san ganin sa da nake yi be sa ya fasa zaman gidan ba.

Wasa wasa ina nan zaune har aka kira azahar, na mike nayi na kuma komawa na zauna, rashin abin yi yasa gaba daya tunani ke neman yi min yawa.

Ina so in fita falo sedai ina jin kunyar hakan, ba wai kunyar Sa'adah ba, a'a kunyar kai na da kaina nake yi da kuma kunyar me gidan ya dawo ya same ni, da ba dan haka ba ai da ko kallo ne naje na yi dan korar tunanukan dake neman addaba ta.

Daga karshe se kawai na jingina da jikin bed na shiga takarar karatun Alkur'ani, a nutse nake karatu na da murya ƙasa ƙasa dan kar in damu me gidan, bayan haka ma kuma ga waka da na ji sun kunna ita da yan uwan ta da suka zo ne ko kawayen ta ban sani ba, sedai ina jin shewar su a falon tun dazu.

Ban yi tunanin dama ganin wani yazo waje na ba daga vangaren Mama har zuwa na Abba, balle kawaye da tuni na watsar da kowa, sedai ban yi tsammanin ba za'a aiko min da kayan sawa na ba, dan ban san yadda zan yi rayuwa ba kaya ba, se ga shi har close to sallar magrib ba wanda ya dube ni da batun abinci balle kuma kaya.

A haka aka kira magrib din na tashi da kyar duk jikina ba karfi, irin yadda kwana biyu nake faman wahaluwa da yunwa ban taba samun wannan matsalar ba a kaf rayuwa ta.

Duk yadda Mama ke jin haushi da yin fushi da ni bata taɓa min horon yunwa ba, abinda tace shine kawai ba zata dafa abinci ta bani ba, wannan yasa kafin ta zo yin girki ko ta gama zan shiga kitchen in dafa duk abinda nake so dan bata min iyaka da abinda zan ci da kuma wanda ba zan ci ba.

Gaba daya a kwana dayan da nayi gidan Masdooq na yi wani iri dani, idanuna sun yi zurfi zuru, haka sun dan fada sedai ban da su babu abinda ke nuna wani canji a tattare da ni.

Se bayan na idar da sallar magrib sannan yar aikin dai ta sake kawo min abinci, yanzu a cikin wani plate mara zurfi, abincin kuma iya tsakiya.

Ban yi korafi ba na karba da godiya na a aje a gaba na na shiga nazari, in na fahimta na kuma gane Sa'adah na neman yi min horon yunwa ne, a wuni ba'a ban abinci ba in an tashi a kawo min wanda aka san ko kwatar isa na baze yi ba, wato dai kora da hali take neman yi min.

A sannu na girgiza kai ina sakin wani busasshen murmushi mara armashi, lallai Sa'adah bata gama sanin wace ce ni ba, sa'ar ta daya ta samu mata sun yi laushi, da ace a da da nake amsa sunan Aimah ne da tuni wani zancen ake ba wannan ba, sedai a yanzu da na koyi rayuwa zan yi hakuri in zuba mata ido, duk abinda ta zo da shi in har be zama da cutarwa ba zan karbe shi in yi manage din rayuwa zuwa sanda Allah ze yaye min wannan jarabawar.

A hankali na jawo abincin nayi Bismillah na fara ci, tun a lomar farko hawaye ya cika min fuska na kuma hadiye da kyar saboda irin gishirin da aka cikawa abinci, ni ba wani abinda zan ci ba balle na hakura da ci, haka dole na dinga tura shi, dake ma ba yawa ne da shi ba loma biyar nayi ya kare.

Na ture plate din gefe na tashi na wanko hannu na na dawo na zauna, kawai se kuka ya kwace min, na shiga rera shi a hankali, daga yadda sautin sa ke fita duk me saurare na ze san ina cikin severe pain, Ina cikin radadi me zafi a raina da rayuwa ta, sedai bayan kukan babu abinda zan iya yi.

Abin ne ya hade min goma da ashirin, tuna Mama na gadon asibiti domin ni yana damuna matuka, haka na yi ta kuka har aka kira Sallar Isha, na tashi na yi ta na sake komawa na zauna.

Yau ma na ji shigowar me gidan haka kuma a kunne na matar sa ta tarbe shi dan falon bakin ba a wani waje daban yake ba tun da gidan ba wani girma na daban ne da shi ba, ga kuma kasantuwar windows din sa na falo na a compound me na bedroom kuma a cikin falon.

A sannu na lumshe ido na kawai kaina blank ban san takamaiman tunanin da nake ba, bayan shudewar wasu mintuna da dawowar sa aka kwankwasa min kofa, na amsa daga zaunen tare da bada izinin shigowa, yar aikin su ta shigo jaye da biyu daga cikin manyan jakunkunan kaya na, na dan mike zaune daga kishingiden da nayi na mata godiya ta aje ta fita.

Tashi nayi na ja jakunkunan zuwa bedroom, ko da na bude daga sama sama kayan shafa na ne wato skincare, se kayan wankin baki na su mouth wash, se kuma mayukan gashi na, daga kasa kadan kuma turaruka na kama daga kan na jiki zuwa na kaya zuwa na daki na, se kuma kasa da su undies dina, daga su kuma se towels dina da kayan bacci na kala hudu, se a karshe kuma mayafai na.

Dayar kuma kayan sawa ta ne set goma a ciki, se takalma na gudu hudu, baki, golden, silver da kuma coffee, kowannen da jakar sa, se kayan kwalliya ta kadan, shikenan se hijabs dina guda uku da zanin gado biyu.

Na dade ina kallon kayan da mamakin me yasa ba'a hada min duka kaya na ba aka tsakuro min wadannan, a gida wardrobe ce da ni me murfi hudu cike damkan da kayan sawa ta na daga dukkan nau'i, kayan shafa ta kuwa bayan wanda ke cike kan mirror har da akwati guda nake da su raggowa, haka kayan wanka da na wankin baki bayan wanda na jere a toilet dina suma akwati daya gare ni cikakken da su dan bana jiran su kare kafin in siya wasu, takalmin da jaka tare da mayafai kuwa kai kace zan bude kanti ne, amma ace iya wannan kadai aka ga dacewar a bani.

A hankali na sauke ajiyar zuciya ina fa da wa kaina duk yana cikin jarrabawa ta da ya kama ta nayi hakuri da, kuma ko iya hakan wanda ya debo ya taimake ni dan ban taba kwana biyu da kaya ko da biyu ba se ga shi nayi da kaya daya.

Haka na tashi na jera su a wardrobe din dakin, komai a ciki na jera ban da kayan shafa da na zuba kan mirror se kayan shower gels da other turarukan wanka na da kayan wanke baki da na kai toilet na jera cikin cupboard tare da towels dina.

Duk da dare ne haka na zuba shower gel dina a kasan toilet din ba wanke tass dan dama karfin hali ne yasa nake iya amfani da shi bayan na wanke da ruwa, abin nan da ake kira ba yadda zaka yi.

Cikin samun sassaauci na shimfida daya daga cikin bedsheets din guda daya na kwanta bayan na feshe dakin da turaruka na masu sanyin kamshi na kwanta zuciya ta na dan yin sanyi.

Ina son kamshi, ina son me son kamshi kamar yadda zan iya bayar da last kobo na wajen siyan kamshi wato turare shiyasa suna cikin priority na wajen siyayya, kamshi na rage min kaifin damuwa duk girman ta, ya kara min kwarin giwwar jarumtar karbar ƙaddara, kamshi na rage min yawan tunani a raina, shi ya taimaka min da ina gida ban fita hayyaci na ba yayinda kowa ya juya baya gare ni.

Cikin sauƙin samuwar zuciya na yi bacci na tashi, ina me ambaton Allah da gode masa, na gabatar da sallar asuba, na zauna nayi azkhar dina tare da bitar wasu surahs na Alkur'ani.

A haka gari yayi haske, na tashi na shiga gyaran dakin daga falo zuwa bedroom, ina gamawa na shiga wanka, da ruwan sanyi nayi wanka dan duk yadda na so kunna ruwan zafin a toilet heater taki yi, se kawai nayi na gama na fito bayan na wanke toilet din.

Shafa na zauna nayi kan mirror, ina yi ina lumshe ido dan dadin kamshin mayukan, ina gamawa da skin dina na koma kan gashi na na mulke shi da mayuka na masu tsada da gyara gashi na taje shi da kyar kamar kullum sannan na hade shi waje guda kana na tashi zuwa wardrobe dan neman kayan da zan sa.

A kan kayana set goma na sauke ido na cikin tunanin wanda zan sa, idanuna suka fada kan bakin straight skirt da red shirt din sa, na dauko su na saka bayan na saka undies, barin turare nayi wa jiki na, ina gamawa na sake gyara dakin kana na wuce falo na kishingida kan sofar da ta sha wanka da turaren daki na.

A wannan safiyar karfe tara aka kawo min breakfast, be kai na jiya ba haka nan cinye na tashi, na sake komawa yadda nake.

Gaba daya jikina ciwo yake haka jina nake kamar a prison, ban saba da irin wannan rayuwar ba ta kunshewa a daki, ban saba da rayuwar zama waje ɗaya ba dan ina da ayyukan da nake yi, kuma ko da aka hanani bana zama, duk wani aiki a gidan mu kafin Mama ta fito yi nayi duk da bata godewa se ma zagi da nake sha, ga kuma waya ta da ke ɗebe min kewa sosai da sosai.

A haka na wuni, yau ma abinci se daf da magrib, wannan karon ba yar aiki ce ta kawo ba, Madam din da kan ta ta kawo min, suka shigo ita da wata yar uwar ta ta bangaren baban ta, yarinyar se yatsine yatsine take yi tana bin dakin da wani kallo na wulakanci.

Lokacin da suka shigo ina kwance kan sofa idanuna a lumshe ina karkada kafa a hankali baki na na motsi cikin karatun suratul Noor da nake yi.

Ba sallama ba komai se ji nayi kawai an shigo min, ko da na bude ido se na gan su tsaye kaina kowacce tana min wani kallo na rainin hankali musamman yar uwar Tata, ita Sa'adah din wani

murmushi ne take min irin na to ya kika gani din nan.

Na mike na zauna sosai ina bin su da kallo ban ce komai ba, se kawai yar uwar ta tana wani harara ta

"Ke baki iya gaisuwa bane?".

Ban ce komai ba na cigaba da kallon su ina nazartar su, Sa'adah ce ta janye daga gaba na ta fara zagaya dakin

"Ke me ya dame ki da se ta gaida ki, yarinyar da tarbiyya bata wadace ta ba, ko kin manta iyayen ta ma ba barin su tayi ba dan yanzu haka fa gyatumar ta na kwance asibiti saboda bakin cikin ta".

"Kuma fa haka ne, to Allah ya raba mu da rayuwa mara ma'ana".

Har lokacin kallon su nake yi, zuciya ta na zafi tana tunzura ni amma dai na dake ban ce komai ba haka kallon da nake yi musu be canja ba, su ka gama zagaye zagayen su har cikin bedroom sannan suka fito, har sun nufi kofa Sa'adah ta juyo bakin ta a washe

"Bahaushe yace wai ikon Allah me doki ya koma kuturi, a shekarun baya kina jiji da kai kina izza wai ke me miji, se gashi yanzu duk wannan takamar ta bar ki ta dawo gare ni, a wancan lokacin kika hana shi daukar phone call dina da replying messages dina, a karshe kuma kika saka yayi blocking dina, hhhhh, me kike tunanin yanzu in nace ban yafe ba zan rama duk abinda kika min koma fiye?, A yanzu dai na san kin san Masdooq a tafin hannu na yake ko?, Kuma sunan wanann gidan yanzu gidan Sa'adah ne ba Aimah ba, so ki shirya ma yin duk irin rayuwar da Sa'adah ta zaba miki, dan a yanzu ki dauka makomar rayuwar ki na hannun Sa'adah ne se wadda ta zaba miki, farin ciki ko akasin haka".

Da haka suka buɗe kofa, har zasu fita na kasa daurewa dan kuwa har yanzu akwai ragiwar old Aimah a tare da ni, se kawai na mike

"Masdooq na a hannun ki yanzu bayan Aimah ta gama toying da rayuwar sa ta jefar?, Excuse me, ko kin manta irin soyayyar rai da mutuwa da Masdooq yayi wa AIMAH ne?, A kaina ne fa mijin naki da kike tutiya ya kasa kallon ki duk kuwa da yadda kika nace masa, wanda har se da na bar shi ya rasa ni sannan aka kakaba masa ke, ko kin zata ban san haɗa ku aka yi ba, a hakan ma ya shanya ki tsayin shekara kafin da maagiya da komai na samu ya karbe ki matsayin mata, ko kin zata a karan kan shi ya karbe ki? No, nice nayi masa dabarar cewa ya karbe ki ni kuma zan dawo masa, so kar kiyi wani prouding dan kin kasance matar sa bayan se da rarraahi da ban baki ya karbe ki, for your information, har a tashi duniya babu macen da Masdooq ze so ko da kwatankwacin son da yayi ma Aimah ne Sa'adah dan kuwa akan Aimah ya kamu ciwon zuciya saboda tsabar soyayya, wasu kuwa ko zazzaɓi ba'a taba yi a kan su ba, hasalima kwantai sukai aka rasa me so se da aka nanawa wasu, ke tsaya ma, wai baki yi

mamakin sunan mahaifiya ta da ya sanya wa yar ki bane?, To shi ma sunan ni na zaba kuma ya zauna, kuma in zaki dawwama kina haihuwa Aimah ce zata yi ta sawa ƴaƴan ki suna, so zaki iya tafiya, na san iya haka ya ishe ki tunani".

Gaba dayan su daskarewa suka yi a tsaye, a yadda kwana biyu a gidan ta kebe kan ta se suke tunanin ta tsora ta ne, sun zata zuwa yanzu abubuwan dake faruwa sun kashe bakin ta, ashe ashe ba haka bane?.

Wai ma tsaya, shin dagaske ne Aimah ce ta sa Masdooq ya karbe ta? Kuma wai shi ya zabawa yar ta suna, shine har yake kiran ya princess? Lallai akwai tashin hankali yau, wallahi bari ya dawo ba zata yadda ba!.

Yin wannan tunanin yasa Sa'adah ficewa daga dakin da sauri har bata ganin gaban ta, yar uwar ta kuma ta juyo ta dube ni ina kishingide ina girgiza kafa fuska ta dauke da wadataccen murmushi, ta haɗa hannayen ta biyu suka bada sautin dasss, ta min wani kallo tare da girgiza kai alamar zamu gauraya, Ni kuwa na sake mata kyakkyawan murmushi na me tsari da ya bayyana kyawawan fararen haƙora na alamar ina jira, ta juya ta fice da sauri ta bi bayan yar uwar ta................✍️

Kilin kilin kilin, to fa, ga Aimah ga Sa'adah, Sa'adah ta takalo magana ita kuma Aimah ta mata me gaba daya.

Shin da gaske ne Aimah ce ta zabawa princess suna? Kuma wai da gaske ne ita tasa ya karbi Sa'adah matsayin mata??

Lallai Hausawa sun yi gaskiya da suka ce baki ya san me ze fada be san me za'a fada masa ba!.

Vote,
Comment
And share fisabilillah!

Heart you all ❤️.

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 005

____________________Ina nan zaune cikin rashin sanin abin yi har na ji fitar me gidan, ko da na duba time it's to eleven, ban yi mamaki ba sanin dama baya fita da wuri duk weekend, yanzu haka fitar da yayi ba office za shi ba gidan Hajiya Yayah ne za shi gaida su kamar yadda ya saba.

A baya dai na san bayan azahar yake dawowa gida, daga nan kuma baya sake fita se yin sallah kadai, duk da irin wulakanci da nuna masa ban san ganin sa da nake yi be sa ya fasa zaman gidan ba.

Wasa wasa ina nan zaune har aka kira azahar, na mike nayi na kuma komawa na zauna, rashin abin yi yasa gaba daya tunani ke neman yi min yawa.

Ina so in fita falo sedai ina jin kunyar hakan, ba wai kunyar Sa'adah ba, a'a kunyar kai na da kaina nake yi da kuma kunyar me gidan ya dawo ya same ni, da ba dan haka ba ai da ko kallo ne naje na yi dan korar tunanukan dake neman addaba ta.

Daga karshe se kawai na jingina da jikin bed na shiga takarar karatun Alkur'ani, a nutse nake karatu na da murya ƙasa ƙasa dan kar in damu me gidan, bayan haka ma kuma ga waka da na ji sun kunna ita da yan uwan ta da suka zo ne ko kawayen ta ban sani ba, sedai ina jin shewar su a falon tun dazu.

Ban yi tunanin dama ganin wani yazo waje na ba daga vangaren Mama har zuwa na Abba, balle kawaye da tuni na watsar da kowa, sedai ban yi tsammanin ba za'a aiko min da kayan sawa na ba, dan ban san yadda zan yi rayuwa ba kaya ba, se ga shi har close to sallar magrib ba wanda ya dube ni da batun abinci balle kuma kaya.

A haka aka kira magrib din na tashi da kyar duk jikina ba karfi, irin yadda kwana biyu nake faman wahaluwa da yunwa ban taba samun wannan matsalar ba a kaf rayuwa ta.

Duk yadda Mama ke jin haushi da yin fushi da ni bata taɓa min horon yunwa ba, abinda tace shine kawai ba zata dafa abinci ta bani ba, wannan yasa kafin ta zo yin girki ko ta gama zan shiga kitchen in dafa duk abinda nake so dan bata min iyaka da abinda zan ci da kuma wanda ba zan ci ba.

Gaba daya a kwana dayan da nayi gidan Masdooq na yi wani iri dani, idanuna sun yi zurfi zuru, haka sun dan fada sedai ban da su babu abinda ke nuna wani canji a tattare da ni.

Se bayan na idar da sallar magrib sannan yar aikin dai ta sake kawo min abinci, yanzu a cikin wani plate mara zurfi, abincin kuma iya tsakiya.

Ban yi korafi ba na karba da godiya na a aje a gaba na na shiga nazari, in na fahimta na kuma

gane Sa'adah na neman yi min horon yunwa ne, a wuni ba'a ban abinci ba in an tashi a kawo min wanda aka san ko kwatar isa na baze yi ba, wato dai kora da hali take neman yi min.

A sannu na girgiza kai ina sakin wani busasshen murmushi mara armashi, lallai Sa'adah bata gama sanin wace ce ni ba, sa'ar ta daya ta samu mata sun yi laushi, da ace a da da nake amsa sunan Aimah ne da tuni wani zancen ake ba wannan ba, sedai a yanzu da na koyi rayuwa zan yi hakuri in zuba mata ido, duk abinda ta zo da shi in har be zama da cutarwa ba zan karbe shi in yi manage din rayuwa zuwa sanda Allah ze yaye min wannan jarabawar.

A hankali na jawo abincin nayi Bismillah na fara ci, tun a lomar farko hawaye ya cika min fuska na kuma hadiye da kyar saboda irin gishirin da aka cikawa abinci, ni ba wani abinda zan ci ba balle na hakura da ci, haka dole na dinga tura shi, dake ma ba yawa ne da shi ba loma biyar nayi ya kare.

Na ture plate din gefe na tashi na wanko hannu na na dawo na zauna, kawai se kuka ya kwace min, na shiga rera shi a hankali, daga yadda sautin sa ke fita duk me saurare na ze san ina cikin severe pain, Ina cikin radadi me zafi a raina da rayuwa ta, sedai bayan kukan babu abinda zan iya yi.

Abin ne ya hade min goma da ashirin, tuna Mama na gadon asibiti domin ni yana damuna matuka, haka na yi ta kuka har aka kira Sallar Isha, na tashi na yi ta na sake komawa na zauna.

Yau ma na ji shigowar me gidan haka kuma a kunne na matar sa ta tarbe shi dan falon bakin ba a wani waje daban yake ba tun da gidan ba wani girma na daban ne da shi ba, ga kuma kasantuwar windows din sa na falo na a compound me na bedroom kuma a cikin falon.

A sannu na lumshe ido na kawai kaina blank ban san takamaiman tunanin da nake ba, bayan shudewar wasu mintuna da dawowar sa aka kwankwasa min kofa, na amsa daga zaunen tare da bada izinin shigowa, yar aikin su ta shigo jaye da biyu daga cikin manyan jakunkunan kaya na, na dan mike zaune daga kishingiden da nayi na mata godiya ta aje ta fita.

Tashi nayi na ja jakunkunan zuwa bedroom, ko da na bude daga sama sama kayan shafa na ne wato skincare, se kayan wankin baki na su mouth wash, se kuma mayukan gashi na, daga kasa kadan kuma turaruka na kama daga kan na jiki zuwa na kaya zuwa na daki na, se kuma kasa da su undies dina, daga su kuma se towels dina da kayan bacci na kala hudu, se a karshe kuma mayafai na.

Dayar kuma kayan sawa ta ne set goma a ciki, se takalma na gudu hudu, baki, golden, silver da kuma coffee, kowannen da jakar sa, se kayan kwalliya ta kadan, shikenan se hijabs dina guda uku da zanin gado biyu.

Na dade ina kallon kayan da mamakin me yasa ba'a hada min duka kaya na ba aka tsakuro min wadannan, a gida wardrobe ce da ni me murfi hudu cike damkan da kayan sawa ta na daga

dukkan nau'i, kayan shafa ta kuwa bayan wanda ke cike kan mirror har da akwati guda nake da su raggowa, haka kayan wanka da na wankin baki bayan wanda na jere a toilet dina suma akwati daya gare ni cikakken da su dan bana jiran su kare kafin in siya wasu, takalmin da jaka tare da mayafai kuwa kai kace zan bude kanti ne, amma ace iya wannan kadai aka ga dacewar a bani.

A hankali na sauke ajiyar zuciya ina fa da wa kaina duk yana cikin jarrabawa ta da ya kama ta nayi hakuri da, kuma ko iya hakan wanda ya debo ya taimake ni dan ban taba kwana biyu da kaya ko da biyu ba se ga shi nayi da kaya daya.

Haka na tashi na jera su a wardrobe din dakin, komai a ciki na jera ban da kayan shafa da na zuba kan mirror se kayan shower gels da other turarukan wanka na da kayan wanke baki da na kai toilet na jera cikin cupboard tare da towels dina.

Duk da dare ne haka na zuba shower gel dina a kasan toilet din ba wanke tass dan dama karfin hali ne yasa nake iya amfani da shi bayan na wanke da ruwa, abin nan da ake kira ba yadda zaka yi.

Cikin samun sassaauci na shimfida daya daga cikin bedsheets din guda daya na kwanta bayan na feshe dakin da turaruka na masu sanyin kamshi na kwanta zuciya ta na dan yin sanyi.

Ina son kamshi, ina son me son kamshi kamar yadda zan iya bayar da last kobo na wajen siyan kamshi wato turare shiyasa suna cikin priority na wajen siyayya, kamshi na rage min kaifin damuwa duk girman ta, ya kara min kwarin giwwar jarumtar karbar ƙaddara, kamshi na rage min yawan tunani a raina, shi ya taimaka min da ina gida ban fita hayyaci na ba yayinda kowa ya juya baya gare ni.

Cikin sauƙin samuwar zuciya na yi bacci na tashi, ina me ambaton Allah da gode masa, na gabatar da sallar asuba, na zauna nayi azkhar dina tare da bitar wasu surahs na Alkur'ani.

A haka gari yayi haske, na tashi na shiga gyaran dakin daga falo zuwa bedroom, ina gamawa na shiga wanka, da ruwan sanyi nayi wanka dan duk yadda na so kunna ruwan zafin a toilet heater taki yi, se kawai nayi na gama na fito bayan na wanke toilet din.

Shafa na zauna nayi kan mirror, ina yi ina lumshe ido dan dadin kamshin mayukan, ina gamawa da skin dina na koma kan gashi na na mulke shi da mayuka na masu tsada da gyara gashi na taje shi da kyar kamar kullum sannan na hade shi waje guda kana na tashi zuwa wardrobe dan neman kayan da zan sa.

A kan kayana set goma na sauke ido na cikin tunanin wanda zan sa, idanuna suka fada kan bakin straight skirt da red shirt din sa, na dauko su na saka bayan na saka undies, barin turare nayi wa jiki na, ina gamawa na sake gyara dakin kana na wuce falo na kishingida kan sofar da ta sha wanka da turaren daki na.

A wannan safiyar karfe tara aka kawo min breakfast, be kai na jiya ba haka nan cinye na tashi, na sake komawa yadda nake.

Gaba daya jikina ciwo yake haka jina nake kamar a prison, ban saba da irin wannan rayuwar ba ta kunshewa a daki, ban saba da rayuwar zama waje ɗaya ba dan ina da ayyukan da nake yi, kuma ko da aka hanani bana zama, duk wani aiki a gidan mu kafin Mama ta fito yi nayi duk da bata godewa se ma zagi da nake sha, ga kuma waya ta da ke ɗebe min kewa sosai da sosai.

A haka na wuni, yau ma abinci se daf da magrib, wannan karon ba yar aiki ce ta kawo ba, Madam din da kan ta ta kawo min, suka shigo ita da wata yar uwar ta ta bangaren baban ta, yarinyar se yatsine yatsine take yi tana bin dakin da wani kallo na wulakanci.

Lokacin da suka shigo ina kwance kan sofa idanuna a lumshe ina karkada kafa a hankali baki na na motsi cikin karatun suratul Noor da nake yi.

Ba sallama ba komai se ji nayi kawai an shigo min, ko da na bude ido se na gan su tsaye kaina kowacce tana min wani kallo na rainin hankali musamman yar uwar Tata, ita Sa'adah din wani murmushi ne take min irin na to ya kika gani din nan.

Na mike na zauna sosai ina bin su da kallo ban ce komai ba, se kawai yar uwar ta tana wani harara ta

"Ke baki iya gaisuwa bane?".

Ban ce komai ba na cigaba da kallon su ina nazartar su, Sa'adah ce ta janye daga gaba na ta fara zagaya dakin

"Ke me ya dame ki da se ta gaida ki, yarinyar da tarbiyya bata wadace ta ba, ko kin manta iyayen ta ma ba barin su tayi ba dan yanzu haka fa gyatumar ta na kwance asibiti saboda bakin cikin ta".

"Kuma fa haka ne, to Allah ya raba mu da rayuwa mara ma'ana".

Har lokacin kallon su nake yi, zuciya ta na zafi tana tunzura ni amma dai na dake ban ce komai ba haka kallon da nake yi musu be canja ba, su ka gama zagaye zagayen su har cikin bedroom sannan suka fito, har sun nufi kofa Sa'adah ta juyo bakin ta a washe

"Bahaushe yace wai ikon Allah me doki ya koma kuturi, a shekarun baya kina jiji da kai kina izza wai ke me miji, se gashi yanzu duk wannan takamar ta bar ki ta dawo gare ni, a wancan lokacin kika hana shi daukar phone call dina da replying messages dina, a karshe kuma kika saka yayi blocking dina, hhhhh, me kike tunanin yanzu in nace ban yafe ba zan rama duk abinda kika min koma fiye?, A yanzu dai na san kin san Masdooq a tafin hannu na yake ko?, Kuma sunan

wanann gidan yanzu gidan Sa'adah ne ba Aimah ba, so ki shirya ma yin duk irin rayuwar da Sa'adah ta zaba miki, dan a yanzu ki dauka makomar rayuwar ki na hannun Sa'adah ne se wadda ta zaba miki, farin ciki ko akasin haka".

Da haka suka buɗe kofa, har zasu fita na kasa daurewa dan kuwa har yanzu akwai ragiwar old Aimah a tare da ni, se kawai na mike

"Masdooq na a hannun ki yanzu bayan Aimah ta gama toying da rayuwar sa ta jefar?, Excuse me, ko kin manta irin soyayyar rai da mutuwa da Masdooq yayi wa AIMAH ne?, A kaina ne fa mijin naki da kike tutiya ya kasa kallon ki duk kuwa da yadda kika nace masa, wanda har se da na bar shi ya rasa ni sannan aka kakaba masa ke, ko kin zata ban san haɗa ku aka yi ba, a hakan ma ya shanya ki tsayin shekara kafin da maagiya da komai na samu ya karbe ki matsayin mata, ko kin zata a karan kan shi ya karbe ki? No, nice nayi masa dabarar cewa ya karbe ki ni kuma zan dawo masa, so kar kiyi wani prouding dan kin kasance matar sa bayan se da rarraahi da ban baki ya karbe ki, for your information, har a tashi duniya babu macen da Masdooq ze so ko da kwatankwacin son da yayi ma Aimah ne Sa'adah dan kuwa akan Aimah ya kamu ciwon zuciya saboda tsabar soyayya, wasu kuwa ko zazzaɓi ba'a taba yi a kan su ba, hasalima kwantai sukai aka rasa me so se da aka nanawa wasu, ke tsaya ma, wai baki yi mamakin sunan mahaifiya ta da ya sanya wa yar ki bane?, To shi ma sunan ni na zaba kuma ya zauna, kuma in zaki dawwama kina haihuwa Aimah ce zata yi ta sawa ƴaƴan ki suna, so zaki iya tafiya, na san iya haka ya ishe ki tunani".

Gaba dayan su daskarewa suka yi a tsaye, a yadda kwana biyu a gidan ta kebe kan ta se suke tunanin ta tsora ta ne, sun zata zuwa yanzu abubuwan dake faruwa sun kashe bakin ta, ashe ashe ba haka bane?.

Wai ma tsaya, shin dagaske ne Aimah ce ta sa Masdooq ya karbe ta? Kuma wai shi ya zabawa yar ta suna, shine har yake kiran ya princess? Lallai akwai tashin hankali yau, wallahi bari ya dawo ba zata yadda ba!.

Yin wannan tunanin yasa Sa'adah ficewa daga dakin da sauri har bata ganin gaban ta, yar uwar ta kuma ta juyo ta dube ni ina kishingide ina girgiza kafa fuska ta dauke da wadataccen murmushi, ta haɗa hannayen ta biyu suka bada sautin dasss, ta min wani kallo tare da girgiza kai alamar zamu gauraya, Ni kuwa na sake mata kyakkyawan murmushi na me tsari da ya bayyana kyawawan fararen haƙora na alamar ina jira, ta juya ta fice da sauri ta bi bayan yar uwar ta................✍️

Kilin kilin kilin, to fa, ga Aimah ga Sa'adah, Sa'adah ta takalo magana ita kuma Aimah ta mata me gaba daya.

Shin da gaske ne Aimah ce ta zabawa princess suna? Kuma wai da gaske ne ita tasa ya karbi

Sa'adah matsayin mata??

Lallai Hausawa sun yi gaskiya da suka ce baki ya san me ze fada be san me za'a fada masa ba!.

Vote,
Comment
And share fisabilillah!

Heart you all ❤️.

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 006 [ 21/06/2024 ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Oummey
Free book!!!

Ouummey 006

Page 6️⃣

___________________Dariya na fashe da ita bayan fitar su, na dade ina kyakyatawa kamar ba ni ce cikin damuwa ba kafin na samu na tsagaita, sedai da na tuno irin yadda Sa'adah ta fita a fusace hankali a tashe se in sake fashewa da dariya, ba su s an duk burga ba ce nayi musu, ko daya a abinda na fada ba wanda ya faru, ban ma san yaya aka yi ya karbi matar sa ba, na dai san se da suka shekara tana zaman jiran sa kafin ya hakura da guje gujen da yake yi ya karbe ta, shima a bakin Mama nake ji da take fada cikin gore goren ta na nayi asarar miji.

Yar ta kuwa, ban da Sa'adah bata da kai ai be kamata ta yadda da ni ba, duk da Mama mahaifiya ta ce amma shi kuma ai kanwar mahaifiyar sa ce shakikiya, dan haka saka sunan

Safiyya wa yar ta princess ba shi da alaka da ni, dan ko Barka kunya da gudun maganganun mutane basu bar ni na zo ba.

Su wai a tunanin su da zasu fadawa Aimah ciwo ne ta zuba musu ido, lallai har yau da sauran Sa'adah a sanin wacece ni, dan ma tayi Sa'a tazo a lokacin da ruwa ya daki babban zakara.

Da wannan nishadin na karya, kar kuyi mamaki dan nace nishadi, ni din a da kafin duk wani tashin hankali ya kutso rayuwa ta me tsokana ce, faran faran da saukin sabo, da dan karan surutu da iyayi, tun bayan faruwar komai kuwa se duk wannan halin nawa yayi sanyi, shiyasa yanzu nake jin dadi abina.

To fa, aka ce wai ba fada da malam ba daren, yau kam na jigatu dan abincin ranar da ake dan yafata min shiru har bayan Isha kafin a kawo min na dare, wato dai na yi na abincin rana na.

Haka na jawo na shiga ci zuciya ta ba dadi, nan da nan na tashi da dan abincin dama ba wani na azo a gani bane, a wajen na cigaba da zama na kasa tashi na wanke hannu, tunanin yadda zan yi kan lamarin abincin nan nake dan bana jin zan iya hakuri da jurewa tafiya a haka, dole se nayi wani abu.

Amma wani abu kamar me kenan?, Me gidan dai tun zuwa na gidan yau kwana uku da yini daya ban taba sa shi a idanu na ba se dai na ji motsin shigar sa da fitar sa, Hajiya Yayah?, No Hajiya Yayah is not a good option Dan ban manta nasihar ta ba a ranar da ta rakoni, wadda ta karkare da yabon Sa'adah da fadin sun shaidi kyawawan halayen ta, na san ko na fada ba yarda za'a yi ba, watakila ma ace ina neman ta da tashin hankali tun da ni nayi kaurin suna.

Ban da su kuma wa nake da shi a yanzu?, Yayye na sun sallama ni, Mama kuwa tun kafin na bar gidan muka fara da ita dan ban manta dukan da ta min ba ranar da aka daura auren, BA NI DA KOWA yanzu kenan dan zan kaiwa kuka na!.

A hankali na ja majina ina kokarin tsaida zubar hawayen da ban san da su ba se da na ji damshin su, lallai a rayuwa duk dan da yace ba za'a fada masa ba yana tare da wahala da tarin kalubale dan kuwa rayuwar sa ba zata yi albarka ba balle ayi zancen kwanciyar hankali, ni din nan babban darasi ce da misali me girma ga ire ire na masu taurin kai, kafiya, tsayayya da kuma rashin hakuri.

Da kyar na tsayar da hawayen na share su daga kunci na kana na tashi na wanke hannu na koma na zauna, tagumi hannu bibbiyu a kunci na ina tunano rayuwa ta ta baya cikin tsananin begen da ma ana juya hannun agogo ya koma baya.

******Sa'adah*****

Gyara dining din da suka gama cin abinci tayi ta wanke komai ta mayar inda ya kamata kana ta shiga dakin ta dan yin sabon wanka kafin ta tadda sanyin ran ta.

Tana shirya wa tana tunanin maganganun da suka yi da Zee yar uwar ta, irin rarrashi da ban bakin da ta mata wanda ta san ba dan shi ba da tuni ba wannan zancen ake ba.

"Kar ki sake ki bawa duk wani banzan kalaman ta damar yin tasiri a ran ki, komai da ta fada karya ne, burga ce zata miki irin ta ta dan ai dama kin san ta, ban da yanzu ma bata bari a fada mata tayi shiru, shine halin ya motsa take neman bata miki rai ta hana ki kwanciyar hankali da mijin ki, tana bakin cikin ko kallo bata ishe shi ba, da ita da shara duk daya dan ai kin ce be taba nuna ya san da ita a gidan ba, se ma kayan ta da Hajiya Yayah ta hado shi fa su ne ya bawa yar aiki ta kai mata, ko ba haka ba ne?".

Bata manta ba kai ta gyada mata dan bata jin zata iya magana, ganin haka yasa zee ta cigaba

"To kin gani, so take ta raba ki da walwala da jin dadin ki ganin ita bata samu ba, ni dake duka mun sani Masdooq ya so ta, amma ai wannan a da ne ko, dan na tabbatar da yana san ta da be banzatar da ita har haka ba, kiyi tunanin yadda a da jikin sa yake bari kan ta, amma yanzu fa, duk ba wannan, dan haka ki kwantar da hankalin ki karya ce duka zancen ta babu ko ɗaya daya kasance gaskiya".

"Akwai Zee, batun ciwon zuciya gaskiya ne, haka batun shekara daya kafin ya amshe ni ma gaskiya ne, kuma in ba shi ya bata labari ba a ina zata sani, bayan kowa ya daina kula ta a cikin family lokacin?".

"Amma ke shashasha ce, mahaifiyar ta fa, ko kin manta kanwar mahaifiyar sa ce?".

"Ai lokacin itama ta daina kula ta, dan na fada miki yanzu haka tana asibiti dan bata so wannan maida auren ba, Hajiya Yayah ce tayi insisting dan kar a cigaba da nuna su a gari".

"Ko ta daina kulata ai zata iya tsintar zancen in tana fadawa wasu ko, kin ga Sa'adah bari na miki baro baro, wallahi daga lokacin da kika ce zaki dinga bari zancen kishiya na tasiri a ran ki to fa zaki wahala, ki shirya rasa farin ciki da kwanciyar hankalin ki wanda dama abinda take so kenan shi yasa ta haɗa karya da gaskiya ta faɗa, in har kuma kina san ki cigaba da zama cikin farin ciki da soyayyar mijin ki to ki watsar da zancen ta, ba wannan kadai ba har wanda zata yi a gaba, ke gwara ma ki hakura da yada mata da magana dan na lura in ta tashi ramawa na ta na fin naki zafi  da ciwo, gata tana da dauriya da juriya dan kuwa duk maganganun da muka yi mata bata bar murmushi ba, ke kuwa fa jibe ki kuka kike zaune kina yi, dan haka for your own peace of mind, ki daina takalarta tun da zantukan ta na da tasiri a ran ki".

Da wannan kalaman da wasu na rarrashi da kwantar da hankali Zee ta samu Sa'adah ta saki ranta ta koma sabgogin ta, sedai a ranta da kuma bisa shawarar Zee ta kudure yiwa Aimah kora da hali, yunwa dai ai ba kanwar gyatuma nace bare gyatumi ko, kuma ance bata jure yunwa, to kuwa su zuba su gani!!!.

Kwana biyu da ya biyo baya haka ta cigaba da yi wa Aimah, da safe ta bata kamar na yar goye, da rana kuma babu, se da daddare shima kamar ta roka, sedai abinda ya bata mata rai Aimahr bata taɓa bata fuska ba bare tayi korafi.

Yau da suka cika sati da auren Aimah suna zaune bayan Isha a falo ita da Masdooq, hira ne suke yi cikin nishadi se murmushi suke yi, kan ta na kwance kan kafadar sa shi kuma yasa hannu ya zagayo ta jikin sa, can ya zare hannun tare da gyara zama ya kira sunan ta.

"Sa'adah".

Jin yadda ya kira ta with a serious tone yasa ta zame kan ta daga kafadar sa ta tashi ta zauna sosai tana duban sa tare da amsawa.

Kuriii tayi masa da ido zuciyar ta na bugawa uncontrollably, gaba daya yanayin fuskar ta ya canja ta kure shi da ido, cikin nutsuwa ya sake maimaita mata abinda ya fada da farko

"Nace ki kira min Aimah zan yi magana da ku".

Lumshe ido tayi cikin rashin sanin abin yi ta ja doguwar ajiyar zuciya se kuma ta mike jiki ba laka tayi hanyar falon baki, shima nunfashi ya fesar dan yana lure da yanayin ta, sedai dole ya sauke hakkin nan, ba ze iya take fadar Allah saboda farin cikin ta ba, yadda tayi hakuri lokacin da aka daura auren yanzu ma haka zata hakura, ze tabbatar ya lallashe ta har hankalin ta ya kwanta.

******

Ina kwance kan doguwar sofa, sanye da straight English gown da coffee color nayi rub da ciki cikin tunanin halin da Mama ke ciki, ba wanda yazo min balle na tambaye shi, wayata ba caji kwana bakwai kenan da take kashe, gaba daya raina a dagule yake, na rasa mi zan yi in sami walwala, q haka na ji an turo kofar falon kamar a fusace.

A dan firgice na mike zaune se kawai nayi arba da Sa'adah dake tsaye tana cika tana batsewa, na bita da ido cikin sauraren da me tazo kuma yau, tsayin lokaci bata yi magana ba se kuma ta ja dogon tsaki kamar zata tsinke harshen ta kafin ta juya

"In kin ga dama ki zo yana kiran ki".

Ta fada ciki ciki gab da zata fita daga dakin, da mamaki nake bin ta da kallo, in zo yana kiran? Shi wa kenan!

Kamar ringing din bell sunan sa ya kada cikin kaina, na zaro ido tare da mikewa, se kuma zuciya ta ta shiga fada min a'a tabbas ban dai ji daidai ba, Masdooq baze kira ni ba, mutumin da nayi sati daya be nuna ya san wata rai ta karu a cikin gidan ba, be taba lekowa ya ga ya ba

kwana ko ya na tashi ba, bana tunanin yau kam ze kira ni.

Se kuma zumbur na sake mikewa, na sani tun da can ba ya san jira, zan je, in ma ba shi dīn ba ne zan ga kowa ye in Kuma ji dalilin kiran.

Ban nemi mayafi ba haka kuma ban damu da rashin dankwali na ba dan damá ba san shi nake yi ba, a haka na zura slippers dina me taushi black na fito.

Tun da n nufo fakon gaba na ke faduwa, haka kuma na ji kafafu na kamar suna rawa, ina fitowa dan corridor din da ke tsakanin falon su da na guest din na hango shi zaune kan kujera, gaba na ya tsananta faduwa amma dai na dake na karasa da sallama, ban iya na kalle shi ba na samu one sitter daga can gefe na zauna, se da na daidaita murya ta dake dan rawa sannan na gaishe shi.

Jin shiru be amsa ba yasa na dago in a slow motion, se na samu idanun sa na kan matar sa, hannayen su sarke da juna, ta marairaice fuska shi kuma yana mata magana da ido.

Dauke kai na nayi na mayar kan tv babu wata damuwa akan fuska ta, har kusan minti goma kafin yayi gyaran murya yayi Bismillah tare da addu'o'i sannan ya dora da batun da ya sa ya kira mu.

Ba komai bane face neman mu zauna lafiya,mu hada kan mu mu kuma gujewa surutai da zugar mutane, se kuma ya fuskanto ni ba tare da ya ambaci suna na ba, tare da kausasa murya

"Mata ta bata iya tashin hankali ba, haka kuma me hakuri ce da biyayya, bata san tsayayya ba balle taurin kai da rashin jin magana, ina fatan ki koya daga gare ta ko kya samu damar gyara kura kuran ki na baya, ban na san rashin kunya gare ta dan ko ba aure Ita din gaba take da ke, na san halin ta babba da karami dan haka in naji sabanin kwanciyar hankalin da na saba gani a gidana to daga gare ki ne, ke kuma dear".

Ya fada tare da juyawa ga Sa'adah yana sake matse hannun ta cikin nasa, kana ya sassauta Muryar sa zuwa sigar rarrashi da neman alfarma

"Ki.dauke ta kamar kanwar ki Please, abinda ta kuskure ki gyara mata kin san tana da lapses da se an taimaka mata ta gyara, in da ta gaza ki kama mata, ki kuma cigaba da yi min biyayyar da na sanki da ita, ki kara kaimi wurin kyautata min, ina tabbatar miki in kika yi hakan babu wata ya mace da zata iya kai ko da kwatankwacin matsayin ki a raina talkless of ta kamo ki har ta fili".

"I'll insha Allah Hubby".

Ta fada tana rungume shi, shima ya sa hannu ya kulle ta a jikin sa. Duk abin nan da suke yi ina zaune ina assimilating kalaman sa a kaina, ta wani bangaren a boye yana nufin ina da mugayen halaye sabanin salihan na matar sa, dan haka duk a ka sami matsala to fa ni ce..................✍️.

Vote
Comment
Share fisabilillah

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 007 [ 21/06/2024 9:10 pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Oummey
Free book!!!

Ouummey 007

Page7️⃣

______________________Karo na biyu kenan ko nace na uku, Mama na ta fadi hakan lokacin da take dukana, haka Hajiya Yayah ta fada min haka da tana min nasiha, yanzu gashi shima ya bayyana.

Lallai dolen dole ma haka ne, na sani a da ina da taurin kai da kafiya, tsiwa, da rashin kunya in an tabo ni, haka kuma ban fiya hakuri ba, se dai ban da su ban san wasu halaye nawa marasa kyau ba dan bana neman tsokana kawai dai in an taba ni bana bari ne, haka ina da saurin sabo, kawaye na kuma na fadin ba ni da rowa dan abu na be rufe min ido ba, ta daya bangaren ina da tausayi, dan kusan almajira layin mu duka se da na sa aka sa musu kwano a gidan mu, daga baya da nake sana'a take kai min kuwa rabin samu na a gidan marayu da kan almajirai yake karewa, amma ban sani ba ko ina da wani hali mara kyau ne da ni ban fahimta ba, sedai koma yayane yanzu na yadda, halaye na basu da kyau sam tun da har baki uku suka fada.

"Kwana bibbiyun yayi Hubby".

Kalaman ta suka maido ni hayyaci na, na kuma fahimci ana batun rabon kwana ne, lamarin da ya sake sa gaba na ya yanke ya fadi, ban sani ba ko tsoro ne ya sa hakan ko kuwa fargaba, ba na ce ba.

"To shikenan, Allah ya bamu zaman lafiya baki daya, me girki zata dafa da kowa a lokacin kwanan ta, kina iya tafiya".

Zumbur na mike sanin da ni yake, ban tsaya komai ba kuma nayi falon da nake, hankali na baya tare da su balle wata soyayyar da suka fara a falon ta dame ni.

Kan kujera na fada jagwab, se na sami kaina da addu'a da fatan Allah ya sa ba da ni za'a fara zagayen kwanan ba yau, se kuma naji dariya ta kwace min lokacin da zuciya ta ta fada min babu abinda ze kawo shi daki na, ko da ace da gaske ya raba kwanan sedai ya tafi dakin sa ya kwanta, to mutumin da na lura ma san baya san kallan fuska ta me ze kawo shi kusa da ni.

Da wannan tunanin hankali na ya kwanta tas na tashi na canja kaya na zuwa na bacci na kwanta bayan na kara feshe dakin da room fresheners.

Addu'o'i na nayi na bacci na rufe idanu na cikin neman bacci, sedan cikin ikon Allah shiru yaki zuwa, har kusan awa uku ina kwance se juyi nake,daga karshe dai na shiga karatun suratul Kahf a raina idanuna a rufe kamar me bacci.

Wajejen karfe sha daya na dare naji an Turi kofar daki na, na dan firgita amma se na sake lafewa zuciya ta na bugu a kai a kai, ban ji an shigo bedroom din ba tsayin lokaci se na sadada a hankali zuwa window na daga curtains din hannu na na rawa, se kuwa na sauke idanu na a kan shi, yana tsaye yana karewa dakin kallo kafin kuma ya karasa kan doguwar sofar dake nan ya zauna, a hankali na ga ya cusa yatsun sa cikin sumar kan sa yana hargitsawa.

Tsayin lokaci yana a haka kafin yayi addu'a ya gicciye ya kwanta, kujerar tayi masa kadan sosai dan kuwa dogo ne Masha Allah, ni kaina da na fi Sa'adah tsayi kaina be karasa kafadar sa ba da kadan, ita kuwa a damtsen hannun sa kan ta yake.

A sanyaye na saki curtains din na koma kan bed na zauna, daga ganin yadda ya kwanta ba se an fada min ba yazo kwana ne, wato dai rabon kwanan da ni aka fara, wanda na sani dama haka ya kamata se dai yanayin yadda auren yake ya sa naji bana san hakan.

A zaunen ina tunani se bugawar karfe ɗaya na dare naji, dole na koma na kwanta, wani abin mamaki kuma ko minti biyar ban yi ba bacci yayi gaba da ni.

Kiran sallar farko ya farkar da ni kamar yadda na saba tashi kullum, na zauna har baccin ya dan saki idanuna kafin na tashi zuwa toilet nayi alwala na fito, dankwali na shimfida tare da sa daya daga hijabs dina biyu da aka sakomin a kaya na wanda da shi nake sallah na tayar da nafila

kamar yadda nake yi kullum.

Addu'o'i kuwa cikin sallah ta har ba zan iya kayyade adadin da nake roko ba, mafi maimaituwar addu'a ta itace Allah ya kawo sassauci a zuciyar iyaye na, ya sake reuniting tsakanin mu ya kuma yafe min saba musu da nayi tun farko, se kuma Allah ya tashi kafadun Mama ya bata lafiya.

Ina addu'a ina kuka cikin sujjada haka ma da na idar, a haka naji shigowar sa bedroom din, ban yi mamaki ba dan nasan tashin wannan lokacin sabon sa ne tun farko ba kamar ni da se shekarun baya na fara ba.

Alwala yayi ya fito daga dakin, lokacin har na mike dan tayar da wata sallar, a kan idanuna ya buɗe wardrobe ya shiga daga kayana, na sani pray mat yake nema dan haka cikin sanyin murya nace

"Babu pray mat se dai ka dauki dankwali na, nima akan shi nake yi".

Tsaki ya ja ya juya ya bar dakin gaba daya, ni kuma na tada sallah ta.

*****Masdooq****

Ba'a san ran sa ya raba kwanan ba se dai ba yarda ze yi da fadar Ubangiji, a da yaso ya share sedai nasihar da yaji yau a masallaci yasa tsoron Allah sake ratsa shi.

Base iya shiga dakin da take ba dan baze iya haɗa makwanci da ita ba, haka kuma ba ze iya haɗa numfashi da ita ba, kai gaba daya rayuwa da ita a under one roof ne be shirya wa ba, amma tun da Allah ya tsaro hakan ze daure yake kwana a falo har zuwa lokacin da Allah ze yi ikon sa a kan su.

A nan yayi addu'a ya kwanta kan doguwar sofa, sedai kamar abin shiri kamshin ta me sanyi da dadi ne ya kai wa hancin sa ziyara wanda ke nuni da itama wajen zaman ta kenan a falon.

Da sauri ya tashi ya juya zuwa ɗaya hannun kujerar, sedai shima hakan take, kawai dai be kai can karfi ba.

Haka dole ba dan yaso ba ya kwanta, ya dade bacci be dauke shi ba har wajen daya da mintina sannan, saboda yadda be yi bacci da wuri ba yasa be ji kiran farko da wuri ba, se da wasu msallatan suka sake yi tukuna.

A hankali ya mike zuwa bedroom din ta dan a matse yake sosai, baya jin ze iya jira ya kai dakin sa, ko da ya shiga banɗakin kamshi ne ya sake kai masa ziyara da ya sa ya lumshe ido batare da ya shirya ba.

Yana daya daga cikin qualities din ta da a baya suke sake tsuma shi cikin so da kaunar ta, wato tsaftar ta da tsananin soyayyar ta ga turare, zaman sa da ita da kuma neman ribato so daga gare ta yasa shima ya koyi kauna ga turare ta yadda baya jin zafin yiwa turare zuwa hudu ko biyar ya dire empty container.

Hali me kyau ɗaya daya samu daga gare ta wanda har yau be iya ya bari ba, hasalima yana jin dadin hakan, sedai Sa'adah kuma bata fiya tu'ammali da turare ba, ba wai bata sawa ba, a'a tana sawa amma ba irin sawar da ya saba ya ke kuma kauna ba.

Hankali kwance ya gama abinda ze yi ya watsa ruwa tare da maida kayan sa kana ya daura alwala ya fita.

Wardrobe din ta ya shiga bincikawa dan neman pray mat, duk da yayi mamakin ganin tsirarun kaya a kwabar ba kamar yadda ya san ta da san suttura ba, se be baiwa hakan mahimmanci ba, a lokacin ne yaji sassanyar Muryar ta da ada babu sautin da ya Kaita dadi a kunnuwan sa, sautin dake ratsa jinin jikin sa ya kara masa so da kaunar ta ya kuma yi increasing heart beat din sa.

Tsaki ya ja mata bayan jin abinda tace, haushi da tsanar ta suka sake tuko shi, shi be shiga harkar ta ba haka kuma baya san ta shiga tasa, to a kan me zata masa magana.

Wannan yasa ya fusata ya fice daga dakin tare da mata banging kofar.

Sallah ya tada a dakin sa na nafila da shafa'i da wuturi, ana kiran sallar biyu kuma yayi raka'atanul fajr kana ya wuce masallaci.

**Ina idar da Sallah na tashi na shiga gyaran daki na batare da na koma bacci ba, dan ban manta ba jiya yace me kwana ce zata yi girkin duka gida.

Karfe shida da rabi na fita zuwa falon, na dan kare masa kallo sannan na wuce kitchen, ja nayi na tsaya turus cikin karewa kitchen din kallo, nawa ne dai na shekarun baya ba'a can ja komai ba hatta woodds din, kawai dai an canja paint ne, se gaba daya na ga yayi min wani daban haka kayan cikin sun min yan tsurut, dan kuwa lokacin yana nawa a cike yake damkan da kayan amfani kama daga kan electrics zuwa ragowar kaya, dan hatta freezer biyu ne haka ma fridge dogo da karami, yanzu kuwa duk daidai ne.

Shiga nayi kan shawara da zuciya ta kan in taba mata kaya ko kar in tava, amma ai in ban taba ba bani da kayan yin amfani, dan haka tabawar ta zama dole gare ni, se nayi sighing na bude freezer na fiddo naman kaza, wani bowl me dan fadi na dauka na zuba ruwa a ciki se na saka kazar na bar ta ta narke, gefe daya kuma na debo chips na shiga peeling.

Cikin abinda be kai awa ba na hada hadadden farfesun kaza, chips da kwai na kuma dafa shayin da yaji kayan kamshi.

Komai na zuba shi a inda ya dace kana na ake kan kitchen island na fita falo, har lokacin me aikin bata fito ba wanda so da yawa tun shida na ke jin fara aikin ta amma yau shiru, se kawai ban jira ta ba na shiga gyaran falon da kaina, within minutes se gashi na kammala, na koma daki na na dauko turaren daki na na fesa na fesawa na wuta kuma na zuba a burner na jona.

Take kamshi me sanyin dadi ya cika falon se kuma lokacin na koma kitchen na shiga fiddo warmers din zuwa dining, na jera su in style na ake duk abin bukata sannan na wuce bedroom.

Wanka nayi na canja kaya zuwa abaya peach color na gyara gashi na na sa masa ribbon, daga gaba kuma na tsaga shi in style kana na feshe shi da turaren gashi, karamin mayafin abayar na ware na nada shi se ga shi cif a kaina, ta gaba gashi na dake kwance ya fito haka ta tsakiya a bude take, ta baya kuwa parking ɗin chignon dina ya sauka kan wuya na, se ya zama kamar gammo ne me kyau na nada.

Dan kunne na karami da nazo da shi gidan tun aure na wanda gold ne na makala batare da sarkar ba, hannu na kuwa na wadata shi da zobunan aure na.

Bayan kyau na, abu na farko da ke jan hankalin me kallo zuwa gare ni shine iya tsara gayu na, duk munin kaya babu ta yadda za'a yi ya hau jikina kunna ya nuna muni, kai hatta towel da bathrobe a jikina kyau suke yi kamar wani kayan kawa, hakan kuma akwai baiwa a jiki bayan iya gayu, wannan naa cikin abinda kullum nake godewa Allah akai.

Karfe takwas saura kwata na tashi zuwa falo, basu fito ba har lokacin se na zauna kan sofa na kunna TV ina kallon labaran safe, ina zaune Ya Masdooq ya fara fitowa daga dakin sa jikin sa sanye da suits masu kyau maroon color, wanda suka amshi chocolate skin din shi ne kyau suka fitar da tsarin kira da zubin sa na jarumi kuma kyakkyawan namiji.

Yana gyara necktie din sa yana nufar dining, wayar sa makale a kafadar sa yana amsa kira, tashi nayi zuwa wajen sa tare da ja masa kujerar, sedai be zauna ba se ya canja wata kujerar bayan ya bada ratar kujera uku da wadda na ja masa ya zauna.

Ban ji haushi ba se ma dan murmushi da nayi na zauna a wadda na ja, daidai lokacin kuma Sa'adah ta fito ta sha wanka da dan uban sun lace milk and brown color, tayi kyau sosai sedai da alama nawa wankan ne ya dake ta dan kuwa se kawai tayi cak a tsaye tana kallo ka, irin kallon nan na mamaki, ko bata yi tunanin gani na a wajen ba ne, ko kuwa ado na ne ya mamaye ta oho.

Gaba daya se yanayin fuskar ta ya canja ta kasa daga kafa ta karaso har se da mijin ta ya kira ta, se kuma ta saki dan murmushin yake ta nufe shi cikin karairaya, ta ja kujera gefen sa ta zauna bayan ta rankwafa ta yi kissing  goshin sa, hancin sa zuwa lips din sa.

Shi kuma se sakin murmushi yake yi, na sani suna yin komai ne dan su bata min rai, kowanne

kuma da nashi kalar niyyar, shi yana yi ne dan ramuwa ga abinda bai masa shekarun baya wanda ban ga laifin sa ba, ai a addini ma an yarda in an maka baka hakura ba ka rama, ita kuma tana yi ne dan ta bata min rai, ba dan komai ba se dan aurar mata miji da nayi, da kuma wulakancin da tace nayi mata a baya.

Ni dai na zuba masa komai nan aje gaban sa na koma na zauna na shiga zuba nawa, se da suka gama love din su sannan ta zauna, ya kalle ta tare da cewa

"Serve me".

"Gashi nan fa an sa maka".

"Na bar miki, ki dauki wannan ni se ki zuba min sabo, na fi son na ci wanda kika zuba da hannun ki".

Wani malalacin murmushi Sa'adah ta saki, ta jawo warmers ta shiga zuba masa tana masa hira, shi kuma yana amsa ta, Allah ya sani a wannan gabar raina ya ɓaci, amma se na fadawa kaina ai ba komai ba ne cikin irin ni abubuwan da nayi masa, dan haka se na share kawai na shiga cin abinci na.

Na riga su gamawa na masa Allah ya kiyaye daga nan wajen, dan na lura in na zake to kam ina dab da shan kunya so se na kama kai na, na wuce daki abina.

Daga cikin daki ina jin kyakyatun su, ga shi ni ba tv ba bare na kunna ta dauke min hankali daga kan su, waya ba caji balle na danna, haka na cigaba da zama har ya fita, ina tunanin kunnuwa na sun huta se kuma ga Muryar ta tana wake wake, daga baya ma se ta sa a home theatre abin ta tana bi, haka na yi lamo kamar marainiyar da ta rasa iyaye.....................✍️.

Jama'a ba'a commenting fa, wattpadians bakwa comments balle vote, bayan na fada muku littafin nan free ne, comments da vote ne ze sa na samu karfin gwiwar cigaba, akasin haka kuma I'll stop Dan ai saboda ku readera muke duk wannan hakilon, in bakwa appreciating baby anfani kenan, dan typing din kan sa is not easy.

Vote
Comment
Share fisabilillah.

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 008  [ 22/06/2024 8:50pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Oummey
Free book!!!

Ouummey 008

Page8️⃣

____________________Karfe sha biyu da rabi na fita na dora girkin rana, ina cikin haɗa kayan girkin ne kuma Sa'adah ta shigo, bowls din da na yanka veggies din da zan yi amfani da su wajen hada fried rice din ta daga ta juya se kuma ta aje tana jan tsaki

"Mtswww, da Allah kar ki kuma yanka min veggies a cikin wannan bowls din, ban da mugunta ai kin san ba kayan aiki iri  haka bane".

Daga mata kai nayi alamar to kawai dan fikewa fitina na cigaba da aiki na, ta gama ta fita ta dawo ta ce ma balbalawa cooking pot wuta ina neman cutar ta na kona mata saboda bakin ciki, nan ma hakuri na bata kawai, ta dawo tace na kure gudun gas dan rashin tausayi, a nan ne kuma na mata banza dan na san ai shi dai gas me gidan ke siyowa ba ita ba.

Kafin na gama girkin nan ta yi sawu fiye da ashirin cikin kitchen, kuma ko yaushe se ta samu abin fada, kunkuni da harare harare kuwa ba'a magana, dan ina jin ta kasa ƙasa tana fadin ba ze yiwu mutum ya kasa zuwa da kayan kitchen dan rashin gata ba,bita kuma diya me biyayya iyayen ta su siya mata kuma a kashe mata.

Tun da na fahimci so take na tanka se na bawa babu ajiyar ta, ban kuma duban ta ba har na gama na kai kan table na jera, na m gidan kuma na zuba a warmers din da nake ganin sun dace na hada masa basket, kana na koma daki na yi wanka.

Ina fitowa na canja kaya na fito falo na dibi abinci na isasshe, hankali na kwance sanin yanzu zan dinga ci ina koshi.

Da yamma ma haka na shiga kitchen na yi girki, kasancewar na kwana biyu rabo na da tuwo yasa na tuka tuwo shinkafa abina, na daure cikin leda yayi fari tass tayi kyau, gefe daya kuma na hada masa baza miyar taushe na da taji gyada da tantakwashi, ban da naman kaza da na zuba, se na hada banana milk shake dan Ina son sa sosai, na saka a fridge.

Ina aikin na ji dawowar megidan, be neme ba haka nima ban yi karambanin zuwa dakin sa ba, lokacin da na gama ana kiran magrib na fito dan wucewa daki, daidai lokacin shima ya fito dan tafiya masallaci, na dan dukar da kai kasa na masa sannu da zuwa.

Yanzu ma be kalle ni ba bare ya nuna ya san da mutum ma ya sa kai ya wuce fujsar sa ma'abociyar kamala a hade tsaf, na girgiza kai nima na wuce.

Ina idar da Sallah na yi azkhars dina tare da cigaba da lazimi har aka kira Isha itama na tashi na gabatar, ina idarwa da na gama addu'o'i na se na tashi na karawa jikina turare kana na fita dan cin abinci dan naji shigowar maigidan tun dazu.

Ko da naje ba sa kan dining, na ja kujera na zauna tare da lumshe idanuwana, ina a haka na ji bude kofa tare da fitowar su, na ɗan bude ido kadan na bi su da kallo, daga dakin Ya Masdooq din ne suka fito tare suna dariya, da alama dai wani abu n ya basu nishadi.

Lokacin da suka zauna se na tashi na bude warmers na shiga serving din shi, duk da dazu ya nuna baya so amma be sa na zuba ba sedai kirji na na ta duka kar ya gwale ni yanzu ma.

Ina gama zuba komai na fara mikawa gaban sa, dai dai na dauko bowl din coslow zan ake masa ya mike tsaye zumbur kamar wanda aka tsikara cikin ɓacin rai ya kai wa table din gaban mu duka

"Nace ki yi serving dina ne?, Me yasa ke kam ba zaki taba hankali ba a rayuwar ki?, Dalla kwashe wannan haukan naki daga gaba na, daga yau kuma bana bukatar hannun ki wajen zuba min abinci, Sa'adah will be serving me day and night, I mean everytime".

Kasake nayi ina kallon shi, yanzu duk wannan ɓacin ran har da su dukan table dan kawai ba ya san in yi serving din sa ne? Ai da tun farko se yace min baya so kawai, ni kuma I'll respect myself ba zan yi ba, ko da yake na lura kawai neman abinda ze disgani gaban matar sa yake ya kuma bata min rai, dan tun a baya ya san na tsani gwaliya.

A hankali na dubi kasan tiles zuwa jikin table din da coslow din hannu na ya bare, gaba daya gurin ya ɓaci da bama da su cream salad.

A sanyaye na ja baya daga cikin kujerar da nake na fita na kwaso kayan gyaran falo dan gyara wajen, Sa'adah da ke ta sakin murmushi tana shafa bayan mijin ta alamar rarrashi kafin daga baya kuma ta fara serving din nashi ta juyo ta lalle ni cikin fari da ido farrr

"No, ai ba se kin yi wahalar gyarawa ba Aimah, bari na kira Hindu ta gyara, Hindi Hindu, yauwa kin ji gata nan zuwa, dan Allah bar gyaran wajen ki zauna muci abinci".

Ban musa ba na aje abubuwan hannu na na mike na canja kujera na zauna dan waccan da nake kai ta ɓaci da cream salad da bama, na zuba abinci na yi bismalla na shiga ci, ban bari damuwar wulakancin da yayi min ta sa na ki cin abinci ba dan na san in ma nayi hakan babu me damuwa, so s na sake na cika ciki na tas.

Ina gamawa na koma kitchen na dauko milkshake dina, cup uku nayi amma daya kawai na gani, ban damu ba tun da bata kwashe duka ba, dan na san aikin Sa'adah ne, kai a kasa na zo gifta su nace musu sai da safe.

Ban jira amsawar su ba balle naji sun amsa din ko akasin haka na sa kai zuwa daki na.

Ko da na shiga se na aje milkshake din na kasa sha, raina a dagule, da ace ba'a gaban Sa'adah bane yayi min haka ba zan damu ba, amma a gaban ta abin yayi min ba dadi, ni mutum ce me girma ma self respect shiyasa duk in da na san in naje za'a wulakanta ni bana zuwa, shima kuma ya san haka shiyasa yayi min dan ya san zan ji zafi.

Na sani duk abin nan da yake ramawa yake, na Kuma yi masa abinda yafi wanda yayi min yau, amma kuma ni ban masa a cikin mutane, se muna i mu biyu ne,e yasa baze rama iya yadda na masa ba.

Haka nayi ta sake sake daga karshe dai na fada wa kai na na san matakin dauka, daga yau duk na yi abinci ko ita tayi ba zan kuma fita ci da su ba, zan debi nawa na dawo daki na zauna, dama ba abinda zama cikin su ke karamin se ware ni da suke yi kamar mujiya.

Se yanzu hankali na ya kwanta, har na dau milkshake dina na shiga sha a hankali, ina gamawa na koma wanke baki a toilet, na sake gyara gado na duk da dama a gyare yake, na yi addu'o'i na kwanta, cikin ikon Allah babu dadewa bacci ya sace ni.

Yau da asuba kamar jiya na tashi salloli, ina cikin sallah na ji fitar shi daga dakin, ina gamawa na dan koma bacci, karfe shida na tashi na gyara daki na kana na fita hada kari.

Tea da farfesun cow leg nayi se chips da na ga sun maida cimar safiya, tea da bread da na sake gasawa yayi dan ja yayi kyau, na kwashi na su na kai musu dining ni kuma na dau nawa na kai daki sannan na fito na gyara kitchen din da falo.

A nutse na karya bayan nayi wanka na canja kaya, ina gamawa nayi hamdala tare da godiya ga Allah na dan kishingida kan sofa ina jiran abincin ya fada min na tafi na koma bacci tun da bani da abin da zan yi.

A hakan da nake naji bum an turo kofa an shigo, na sani Sa'adah ce shiyasa ban yi wahalar bude ido na ba, tayi tsaye a kaina ta gama kare min kallo ban ce mata ci kan ki ba, se kuma ta juya tana tsaki ƙasa ƙasa

"Ke ana kiran ki".

Ta sa kai ta fita, kamar kar in je dan yadda ta fadi sakon, se kuma dai na cewa kai na ai na canja ko, dan haka zan je.

Na tashi na saka takalmi na na fita zuwa falon, a dining na same su zaune hannayen sa cikin na Sa'adah ta marairaice tana masa magana ƙasa ƙasa shi kuma ya rufe idanun sa tare da jingina jikin headrest na kujerar.

Da sallama na karasa na dan tsaya daga gefe, se kuma lokacin ya bude idanun sa ya zuba su a kai na, abinda tun shekaru biyar baya be kuma faruwa ba!.

Wani irin dokawa kirji na yayi, ba wai iya na kaifin idanun sa a kaina ba, har da na jan da naga idanun sa sun yi, jan da se yana cikin tsananin ɓacin rai ake ganin shi, dan kuwa ya iya sarrafa kan sa da fushin sa.

Rawa na ji jikina ya dauka batare da na san na mene ba, na hade hannaye na da sauri na sarke, na sunkuyar da kai na kasa ga barin kallon sa, tsayin lokaci kafin naji Muryar sa a dishe very low amma a kausashe dauke da wani irin bitterness

"Kashe ni kike son yi ko NU'AIMAH?".

Tashin hankali na ne ya karu jin yadda ya ambaci full sunana, abinda zan iya rantse wa da Allah be fi so a kirga ba yayi hakan, ga kuma batun kisa da ya kawo, baki na bari ya kama yi, ya ki bani hadin kan furta ko wace kalma kamar yadda nake son yi

"Na sani na kuma dade da sani kamata yadda kika dade kina sanar da ni da baki ko a aikace cewa kin tsane ni, wato tsanar ce ta kawo ki ke son ganin baya na?".

Girgiza kai kawai na dinga yi hankali a tashe, hawaye suka shiga kwaranya daga kunci na, zuciya ta matse waje guda,

"Daga yau Sa'adah zata cigaba da girki gaba daya, ita ke da kwana ko ba ita ke da shi ba, jeki, Allah ya fiki".

Durkushewa nayi a wajen sautin kuka na na fara fitowa fili, magana nake son yi har lokacin amma na kasa, shi kuma sautin kukan ke takura masa yake kara fusata shi, a ganin sa a cuce shi kuma shi za'a yi wa kuka?

Se kuwa ya daka min tsawa, irin tsawar da ban taba jin wadda ta firgita ni ba kaf rayuwa ta, na mike a rude na kwasa da gudu zuwa daki na kukan na kwace min gaba daya.

Kan sofa na zame na shiga yin sa, dama akwai dannannun damuwoyin a kasan raina, bana san in fiya kuka ne kar na sawa kaina rauni da yawa, sedai yanzu gaba daya se suka taso, kukan nake yi tun ina yi a hankali har na fara dukan sofar, zuciya ta fada min take me yasa se ni kadai? Me yasa ƙaddara ta ta zama me zafi? Me yasa jarrabawa bata karewa a rayuwa ta? Shin bana tuba ba?, Ba na yi nadama Ba? Me yasa ba za'a bani dama ta biyu ba?!!!.

A haka ya shigo ya same ni batare da na san da shigowar ta sa ba, se kawai jin maganar sa nayi daga sama

"Kina kuka ne dan ban mutu ba?, Hmm, ba abin mamaki bane, sedai na fiki takaicin rayuwa tare da ke, na fiki tsanar zaman ki a karkashin inuwa daya da ni, bari kiji wani abu, na tsane ki Aimah, na tsane ki fiye da yadda na tsani mutuwa ta, ke ce rai daya da bana fatan haduwa da ke ko a kiyama, sedai ni da ne me biyayya, na san mutunci da darajar mahaifana, wannan abu biyu kisa a ran ki zaman su kike yi a nan, wato biyayya da darajar su Hajiya Yayah, and batun tea da kika cikawa sugar dan ki kashe ni be yi aiki ba, ki canja sabon salo, ku kuwa ki dauko fetir da ashana, wala Allah in a shekarun baya be yi amfani ba yanzu kiga yayi".

Tun da ya fara magana kuka na ya dauke cak ina sauraren shi har ya gama ya fita, da alama dama abinda yazo sanar min kenan, wato ya tsane ni, sedai ba abinda ya dauki hankali na ba kenan a zancen sa, batun sugar da yake yi, wane sugar na cika wa tea bayan na san be so tun da bare kuma yanzu da yake da ciwon zuciya, shiyasa ma shi da sugar din ake tafasa ruwan tea din.

Kuma ko yanzu a gaba daya shayin gidan sugar cubes goma kadai na saka, wanda na san babu ta yadda za'a yi ace wai yayi yawan da har ze tada hankali, naga mutum daya ma na shan cube biyar takwas balle tea din mutum uku an sa masa guda goma, lallai abin da mamaki.

Se kuma na tashi zaune da sauri, duk da ina hana kai na yin tunanin amma ina, dole se dai hakan, mu uku ne fa a gidan se kuma hindu da in ranar aiki na ne yarinyar ba abinda take yi ban da gyaran bedroom din Sa'adah, kasa hakuri nayi kawai na mike na fita ko takalmi ban iya tsaya wa na saka ba.

A falo na tadda Sa'adah dan lokacin me gidan ya fita, daga gefen ta na tsaya na sassaita murya ta kafin na kira sunan ta, ta juyo ta dube ni dan haka na dora da batun da ya kawo ni, wato tambayar ta ko ita ta kara min sugar a tea.

Murmushi tayi me kama da dariya kafin ta dube ni a kaikaice

"Me kike tunani to Aimah?, Shin kin ga laifi na dan ina kokarin kwace mijina daga gare ki? Ke fa kika koya min killace shi ga iya mutum daya, yanzu kuma dan ina aikata hakan se ki ji ba dadi?,

Well, bari na amsa ki, eh ni na kara sugar cikin tea din sa dan na san daga yau ba ze kuma cin girkin ki ba, ga shi kuma nayi nasara, daga nan fa? Saura hana shi kwana a dakin ki, hakan kuma na tafe, kin san me? Shi ma kuma zan yi nasara!!!".

Daga haka ta kyalkyale da dariya ta maida kan ta ga TV, na jima a tsaye ina kallon ta kafin na daga kafafu na da sukai sanyi na juya zuwa daki.

Wato a ko ina akwai kalubale, a gida dai babu yunwa, babu rashin sha babu kuma rashin suttura, sedai babu kyakkyawan kallo ko kyakkyawar magana daga wajen iyaye na, hantara, kyara, zagi da tsaki ne ke shiga tsakani na da mahaifiya ta, yayye na kuwa zagi har da duka in na yarda ba tsaya kusa da su, baban mu shi gaba daya ma baya min.

A nan kuma Sa'adah ce ginshikin damuwa ta, se kuma shi uban gayyar gaba daya.

Amma ba komai dan na san kome ke faruwa da ni a yau ni na jawowa kai na, da tin farko na zama me biyayya da jin maganar iyaye na da haka bata faru ba, duk da cewa su ma da na su laifin a ciki amma be kai nawa ba, shiyasa duk wanda ya san labari na yake tattare duk laifin ya dora min.

Tun daga ranar na koma yar gidan jiya, wato batun yunwa dan kuwa horo me kyau Sa'adah ke min kan batun abinci, ni kuma na yi rantsuwar ba zan kuma fita yin kari tare da su ba.

Haka nake hakurin dole, take kuma na fara rama, idanuna suka zurma kashin yunwa yace salamu Alaikum.

Mun dau tsawon sati uku a cikin wannan yanayin, duk ranar girki na yana kwana a falo, daga zarar ya fita sallar asuba kuma se wani daren, shima se sha daya zuwa sha biyu sannan ya shigo.

A sannu a sannu kayan shafa na suka kare wato skincare, saukin tama shower gels dina uku ne kuma duk an sako min su, dan haka bani da damuwa a wannan bangaren, sedai dake da shi nake amfani wajen wanke toilet yasa guda daya har na ci rabi.

A sati na hudu ne na gajiya, lokacin wata na biyu da rabi a gidan, ranar talata wato jiya ba'a bani abincin dare ba, tun tea din safiya ne a ciki na, karin ma kuma se after 10am aka bani, lokacin hatta idanuna bana gani daidai da su saboda yunwa, ga jiri da ke damu na, nan da nan na cinye dan chips din da ta zuba min da Black tea tare da bread slide biyu, kuma ban ji komai ba, na dai daure na je toilet na sha ruwa na dawo na zauna na zuba tagumi..................✍️.

Vote
Comment

Share fisabilillah.

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 009  [ 22/6/2024 8:51pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Oummey
Free book!!!

Ouummey 009

Page9️⃣

________________Abincin rana a kawo ba'a kawo ba shiru har after four, lokacin kam na kai karshen dauriya dan haka na mike ina rangaji na nufi kitchen din.

Cikin Sa'a babu kowa a ciki, jiki na rawa na shiga kokarin daga indomie, tsurar ruwa kawai na dora na zuba mai da yajin indomie din na zauna jiran ya tafasa na watsa indomie din dan bani da karfin yi mata kowane iri hadi.

Ganin ba zan iya itama zamana tafasar ba na bude fridge na dauki fresh milk na fasa na shiga sha a yunwa ce kai kace ban taba shan fresh milk ba.

Ina sauke kwalin fresh milk din daga baki na Sa'adah ta shigo, ban dube ta ba na jefa empty container din a dustbin kana na koma gaban gas.

Da mamaki take kallo na kafin kuma ta sha kunu ta matso jikin freezer ta harde hannun irin na

matan gida

"Wa ya baki izinin shigo min kitchen balle ki taba min kaya?".

"Yunwar ciki na ce, na gaji da jiran yunwar da kike min ne yasa na fito dan i can't take it anymore".

"Okay shiyasa kika shigo min kitchen kike min gaban kan ki?".

Ban lalle ta ba ina bare indomie ina sawa a ruwan dake tafasa na bata amsa

"Kina magana kamar gidan ki ne na ke Miki abinda ba ki so, ko kuwa kin manta kitchen din na mijin mu ne?".

"In kitchen din na sa ne kayan kitchen din fa?".

"Eh kitchen da kayan abinci na sa ne, kayan kitchen kuma naki ne, and am sorry for taba miki kaya batare da izinin ki ba".

"Oh ai na zata su ma din zaki ce na sa ne, da na sanar da ke wannan kayan iyaye na ne suka siya min cikin alfahari da irin diyar da suka haifa kuma suka aurar cikin girma da daraja batare da tayi abinda ya zubar masu da kima ba, ko kuma ya sa aka ga basu iya tarbiyya ba".

Wani kallo na juyo nayi mata, sedai ban tanka ba na juya ina juya indomie din cikin tausar zuciya ta da ta fara harzuka, duk abinda za'a min in a karan Kai na ne zan iya hakura amma ban da a sako iyaye na, tun da haka nake kuma har yanzu ban canja ba, shiyasa yanzu naki yanka wa Sa'adah dan kar ta cigaba in yi loosing control, karshe in zo in Yi abinda zan yi nadama.

Na zata ai tun da ban kula ta ba shikenan zata hakura ta bar zancen, sedai ina se ta gyara tsayuwa ta cigaba

"Shi dai dan da ya raina iyaye be yi ba dan haihuwar sa ma asarar ce, gwara ace tun yana ciki aka yi barin sa aka huta, Allah ka raba mu da haihuwar asara, wasu iyayen kam sun yi asarar haihuwa tun da har suka gaza tarbiyyantar da ya'ya ".

A wannan kadamin ne na kasa hakuri, duk kuwa da yadda na so yin na gaza har na juyo idanu jajir ina duba Sa'adah, nuna ta nake da spoon din da nake juya indomie kana cikin kausasa harshe na ce

"Duk abinda zaki yi min kiyi be zama lallai na kula ki ba dan zan iya hakuri na jure, amma ko da wasa, ko a cikin mafarki kar ki sake ki shigar da iyaye na shirin shirme da haukan ki dan zan iya gwada miki haukan da ya fi baki, na fada miki ".

Da alama dama haka take so dan kuwa murmushi ta sake,

"Ni ce mahaukaciya kenan, ko da yake a wajen ta gida na koya kin san itace shugabar mahau...."!

Ban bar ta ta karasa kalaman ta ba se da saukan marin da ni kaina na san ze yi zafi a kuncin ta, dama kuma da niyyar yayi zafin na daga hannu na, da sauri ta ja baya tana zaro ido dafe da kuncin ta

"Ni kika mara?".

"Na mare ki, kuma zan kara marin ki in har kika cigaba da kokarin gwada min dabban ci da akuyanci".

"Hmmm, lallai yarinya kin tsokano wa kan ki fitina, ba zan rama mari a kuncin ki ba, sedai zan mari rayuwar ko ta inda ze fi miki ciwo da radadi, se na tabbatar kin yi danasanin kai hannun ki jikina".

"Ba yau na fara dana sani ba, ba kuma yau na fara nadama ba, in har nayi abinda ze wanke min zuwa na ji dadi a lokacin da nake so, bana damuwa da nadamar da zata biyo baya".

"Aikuwa zaki fara wannan karan".

Tsaki nayi mata ta fita daga kitchen din ni kuma na karasa dafa indomie din, ina gamawa na zuba a plate na aje kan kitchen island, na dan bar ta ta sha iska sannan na fara ci, hana dan ci da yawa se kuma na dauki plate din zan tafi daki.

Wani wawan santsi ne ya kwashe ni a kofar kitchen din na zame na fadi, kafa ta ta bugu sosai ta yadda na kasa daurewa se da na saki kara, indomie din ta kife again a kan kafar, dan ma wai ta dan huce kadan amma duk da haka da zafi sosai.

Babu kowa a falon babu kuma wanda ya fito dan taimaka min, da kyar na ja jiki na mike bayan na kai kusan minti biyar a zaune a wajen, cikin dingishi na mike ina takawa lebe na cikin baki na cije shi saboda azaba, a hakaa na kai kofar dakin hindu, na bubbuga ta buɗe, tana gani na ta sunkuyar da kai, kofar kitchen din na nu na mata cikin muryar dake bayhana zafin da nake ji nace mata nayi bari ta gyara, amma ta kula akwai ruwa a wajen kar ta zame.

Daki na wuce na zauna a kan kujera ina runtse ido dan ba kadan ba na bugu kuma nake shan azaba, ruwan da na gani zube a wajen ya tabbatar min shirya min faduwar a kai, ba kuma kowa bane se Sa'adah, dan san da na shiga kitchen din babu ruwa a hanyar, haka kuma ni ban zubar da ruwa ba, bugu da kari ita ta shiga ta fita, lokacin da zata fita kuma ban kalle ta ba balle na san me tayi.

Hannu na sa na taba kafar daidai gwiwa ta, zafi da radadi suka ratsa ni, idanun suka cika da kwalla, a raina kawai tunanin me na yi wa wannan baiwar Allahn nake yi da har ta shirya min mugunta.

In dan na mare ta ne ai ita taja ko, tun da se da nace kar ta zagi iyaye na amma ta zagar min Mama, shine take nema ta sabauta ni, yanzu da da na fadi karyewa nayi kenan ita ba ruwan ta?, Lallai dole na kula da zama na da Sa'adah dan wasa wasa ba karamar muguwa bace.

Haka na wuni cikin radadi, sallar magrib da Isha kuwa duk a zaune nayi, suma da kyar ina hawaye ina numfarfashi, kafin kace tara tayi gaba daya kafata ta kumbura, da jan jiki na kai toilet na taro warm water sosai na sa towel a ciki na dinga dannawa ina yi ina hawaye zafi, a haka nayi tayi har na dan ga kumburin ya ragu sosai amma ba wai ta daina zafi bane.

Yau da ke me gidan ba'a daki na yake ba ban sa shi a ido ba dan ban fita ba tun bayan a binda ya faru, shi kuwa dama ba ya shigowa waje na se ran girki na, shima a falo yake kwana dan haka se in iya cewa tun ranar da yace kar na sake girki ban kuma sa shi a ido na ba.

Haka na kwana cikin wahala, ina ji ana kiran sallar farko amma na kasa tashi, se da aka kira sallar biyu sannan na kuma samo warm water a toilet na kuma gasa kafar, cikin ikon Allah na ji saukin ta har na tashi nayi alwala nayi sallah, sallar ce dai se da dabara dan wajen yin sujjud da zama ina shan azaba, a haka dai na yi.

Yau ko gyaran dakin da nake ban iya nayi ba, se sama sama na dan kaikaye shi na koma na zauna, dake ina gyara wa kullum kuma gyara sahihan se yau din be nuna rashin gyara ba, kamshin turare na da ya kama dakin na tashi a hankali.

Karfe takwas ina zaune na ji muryar sa na tashi cikin daga sauti yana kira na, da alama dai yana falo dan ta can nake jin kiran.

Na kakkama kujera na mike da kyar na gyara zaman doguwar straight gown din dake jikina, a da daidai jiki na ce tsam kuwa, amma a yanzu kam ta yi min yawa dan kuwa yawo nake a cikin ta.

A sannu nake takawa saboda kafata har na kai falon, na same shi zaune kan two sitter, Sa'adah zaune kusa da shi idanun ta na ruwa haka kuma sun dan yi ja.

Kasa zama nayi saboda in zan zauna shima zafi ne haka in zan tashi, daga tsayen na gaida shi kana nace ga Ni

"Wane tsabar gigin rashin mutunci ne ya kai hannun ki fuskar matata da sunan mari? Sa'ar ki ce ita? Sanin halin ki ne yasa na yi warning din ki akan ta fa tun farko, wato har yau taurin kan ki da rashin mutuncin ki suna nan ko?".

Cikin mamaki na dubi Sa'adah, ina ce dai ta zuba min ruwa na fadi, to ba shi kenan ba ta rama, me ye kuma na zuwa ta faɗa masa, amma tun da haka ne bari na fada masa abinda tayi min, na san shi kan sa in yaji Mama ta zaga lalle dole ya bata rashin gaskiya, na ayyana hakan a raina.

"Zagin Mama tayi, ni kuma na kasa jurewa na mare ta".

"An fada Miki kowa ma bai san darajar iyaye ba ne irin ki, ko kuwa ance miki in duk jikina kunne ne zan yarda Sa'adah zata yi haka, ko kuwa ke din ce ban sani ba, to bari kiji yadda na san bakaken mugayen halayen ki haka na san kyawawan salihan halayen matata, dan haka ki fada min wani dalilin ba wannan ba,bin kuwa ba haka ba yanzu kiga abinda baki yi tsammani ba".

Tsabar mamaki kasa rufe baki nayi, Mama fa ta zaga, na gaya masa amma ya Musa, saboda matar sa waliyya ce kenan ko me, har da fadin wai yasan halayen ta, yana nufin kenan karya nake yi?.

"Wallahi Mama ta zaga daga na shiga in dafa indomie, kuma ba bata hakurin taba mata kayan ta da nayi batare da sanin ta ba, shine kawai ta hau fada min maganganu, kuma in har ka shedi bakaken mugayen halaye na ya kamata ka tuna karya bata cikin su".

"Wallahi ban zagi Mama ba hubby, ya za'a yi na zage ta bayan kanwar Hajiya Yayah ce, kallon uwa fa nake yi mata, yadda zan girmama mahaifiya ta haka nake girmama naka dan na san sun min komai tun da suka haifa na aura, kawai na shiga kitchen na samu tana dafa indomie shine cikin batkwanci nace wato dai har yanzu cin ta na nan, ban da haka duk yawan abincin da ta zuba amma be ishe ta ba, shikenan fa ta juyo ta shiga fada min magana wai ai abincin na mijin mu ne ba daga gidan mu aka kawo ba, ni kuma duk na zata wasa ne se nace dama ta ya za'a kawo abinci daga gidajen mu bayan tuni an sallama maka mu, shikenan fa wai kar na zagi iyayen ta, nace to ina abin zagi a magana ta, ke dai kin cika abin dariya, kawai se ta fara fade faden magana wai an fada min bata san haɗa mu aka yi ba, wai saboda ita se da ka shanya ni tsayin shekara kafin ka karbe ni mata, waye meye, shine Ni kuma na fusata nace kar tayi min rashin kunya, se ta rike kugu ta bar daga abincin wai in tayi fa ya zan da ita, ganin haka se kawai na juya zan fita daga kitchen din ina cewa ai dama ba kunya ya ishe ta ba nima manta wa nayi yasa na mata wasa, har na kusa fita daga kitchen din se ji nayi tace kin ga, ni kuma na zata wani abu ne se na juya shine fa se saukar mari kawai na ji a kunci na, wai karewar rashin kunya ta mare ni se in tabbatar bata da kunyar".

Sake baki nayi ina bin Sa'adah da kallo cikin al'ajabi da mamakin irin yaddaa ta iya zauna wa ta shirya wannan karyar, ta tsara ta haka kuma ta tsaru yanzu kuma tazo take bada haddar ta.

Mai da duba na yi kan sa lokacin da ta gama dan in ga yadda ya karbi maganar, se kuwa na tadda idanun sa akai na yana watsa min wani mugun kallo kamar ze dauke ni da su, se kuwa cikin kokarin kare kai na na daga hannu na shiga rantsuwa

"Wallahi tallahi karya take, wannan matar karya ta shirya maka wallahi, ke Sa'adah ashe ba karamar munafuka....".

Ban dire kalmar munafukar ba nima na samu nawa marin daha mijin Sa'adah, idanun sa sun yi jajir yana huci, ba zan ce ga sanda ya taso ba balle yazo gaba na, nidai saukar marin kawai na ji wanda ya dauke min ji da gani na sakanni nayi baya na fada kujerar baya na har ina sake buge kafata ne ciwo.

Ko da gani na ya dawo idanu na sun sauya kala, ɓacin rai ne karara rubuce a kan fuska ta, ba dan komai ba se dan yanke min hukuncin qbinda ban aikata ba da aka yi, ban kuma gama fita daga wannan ɓacin ran ba yace

"Ki kuma tashi ki dauko mayafin ki muje gida Baba na kira, jakar yarinya annoba kawai, tun da nake zaman aure da Sa'adah ba'a taba jin kan mu ba shekaru biyar kenan, amma daga shigowar ki rayuwar mu kin fara haddasa mana fitina da tashin hankali, ke din Annoba ce kuma musiba ga rayuwa ta, sanin ki be amfana min komai ba face nadama da danasani".

Wadannan kalaman na sa sun fi marin da yayi min zafi ne sa ba kusa ba, zafin su ya wuce digar dalma kan fata, radadi da ciwon sa kuwa ba zan iya fasaltawa ba.

Abinda na sani shine wannan rana tana cikin bakaken ranaku gare ni, kalaman sa sun yi wa kunne na wani irin shiga da ya rike su, zuciya ta ta haddace su ta tura wa kwakwalwa ta tayi storing, suka zama abin tunawa gare ni cikin kowace dakika.

Abinda ya biyo bayan kalaman suka sake sare min gwiwa suka cire min dukkan wani hope na rayuwata farin ciki, suka saka min ciwon da ya zama silar mummunan ciwon da na taba yi a rayuwa................✍️.

Vote
Comment
Share fisabilillah.

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 010  [ 24/06/2024 7:41pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Oummey
Free book!!!

Ouummey 010

Page 🔟

___________________Kamar yadda yace mayafi na dauko muka tafi amsa kiran Baba, wato muka tafi gidan su Ya Masdooq wajen mahaifin sa da muke kira Baba.

Duk da nayi mamakin yadda aka yi Baba ya san da matsalar amma ta wani bangare zuciya ta na cike da hope a kan sa, irin son da ya gwada min a baya kamar ƴar cikin sa da yadda yake jiɓintar lamari na ya sa nake jin zan samu adalci a can gaban su.

Se kuma daga baya na daina tunanin yadda aka yi ya san da fadan, babar Sa'adah kanwata sa ce, Sa'adah ta kira ta ta sanar mata, ita kuma shine ta kira Baba wan ta ta fada masa, wannan fa a nawa tunanin ne dan har yau ban san yadda aka yi batun yaje ga Baba ba.

Abinda na sani shine Baba na matukar san Aunty Hauwa Babar Sa'adah dan su kadai iyayen su suka haifa, aka kuma mutu aka bar su tare, shi ya dau ragamar kulawa da ita duk da cewa suna zaune ne hannun kawun su, Baba na matukar son Aunty Hauwa, yana ji da ita kamar me dan yana ganin ita kadai ce jinin sa shakikiya kwaya daya, haka kuma yana ganin ta macece me rauni, shiyasa har bayan auren ta duk abinda take so in ta kira Baba se yayi mata, wannan yasa ma har suka dan fara samun matsala da Hajiya Yayah dan wani sa'in ana take mata hajji wajen neman dole se an mata abinda take so, kafin daga baya su bar garin ita da mijin ta, wannan yasa suka samu zaman lafiya.

Ina wannan tunanin se jin tsayuwar mota nayi, na dago na dubi gidan ta glass ɗin window back seat din da nake zaune, na yunkura ina runtse ido saboda zafin da kafata ke yi, da kyar na fito nayi gaba batare da na tsaya duban su ba, can na bar su sun tsaya yana lallashin matar sa.

Da sallama na shiga falon, Aunty Luba da Hajiya Yayah na zaune suka amsa min, ganin su yasa zuciya ta yin rauni sosai, idanuna suka cika da hawaye.

Na daga kafa a sanyaye na karasa gaban Hajiya Yayah na zube ina gaishe ta, kuka ya kwace min na kifa kai na kan laps din ta ina yin shi, bata hana ni ba haka ma Aunty Luba, suka bar ni nayi shi sosai ta yadda har jiki na dake rawa ya daina, kana na dago bayan na share hawaye na na gaida Aunty Luba, ta amsa min can kasa tana cigaba da feeding babyn ta da take yi.

Se lokacin ina lura ashe su Ya Masdooq din sun shigo ina kuka, na janye ido na koma na sake kifa kai na jikin kafafun Hajiya Yayah, a hankali na ji saukar hannun ya kan baya na tana shafawa alamar rarrashi sedai bata ce komai ba, tsayin lokaci tana min haka har na ji zuciya ta ta fara sanyi na shiga sakin ajiyar zuciya a kai a kai, mintuna kusan biyar kafin ta dago ni ta zuba wa fuska ta ido sannan can kasa tace min

"Kiyi hakuri, ki cigaba da hakuri, shine abinda zan ce miki a yanzu NU'AIMAH".

Daga mata kai nayi, se ta janye ni daga jikin ta ta tashi zuwa sama ta sanar da Baba zuwan mu, suka sauko tare da baban, ya zauna a three sitter itama Hajiya Yayah ta zauna gefen sa.

Murya a dishe saboda kukan da na sha na matsa gaban Baba ina gaida shi, ya dago ya tsare ni da ido na lokaci me ɗan tsayi kafin ya kau da kan sa ya amsa.
Duk da gwiwa ta ta fara sanyi amma dai ban sare ba, na ja gefe nayi lamo kamar wata marainiya, su Ya ma suka gaida shi ya amsa musu cikin fara'a musamman Sa'adah, a kuma lokacin ne naji a raina tabbas adalcin da nake nema ba zan samu ba.

Baba bayan ƴar sa ze bi, daga yadda ya amsa min gaisuwa da yadda ya amsa tata na gane hakan, se zuciya ta ta sake karyewa, amma dai na jure.

Gyaran murya Baba yayi ya tambayi Ya Masdooq me ke faruwa a gidan namu? Aunty Hauwa ta kira shi hankali tashe wai Sa'adah ta kira ta tana kuka tama kasa sanar da ita me ke faruwa.

Ya ya gyara zama ya dukar da kai kasa kafin ya sanar da iya abinda ya sani, wato ya dawo daga aiki ya tarar idanun Sa'adah jajir alamun ta sha kuka, ga kuma shatin hannu a kumatun ta na mari, ko da ya tambaye ta me ya faru se ta sake kecewa da kuka, yayi iya yin sa taki sanar da shi komai se kuka da take yi.

Daga karshe dai se da ya mata tsawa ya rufe ta da fada sannan cikin shasshekar kuka ta sanar da shi abinda ya faru, ya so kuma tun a daren ya dau mataki sedai ta hana shi da fadin ita ai ta hakura kar yayi mata magana, kawai dai abin yayi mata ciwo ace kanwar bayan ta da ta bawa kusan shekaru hudu zuwa biyar ce ta mare ta.

Be sauraren ta ba ya sake neman fita, se ta tare shi da fadin to shikenan ta yadda ya dau mataki amma dan Allah ya bari zuwa safe, yanzu dare yayi.

Ko da safiya tayi shine ya haɗa mu gaba daya dan jin me ya faru amma se na fara masa karya

wai Sa'adah ta zagi Mama na ne shiyasa na mare ta, haka kuma again a gaban sa dan rashin kunya bayan Sa'adah ta sake sanar da shi yadda abin ya faru na karya ta ta na kuma kira ta da munafuka, lamarin da ya sa ya gaza hakuri ya mare ni saboda takamin burki kan tsagerancin da nake neman kawo wa gare shi".

Kaina na sunkuye ina sauraren abinda yake fada har gama, ta gefen ido na ga sanda Baba ya gyada kai kana ya juya ga Sa'adah ya tambaye ta me ya faru.

Ban yi zaton dama ta fadi gaskiya ba a nan din ma dan na san ba zata karya ta kan ta a gaban mijin ta ba, beside daga ganin yadda komai ya faru an shirya shi ne, zan iya cewa Sa'adah ta shirya abin ta da mahaifiyar ta, motive din su akan haka ne ban sani ba, nayi zaton Baba ze saurara daga gare ni kamar yadda ya saurara daga kowa dan har na nutsar da kaina ta yadda zan yi bayani a nutse, sedai kawai se jin saukar hukuncin Baba nayi daga sama

"Lallai NU'AIMAH kin kawo rashin kunya da rashin mutunci tun da har kika iya daga hannu kika mari Sa'adatu, wadda na san ko da bata girme miki a aure ba ta baki shekaru biyar zuwa shida a rayuwa, kin ga kuwa in har kina da hankali da nutsuwa tare da sanin ya kamata be kamata ki ko zage ta ba balle a kai ga duka, dan haka kai Masdooq kayi min daidai na hukunta ta da kayi, ina fatan hakan ya zama karo na karshe da zaki kuma kwatanta hakan ga wani ma a waje ba ita ba, haka kuma zaki bata hakuri tare da alkawarin ba zaki sake ba dan tabbatar da zaman lafiya a tsakanin ku.

Ke kuma Sa'adatu kiyi hakuri da abinda ya faru, zata baki hakuri kuma muma mun ari baki mun baki, ina fatan ki yafe mata ki kuma cigaba da kallon ta matsayin kanwar ki, ki kuma cigaba da kokari wajen kun zauna lafiya ko dan saboda kwanciyar hankalin ku da na mijin ku. And daga yau duk abinda ya faru ba na san ki sake kira ki sanar da Hauwa, ni din nan mahaifin ki ne haka ma Hajiya mahaifiyar ki ce, duk abinda ya faru ki kira ki sanar da mu zamu duba muyi hukuncin da ya dace insha Allah.

Kai kuma Alhaji...".

Baba ya fada referring to Ya Masdooq dan haka yake kiran sa,

"Ka cigaba da kokari wajen ganin ka yi adalci tsakanin matan ka, kar ka yadda ka wulakanta uwargidan ka saboda amarya, haka kar ka yadda ka take hakkin amarya saboda uwargida, kowacce da matsayin ta haka kuma kowacce na amsa sunan matar ka ne, duk wadda ka cuta ko ka zalunta Allah baze bar ka ba, ka zama tsayayyen namiji kuma jajirtacce a gidan ka, ina muku fatan zaman lafiya baki daya.

NU'AIMAH ki bawa yar uwar ki hakuri yanzu dan komai ya wuce ".

Tun da Baba ya fara magana se yanzu na dago na sauke dubana kan sa, idanuna sun yi jajir har fiye da yadda yayi Dady da na yi kuka, na zuba wa Baba ido yayinda shima yake kallo na

kafin ya kautar da idon sa daga kaina

"Ki bawa Sa'adatu hakuri".

Baba ya maimaita min umarnin sa, na juya na kalli Sa'adah da ta sunkuyar da kai, ban kuma kallon kowa ba daga ita na maida duba na ga Baba

"Baba zagin Mama na tayi, wallahi ba gaskiya ta faɗa maka ba".

Hade rai Baba yayi ya zuba min ido, a lokacin ban san me yasa na cigaba da kallon sa batare da na sauke nawa idon ba, ina jin hakan baya rasa nasaba da raguwar girma da darajar da nake ganin Baba da su a ido na sanadin hukuncin sa da ya nuna ƙarara ya dauki bayan ƴar sa

"Nace ki bata hakuri".

"Baba ta kira ni mara tarbiyya, ta zagi Mama na tace bata da tarbiyya shiyasa ta kasa bani, ta aibata iyaye na Baba, shin ita bata da hukunci kan wannan laifin nata?".

Mikewa Baba yayi kamar a fusace sedai ƙarara fuskar sa ta nuna ɓacin rai

"Ko da ace ta fadi hakan ai ba karya tayi ba NU'AIMAH, ko yanzu kin nuna baki da tarbiyyar, a matsayi na na mahaifi ga mijin ki na baki umarni amma kika ki yi, se ma kike neman yi min rashin kunya, dan haka ba zan yi mamaki ba dan ance kin yi wa yar uwar ki rashin kunya har da mari tun da gashi nima kin gwada min.
Sam baki dace da dana ba, dan shi ɗin me biyayya ne, daya daga cikin misalin biyayyar sa shine karbar auren ki duk da kuwa baya so, amma saboda mahaifiyar sa ta isa da shi be ce mata a'a ba, nima da nayi adawa da auren ya bani hakuri, duk ba dan komai ba se dan farin cikin mahaifiyar sa gata nan, yanzu kam na tabbatar dole iyayen ki su tsane ki dan halin ki sam ba shi da kyau, ina miki fatan shiriya, Alaji kwashi matan ka ku tafi". Yana fada ya haye sama

Tun da Baba Alaji ya fara magana na tsare bakin sa zuwa fuskar sa da kallo emotionless, fuska ta blank babu wani reaction a kai, daga karshe da ya gama jawabin sa nayi wani busasshen murmushi da na san sam be yi wa fuska ta kyau ba, kana na dubi Hajiya Yayah

"A shekarun baya can Baba ya so ni kamar Aunty Luba, ya nuna min kauna fiye da wadda ma ya nuna wa Aunty Luba a zahiri, ina son zuwa gidan nan na zauna saboda Baba da nake jin kaunar sa lokacin fiye da ke da ke yar uwar mahaifiya ta, saboda ke kina min fada, shi kuma lallaba ni yake ya min nasiha, ya siya min duk abinda nake so, wani sa'in kafin nacewa Babana yayi min abu na kira Baba na fada masa, so da yawa saboda shi nake kwaso kaya na taho Hutu nan, kuma ina jin dadin zaman nan din musamman da Sallah in ya dauki hukun kasuwa saboda bade bari kiyi min fada ba, kuma ze kai ni yawo ya siya min kayan wasa da na kwadayi.

Wannan yasa har girma na har kawo dazu nake kallon Baba as mahaifi na ba wai mijin yayar

mahaifiya ta ba, haka kuma ba wai mahaifin Ya Masdooq ba, ba kuma wan mahaifiyar Sa'adah ba, shiyasa kuma nake da kwarin gwiwar amsa kiran sa saboda sa ran zan samu adalci daga mahaifi na, sedai a yanzu a yanzu....".

Na hadiyi miyau wanda kalace ne babu wani ishasshe a baki na

"Hajiya Yayah, Baba ya nuna min shi ba mahaifi na bane, matsayin da na ba shi baze iya rikewa ba, Baba ya nuna min wariyar launin fata, ya zabi ƴar sa a kaina, ya nuna min ita jinin sa ce, ni kuma jinin matar sa ce, Baba be gwada min adalci ba, ya saurari dan sa da ƴar sa, ni kuma bare ya yanke min hukunci da nasu side of story din, nayi magana kuma yace ban da tarbiyya, ban sani ba ko a wajen ki ma ni mara tarbiyya ce, sedai ko da hakan ne a ran ki ba zan ji haushin ki ba, dan na dawo daga rakiyar fifita bare a kan jini na, ke ko bq komai shakikiyar mahaifiya ta ce, duk lalacewa ta dole a alakanta ni da ke, Nagode Nagode sosai da kaunar ki gare ni, ta fili da ta boye, amma dan Allah ina son ki saka Ya Masdooq ya sake ni kamar yadda kika saka ya karbi aure na batare da yana so ba.

A da nayi tunanin zan yi hakuri da duk wani obstacle daze zo ta cikin auren nan na jure na zauna, ko dan ke da iyaye na, amma a yanzu da Baba ya fadi ban dace da dan sa ba se na ga haka ne, ni da shi kamar ruwa da wuta ne, shi me biyayya ne ni mara jin magana ce, shi ne tarbiyya ne ni bani da ita, shi.........".

Tsawar da Hajiya Yayah ta daka ne yasa na kalli wajen da yake tsaye ga kuma sunan sa da ta ambata

"Kul, kul wallahi, kul din ka  Masdooq, ka sake hannun ka ya sauka a jikin ta wallahi se na bata maka yadda baka taba zato ba, shashasha kawai".

Na kalle shi hannun sa tsaye acikin iska daya daga ze mare ni, na girgiza kai

"Kar ki mare shi saboda ni Yayah, da izinin ubangiji ba zan kuma zama sanadin ɓacin rai ko kukan wani ba".

Bata ce komai ba t a karaso gaba na ta ja ni jikin ta ta rungume, lumshe ido nayi zuciya ta na bugawa, sedai ban ji komai ba na sauki a raina, maybe da kafin yanzu ne, may be da ba'a kai wannan bigiren ba, se dai a yanzu ina jin kamar lokaci ya riga ya kure!!!

Ko da muka koma gida ban daga kai na dubi kowa ba, kaina a kasa na shige daki, na zauna kan kujera dafe da kai na da nake jin kamar ze fashe, gaba daya ya cushe ya cunkushe da tunani, na rasa ma daya da zan yi....................✍.

Ya kuka ga hukuncin Baba? Shin akwai son rai da rashin adalci kamar yadda Aimah ta fada, ko

kuwa dai itace bata fahimci lamarin ba????

Vote
Comment
Share fisabilillah.

Ouummey 📚✍.

Ouummey 011 [ 24/06/2024 7:42pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍ Oummey
Free book!!!

Ouummey 011

Page 1️⃣1️⃣

________________Se kawai na kwanta ringine ina kallon ceiling din dakin, zuciya ta na kuna idanu na sun yi jajir sedai alkawari nayi ba zan kuma kuka akan komai da ya shafi auren nan ba, ba zan kuma kuka akan komai ma da ya shafi rayuwa ta ba, na sallama kowa kamar yadda suka sallama ni, ba ni da kowa, shi kuwa Ya Masdooq na aje shi a can wani gefe na zuciya ta, na bashi matsayin wanda ya bani wajen zama yake kuma taimaka min da abinci, ban da haka babu komai, babu komai, babu komai!!!, Na maimaita wa kaina.

Tun daga ranar ban kuma fita falo ba, komai na rayuwa ta a dakin nan nake yin sa, bana komai ban da gyaran daki, wanka sallah da cin dan abincin da aka sammin, tunani kuwa yace

Bismillah.

Duk na zauna bani da abin yi se tunani, tun daga farkon rayuwa ta da nayi wayo har zuwa yanzu da komai ya lalace.

Sa'adah kuwa baya fasa min izayar abinci ba, yanzu da ta karo sabon salo ma se ta hanani abincin in ta ga dama, ta shigo ta kare min rashin mutunci ita kadai, wataran ma har da gayyar kawayen ta ko dangin baban ta, ban taba daga kai na kalle su ba, kar kari suyi su gama su gaji su fita.

A haka aka dawo da princess daga gidan Aunty Luba, shima daga kwancen da nake naji dawowar ta tare da babanta, suna ta farin ciki abin su, a very happy family, wannan yasa na sake killace kai na kar na bata musu farin cikin nasu tun da ni ai annoba ce.

Sannu a hankali lokaci na tafiya rama ta na karuwa, damuwa da tashin hankali sun min yawa, ga kuma horon yunwa agefe, na rame sosai ta yadda kayana se an saka mu mu biyu a ciki, fuska ta duk tayi zuru zuru, babu hadin wannan sabuwar Aimah din da tsohuwa ban da na suna.

Kafa ta da na fadi a kan ta tun kwanaki na min ciwo sa'i da lokaci, ya zamana ma duk sanda zan yi sujjud se da dabara, ba wanda ya san halin da nake ciki haka nima ban sanar da kowa ba, to wa zan sanarwar Bayan bani da kowa?!.

Wannan yasa na cigaba da gasata da ruwan zafi kawai, se kuma ta rage zafi amma kamar kashin gwiwar tawa ya rabu biyu, ba kamar da da yake daya ba, aka zo ma ta daina zafin gaba daya, se in na bige ko na taka kafar da karfi.

Wata uku bayan incident din na shiga fama da wani irin ciwon kirji me azabar wahalarwa, in ya tashi ji nake kamar ba zan rayu ba, ga gefen ciki na da ban isa na mike tsaye ba se in ji kamar an daure min gefen wajen.

Tun ina kokarin kautar da kai har na hakura na mika wuya cewa ulcer ce ta kama ni, ulcern kuma irin me karfin nan, sedai yanzu ma ban yi kokarin sanar da wani ba, na cigaba da rayuwa a haka da dadi ba dadi, da lafiya da babu, ina dai yin addu'a a ruwa in sha.

******

Kamar kullum yau ma haka ta tashi a firgice, jikin ta duk ya jike da zufa, se zare ido take yi kamar zata gan ta a gaban ta.

A hankali ta kai hannu ta gyara gashin ta da ya barbaje sanadin kwanciyar da tayi, ta daure gashin waje guda kana ta aje hannun ta a sanyayen.

Sati biyar kenan da fara wannan mafarkin nata, safe, rana da dare in dai zata kwanta se tayi mafarkin ta , cikin different conditions, se dai ko daya babu yanayi me dadi ko kyau, musamman ma na yau, shiyas aya firgita matuka.

Tana cikin ran ta kullum, a ko da yaushe tunanin ta na kawo mata farmaki, sedai tana korar shi da karfi dan bata san duk wani abu da ze tuna mata da ita, sedai bata san me yasa ba yanzu take wannan mafarkin da ita, ta sani bata sa damuwar ta a ranta ba balle tace, to ko dai tana cikin wani hali ne a can din?.

Se kuma da sauri ta girgiza kan ta tana Kore tunanin, ta fi kowa sanin ina ne take, guri ne da ta tabbatar za'a kula da ita irin kular ma da ita fushi baze bari tayi mata ba, ta tabbatar ba ze cutar da ita ba ko da kuwa ba ze karbe ta da wuri ba, dan haka batun tana cikin wani hali ma be taso ba.

Se ta mike da kyar dan jikin ta ya mata nauyi, ta shiga toilet tayi alwala ta fito ta zura hijab ta tada Sallah.

Duk cikin sujjadar ta bata saka ko da mutum daya ba cikin yaran ta de ita kadai, addu'a ce ta shiga yi mata irin ta uwa ga yar ta, daga karshe kuma ta fashe da kuka.

A haka ta idar da sallar ta naɗe sallayar ta aje ta koma gefen gado ta zauna, zuciyar ta duk babu dadi, Allah ne shaida tana matukar so da kaunar tilon ƴar ta, kauna mara algus wadda ita ta jagoranci tabarbarewar rayuwar ta wanda ita har yanzu bata gane hakan ba.

A ganin ta dukkan wani so da kauna tare da gatan da duk wani da ze samu a funiya ta bata, ta mata komai Hajiya mahaifinta da yan uwan ta, amma a karshe se ya zabi bata su a idon duniya, ta bijire musu akan wani da namiji, ta zabi ɓacin ran su kan farin cikin ta.

Wannan shine abinda har yau har gobe ke yi mata katanga da yafewa yar ta daya da Allah ya bata, yasa take kuma nuna halin ko in kula gare ta, tare da bayyana tsananin fushi a gaban ta, yayinda a badini zuciyar ta cike take da dimbin so, kauna tare da tausayi kan yar ta.

Ta dade a zaune kafin ta koma ta kwanta, tana ayyana lallai gida zara tafi, jiyyar ta isa haka tun da ta warke, ba zata cigaba da zama a gidan ɗa ba tana takurawa matar sa, duk da bata nuna hakan ba saboda yarinya ce ta gari amma ba zata kure su ba.

A haka bacci ya sake yin gaba da ita, bakin ya motsa a hankali da sunan kaunar ta

"Aimahhh".

**********

Ina zaune kasan gado kamar yadda na saba, na jingina kaina jikin kujera na hade kaina da

Giwa kamar yadda ya zam min dabi'a, karfe sha daya na dare ne lokacin amma idanu na kamas babu alaman bacci ko digo, haka nake fama tun watan da ya wuce, se in nemi bacci in rasa se dare yayi tafi wajejen asuba, da yawan lokuta se ma nayi sallar asuba nake samun baccin, shima karfe takwas kuma ya kare, wannan yasa kullum cikin ciwon kai nake, tun ina yi kadan kadan har ya zama persistent dan yanzu baya ma tafiya akasin da da zan yi ya tafi.

Motsin kofa da naji be sa na dago ba dan na san shi ne, har yanzu be dena zuwa daki na ya kwana a falo ba in ranar kwana ne, sedai tun wancan incident din be kuma tako bedroom dina ba, nima kuma ban taba fita ba in yana falon.

Duk da abin mamaki ne da daure kai jin shi ya turo kofar bedroom dina ya shigo amma ban daga kai daga yadda nake ba balle na kalle shi, ina jin tsayuwar shi da ban san me yake kallo ba ko me yazo nema, dama dai dakin babu haske dan na kashe, tuntuni na maida dakin dakin duhu dan na manta rabon da na kunna haske ma wa bedroom din.

Hasken da ya mamaye dakin ya sa na sake curewa waje ɗaya, ko da ya gama ganin in da nake se ya kashe hasken ya tako gaba na.

Ban aune ba se ji nayi ya dauke ni gaba daya ya kwantar kan bed, kan in ma yi tunanin me ze faru na ji shi a sama na, haka kuma be bani wata dama ba ya shiga gudanar da abinda ya kawo shi gare ni.

Ko da na fahimci niyyar sa ban yi masa musu ba balle nayi tirjiya, na cigaba da kwanciya kamar yadda ya shimfide ni, babu wani tausasawa balle nuna kauna ya sauke nauyin sa a ciki na, yana samun nutsu kuma ya tsallake ni ya fita daga dakin yana jan tsaki.

Na dade a yadda ya bar ni batare da na iya motsawa ba saboda yadda zuciya ta ta kara nauyi a kirji na, har nake jin kamar zata faso ne ta fado, seda kyar na iya daga wa zaune, sannan a hankali na dauko daga gadon, kafa ta me ciwo ta famu, jikina yayi nauyi na wahala, haka kuma ina jin radadi a wajen dan this is my second time, a daddafe na kai kaina toilet na tara ruwan zafi na shiga, na yi ruwa uku sannan na ji dafi na hada sabo na shiga tsoma towel ina danna kafata, har na ji itama zafin ta ya ragu sannan nayi wanka na tsarki da normal na fita.

Dayan bedsheet din na saka na cire wannan na aje shi gefe, na kwanta bayan na saka kaya, nan da nan se zazzaɓi me karfi, jikina ya shiga rawa sosai, na tashi na watso duk kayana zuwa kan bed na rufa dasu.

A haka aka kira asuba na tashi na yi ba dawo na sake kwanciya, na ki bawa kaina damar yin tunani game da abinda ya faru dan a yanzu haka ma nauyin da zuciya ta tayi ji nake kamar an dauko katon dutse ne an dora min a kirji na, ba na san kara yin wani tunanin balle nauyin ya karu, in haka ya faru ina jin kirji na ballewa ze yi zuciyar ta fito fili.

Washegari a gado na wuni, kaina na mugun ciwo dan baccin ma yau karfe shida ya gudu, ji

nake kamar kan ze fadi, na dafe shi da duka hannuwa na biyu ina kiran sunan Allah, idanu na sun yi jajir na azaba, haka na cigaba da fama har wani daren.

Kwana biyar nayi ina fama cikin halin ciwo, ji nake kamar na cire kan na jefar, addu'a duk wadda tazo baki na yi nake, har se da aka kwana biyar din nan sannan na sami kai na.

Mu ka cigaba da cuda rayuwa, ni dai gani nan ne kawai sunan ina da rai, amma ba zan iya nuna abu daya nace ga shi na jin dadi ba a rayuwa ta, farin ciki kuwa tuni muka yi hannun riga da shi, ina rayuwa ne kawai na yi sallah an ci abinci na kuma yi tunanin, wanda yawan tunanin da nake da kuma damuwar dake dankare a raina yaa haifar min da mummunan ciwon depression.

Ba se wani ya fada min ina da shi ba, da kai na na gane ina da shi, bana iya rayuwa a waje ne haske se cikin duhu, bana san jin muryar kowa a kusa da ni, na fi gane rayuwa ni kadai, se in ringa Jin kamar ana min magana har ma na bayar da amsa kafin na farga babu kowa a tare dani, ni kadai se in dinga hira da maganganu da kai na, ga kuma se in dinga ganin abun da be faru ba as ya faru.

Ranar da na gama gane ina tattare da depression ne ranar da na koka kamar raina ze fita, bayan tsayin lokaci na bawa kaina damar zubar da hawaye, na fahimci rashin kuka na na cikin abinda ke kara min nauyin zuciya dan haka na saki rai nayi kuka na sosai, wanda ba laifi na dan ji saukin nauyin da zuciya ta tayi min.

Ko da na gama kukan addu'a na daga hannu nake kokarin yi, sedai bayan Allah kai ne Allah, Allah ka iya min kayi min, Allah .... Allah...., Na kasa fadar komai se kuka da sheasheka, ajiyar zuciya kuwa in nayi zafin ta nake ji cikin kirji na, numfashi in Ina yi se na ji kamar kirji na na budewa ne ya kuma koma ya hade.

Allah ya sani, ina cikin tsananin ciwoooooo............✍️.

Jama'a a kawo wa Aimah dauki😭😭😭😭😭, innalillahi wa inna ilaihi rajiun 😭😭😭😭😭😭😭.

#team_sa'adah
#team_masdooq
#team_Aimah
#destiny
#oummey

Vote
Comment
Share fisabilillah.

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 012  [ 25/06/2024 6:50pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Oummey
Free book!!!

Ouummey 012

Page 1️⃣2️⃣

____________________Irin azabar da nake ji ya tabbatar min da kyar in ba rayuwa tace ta zo karshe ba, ga mamaki na maimakon naji firgici se naji har zuciya ta ina son mutuwar, gwara na mutu ko na huta da wannan azabar rayuwar da nake ciki, gwara na mutu kila rabo na na kiyama ne ba duniya ba, fatana kawai Allah ya sa na cika da imani.

Yin wannan tunanin yasa duk zafi da radadin da nake ji ban kira wayyo ba, ambaton Allah da kalmar shahada ne kan harshe na, a yunkuri na na in na tashi mutuwa na dace da rahmar Allah.

Haka na kwana cikin wannan ciwo da azabar, na wayi gari cikin sa na kuma wuni kana na sake kwana, lokacin kuwa tuni na fara ficewa daga hayyaci na, dan idanuna na ma bana iya budewa, numfashi na ma baya suka ciki na, daga can saman kirji naa yake tsayawa.

Da sanyin asubar washegari gaba daya nayi loosing, tun ina kokarin fisgo numfashin har hakan

ya gagara ni nayi passing out!.

*********

Ba ya san shiga hakki haka kuma yana kokarin kiyayewa da wanzar da adalci tsakanin su, shiyasa rannan da yake a matse ba ze iya hakurin jure har kwana ɗaya ba kafin yaje ga Sa'adah, ya kau da komai ya rarrashi zuciyar sa yaje gare ta, sedai yayi mamakin samun ya cikin duhu dan basa shiri ko kadan, ko a da da kyar yayi yaki da ita kan kwana cikin haske kafin ta daina, be sha madarar mamaki ba se da ya kunna fitila ya same ta manure a gado, ba hakan ne ya bashi mamaki ba dan may be taji shigowar sa ne yasa ta makure, mamakin na irin ramar da ya gani a jikin ta ne.

Rama me asalini muni da rashin kyau, gaba daya ta canja kamar ba Aimah ba ta koma wata a ba can, a lokacin yana cikin gigicewar matsuwar da yayi, dan haka ya ture komai yayi abinda ya kawo shi.

Duk da be bita a hankali ba, haka babu wani lamari me nuna shauki balle motsa ta amma ba hakan ya sa ya kasa gamsuwa ba, 100% ya ji shi zam zam, ko da ya gama ya dago dan taimaka mata ta gyara jikin ta se kawai incident din wancan lokacin ya fado masa.

Baze taba manta wannan ranar ba dan tana cikin ranakun farin ciki na rayuwar sa, duk kuwa da cewa ba da san ranta komai ya faru ba, haka kuma akasin yanzu lokacin she fought him ba hakan ya hana shi enjoying moment din ba.

Base manta yadda ya dinga lallashin ta da kalamai masu nuna tsantsar soyayyar ta ba gare shi amma ta sa hannu ta tankwabe, instead ma se ta shiga kira masa sunan wani katon gardi akan gadon auren sa, me ya kai wannan takaici da ɓacin rai, ace ka kasance da matar ka ta sunna amma ta na kukan da ta san haka ze faru da ta bawa wani kanta a waje dan kar ka samu abinda yake rightfully yours? Addini ya mallaka maka iyaye suka shaida?, Babu!.

Awajen sa da ma wajen duk sauran maza kamar sa masu kishin abinda suke so babu abinda ya kai wannan ɓacin rai, takaici, bakin ciki da tashin hankali.

Gama wannan tunanin gaba daya se ran sa ya ɓaci, zuciyar sa ta dugunzuma, ji yake kamar lokacin ne abin ke faruwa, wannan yasa ya tsallake ya bar ta a wajen bayan ya ja dogon tsaki.

Sedai ko bayan wasu kwanaki ramar da tayi na fado masa lokaci zuwa lokaci, yana jin kamar ya damu da hakan, har wani bangaren na zuciyar sa na jin haushin kan sa da kan sa na damuwa da wadda bata damu da shi ba.

Karfi da yaji ya saka kwanji ya kori tunani da damuwa kan ramar ta, ya maida kan sa very busy dan ma kar ya tuna ta, yana dawowa gida kuma Sa'adah na jiran sa da tarin salo salo na kaunar ta, wannan ya taimaka kwarai wajen mantar da shi halin da take ciki.

Yau ma girkin ta ne, haka kuma baya jin sa daidai, duk yadda yaso ya daure kuma ya kasa, hakan ya sa ya aje pen din da yake rubutu ya tashi, suit din sa da ya cire ya dauka a hannun sa ya fita daga office din, ko kula tambayar da secretary din sa ke masa na ko lafiya be yi ba, dan be saba tashi a lokaci irin haka ba, shiyasa secretary din ya damu yake tambayar lafiya, amma Masdooq be iya ya amsa masa ba, se fadi da yake a rufe masa office.

A gurguje ya sauka kasa zuwa wajen motar sa, ya shiga tare da ta da ta ya dauki hanyar gida, yana tafe yake duba lokaci, 2:13pm, ya dauke ido daga kan wrist din sa ya maida kan titi.

Cikin ikon Allah ya karaso gida lafiya, ya yi parking motar sa tare da amsawar gate man Barka da dawowar da yake masa ya shige ciki a gaggauce.

Wanka ya fara zuwa bedroom din sa yayi, ya saka three quarter kadai without riga ya fito tare da nufar dakin Aimah.

Be damu da shiru na rashin motsin da ya ji gidan yayi ba dan Sa'adah ta fada masa zata bikin yar cousin din babanta, ita kuma dama ba fitowa take yi ba, hindatu kuma an koma School ita da princess.

Hannu yasa ya Murda kofar dakin ya shiga da sallama ciki ciki kamar yadda ya saba, ya hade rai kamar ba shi ne fuskar sa ke a sake ba yanzu, be jira ba ya karasa kofar bedroom din itama ya bude ya shiga.

Sanin inda switch yake yasa yayi an direct tare da kunnnawa haske ya wadaci ko ina.

Kan dankwalin ta ya ganta kwance, sunaye cikin hijab din da ya kode saboda wanki kasancewar su biyu kadai gare ta.

Dan tsayawa yayi ya zuba mata ido se kuma ya kashe hasken yayi inda take, kamar rannan yau ma hannu ya kai dan kwantar da ita kan bed, sedai ga dimbin mamakin da ya razana jarumtar sa se ta biyo shi gaba daya alamun babu rai tattare da ita, yayi kasake cikin rashin yarda da abinda yaji, zuciyar sa na dukan uku uku ya daga ta gaba daya se kuwa tayi yaraf a hannun sa.

Cikin tsananin tashin hankali da dimuwa ya kwantar da ita a gado ya tafi ya kunna fitila, ya dawo da sauri jikin sa na bari ya hawo gadon gaba daya ya jawo ta jikin sa ya shiga bubbuga ta yana kiran sunan ta.

"Aimahhh, ke AIMAH, NU'AIMAH".

Duk irin kiran da yake mata babu alamun zata tashi, gaba daya ya rude ya rasa ma me ya kamata yayi, se kuma kamar an tuna masa yayi toilet da gudu ya debo ruwa , tsabar rudewa a

hannu na ya debo ruwan, ya taho ya shafa mata shiru, ya koma da sauri ya debo a cup da ya gani a wajen ya dawo ya shiga shafa mata, amma duka ta ki tashi, se kawai ya juye mata gaba daya, amma ga mamakin sa nan ma shiru.

Nan fa hankalin sa yayi ainahin tashi, zuciyar sa kuwa bugun da take ya zarce ka'ida, ya tasa ta gaba ya ma rasa me ze yi, idanun sa sukai jajir kamar an zuba jini.

Tunani yake ta ina ze fara sanar da rasuwar ta wa iyayen ta, ga kuma Hajiya Yayah, in aka cire su shi kan sa he's heartbroken seeing her lying, be san har yanzu akwai raguwar soyayyar Aimah a ran sa ba se yanzu.

Be ankara ba ya ji wani irin kukan tashin hankali ya kwace masa, ba wai kuka yake da sauti ba, a'a tsagwaron hawaye ne masu matukar kuna da zafi.

Kusan mintin sa ashirin a zaune a wajen cikin tunani, se kuwa sunan asibiti ya fado masa, duk da wata zuciyar na fada masa ta mutu ganin yadda yayi ta zuba mata ruwa amma taki farfadowa sedai mafi rinjaye na zuciyar sanar da shi yake bata mutu ba, da ran ta, ba zata mutu ta bar shi ba, ba zata sake tafiya ta kyale shi ba, dole zata rayu, ko ba dan kowa ba ko dan shi, dan haka da sauri ya tashi zuwa bedroom din sa ya zura jallabiya.

Saboda tsabar dimauta a baibai ya saka rigar, ya wuce zuwa dakin ta ya sunkuce ta gaba daya, dama ta rame  sosai ba wani nauyin azo a gani ne da ita ba, sauƙin abin ma da hijab a jikin ta da haka ze fita da ita batare da ya lura ba.

A mota ya sata, seat din baya, ya shiga seat din gaba ya tada motar ya fice da gudu bayan gateman ya bude masa, gaba daya hankalin sa baya kan titin da yake tuki, yana tafe yana waiwayo wa ganin ko ta farka, a haka Allah ya kawo su nearby wata private hospital ma kyau, tun daga nesa yake sakin horn, gateman din hospital din dake ya gane emergency ne tuni ya wangale masa gate din, yana zuwa ya shige, ko gama parking me kyau be yi ba ya fita ya buɗe bayan motar tare da dauko ta ya yi cikin hospital din yana kwala kiran nurses.

A guje suka kawo gado aka dora ta tare da turawa, emergency unit suka yi da ita jim kadan likita yazo ya shige.

Tsayin awanni suka yi a dakin kan Aimah, a waje kuwa suka bar Masdooq cikin tashin hankali da zulumi, se kai da kawo yake yi cikin damuwa idanun sa kuwa ba kyan gani, gaba daya jikin sa rawa yake yi haka zuciyar sa wani abnormal bugu take yi, ya sani alama ne na ciwon sa ya motsa se dai ba hakan ne a gaban sa ba, farfafdowar ta ne kawai ze sa hankalin sa ya kwanta, har nutsuwar da ya rasa ta dawo gare shi.

Awa uku doctors din suka yi a kan ta kana suka fito, su uku ne, da na farko da ya fara shiga se wasu mace da namiji da suka yi joining din sa daga baya, se kuma nurses.

Babban ne ya kalli Masdooq da ya taho gare su da sauri, wani kallo ya masa batare da ya amsa tambayar da yake masa ta ya jikin ta ba, ya jefo masa tasa tambayar

"Her brother or husband?".

"Both".

Ya amsa har yana sarkewa dan sauri, ganin kallon da likitan ke masa ya sa ya kara da fadin

"She's my cousin and my wife".

"Follow me".

Likitan yace yana juya wa ya shiga tafiya, be yi kasa a gwiwa ba ya rufa masa baya cikin taraddadin me ze ji, tashin hankalin bata farfaɗo bane ya danne mamakin wane irin rashin lafiya ne tayi haka har ya kai ta ga rasa numfashin ya, yanzu kuwa ze so ji.

Stepping in yayi cikin office din after the doctor, ya ja kujerar gaban table din ya zauna shi kuma likitan ya zare labcoat din da ke jikin sa ya sakale kana ya shiga toilet, tsayin mintuna sannan ya fito yana goge hannun sa da wani towel kana ya maida fuskar sa itama ya goge, sannan ya zauna kan kujerar sa yana duban Masdooq.

Se da ya gama kare masa kallo lamarin da yasa gaban Masdooq cigaba da duka haka kuma hakurin sa ya fara karewa, he's loosing it ga wannan wild behavior din na likitan, ya ze sa shi gaba yana kallo bayan yasan he's eager to know abinda ke damun matar sa, irin as if abin ma be dame shi ba.

Yana shirin yin magana dan har ya hade rai se likitan ya riga shi bayan ya sauke ajiyar zuciya

"Mr Masdooq".

Kallon shi kawai ya cigaba da yi batare da ya amsa ba, likitan ya cigaba

"Daga ganin ka da irin shigar jikin ka baka yi kama da wanda talauci yayi wa kaka gida, theb how comes matar ka ta kamu da irin wannan ciwon? And very severe and critical ma irin haka?".

"Please Dr go straight to the point Dan am loosing my patience, me yake damun matata?".

"Well, matar ka na fama da cutar ulcer, the most severe form dan she's in a very critical condition".

Tsammmm yayi yana duban likitan without blinking his eyes, he's dumbfounded jin wai a gidan

shi ne a ka samu ulcer, and a yadda likitan yace severe and critical, se yaji gaba daya kan sa ya shafe komai ya nace masa.

"Likita me ya jawo ulcern?".

Wani kallon kar ka raina min hankali likitan yayi masa,

"Mr man, da ganin ka dai an ga me ilimi, and batun me ke jawo ulcer hatta layman yasan basic abinda ke kawo ta, then why are you pretending not to know?".

"Nooo, na sani, kawai dai na rasa me zance ne, am surprised a gidana aka samu ulcer irin wannan me karfin, shiyasa na tambaya in akwai major cause din ta other than yunwa".

"Kana nufin kace baka san sheve been starved for 2 days ba?".

"Wallahi Dr I knew nothing about it ".

"A binciken mu yanzu haka kwanan ta kusan biyu rabon ta da abinci, and ulcern yaci karfin ta sosai dan har ya fara taba mata kirji, shiyasa take having difficulty in breathing, so zamu rike ta a nan for some time kafin muga ya jikin dan mun daura mata drip kasancewar babu ruwa ajikin ta, haka kuma bata da karfi, in kuma ze samu zamu kara mata jini ko rabin leda ne, in kuma ba halin jinin ba dole ba ne dan zamu dora ta kan medication da ze kara mata jinin sosai, haka kuma dole a kula da cimar ta, ya zama tana cin a very healthy diet, ta yawaita cin hanta, vegetables and fruits da duk abinda aka san will help provide fluid wa jikin ta".

A sanyaye Masdooq ya gyada wa likita kai shi kuma ya dukar da kai yana rubutu kan file din Aimah.................✍️.

Speed recovery our AIMAH 🥺🥺.

#justiceforAimah
#team_Aimah
#team_masdooq
#team_saadah
#destiny
#ouummey

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 013  [ 25/06/2024 6:51pm  ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Oummey
Free book!!!

Ouummey 013

Page 1️⃣3️⃣

_____________________Tun da ya shigo dakin yake bin ta da kallo jikin sa a sanyaye, ya rasa ma me zece, ya rasa tunanin me ze yi, se kawai ya karasa gaban ta ya zauna looking at how helpless she's lying on the bed.

Me ya jawo mata ciwon ulcer, shine kawai abinda yake san ji yanzu, sedai ba shi da wanda ze tambaya, ita da ze tuhuma din kuma gata kwance bata ma san inda kan ta yake ba.

Is it rashin son sa da kaunar sa ya sa a wannan karon kuma ta yanke yiwa kan ta horon yunwa? Ko kuwa me ne ne?

Shi dai ya san gidan sa ba rashin ci ba rashin sha, abinci kan yayi rabi ma ya karo wasu, he has the believe that abinci is the first priority and the first need na dan Adam, so baya wasa da siyan kayan abinci wa gidan sa da gidan iyayen sa, Sometimes har fada Hajiya Yayah ke yi tace abincin su be kare ba ya yi wani abu da kudin, amma no shi yafi san kullum yaji shiru babu wani korafi kan rashin wadatuwar abinci.

And not only food yake kawowa, healthy diet yake providing ma iyalin sa dan kuwa nama se ya kawo kala uku ban da kifi, su kwai, su veggies su fruits duk se ya siya every month, ya kare ko be kare ba be fasa siya.

Amma ace wai tana kwance a gadon asibitin nan ne saboda cutar yunwa, wane irin abin kunya ne hakan gare shi, me mutane zasu kalle shi in suka ji wannan maganar.

Haka ya gama tunanin sa be samu makama ba, a karshe ya barwa kan sa yin bincike dan gano

komai, ko da ya duba wrist watch din sa is ten minutes after 6, se ya tashi ya nufi kofa, har ya bude ya juyo ya kalle ta yana tuno likitan yace se after five hours sannan possibly zata iya farkawa, so se ya fita tare da rufe kofar.

Nurse station yaje ya samo guda daya ya bata kudi kan ta zauna masa da ita kafin yaje gida ya dawo.

Ko da ya koma Sa'adah bata dawo ba, se princess da Hindu, suka gaishe shi princess ta ɗane shi, ya daga ta cikin farin ciki yana mata wasa kamar yadda suka saba, sedai be dade ba ya sauke ta yace ze yi alwala ya fito.

Ko da ya fito hindu na sake mopping floor din falo, ta masa adawa lafiya haka ma princess ya amsa su, har ya kama handle din kofar falo se kuma ya dawo ya zauna kan one sitter, ya kalli princess yace taje dakin sa ta dau phone din sa tayi game.

Se da ta shige sannan ya kalli Hindu dake kwasar kayan gyaran dan barin falon kamar yadda Madam din ta ta umarce ta ta dinga yi duk Masdooq din ya shigo falo, sedai baya kai ga fita ba ya tsayar da ita tare da cewa ta dawo.

Kan carpet ta tsugunna daga opposite him

"I'll ask you, and I want everything daze fito bakin ki ya zama actual truth, not otherwise, in Kuma kika min karya I'll punish you before sending you back to your parents, kin ji me nace?".

Jiki na rawa hindu ta amsa dan tun da take da shi magana bata taɓa hada su ba bayan gaiuwa, shima daga lafiya be kara kallon ya, ga kuma maida ita gida da yake magana, ina zata so komawa gida bayan a nan rayuwar ya dauko hanyar gyaruwa da daukaka ta sanadin ilimin da suke bata batare da duba da ita din wacce ba saboda tsabar karamci.

"Aimah na fitowa ta ci abinci tare da Maman princess ne ko kuwa diba take ta tafi daki?".

"A'a.. a'ah, Aunty ce ke zuba mata ta bani na kai mata, wataran kuma ta kaji mata da kan ta".

Cikin mamakin jin wai Sa'adah ke zuba mata abinci ya dubi hindu sosai

"Okay bata fitowa ta diba da kan ta kenan, ko kuwa ta taba fitowa ne Maman princess ta mata wani abu, ko zagi haka ko makamancin s".

"A'a yallabai, bata fitowa ne gaba daya, dan tafi wata uku bata fito ba ma daga dakin".

Jinjina kai yayi

"Okay, yaya yawan abincin da ake zuba matan?".

Zare ido tayi ta shiga inda inda

"Iyeee, na'am, uhm, ai Anty ke zuba mata ba ni ba".

Zuba mata ido yayi cikin nazari

"Amma kamar naji kin ce ana baki ki kai ko?".

Da sauri baki na rawa tace

"Eh, tana bani".

"Then nace ya zukumin abinda ake bakin, and mind you kin ji me nace kan kiyi min karya".

"Eh, dama dai kadan ne, dan Anty tace wai bata da cin abinci, wataran ma se tace ai ba se an bata ba wai ai tace mata tasha fresh milk ".

"If I get you right, Sa'adah na sawa Aimah abinci kadan, sometimes ma se tace kar a bata tace ta sha fresh milk,bis that what you said?".

Cikin rawar jiki ta gyada kai, yayi tsai yana duban yarinyar, kafin cikin tone din sa da ya fara canjawa saboda ɓacin rai yace ta tashi ta zubo masa zukumin  abincin da ake bawa Aimah.

Da sauri kuwa ta yi kitchen, mintuna kadan ta fito rike da plate din da aka ware dan bawa Aimah abinci, ya karbi abincin ya juya cikin madauakakin mamaki dan kuwa abincin ko princess in taci se ta nemi kari, ya kalli Hindu

"Spoon nawa ne wannan?".

"Serving spoon daya ne da rabi ".

"Karfe nawa da karfe nawa ake bata abincin?".

"Breakfast by ten or minutes before ten, launch kuma after Asr, se dinner after Isha ".

Gaba daya se yaji shi kamar wani mara rai, kawai duban Hindu yake, kafin daga karshe yace ta tashi taje, ta mike da sauri kuwa tayi dakin ta, tana dafe kirji ta dake bugu.

Tun da ta wuce yake zaune wajen rai bace, wato kawoi gashi nan ne amma SA'ADAH ta mai da shi wani wawa a cikin gidan sa, ta mai da shi shashasha tana raina masa hankali, duk yadda take nuna kulawa da kauna ga Aimah ashe na karya ne, yaudara ce kawai da tsabar makirci.

Be manta ba yadda kullum take damun sa kan yayi wa Aimah magana su dinga cin abinci tare, tun yana mata banza har ya tambaye ta shin ta hana ta fitowa ne, tace a'a then yace to kar ta kara samun sa tun da ita ta zabi hakan ba wani ya hana ta ba.

Wai ma tsaya, kenan watannin baya incident din da ya faru ze iya zama Sa'adah karya take Aimah ce me gaskiya?

Da sauri ya girgiza kai, a'a Sa'adah ba zata yi haka ba, ya san ta ya san me zata yi da wanda ba zata yi ba, wannan ma kishi ne ya sa ta aikata haka, kuma ze mata magana.

Se kuma wata zuciyar tace ai yanzu ma ya san ta din amma ta aikata abinda be taba sanin zata iya aikatawa ba, kuma shi ma wancan karan ai lamari ne na kishin tun da Aimah kishiyar ta ce a lokacin, wai tsaya ma, me yasa ta lokacin be saurare ta ba kamar yadda taso, me yasa be yi bincike ba ya zartar da hukunci?

Zuciyar shi ta bashi amsa da yaudarar Sa'adah da kwarewar ta wajen iya displaying innocent face, amma tambayar sa daya a nan ita ce, shin tun da haka Sa'adah take shi ta binne ko kuwa yanzu ne ta canja.

Se yanzu yake jin takaicin rashin CCTV cameras da be sa a gidan ba, ba kuma komai ya hana ba face ganin ai hakan wani nau'i ne na sa ido ga mace, bayan shi ya yarda da tasa then me camera zata dauka masa bayan wanda ya sani, se gashi tun kan aje ko ina Sa'adah prove him wrong, ta tabbatar masa ya yarda da wacce be kamata ya yarda ba, ya mika yarda da amana inda ba'a iya killace su ba.

Da kyar ya iya mikewa zuwa dakin sa, ya yi wanka da ruwan dumi kana yayi alwala yasa riga ya tafi masallaci.

Ana idarwa ko azkhar be zauna yi ba ya dauki car key ya wuce asibiti.

Har lokacin bata farka ba, yayi wa nurse din da ya bari godiya, ta amsa tana fadin in yana bukatar ta ya kira ta tana station din su, ya amsa mata da ka dan yanzu ba shi da strength din bude baki yayi magana, mamakin Sa'adah ya kashe masa duk wani kwarin gwiwar sa, ya kuma saka masa shakku kan ta da halayen ta da yake ihun ya sani.

Yana zaune a ka kira Isha ya tashi ya shiga Masallacin asibitin yayi kana ya dawo ya sake zama, a lokacin ne wayar sa tayi ringing, sunan Sa'adah ya shiga yawo kan screen din, ya kasa dauka se ya zuba wa wayar idanu har kiran ya katse wani ya shigo, dama wayar na a vibration ne dan ya cire sound saboda likita da yace ba'a bukatar duk abinda ze yi disturbing sleep din ta dan bacci suke so tayi ta yadda kwakwalwar ta zata huta haka kuma medication din ze ratsa jikin ta.

Se da ta sake kira a karo na uku sannan ya tashi ya fita daga daki ya amsa kiran tare da

kangawa kan kunnen sa batare da yace komai ba.

"Hubby na dawo baka nan, Hindu tace min ka dawo ka fita ne, hope all is well?".

Ya sani dalilin da yasa ta tambaya dan ta san shi ɗin ba ma'abocin yawo bane, haka daga an idar da Sallar Isha baya kara fita ko ina se kuma gobe.

Dan gyara murya yayi ya saisaita kan shi yace

"Mun je duba wani abokin aikin mu be da lafiya, will be back soon".

"Ayya, Allah ya bashi lafiya amin, okay se ka dawo, bye".

Ciro wayar yayi daga kunnen sa tare da kallon su nan ta ya girgiza kai, ban ze mata maganar ba, ze zuba mata ido ne yaga iya gudun ruwan ta, ya ga iya gejin rashin imanin ta, kafin ya san matakin dauka.

Se after nine Aimah ta farka, a  hankali na shiga bude ido na da naji sun min nauyi na sauke ido kan ceiling dakin wanda ya kasance farin rubber ceiling me kyau babu dison kowace kala, wani irin dadi ya ratsa ni, ba na komai ba se na ganin na mutu, abinda nake ta fata tun shekaru biyar cikin ta shida da suka wuce.

"Alhamdulillah, Allah na gode maka, ya Rabb ka sa na dace da rabo a nan kiyama tun da baka yassare min na duniya ba".

Na fada can kasa, sedai tun da dakin babu hayaniya za'a iya ji na.

Wannan maganar da nayi ce ta jawo hankalin Ya Masdooq har ya gane na farka, da sauri ya matso da kujerar da yake zaune zuwa gaban gadon, ya zuba min ido yana ambata min sannu, wadda ko guda daya tasa ban amsa ba.

Hasalima tunani nake yi me yake a nan, ko shima ya mutu ne bayan na mutu?.

Ganin ya juya zuwa wajen kofa ya fita yasa na maida ido na rufe, a haka na ji an bude kofar an shigo, na ɗan bude ido na kalle su kafin na bude gaba daya, a kan likitan da ya shigo dakin na sauke duba na cikin mamaki.

Ya karaso gaba na ya tsaya tare da sa hannu ya rike nawa ya zare min ruwan da ya kare dan saura kadan, se kuma ya saki ya juyo yan kallo na

"Sannu, sannu mu patient, yanzu fada min ina ne ke Miki ciwo, ko bakya jin sa daidai?".

Yanzu kam kasa rike tambaya ta nayi, na yi ta gaba na na dukan tara tara na amsar da zan

samu

"Wai likita dama ba mutuwa nayi ba?".

Tsai Dr yayi yana kallo na kafin yace

"Me yasa kika yi tunanin kin mutu?".

"Saboda i saw everything na dakin nan fari, kuma ba ƙazanta, kuma na sa rai sosai da mutuwar dan itace abinda nafi so yanzu duk duniya"

Likita ya juya ya dubi Ya Masdooq da ya kasa cewa komai se ji na

"Kar ki sare da rahmar Allah, ita din ta zagaye kowa da komai, rayuwar ki kuma ba ta kare ba jikin allon ƙaddarar ki, dan haka se kin cikashe ranakun da Allah ya tsara miki tuntuni, dan haka tashin ki ba abun mamaki bane".

Gyada kai nayi na maida idanun na rufe, Dr be san yadda raina yake bace bane shiyasa ya zauna karanta min wannan zancen da be ko kai ko ina ba a raina, shi be san wace ni ba balle irin rayuwar da nake gudanarwa, da ya sani da be fadi haka ba.

Likita ya gama duk abinda ze min ya fita ya turo mana sister Ryhan ta taimaka min na wanke baki haka na dan yi wanka sama sama, kakkauran tea ta haɗa min na sha duk da ba sosai ba.

Se kuma bayan na gama sannan na lura da Ya Masdooq dake tsaye yana kallon komai dake faruwa, na maida ido na rufe cikin tunanin yadda aka yi na ganni asibiti, haka kuma waye ya kawo ni asibitin dan na san ba dai shi ba, a yadda ya tsane ni in ya ga zan mutu na tabbatar se ya fi kowa murna da jin dadi.

Ban san tahowar da ba se karasowar sa na gani, ya ja kujera ya zauna gabana, gaba daya se kuma ya rasa me ze ce min, dan haka ya cigaba da zama kawai.......................✍️.

Vote
Comment
Share fisabilillah

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 014  [ 26/06/2024 9:13pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Oummey
Free book!!!

Ouummey 014

Page 1️⃣4️⃣

___________________mun dade a haka kafin kamar wanda aka matsi bakin da yace

"Sannu, ya jikin?".

Kamar ba zan amsa ba dan bana san magana, musamman da Dr ya shaida min ban mutu ba, wanda takaicin hakan ya cika min rai, se kuma na amsa can kasa a hankali idanuna har lokacin a rufe

"Da sauki".

"Allahu yashfeek".

Kin amsawa nayi dan ni ba addu'ar samun lafiya nake so ba, addu'ar mutuwa nake bukata.

Daga haka muka ja baki muka yi shiru, ni idanu a rufe ina fadawa zuciya ta shi ya kawo ni asibitin, dan in ba shi ɗin ba babu me shiga inda nake balle a san halin da nake ciki.

Shi kuma ta bangaren sa ban san me yake tunani ba, tsayin lokaci muna a haka kafin ya mike

"Dare yayi zan je gida, akwai nurse da zata kwana da ke, kina bukatar wani abu ne daga gida in zan taho gobe?".

Girgiza masa kai nayi kaina a kasa, ganin haka ya yi min sai da safe ya juya batare da ya jira amsawa ta ba da ni ma ba amsawar zan yi ba ko ya tsaya.

Be dade da fita ba nurse Ryhan ta shigo, ta min sannu tare da zama tana daddanna waya, sa'i da lokaci kuma tana min hira wanda iyaka ta murmushi, gyada kai ko girgiza wa, daga karshe ma na rufe idanu kamar na yi bacci dan bana san hirar, itama da tai magana daya biyu ta ji shiru se ta juyo, ganin idanu na a rufe se tayi tunanin na yi bacci, dan haka ta gyara zaman ta ta cigaba da chatting din ta.

A hankali baccin gaske yayi gaba da ni, dan alamu sun nuna allurar bacci aka yi a ruwan da aka sa min.

Ban farka ba se biyar na asuba, na juya daya gadon dake gefe in da nurse Ryhan ke kwance, a hankali kuma na yunkura na mike zaune, na dan jima a zaunen se kuma na sauka ina takawa a hankali zuwa toilet.

Fitsari nayi na daura alwala na fita, se kuma na tsaya tunanin me zan saka in yi sallah, gadon da nurse Ryhan ke kwance naje na shiga tashin ta a hankali, ko da ta farka se ta buɗe ido sosai gani na a tsaye, tambaya ta tayi lafiya na sanar da ita abinda nake bukata.

Cikin dan shakku take kallo na se kuma ta tambaya wai zan iya kuwa, Murmushi nayi mata tare da gyada kai cikin tabbatarwa, se ta tashi ta fita zuwa wajen su, bata dade ba ta dawo rike da hijab da pray mat ta shimfida min ina ta godiya kana ta koma ta kwanta, ni kuma na saka hija din na tada sallah.

Ko da na idar na so biya. Bashin sallolin da na rasa amma ban san kwana nawa nayi a kwance ba, so se kawai nayi adadin da nayi na bar shi, na zauna na shiga karatun Alkur'ani da hadda ta, sabida damuwa yasa har hadda ta se da ta tabu, ina bukatar Kur'ani ko dan tilawa amma ban san yadda zan samu ba.

Karfe bakwai na tashi daga kan pray mat din na koma kan bed na kwanta, a hankali nake jan nunfashi saboda kirji na dake neman tashi saboda ruku'u da sujjud da nayi, nayi lamo ina tunanin shin ni haka rayuwa ta zata kare cikin wahala, tun da mutuwar taki tazo ta dauke ni?.

Ban san awannin da na dauka ina tunani ba, ban san adadin awannin da na bata ba se da naji hannun Ryhan kan kafada ta, na bude ido na kalle ta,

"Lafiya kike kuwa? Ana ta magana amma shiru bakya ji?".

Nunfashi na sauke na sa hannu na dafa gefe da gefe dan tashi zaune, se ta sa hannu ta taya ni na zauna

"Ba komai sister, bacci ne ya fara dauka ta".

"Ga mijin ki nan yana ta Miki sannu, ya dan jima a nan amma baki ji ba".

Seda gabana ya fadi jin tace wai mijina, kamar kuma ban san wanda take nufi ba na bi inda hannun take nunawa, na sauke duba na kan shi shima idanun sa a kan mu, da sauri na kau da kai.

Kai na a kasa na amsa sannun da nayi masa tare da gaishe shi murya can ƙasa, ya amsa se dakin yayi shiru.

Can sister ta dawo dakin ta nufi gefen Masdooq ta duka inda ya aje kayan tea ta shiga haɗawa, tea me kauri ta haɗa min tare da farfesun hanta da ban san inda aka samo shi ba, ta dauko zuwa gadon da nake ta zauna ta debo a spoon ta fara bani ina karba tare da tea din har se da na kau da kai nace na koshi.

"Daure ki kara kin ji, baki ci wani da yawa ba".

"No hakan ma is okay, ai hanjin ta har yanzu be gama warwarewa ba so ba'a san a masa Lodi".

Dr dake shigowa ya fada, duk muka daga kai muka kalle shi, yayi min murmushi yana karasawa wajen Ya Masdooq ya bashi hannu suka yi musabaha se kuma ya karasa ya shiga duba ni, se kuma ya ciro wata paper daga aljihun sa ya mikawa Masdooq

"Pls aboki kaje pharmacy ka amso wadannan drugs din".

Karba yayi ya fita yana dubawa, se ya. Sake duban nurse Ryhan

"Kije wajen Dr Fahad kuyi round tare".

Itama fita tayi leaving behind only ni da Dr, ya juyo ya dube ni looking very serious and professional, yace

"Nu'aimah Bashir".

A hankali na amsa Dr, ya dube ni sosai cikin nutsuwa

"Shin kin san kuwa kina da dauke da juna biyu?".

Duk da cewa da Hausa ne Dr ke maganar amma se na ji duk ban gane ba, ganin yadda na yamutsa fuska na rashin fahimta se ya cigaba da magana

"I mean kina dauke da ciki na haihuwa, you're pregnant Nu'aimah".

Wani irin waro ido nayi waje kirji na na duka dak dak dak, zuciya ta tayi wani irin zillo a cavity din ta kafin ta koma ta zauna

"Ban fahimce ka ba, ni Nu'aimah din kake maganar ina da ciki? Kuma ciki na haihuwa Dr, to taya ya, ta ina?".

Ganin duk yadda na rude yasa calmly yace

"Calm down, ki kwantar da hankalin ki, ba wani abu bane na daban, i know and you too know you're a married woman, so is very possible kiyi ciki, so please ki daurare ni dan akwai dalilin da ya sa na fada miki tun kafin na sanar da megidan ki".

Da sauri na dago na kalle shi, yana nufin be fadawa ya Masdooq ba? Kenan be san ina da ciki ba tun da yace ni ya fara sanarwa, se kuma na dago da sauri baki na na rawa

"Kana nufin baka sanar da shi ba?".

"Yes, ke na fara fadawa dan ina so in fada miki in rayuwar ki ta cigaba a haka you and the baby will be at a very dangerous risk, rayuwar ki da ta babyn zata shiga hadari matuka dan jinin ki ya hau irin hawan da ba'a so ga masu ciki, haka kuma zama da kike da yunwa shima yana barazana wa pregnancy ɗin, so in har kina son abinda yake cikin ki se kin kwantar da hankalin ki jinin ki ya sauka, haka kuma se kina samun abinci me kyau dan samun nutrients wa cikin".

Duk bayanin da yake yi ba fahimtar sa nake ba, abu daya zuwa biyu nake jin yana maimaita wa, baby and pregnancy, wai dagaske yana nufin ni Aimah nake dauke da baby, ciki dai na haihuwa.

Na kai hannu a hankali kan cikina murya can ƙasa cike da kokonto nace

"In har da gaske ne ina da ciki to wata nawa ne?".

"One month two weeks".

"Dr ka fada min gaskiya, dan Allah da gaske ne ina da cikin haihuwa, ko kuwa dai na cin abinci kake magana?".

Kura min ido yayi na dan lokaci se kuma ya kautar tare da gyada kai

"Eh cikin haihuwa gare ki, you're carrying a baby in your womb".

Wani irin dariya ce ta kwace min da ta taho da zubar hawayen farin ciki, irin wanda na manta rabon da na samu kai na a ciki, na saka dukkan hannuwana ina shafa mara ta zuwa ciki na, ina jin wani yanayi me wuyar fassaruwa a zuciya ta.

Kamar kuma an tunatar da ni se na dago da sauri na kalli Dr dake bina da kallo har lokacin

"Dr please zan iya neman alfarma, dan Allah?".

A hankali ya gyada min kai, se na matso bakin gadon sosai na sauka zuwa wajen kofa na rufe, yana bina da ido be ce komai ba har na dawo na zauna kan kujerar da Ya Masdooq ya tashi ina fuskantar sa

"Dan Allah bana so ka fadawa mijina ina da ciki, dan Allah ka taimaka ka rufa min wannan asirin".

Kallon mamaki yanzu yake min se kuma ya tambaye ni saboda me?

A lokacin abinda zan fada yazo min kamar wadda aka tsarawa

"Mun samu sabani ne da shi ta yadda har na kauracewa cin abinci dan ganin na karkato hankalin sa kai na, wannan ne dalilin samun ulcer ta, kuma har yanzu dai be sakar min ba kamar baya, na sani in nayi masa albishir din ina da ciki ze yafe min mu koma kamar baya, dan Allah help me and save marriage doctor".

Kamar be yadda ba kamar kuma ya yadda , ya zuba min ido kamar yana karantar gaskiya ta ko akasin ta, se kuma can ya mike yace

"Well, it's okay, Ina fatan hakan ya zama sanadin kawar da dukkan wata matsala ko rashin fahimtar da ke tsakanin ku, albarkacin haka ki min addu'a ni ma Allah ya bani rabo irin haka ko na ga dan kai na, by the way congratulations".

"Insha Allah Allah ze baku masu albarka ba ma daya ba ba biyu ba, thanks so very much doctor for saving my marriage, thanks for your kindness and may all your dreams come true".

Da Ameen ya amsa min yana murmushi ya buɗe kofa ya fita, na bishi da ido cikin tausayi ganin yadda yanayin sa ya canja gaba daya, se na samu kaina da yi masa addu'ar Allah ya bashi yaya nagari masu albarka, Amin.

Ina sauke hannu na na maida kan marata, shafa wa nake yi a hankali ina jin saukar wani irin sanyi a raina, ba zan bari ya san da cikin nan ba dan na san ba ze so shi ba, a baya ni na guji hada jini da shi, a yanzu kuma na san shima ze yi duk yadda ze iya wajen ganin jinin sa be gauraya da nawa ba, ciki kuwa harda abortion, abinda Ni kuma ban zan yadda da shi kenan, dan kuwa wani irin sibda kaunar cikin nake.

Yanzu da bani da kowa shine right time da zan haihu, ko dan na samu wani rai daya ko biyu da zan kalla in kuma nuna da dukkan kwarin gwiwa a matsayin nawa, dan haka zan kare cikin nan,

zan yi duk yadda ya kama wajen ganin be salwanta ba, a yanzu shine abu daya da nake jin farin ciki domin sa.

A haka Ya Masdooq ya turo kofa ya shigo hannun sa rike da ledar drugs din da ya siyo, ganin yadda nake ta shafa mara da ciki yasa ya karaso da sauri asking if suna ciwo ne, na cire hannun da sauri ina girgiza kai, se ya koma ya zauna kan seat din sa, muka yi shiru kowa da tunanin da yake, har zuwa karfe sha daya sannan ya tashi ya tafi gida, lokacin Ryhan tazo ta bani drugs din ta kuma daura min sabon drip wanda shine na uku daga jiya zuwa yau.

Karfe ɗaya da rabi ya shigo hannun sa rike da ledoji, ya aje gaban gado na kana ya ciri ta fruits ya shiga toilet ya wanke, sannan ya yayyanka min da kan sa ya kawo gabana, a hankali na ke dauka ina ci duk da kuwa ban so ci din ba, amma ina ganin su na ji ba abinda nake so a lokacin se su, sosai ba sha fruits din, hakan kuma ya masa dadi dan na gani a fuskar sa.

Karfe biyu na kuma shan magunguna na na rana, wanda ban dade ba bacci ya kwashe ni dan har da na baccin a ciki.

Se after four na farka, na sauka na shiga toilet nayi alwala na fito nayi sallah da kayan da Ryhan ta kawo min dan bata karba ba, ina idarwa na sake komawa bed na kwanta hannu na kan kasan marata wanda wunin yau bani da aiki se shafawa, se in Ya na nan ne nake hakura dan kar yayi tunanin wani abu.

Seda na kwana uku a asibitin sannan aka yi releasing dina, kullum kuma Ya zezo so uku ko hudu, kuma duk zuwa se ya taho da wani abun da zan ci wanda mara lafiya ze iya so.

Shi da Ryhan suka yi aikin jinya ta se Dr da ya kula da ni sosai, ranar da ya bamu sallama na masa godiya ba kadan ba, na farko dan kulawa da yayi duk da aikin da ne, se kuma na alfarmar da yayi min...................✍️.

Vote
Comment
Share fisabilillah

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 015  [ 26/06/2024 9:14pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Oummey
Free book!!!

Ouummey 015

Page 1️⃣5️⃣

__________________har parking space Ryhan ta rako mu, ta so karbar number ta na sanar mata bani da waya an sace, se ta bani Tata wai in kira ta duk sanda nayi waya dan muyi zumunci, da murmushin da na kakalo na amsa ta da insha Allah, muka rabu cikin mutunta juna.

A baya na zauna saboda Dr da yace ina bukatar wajen da zan mike sosai, na sani yayi haka ne dan abinda yake ciki na, a zahiri kuma se yace saboda ciki da kirji na ne, hakan muka tafi motar shiru kamar ba masu rai Banda numfashin mu dake tashi.

Tun fa muka fita daga hospital din naji duk zuciya ta babu dadi sanin ina ne zan koma, yanzu da nake da ciki na kuma san zama da yunwa ze illata abin ciki na se na ke tunanin yaya zan yi a gidan da har abinci ana hana min in aka so azabtar da ni?.

Sedai har muka kai ban samu wani solution ba ko yaya, jiki a sanyaye na fito daga motar, ya fito da sauri yana tambaya ta zan iya?, Da kai na amsa masa wanda haka nake masa duk zaman da mukai a asibiti, bayan gaiuwa duk wata magana da ze yi da kai nake amsa masa.

A nurse cikin kiyayewa nan shiga gidan, ko ina shiru har nan shige daki na ba motsin kowa, ban kai ga zama ba shima yayi sallama ya shigo ya tsaya daga bakin kofa ni kuma na kai zaune kan sofa.

Gyaran murya yayi

"Likita yace kin fama da ulcer, kuma kina a second to the last stage, so ba'a san kina zama da yunwa, dan haka na saka miki duk wani emergency abu da zaki iya ci kafin a gama abinci, komai yan cikin fridge , some kuma wardrobe din ki, and in sun yi kasa ko kina bukatar wani abun kya iya sanar da ni, Allah ya kara lafiya".

Daga haka ya juya ya fita daga dakin, ni kuma na tashi zuwa bedroom, a can na tadda sabuwar fridge babba an girke min, ban yi mamaki ba dan tun da yace an saka min abubuwan ci to fridge din ma daga gare shi ne, se na fita na duba madaidaicin da yake rumfa, cike yake da ruwan

roba kusan kayan daya da rabi, se juices kala uku.

Da na koma bedroom se na bude wannan, shi kuma cike yake da su fresh milk, yoghurts, snacks, fruits, custard, cerelac, kayan gwangwani da dai duk wani nau'in emergency feed.

Gefe daya da fridge din ƙatuwar kettle ce da cups, se kuma plate da electric cooker, kwalin indomie da kuma bottle din palm oil.

Na zauna tare da zuba wa kayan ido sosai cikin nazari, in har tunani na ya bani daidai Masdooq be san horon yunwar da matar sa ke min ba se yanzu, da ya gane kuma shine yayi min wannan siyayyar saboda baze iya mqta magana ba, ko kuwa yayi tace ba zata dinga girki da ni ba, to koma dai menene ni dai na gode, dan ban yi zaton haka, na ji dadi dan na san insha Allah batun ulcer yayi affecting baby na kuma babu shi yanzu.

Wanka nayi duk da ban dade da yi ba a hospital, Dan dakin a gyare yake daga falo zuwa bedroom da toilet din, na sani hindu ya saka ta gyara, dan in ba ita ba babu me yi.

Ina fitowa na gabatar da azahar da ta riske mu a hanya, kana na matsa jikin fridge na dauko can din kifin gwangwani da lemo rani, na hada da bread na ci na tashi, na kuma ji ni daidai alhamdulillah, se kuma na kwanta bacci abina bayan na sha magani na.

Tun daga lokacin se Allah ya yanke min izayar Sa'adah na abinci, so da yawa kafin ta gama gabtalin ta ta aiko abincin ni na riga na cika tumbina, wannan yasa wannan muguwar ramar ta ragu, sedai ban maida jiki na ba saboda laulayi kuma da ya sako ni gaba, sauƙin abin ma ba inda nake fita ko falo, wannan yasa ba wanda ya san halin da nake ciki.

Har yanzu kuma Ya Masdooq be fasa zuwa daki na ya kwanta ba tun ranar girki na, sauƙin da aka samu shine yanzu ya kan leko da asuba kafin ya fita, ko da kuwa ba'a daki na yake ba se ya shigo da asuba, daga nan kuma se wata asubar.

Haka muka cigabq da gurgura rayuwar har wajen wata biyu bayan dawowa ta daga asibiti, babu batun yunwa babu labarin ta, sedai damuwa da har yanzu na kasa curewa daga raina, yanzu ni kadai zaka iya samu na ina hira da kai na kan batun haihuwa ta, sunan da zan sawa baby na kuwa tuni na zaba, wanda da yardar babyn nayi haka dan kuwa hannu na dora kan flat tummy na da yake a shafe har lokacin ina fadawa babyn sunan da na zaba mata in macece , da wnada na zaba masa in namiji ne, aka yi dace kuma naji kamar cikin ya motsa a lokacin, se kawai na saka dariya ina fadin baby ya amince.

Samuwar cikin nan ya kara ta'azzara lamarin depression dina, har yanzu ina zama cikin duhu na, haka ga ƙaruwar hira da nake yi sosai ni kadai, wanda ni a raina na san da baby na ke, kuma se wataran in ji babyn na amsa min, wanda zahiri ba amsawar yai ba just hallucination ne nake yi.

A sannu a sannu abin yake karfi, tun bare da cikin ya fara fitowa, se in zauna in dafe cikin ina fada mishi yadda kowa ya guje ni, yadda shi kadai ne abinda zan nuna da sunan na wa, yadda nake son ya zame min sanyin idaniya, wataran kuma in fara bashi labari na tun daga farko har kawo rayuwa ta gidan mahaifin shi.

Lokacin da ya fara kicking kuwa ai se lamura suka sake tabarbarewa, dan ni kaina na san na fara haukacewa, haka zan yi ta tatsuniya da sunan baby nake wa, ni kadai bai ta dariya, wataran kuma kuka, wataran wasa , nasiha har da fada.

Babu wanda ya san halin da nake ciki dan kuwa ba wanda ze ganni yace ban da lafiya, dan na dan ciko abina se abinda ba'a rasa ba, shi kuma tun da na san lokacin shigowar sa bana wani yarda na yi abin a gaban sa, yawanci ma yafi tadda ni ina sallah tun da da asuba yake shigowa, wannan yasa be taba sanin akwai wata damuwar ba kuma, a tunnain sa shikenan yayi maganin matsalar yunwa, to ba sauran wata.

Sa'adah kuwa ban san me yace mata ba ta daina shigo min daki, abinci sedai ta bawa hindu ta kawo min, in mutum ze wuni a gidan nan kai koma kwana base taba tunanin akwai wata rai dake rayuwa a ciki ba bayan masu gidan, balle ayi batun matar gidan ce.

Ciki na na wata biyar ya fito sosai, zuwa lokacin kuma duk matsalar rashin hankali na dake tashi sa'i da lokaci ban kasa tsare cikina ba, dan kuwa na koma rayuwa fa hijab dare da rana, duk kuwa tsananin zafi bana cirewa dan bana san yin kuskuren barin abinda ze zo ya zame min matsala.

Dan akan cikin nan ji nake yi na shirya kome ze faru sedai ya faru amma ina son abinq, Ina son kaya na, ba zan bar kowa ya cutar min da shi ba.

Yau ina zaune a bakin bed, sanye da hijab dina na gado, ta ciki kuwa hannu na na dafe da cikin da ya dan tasa, kamar yadda na saba na gyara zama

"Ka tuna nayi maka alkawarin baka labari na ko baby?, Na sani zaka so jin labarin Mammyn ka ko, to bari kaji labari na, se ka yanke shin laifin nawa ne ni kadai ko ni da su Mama, shin hukuncin da suka yanke min daidai ne ko kuwa?, Amma kafin nan promise me ba zaka tsane ni ba in kaji labarin nan, dan in ka tsane ni se na kashe kaina, I'll kill myself dan ba zan iya rayuwa ba kai ba baby".

Cikin ikon Allah se ga wani kick daga cikina da har se da na dan runtse ido dan na ji zafi amma ba zafin ne a gaba na ba, farin ciki nake baby ya amsa ba ze guje ni ba, dan wannan kick din na dauke shi ne as promise.

Na share hawayen da suka zubo min dan yanzu kam ba dawo daidai, na shiga tunanin rayuwa ta ta baya, daki daki kamar wadda ake haskawa a majigi!.

★★★ NU'AIMAH BASHIR★★★

me karatu kamar yadda kika sani sunana Nu'aimah, ƴa ta karshe a wajen Alh Bashir, magidanci me cike da rufin asiri da wadatar zuci.

Matar sa daya kuma mahaifiya garemu, Safiyya da muke kira da Mama.

Asalin Mama na yar kasar Ethiopia ce gaba da baya, yaki da ake yi a kasar yasa su tarwatsewa suka fantsama duniya, a haka ne Nene, kakata da ta haifi Mama ta shigo Nigeria ita da yaran ta biyu duka mata, wato Mama da Hajiya Yayah.

A kasar Nigeria tayi aiki tukuru wajen kula da ƴaƴanta da kan ta, har Allah ya hore mata ta siya gida dan karami suka tashi daga hayar da suke yi suka koma ciki.

Hajiya Yayah ta hadu da Baba ne a restaurant din da take aiki, lokacin shekarun ta sha shida, babu bata lokaci baba ya bayyana mata kaunar da yake mata, dan kuwa love ne St first sight.

Be sha wahala ba Yayah ta amince masa, Liman din unguwar da suke zaune ne ya yi waliccin ta, sauƙin abin da ya kasance shima Maraya ne, daga shi se yar uwar sa, se kuma kawun da da suke zaune a wajen shi.

Haka aka yi aure cikin rufa ma juna asiri dab lokacin Baba be da kudin da yake da su yanzu.

Shekara har uku bayan auren su amma Hajiya Yayah bata taɓa ko barin wata ba, lokacin kuma aka yi bikin Mama da Abba, wnada ya kasance malamin makarantar bokon su, shima dai lokacin babu wani arziki na daban se godiyar Allah da wadatar zuci.

Cikin hikmar Ubangiji wata biyu da aure se ga Mama da cikin wata daya, lamarin da ya faranta ran duk wani masoyin mama tun bare hajiya Yayah dake baro gidan ta ta taho namu wajen Mama, dan ita ke kula da ita kasancewar laulayi ne take yi me zafi.

Bata samu sauki ba, see da ta haifi babban yayanmu yaya Salman, Hajiya Yayah kuwa ta dauki son duniya ta ɗora ma ya Salman, a yadda na ji labari ganin irin son da take masa ya sa Mama tayi wa Abba maganar bawa Yayah shi in ta yaye shi, sedai yaki, a cewar sa su in suka bata su kuma fa, beside ma dangin sa ba zasu yadda ba.

Haka Mama ta hakura, amma Yayah ta bawa yayen sa, daga nan kuma se rayuwar sa ta rabu biyu, rabi gidan mu rabi gidan Hajiya Yayah.

Wata rashin lafiya da Hajiya Yayahn tayi yasa Mama karvar ya Salman, saboda yadda har asibiti ta kwanta, shi kuwa Abba kamar yana jira ya maza ya sa shi a makaranta, wadda bayan warkewar Hajiya Yayah da ita yayi kandagarkin hana ta ya Salman, wannan shine dalilin dawowar sa zama gidan mu gaba daya.

Shekarar ya Salman uku Mama ta sake samun ciki, wannan karon kusan tare da Hajiya Yayah suka samu dan ratar su wata biyar ne, murna wajen yan uwa kuwa ba'a cewa komai, Hajiya Yayah kuma ta samu sauki wajen kanwar mijinta Hauwa da ta bi ta tsangwame ta shaida bata haihu ba.

Sedai Allah me yadda yaso yasa cikin Hajiya Yayah ya bare, lamarin da yasa kowa cikin tashin hankali, ya kuma sa Mama ta fara nakuda batare da lokacin haihuwa yayi ba, aikuwa ta haifi dan ta bakwaini aka sa shi a kwalba, ya ci sunan Najeeb.

Dole Hajiya Yayah ta gyagije saboda Mama da ta daga hankalin ta, haka suka cigaba da renon Najeeb cikin kulawa.

Daga kan sa kuma se da Mama tayi shekara biyar sannan ta samu wani cikin, lokacin kuwa Hajiya Yayah tayi bari kusan so shida, wannan ya tashi hankalin su da na mahaifiyar su aka shiga neman magani, ba na asibiti ba na gida.

Wannan cikin ma kusan tare suka samu da Mama, ratan wata uku ne kawai tsakanin su, aka yi ta addu'a da rokon Allah kan ya zaunar da wannan cikin ya sa Hajiya Yayah ta haife shi lafiya, se kuwa ga shi cikin ikon Allah wata tara da sati biyu ta haifi dan ta namiji, jawur da shi kamar baban sa, dan baban su ya Masdooq fari ne tas, ba kamar su hajiya Yayah ba da kalar fatar su ta sirka.

Ya Masdooq yazo a lokacin da ake tsaka da so da kaunar sa, dan haka tun yana yaro yake shan gata wajen baban sa, mama, hatta da Abba da kuma raguwar abokan arzika zuwa kakar mu Nene.

Wata uku bayan nan Mama ta haifi Yaya Farouk, wanda shine tsaran ya Masdooq, suka kuma taso kan su a hade kamar yan biyu, sedai banbancin kamanni da halayya.

Yaya Farouk akwai zafi, hayaniya da rashin daukar wargi, ga kuma rashin fara'a se in shi ya so, akasin Ya Masdooq da yake da sanyi, be san hayaniya ko kadan, haka kuma gwargwado yana da sakin fuska amma fa ya tsani raini.

Daga ya Farouk se Ya Ahmad wanda shine sa'an Aunty Luba, daga nan kuma se bayan shekara bakwai aka haife ni ni auta Nu'aimah!!!....................✍️.

Vote,
Comment,
Share fisabilillah

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 016  [ 27/06/2024 6:55pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Oummey
Free book!!!

Ouummey 016

Page 1️⃣6️⃣

___________________Tsananin so da kauna ake nuna min a kowane bangare musamman Abba da Mama da suka dauki dukkan wata soyayya suka aza min, ba dan komai ba se dan na zo a macen da basu taba samu ba, dan Mama na mugun son ya mace, ga shi da Allah ya tashi se yayi ta jera mata maza, wanda ganin yadda take son ya'ya mata Abba ma ke taya ta.

Yanzu kuwa da suka samu se suke ganin dole ne ma su gatanta ni, su nuna min tsananin so dan nuna godiya ga Allah.

Na taso cikin matukar kulawa, so , kauna da tattali daga iyaye na da kuma yayye na, ta kowane bangare ni yar gata ce, Duka yayye na har rufe rigen  dauka ta ake, Ya Salman da ya Najeeb ke cin girma su barwa su Ya Masdooq da ya Farooq, a tsakanin su ake shan rigima dan ya Ahmad me sanyi ne, baya fada bari yake se sun gama sun aje ni sannan ya dauka.

Aunty Luba kuwa tun suna da aka zo da ita taki komawa gidan su ta tubure ita a wajen kanwar ta zata zauna, ita ba zata bi Hajiya Yayah ba gidan su ba baby, tun ana daukar wasa har aka zo tafiya ta ringa rigima har da shidewa, se Baba yace a bar ta kawai, sanda ta gama marmari na zata dawo, se gashi kuma daga nan bata kuma komawa ba, aka tarkato mata kayan ta ta dawo gaba daya.

Ya Masdooq da ya Farouk kuwa sun fi zama gidan Hajiya Yayah dan ya Masdooq na da ɗafa, wannan yasa ba ya barin gida, shi kuma ya Farouk duk inda ya Masdooq yake nan yake zama, wannan yasa zaman su yafi a can, sedai su wuni a gidan mu da magrib Baba yazo ya ɗebe su.

A haka na tashi, cikin matukar kauna da soyayya, na taso a sakarce a shagwabe kamar kowace auta da kuka sani, Mama bata ganin laifin duk abinda zan yi, wannan yasa tsiwa da rashin kunya suka zama yan gaba gaba a cikin halaye na, tun yarinta ba ni da hakuri, in dai a ka yi min se na rama, sedai ban fiya tsokana ba.

Wannan halayen nawa yasa ba ma shiri sam da ya Salman dan ya tsani rashin kunya, sedai Mama bata bari ya hukunta ni, komai nayi a wajen ta yarinta ce.

Ina shekara bakwai su Ya Masdooq suka bar kasar zuwa Sudan yin karatun jami'a dan kuwa suna da 19years lokacin, ya Ahmad kuma yana da shekara 14 yana Jss 3 shi da Aunty Luba, ni kuma primary 3, lokacin Nene tuni ta koma Ethiopia dan an samu kwanciyar hankali, daga cewa zata je duba wasu dangin ta in zata gan su shikenan tayi zaman ta, ba yarda su Mama da su Baba ba su yi ba tace ita kam ta koma gida, sauƙin abin ta ga wani kawun ta, shikenan zaman ta ya koma can.

A shekaru na na bakwai babu inda zan shiga a lokacin baka ji an kira Aimah ba fiye da so ba adadi dan Allah ya zuba min kyau Masha Allah, ga kuma gayu da Mama ke min, tun a lokacin komai nawa unique ne, tun daga kan takalman makaranta ta zuwa school  bags dina, hatta kayan sawa na se na zaba na darje, ga shi cikin ikon Allah se haihuwa ta tazo wa Abba da wanni irin budi, harkoki suka buɗe masa ta hanyoyi daban daban, kudi kuma yace Bismillah.

Wannan ya karawa gata na armashi, komai nake so yi min ake, wani sa'in kafin ma na furta tuni an min, Aunty Luba kuwa ta zama second Mom dina, bata cin kudin break din ta ni take karawa siyan kayan kwadayi, duk kuwa da ana bani kudin break, haka kuma duk wani kayan kwadayi na yara ina da shi a ajiye ana bani kullum zan tafi school, ban da abinci da se na zabi me zan tafi da shi.

Gata iya gata ake nuna min, Hajiya Yayah ce ma me ɗan daure min fuska dan tace in ta hadu gaba daya aka sake min za'a rasa me iya tsawata min, dan kuwa Abba da Mama ba sa hanani duk abinda nake so, kome na nuna ina so to fa shi za'a yi, dan hatta girkin abinci se mama ta tambaye ni me za'a dafa, kai hatta kaya kafin a siya min se na fadi kalolin da nake so, ko kuma a je da ni na zaba.

In kuna Jin ana fadin a very spoiled child to nice, bana tunanin a duniya akwai dan da ze gwada min gata, sangarta, shagwaba da tabara.

Har ina seven years in rigima ta tashi se Mama ta goya ni nake shiru, haka kuma in na ga dama ince a dakin Abba zan kwana, haka kuma za'a yi, su sani tsakiyar su muyi baccin mu shi da

Mama.

Yaya Salman abin be masa daɗi, dan haka shi be sake min ko kadan, wannan yasa a zuciya ta nake jin ai ya tsane ni ne, haka kuma in yana waje cif nake kama kaina dan in nayi kuskuren yin wani iskancin kuma Mama bata kusa to fa se ya sa ni punishment, sometimes Maman ma na nan yake yi, karkari tayi ta fada shi kuma ya toshe kunnen sa.

Kar kuyi tunanin haka Mama da Abba ke wa ragowar yayye na, no!, Dan kuwa Mama da Abba are very no nonsense parents ga yayye na, tarbiyya sosai suka yi tsaye wajen basu, nice kawai da Allah ya jarrabe su a kaina suke min haka.

Har makaranta Abba yaje yaci mutuncin wani teacher da ya sani up and down, ya Kuma kafa sharadin shi yar shi bata lafiya kar a ringa sata duk wani aiki ko punishment.

Da basu ji ba kuwa wani malami ya dake ni seda Abba yayi reporting din shi police station, da kyar aka kashe maganar aka bawa Abba hakuri.

Daga nan kuwa ya canja mana makaranta ni da su ya Ahmad da Aunty Luba zuwa wata private school me shegen tsada da kyau, a nan kuwa da se abinda ya ga dama yake yi saboda duk ƴaƴan manya ne, kowa kudin uban sa ke aiki.

Wannnan yasa na samu freedom din yin wulakanci san rai na, na raina teachers na musu tsiwa da rashin kunya ba yadda zasu yi, Aunty Luba kuma ta tsaya min a wajen dalibai yan uwa na ita da ya Ahmad.

In kana son ka ga fada da bala'in Aunty Luba to a taba ni, a lokacin bana ce mata Aunty, second Mom nake kiranta, ita kuma tana kirana little kiddo.

Ina shekara takwas wata kawar Mama da suka yi makaranta tare suka yi allocating zuwa kusa da gidan mu, dake da gidan haya ne se mijin ta ya siya ya gyara shi sosai suka dawo ciki.

Murna wajen Mama da Aunty suwaiba ba'a magana, haka kuma take yaranta suka zama yan gida a gidan mu haka muma.

Cikin ikon Allah itama duk ƴaƴan ta maza ne sa'annin su ya Ahmad, se kuma kanne na, se babban wansu dan wan mijin ta da take riko, Ya Ibrahim, wanda ya kasance sanadin da kuma silar duk wata ƙaddara ta rayuwa ta!!.

Tun da suka dawo unguwar nan ya zama bani da wajen zuwa da wuce can, Aunty Suwaiba itama kamar Mama ce gare ni, dan bata min fada, komai nayi sedai tayi dariya tace yarinta ce, duk da ita ba haka take wa ƴaƴan ta ba, wannan yasa nake son zuwa gidan, in shiga cikin su Aslam dan ta sa'ana muyi ta guje guje da wasan banza.

A haka wata rana muna wasa na turo Aslam daga bene ya fado yayi targade, Ya Ibrahim ya zane ni kuwa, abinda ba'a taba yi min ba a rayuwa ta, na yi kuka sosai ranar, na ji kuma na tsane shi, naje gida na sanar da mama, amma ko da taji me nayi se hankalin ta ya tashi, ta shiga ta bada hakuri aka tafi wajen me gyara da ita, ko da ta dawo se ta zaunar da ni tana min nasihar rage rashin ji wacce na dauke ta as fada, dan haka se na sake jin haushin sa sosai ganin yau a kan sa abinda ba'a taba min ba ana yi min, haka kuma da Abba ya dawo na fada masa shima se ya shiga rarrashi da fada min ban yi daidai ba.

A lokacin kasa daurewa nayi na fashewa Abba da kuka, se kuma hankalin sa ya tashi ya shiga rarrashi na har na yi shiru, sedai na rike Ya Ibrahim a raina sosai, tun daga ranar kuma na dauke kafa ta daga gidan Aunty Suwaiba.

Juyin duniya anyi na ki komawa, da kanta ta shigo tayi rarrashi na amma na ki koma musu, hatta Aslam din na dena kula shi, abin ya damu su Mama da Aunty Suwaiban, ashe se da tayi wa Ya Ibrahim fada sosai ta kuma ce shi da yaja na dena zuwa dolen sa ya rarraso mata ni.

Haka kuwaa har gidan mu yazo bani hakuri amma nace ni ba ruwa na da shi ba zan kula shi ba, yayi yayi naki, daga karshe ma na tashi daga kan cinyar Mama da nake kwance na tafiya ta dakin Abba.

Mama ce ta sanar da shi yadda ze shawo kaina, ai kuwa kashegari se gashi da ƙatuwar yar tsana ya siyo min, Alh ya zuba min san baby wato yar tsana, wannan yasa har yara na mutane so nake musamman jarirai, na dauke kai naki kallon sa se ya dora min doll din kan cinya ta, ina kyalla ido na gani na kai hannu zan dauka ya riga ni, yace ai se na hakura sannan ze bani, na zumbura baki na kau da kai nace ai Abba na ze siyo min wadda ta fi Wannan.

Tun daga ranar yake hidimar siyo din abinda aka fada masa ina so, kama daga kan kayan ci, na sha da na wasa, se gashi kuwa ba'a dade ba ya shawo kai na nace na hakura.

Se kuma sabon shiri ya balle tsakani nan da Ya Ibrahim, sosai yake siya min duk abinda nake so a lokacin da nake so, mun shaku matuka gaya dan da na dawo daga makaranta in na canja kaya ba inda nake yi se gidan Aunty Suwaiba neman sa, hatta Aslam da muke abokai na dena kula shi se ya Ibrahim, haka Aunty Luba ma suka shaku saboda ni.

Da kuma wannan damar yayi amfani wajen saisaita dabi'a ta, yace in nayi kaza ze siya min kaza ko ze kai ni waje kaza, wannan ya kara mana fahimtar juna matuka.

Shi kuma ya Salman se ya tada balli kan be yadda da wannan alakar ba, dan lokacin na kai shekaru goma, Aunty Luba kuma sha bakwai, so acewar shi yadda zamani ya zama mutane ba abin yadda bane, kannen sa mata ne dan haka be yadda ya sakarwa baligin namiji kamar Ya Ibrahim ba, dan kuwa ya girme wa su Ya Masdooq, amma kuma ya Najeeb ya girme shi.

Se kuwa Mama tayi tsalle ta dire tace bata yarda ba, dan kuwa irin kukan da na sa a gidan, na

ki cin abinci na ki sha, naki wanka baki komai saboda ya Salman ya ce kar ya kara gani na da ya Ibrahim, sosai hankalin su ya tashi musamman Mama da Aunty Luba da Abba, shi kuwa ya Najeeb yana makaranta haka ma su Ya Masdooq, ya Salman kuwa ya bawa banza ajiyar mu.

Abu kamar wasa ya kai mu har ga suma, shine fa hankalin mama ya tashi tace base kashe mata ƴa ba, dan haka ta bani licence din kula ya Ibrahim.

Ya Salman ya fusata, yace shikenan tun da haka tace, ta nuna masa be da iko da ni, amma kam ban da Aunty Luba, be yarje mata mu'amala da ya Ibrahim ba.
A lokacin Mama bata Musa wannan ba dan kuwa second Mom ta zama budurwa, duk da bata gama girma ba amma kam da angan ta anga mace.

Wannan yasa alaka ta yanke tsakanin Aunty Luba da ya Ibrahim, ya zamana ni kadai nake zuwa wajen sa me makon mu biyu, ya fita da ni yawo a motar sa dan lokacin yana NYSC din sa, haka kuma baban sa ya bar masa gado sosai.

Ya min siyayya, muje unguwa tare, muci abinci tare har ma na kwana a gidan su wataran.
Ina girma shakuwar mu na karuwa, da na kai shekaru sha biyu ne shima Abba yace ya kamata a daidaita alakata da ta ya Ibrahim dan ai mace nake, ba ze yiwu a kyale mu sakaka ka haka ba.

A lokacin ne na shigo gida, mun dawo daga wajen aikin Ya Ibrahim, dan in ba makaranta makalewa nake se na bishi, shi kuma baya damuwa yake tafiya da ni.

Hatta makaranta shi yake kai ni ya dauko ni dan kiri kiri na daina bin driver da Abba ya daukar mana, se iya su Aunty Luba ke bin sa, da suka yi graduation last year kuwa se dole kyale shi aka yi ya zama driver gida gaba daya.

Jin abinda Abba ke cewa ya san na fasa ihu tare da fara birgima, na watsar da kayan ciye ciyen da nayi tsaraba, da kyar kuwa aka rarrashe ni ranar, shikenan aka daina batun raba mu da ya Ibrahim, sedai ashe a boye Abba ya same shi ya ba shi amana ta tare da rokon ya kula da ni.

Shi kuwa ya Salman warning yayi masa kan duk wani abu mara dadi ya faru dani se yayi Shari'a da shi, ga shi kuma dama lawyer ne..............✍️.

Vote
Comment
Share fisabilillah.

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 017  [ 27/06/2024 6:56pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Oummey
Free book!!!

Ouummey 017

Page 1️⃣7️⃣

___________________Aunty Luba kuwa ba ni da aminya sama da ita, duk inda muka je se na saka Ya Ibrahim ya min hoto dan na nuna mata, duk kuma abinda na gani se an siya mata, haka duk wanda naci se na rage mata, shakuwa ce sosai a tsakanin mu, haka kuma ita da ya Ibrahim kadai ke sa ni nayi abinda ban yi niyya ba ko na bar abinda basa so.

Se a wannan shekarar ne su Ya Masdooq suka zo gida, da shaidar su na kwalin degree dukan su kuma first class, Ya Masdooq is a aerospace engineer, where as Ya Farooq is an Architect, murna sosai aka yi amma ban da ni, dan kuwa dawowar su yasa rayuwa ta cikin wani yanayi.

Ina bala'in tsoron ya Farooq har fiye da ya Salman, dan kuwa ranar da suka dawo se da ya zane min jiki na tass da cajar waya, dan na bi Ya Ibrahim dangin Maman sa tun safe ba mu dawo ba se tara, aikuwa ya sa ni a daki ya zane bayan ya rufe kofa, wannan yasa aka rasa me ceto na se hayaniya da Abba da Mama ke yi kan ya bari amma be kyale ni ba se da ya ga ina numfashi da kyar.

Tun daga ranar kuwa nake bala'in tsoron sa, in har suka kwana a gidan mu ranar ba ni ba zuwa wajen Ya Ibrahim, shi kuwa ya Masdooq ba shi da hayaniya, magana ma bata dame shi ba, sedai baya hade fuska, amma fara'ar sa ta da ta ragu.

Nikam bana shiri da mutane marasa magana dan ni din magananniya ce, magana rairairai kamar Radio, haka nake in nan fara zuba, wani sa'in se an dakatar da ni.

Sedai shiga dari fita dari ya Masdooq se ya kawo min tsaraba, ice cream, chocolate, biscuit ko kuma kayan wasa, wannan yasa nake shiri da shi sama sama, rashin maganar sa ke bata min rai da shi, dan se in zauna ina bashi labari amma sedai yai ta min murmushi ko yai ta kallo na, in kuma tambaya ce se dai ya gyada min kai ko ya girgiza, se ya ga na bata fuska sannan yake magana, shima q hankali kuma can kasa, sedai Muryar sa na min dadi, fiye da duk wata murya da nake ji ta maza, kai har ma ta wasu matan, wannan yasa nake yawan takura masa yayi magana.

A zaman wata biyun da suka yi shakuwar mu da ya Ibrahim ta dan ja baya saboda ya Farooq, da kuma samun ya Masdooq da nayi, shima yana kai ni yawo, ya siya min duk abinda nake so, sedai baya magana, wannan yasa nake missing ya Ibrahim sa'i da lokaci, musamman in zan bada labari, sedai shima mun shaku da shi, ranar da zasu tafi duk da ina farin cikin tafiyar ya Farooq amma na sha kukan rabuwa da ya Masdooq.

Dake Baba ya sake nema musu masters shiyasa suka juya, wannan karon Australia suka yi, nayi kewar ya Masdooq na dan wani lokaci kafin kuma na ware na sake jonewa da ya Ibrahim, lokacin Aunty Luba tuni ta fara University tana karantar Education biology, an kuma saka ranar ta da ya Salman da ya bayyana yana kaunar ta, itama kuma babu jaq ta amince.

Wata biyar da aka saka na zuwa aka yi auren su, na sha kuka ranar da za'a kai ta, ba yadda bata yi dani ba kan mu tafi gidan tare naki, saboda sanin wane ya Salman, a gidan mu ma ya ba kaya da shi balle gidan sa.

Wannan yasa ba ko yaushe nake zuwa gidan Aunty Luba ba, sedai na dauke wayar mama mu cinye mata kati, ko kuma muyi vedio call.

Lokacin ina shekara sha hudu, tun a lokacin duk wanda ya kalle ni se ha kara, kyakkyawar matashiyar budurwa, me wani irin skin color dake fizgar hankali, attractive face da kuma tsiwa ta zuwa zubin dirin jiki na da ya fara bayyana ta kugu na ke jan hankalin jama'a kai na.

Tun a lokacin bani da burin karatu, abu uku nake matuƙar so da kauna sune makeup and fashion design, se kuma girki, ina matukar son kwalliya, kamar yadda nake son dinki, ba wai ni nayi ba, a'a naga ana yi na burge Ni, kwalliya kuwa ni din nake so naga ina yin ta, shiyasa tun ina ten years na mallaki make up kit na kai na, yanzu kuwa baka taba raba fuska ta da kwalliya, ko da kuwa zan je makaranta ne se na yi nude make up, tun ana min warning da fada har aka bar ni, girki kuwa dole nasa Mama ta saka ni catering schools kala kala, da na gama wannan in naga wata se na tubure an saka ni, shiyasa na kware sosai a fannin girki, yana daya daga cikin favorite hobbies Dina.

Shekara biyu da auren su ya Salman Aunty Luba ta haifi baby boy, shine kuma zuwa na na farko da na je na kwana, dan tattarawa nayi na koma can, har se da aka yi arba'in, shima missing Ya Ibrahim ne ya sa na dawo, dan babu Hanyar haduwa da shi a gidan Ya Salman, shi yake kaini makaranta ya dawo da ni, dan haka nake q takure.

Ina SS2 su ya Masdooq suka sake zuwa, lokacin duk sun hada masters din su, har sun fara aiki ma a can din, yanzu ma ziyara ce suka kawo.

Lokacin kuwa tuni shakuwar dake tsani na da Ya Ibrahim ta rikide ta koma azababbiyar soyayya, wadda bana iya wuni guda ban gan shi ba, ya saba min da kan sa sosai ta yadda a rana se muyi waya so fiye da Ashirin, tun ina SS1 muka fara soyayya, a lokacin kuma na tubure wa Mama ni waya nake so, batare da sanin Abba ba ta siya min dan shi yace se nayi candy tukuna.

Kullum kan ya tafi aiki se ya kai ni school, muna tafe muna shan kaunar mu, in aka Yi break kuwa zan tafi can bayan school na fito da waya ta na kira shi musha hira, daga nan kuma ana tashi ze dawo ya maida ni gida, ina komawa kuma zamu dasa sabuwar waya kamar ba yanzu muka rabu ba, lokacin islamiyya nayi wato karfe uku ze shiga rarrashi na dan kuwa bana san islamiyya, haka ze lallaba ni ya dawo ya kai ni, ana tashi ya kuma komawa ya dauko ni, again mu dora da phone call, wannan yasa by each passing minutes soyayya da shakuwar mu karuwa kawai take batare da tana raguwa ba.

Ina shiga SS2 kuwa na yaye islamiyya, Mama ma kuma ta goya min baya, duk tijarar ya Salman haka ya hakura dan kuwa ina da daurin kugu.

A wannan lokacin shekaru na sha shida, amma kirar jikina se ka rantse bata wa bace, kirar jiki na irin ta models din nan ne, very perfect, daga sama da kasa a cike nake, amma kuma ba wai cikar da tafi ƙarfin shekaru na ba, kuma ba wai kiba ce gare ni ba, ga kuma kula da gata tare da Hutu da tasa fata ta take wani irin daukar ido, ya Ibrahim kuma ya daure min dan kuwa duk inda yaji tallan skin product irin na skin dina a fili ko a social media yanzun nan zaka gan shi da su, baya kyashin ya kashe min ko nawa ne, dan kuwa ba shi da rowa sam.

Ya Masdooq yayi mamakin gani na sosai, ba dan komai ba se dan irin girman da yaga nayi a idon sa, duk rashin maganar sa se da ya tanka, naji kunya har na rufe ido na da tafukan hannu na, Mama kuma na dariya ta bashi amsa da ai ya dade be ganni bane.

Be sha mamaki ba se da na zage na shirya musu kyakkyawar tarba ta kayan abinci ga kuma home made juices, a nan fa ya sake cika da mamaki, haka kuma duk sanda na dago se in ga idanun sa a kai na, tun ina janye wa in na gani har dai na gaji na dage masa gira alamar lafiya? Se kuwa ya sake min kyakkyawan murmushin sa da ya sabbaba min wata muguwar faduwar gaba, ba dan komai sedan yadda ya kawata kyakkyawar fuskar sa, ya kara masa haiba da kwarjini, ya kuma ratsa zuciya ta yasa ni cikin yanayin da a lokacin ba zan iya gane wanne bane.

Wannan karon sati daya suka yi suka koma saboda aikin su da suka baro, sedai ban saki jiki da shi ba kamar baya, dan kuwa da na kusance shi se in dinga jin matsananciyar faduwar gaba, haka kuma se in dinga ganin ya cika gurin gaba daya, yana sanya ni cikin wani yanayi da ba zan iya predicting wanne ne ba.

Tafiyar su se na ji hankali na ya da kwanta, sedai kuma sa'i da lokaci in Ina cikin farin ciki se fuskar sa ta dinga min gizo, se in dinga hango wannan kyakkyawan murmushin nasa, kai hatta littafi in na bude zan yi karatu se in dinga ganin kamar fuskar sa ke a ciki, se da kyar nayi yaki da hakan har na manta shi.

Ya Ibrahim kuwa har lokacin muna tare, kuma be fasa min dawainiya ba.

Muna first term na SS3 ya Ibrahim ya bijiro min da batun aure, nayi mai yiwuwa na fahimtar da shi Abba baze min aure ba dole se na kare secondary, shi kuma ya sanar da ni irin dambarwar da yake fama da ita tsakanin sa da dangin mahaifiyar sa, dan sun bashi mata tuntuni yaki, shine fa suka sami immediate kanin baban sa ba wanda yake hannun sa ba, shima be ja ba dan kuwa yana takaicin rashin auren sa har lokacin, wanda yana da 30 years lokacin, shine fa suka ba shi dama, in ma ya kawo wadda yake so in 2 months ko kuma su ba shi cousin din shi da yaki tun farko.

Wannan yasa ni da shi gaba daya muke cikin tsaka mai wuya, abu ne da na sani wallahi ko zan mutu su ya Salman ba zasu yadda ayi min aure ba lokacin, daga karshe dai na dauki waya na sanar da Aunty Luba, itama duk se hankalin ta ya tashi, muka yi ta neman mafita amma babu, ga lokaci na kurewa, ga shi kullum se ya sanar da ni sabon kiran da ya samu kan haka, dole ba dan na so ba, bayan na gama shan kuka na nace masa mu hakura da juna kawai.

Irin kallon da ya min a lokacin be taba min ba, ya hau fada da sababin dama ba son shi nake ba, se da na sa masa kuka ina fada masa yadda nake son shi sannan ya sassauta, ya fada min muna da mafita daya.

Shine ya kawo shawarar ya fara aurar cousin din na shi, ni kuma daga baya in nayi candy ya aure ni.

Nayi kuka kamar zan cire ido na haka yayi ta lallashi na har dai na hakura tun da babu wata mafitar bayan ta, muka yadda muka amince kan haka, kuma a gaba na ya kira cousin din sa Aseeya da za'a aura masa dinn ya fada mata sharadin mu, in ta yarda to, in bata yarda ba a fasa auren, amsawa tayi da ta yarda, be ce mata komai ba ya kashe wayar.

Se da ya kara lallashi na kafin ya maida ni gida, dan a wani park muka je muka yi maganar.

Wata biyu kuwa aka yi auren sa da Aseeya, lokacin na sawa kai na damuwa, duk na bi na rame na kare, na daina walwala duk na saka masu kauna ta cikin tashin hankali dan har asibiti na

kwanta akai min karin ruwa.

I most say this, ya tsaya min a lokacin dan kuwa kullum da shi ake wuni a asibitin har na gyagije ganin be daina so na ba har lokacin, muka cigaba da yadda muka saba, sedai ban da fita se waya kawai, se kuma da dare yake zuwa.

A haka na kukuta na gama secondary, lokacin watan su bakwai da aure, haka kuma tana dauke da ciki, wnada yayi ta boye min, se ranar da ta zo gidan Aunty Suwaiba sannan na gani dan ya fito sosai, da alama ta kai wata shida ko biyar, haka kuma alamu sun nuna tana da girman ciki.

Ranar kuwa mamaki ya kashe ni, dan nuna min yayi shi baya ko kallon ta, baya son ta dan haka zaman dole kawai yake yi.

Ko da na fada masa ai na ga Aseeya har ma ashe ta kusa haihuwa, duk se ya diririce ya shiga kame kame, hakan yayi min ciwo matuka dan ya yaudara ni, be zama laifi ba dan ya kula matar sa, be kuma zama laifi ba dan ya so ta, sedai me yasa ze min karya?.

Duk se na ji ya fara fita daga raina, na shige gida batare da na kuma sauraren sa ba, hakan ya tayar mai da hankali, ya shiga kira na akai akai amma na ki dauka, se da aunty suwaiba ta shiga maganar sannan muka shirya.

A lokacin ne na bijiro da batun auren mu tun da na gama Makarantar, se ya nuna min in bari Aseeya ta haihu kar a ga kamar be mata adalci ba, da na auna se naga haka ne, ko da ta san da maganar amma ba adalci ayo mata kishiya ga tsohon ciki a jikin ta.

Se kuma cigaba da soyayyar mu, a kuma cikin haka ne su ya Masdooq suka dawo kasar gaba daya, saboda Baba da ya takura se sun baro ƙasar masu jajayen kunnuwa, dawowar da ta zama Mabudin duk wata ƙaddara tsakani na da ya Masdooq!!!..................✍️.

Vote
Comment
Share fisabilillah.

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 018  [ 28/06/2024 7:26pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Oummey
Free book!!!

Ouummey 018

Page 18

___________________walima aka shirya wa su Ya Masdooq da za'a gabatar a gidan Baba, it's more like a family get together dan families din mu kadai aka gayyata, familyn su Mama, familyn Baba se kuma na bangaren Abba.

Karfe biyar aka tsara za'a yi taron, tun karfe biyu na tafi wani babban bakery da nake zuwa ina musu aiki two days in a week, dan na fada muku fa, cooking is one of my favorite hobbies, wannan yasa Mama ta tafi tace in na gama na taho.

Na so direct daga can in tafi gidan Hajiya Yayah, sedai tunanin za'a cika gidan yasa na ji na fasa, na wuce gida na yi wanka da ruwan dumi da ya ji turarukan waka masu kamshi da dadi, sannan na fito daure da towel.

Kan mirror na zauna na saka another clean towel na goge ruwan jiki na, duk da kuwa be wani zauna sosai ba kasancewar glass skin gare ni, ina gamawa na shiga mulke jiki na da mayuka na da are more of perfume saboda kamshin su, na shafa wanann na sak mulka wannan har dai na gama, na dawo na shafe tafin kafa na da nashi man, haka palms dina, se kuma na koma kan gashi na.

Atleast se da na dauki one hour kafin na gama shafe shafe na, na gyara gashi na na tufke shi da kyakkyawar ribbon silver color, dan shine color da zan amfani da shi yau.

Kaya na dake kan bed wanda na gama yi wa turare na dauko bayan na turare jiki na da na jiki na shiga zurawa.

Dark blue din lace ne da ya ji stone work da silver stones masu matukar tsada, lace din ya hadu matuka haka kuma pattern din jikin sa aka cira aka jejjera aka min kan silver net da aka min tai da shi, se ta gefe aka zubo silver net din bayan an bi shi da dinki har baya, se ya bada wani

fashion na daban, making me looking more like a bride.

Ana zuwa kan kwalliya kuwa na gyara zama, na shiga rangadawa kai na casual yet classy and fascinating make up, Ina gamawa se gani na fito kamar ba ni ba, kamar dai wata amarya.

Na dauko silver head na hada da dark blue din scarf din lace din na shiga daurawa, kafin kace me na mammalkawaya shi ya fita fit, gaban goshi na na sake gyara gashi na da na kwantar tun ina gyara gashi, looking so ravishing.

Ina gamawa na dauko purse dina na rike, tare da dan yafa silver chantely veil dina da yake purposely for the outfits.

Na dauko heel shoes dina silver color da yasha adon stones na fito zuwa falo na zauna ina daurawa, na saka na kafar dama successfully amma na hagun se ya makale, kuma na kasa gane wai a ina damuwar yake.

Ina cikin kokawa da takalmin na ji unique kamshin sa ba'a Dior sauvage yana ratsa kofofin hanci na, tun ina ji a hankali har na ji yana karuwa, lokacin kam i can't help it dole na dago, dama gashi tun da safe nake auna kamannin sa na yadda possibly ze kasance yanzu, a kan sa na sauke duba na, yana tsaye jikin kofar falo ya tokare da ƙafafuwan sa, yayinda yayi crossing hands din sa a broad chest din sa.

Kasa dauke ido nayi daga kan sa, zuciya ta na racing a kirji na, wani yanayi na musanman na ratsa jiki na, a hankali ya warware hannun sa ya shiga takowa zuwa gare ni, wanda zuciya ta ke buga wa with each takun da yake kara kusanto ni da shi.

Da kyar na iya janye ido na daga kan shi na lumshe ido ina daidaita nutsuwa ta har zuwa lokacin da naji yayi kneeling a gaba na, a hankali kuma naji tattausa kuma faffaɗan palms din sa sun kama kafata zuwa kan cinyar sa, hakan yasa na bude ido batare da na shirya ba na sake zuba masa.

Kan sa na duke yana gyara igiyar takalmin ta baya, kaykkyawar sumar kan sa me taushi da laushi ko a ido a gyare ta kwanta luf se kyalli take yi, ga kuma kamshi da take yi dan kan sa na kasan fuska ta ne.

Ban san ya gama gyara wa ba se gani nayi ya dago fuskar sa, se kuwa na sakin masa murmushi me kyau da ya bayyana haƙora na gaba daya ina fadin

"Welcome back Ya Masdooq".

Shima murmushin yayi min da ya bayyana dimples din sa na both cheeks tare da lumshe ido alamun amsawa, duk da na tsani ya amsa min da gesture amma fa ba karya wannan murmushin yayi kyau.

Na janye kafata da har lokacin ke kan laps din shi ina fadin

"Dama kana da dimples Ya?, I like it".

Na fada wholeheartedly, shi kuwa se ya sake fadada murmushin sa se kuma lokacin yayi magana tun shigowar sa

"In kina so se in Ciro in baki".

"How I wish hakan ze yiwu, da na ji dadi ba kadan ba".

"Me ze hana ya yiwu, sedai in bakya so".

"Taya ze yiwu to?". I asked out of curiosity

"Ba ki San ana surgery ba?".

Zaro ido nayi ina dafe baki, wane irin surgery kuma, cab ai gwara na hakura

"A'a Nikam na hakura".

Na fada ina kada ido, dariya yayi tare da tashi daga gaba na

"Tashi muje, it's twenty minutes to five".

Tashi nayi ina gyara mayafi na shi kuma ya dauka min purse dita yayi gaba, nayi ma me aikin mu sallama na bi bayan shi.
Da kan shi ya bude min front seat na shiga ina smiling dan naji dadi sosai, shi kuma ya koma drivers seat ya zauna, tun da ya kunna motar nake kallon sa ta gefen ido ganin yadda yayi wani irin kyau, adon sa is very simple yet unique and classy.

Yana sanye da coffee cashmere me shegen kyau da tsada wanda suka yi anko da ya Farooq, Baba ne ya siya musu su kuma suka kai dinkin da kan su, din kin isa very simple irin na matasa, rigar mara tsayi haka kuma tayi fitting built jikin sa, se milk and coffee hula ta tangaran da ke kan sa, hannun sa sanye da silver wrist watch din sa na zallar azurfa haka ma yatsun sa biyu na both hand na sanye da zobunan azurfar, kafar sa kuwa coffee Santiago half cover ne, yayi matukar kyau sosai, wnada kwarjinin sa da ajin sa ya kara masa kyau da daukar hankali.

Kasa yin shiru nayi se da na fadi abinda ke raina, dan kuwa muna hawa titi na juyo side din sa na kira sunan sa

"Ya Masdooq".

Ya juyo a hankali ya kalle ni tare da dage min gira alamun yes yana jina se kuma ya maida kan sa kan titi

"You're very beautiful Ya Masdooq, kayi kyau sosai".

Dariya yayi sosai abinda be fiya yi ba, hakwaran sa farare masu kyau suka bayyana,

"Beautiful kuma?".

"Yes Yaya, though mata ake fadawa haka, amma i can't help in fada maka da. Kayi kyau sosai, looking so so soooo take away".

"Please take me away, an bar miki".

Ya fada jin yadda na fadi take away din, da sauri na kankame hannu na a kirji tare da lumshe ido

"Awnnn, na karba kuma na gode sosaaiii".

Dariya muka yi duka a tare, haka nake, ina da batkwanci haka kuma am frank, ban da boye boye haka ban da nuku nuku, in abu yayi min ko a ina ne zan yaba, in kuma be min ba bana boyewa zan fada in aka nemi jin ra'ayi na.

Haka na dinag jan shi da hira muna tafiya very slow, kamar ba shi yace biyar din takusa ba, ban san me yasa ba amma lokacin wani farin ciki na daban nake ji a raina.

Can waya ta tayi ringing, daga wajen cake din mu ne, na daga muka gama na aje wayar kan palms dina, a hankali ya juyo ya kalli wayar tare da maida kai gaban sa

"So kin yi phone ba labari".

"Tsohon labari kenan ai Ya Masdooq, ku matsalar kasar da kuke ana kiran ku za'a kwashe wa mutum kudi, shiyasa nan taba kiran ku a waya ta ba".

"Uhmmm, wayo se ta bati ko?".

Dariya nayi ina dauke kai gefe, se ya cire hannun sa daya daga kan steery ya mika kan laps dina ya dauka wayar, Samsung ce me kyau, dake babu password se ya shiga dannawa a hankali rabi hannun sa na kan titi rabi na ga wayar, daidai lokacin ya shiga cikin compound din gidan s u da gate din ke bude gaba daya saboda baki.

Tun da muka shigo few mutanen dake compound din suka zubawa motar ido, na kalle shi

bayan na gama parking nace

"Please Yaya kar ka fito, bari na bude maka mota, dan na kwashi tabarakin wannan kwalliyar".

Girgiza kai kawai yayi yana kallo na da Murmushi kan fuskar sa, ni kuwa na bude kofar na fita na zagaya side din da yake na bude masa kofar ina dan dukawa irin yadda ake wa bosses din nan, fitowa yayi na maida kofar na rufe na juyo ina kallon sa baki na a tale da Murmushi, lakace min hanci yayi ya juya zuwa side din su shi da Ya Farooq.

Ni kuma na karasa wajen kannen Abba dake zaune a compound din na gaishe su, gefe daya na gaida yan uwan Baba su ma, ta daya gefen na hango group din yan mata zaune, na karasa na mika musu gaisuwa ta hi din nan, a cikin su ne naga Sa'adah, ganin da se a yanzu na tantance ta sosai.

Ba yau muka fara haduwa ba, mun hadu so biyu a gidan Aunty Luba da ta gabatar min da ita as cousin din ta yar Aunty Hauwa, dan nasan ta ita, da fara'a na dago mu gaisa lokacin se kuma na hade fuska take ganin irin kallon da take min kamar na rainin hankali, ban sani ba ko dan ta ga yadda nayi kwance jikin second Mom tana rarrashi na ina sangarta ne yasa oho.

Se again muka sake haduwa a wani Hutu da na zo gidan Hajiya Yayah, nan ma dai naga same kallo take min, ni kuwa dama akwai tsiwa, wannan yasa muna hada ido na jefa mata harara, daga nan ta daina min wannan kallon sedai tai ta hade rai ita kar a raina ya dan tana da son girma.

Sa'adah ba yarinya bace dan kuwa ta girmi Aunty Luba da shekara daya, kunga kuwa ni ta bani shekara takwas kenan, dan Aunty Luba da ya Ahmad sun bani shekaru bakwai.

Yanzu ma ganin ta yasa ban zauna ba, dan kuwa su yaran kawu muna gud time da su, na daga musu hannu suna min ihun gayu na fa ya fita ni kuma dariya kawai nake musu.

Ba karya suka fada ba, ni kaina na san nayi kyau matuka, kayan sun karbe ni haka kalar ta zauna a jiki na, dama kuma na san me da me ne ke min kyau sosai, na san kuma irin kwalliyar da nake yi da take fitting kowane occasion, wannan yasa da wuya kaga na yi kwalliya ba'a tanka ba, wannan yasa Hajiya Yayah koya min yin addu'a kafin fita daga gida, haka kuma yin A'uzu bikalmatillah ina shafewa a fuska ta kafin na fita.

Ko da na shiga ciki nan ma haka ake ta yabon kyan da nayi, Hajiya Yayah kuwa se hararata take, se da nan fada mata nayi addu'a ta sannan ta janye hararar, ta shiga jerin masu yaba min.

Ina jin dadi sosai in naga nayi kyau ana yaba min, hakan na burge ni, yana kuma sani jina on top, hakan yasa tun da Ya Ibrahim ya gane kullum cikin koda ni yake, hakan kuma na cikin dalilan da yasa nake son sa.

Taro yayi kyau sosai, se kuma da aka fara hotuna ne na tuna ai waya ta na wajen Ya Masdooq, ina son zuwa karba ina tsoron jarabar Ya Farooq, duk da an dade ba'a hadu ba amma ban manta halin shi ba.

Ganin lokaci naa kurewa kar surprise din da na shirya musu ya lalace yasa nayi shahada na nufi part din nasu, tun daga nesa nake jin hayaniya alamun su da abokan su ne a ciki, kamar na juya se kuma tuna plan dina yasa na kai hannu na kwankwasa kofar falon.

Tun ina yi a hankali har na buga sosai dan sun cika dakin da hayaniya da kyar su ji ni, se lokacin aka amsa min da Yes.
Na tura kofar a hankali tare da shiga da sallama, se yuuuu duka idanuwan abokan su suka yo kai na, se kuma maganganu suka fara tashi

"Wow Masha Allah".

"Wow kaga wata kyakkyawa".

"Farooq wace wannan me kyan haka?".

"Tabarakallah Masha Allah".

Kowa dai da wanda yake fada, ni kuwa tuni na tsargu musamman ganin yadda ya Farooq ya hade rai yana harara ta, shima Ya Masdooq ya dan hade tasa fuskar duk da be kai ya Farooq ba, ya zuba min ido ko kiftawa bayayi, a hankali na dan dago na kalle shi tare da marairaicewa, se ya saki fuskar ya kuma dubi abokan su biyar dake zaune

"Kanwar mu ce, Nu'aimah".

Ina jin haka na tsuguna tare da gaishe su in plural, ban jira amsawar su ba na karasa wajen Ya Masdooq ina duban fuskar sa, dan ko kadan naki kallon ya Farooq sanin waye shi...................✍️.

Yanzu n fa zamu tsunduma cikin labarin Aimah ka'in da na'in, wancan duk sharar fage ne.

To You my commenters, Ina ganin maganganun ku na yabo, jinjina har ma da views din ku, ina godiya matuka da hakan, dan kauna ce sila, Allah ya bar mu tare Amin 💕❤️.

Vote
Comment

Share fisabilillah.

Ouummey 📚✍.

Ouummey 019  [ 28/06/2024 7:27pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍ Oummey
Free book!!!

Ouummey 019

Page 1️⃣9️⃣

___________________A gefen sa na zauna dan shi kadai ne zaune kan one sitter, na dan jingina jikin kafadar sa ina marairaice fuska

"Ya ka manta ka tafar min da waya ta dazu, ina so in yi hotuna, kuma zan making call shine nazo karba".

Sighing yayi, shi se ma yanzu ya tuna da wayar, ko da ya karba numbers din shi ya zuba ya kira dan ya samu number ta, se kuma da ya kira yaga ashe tana da number ta sa, so be bata ba ashe.

Kasa na sake yi da magana jin har lokacin ina jin kaifin idanun ya Farooq a kai na

"Yaya Please save me daga Ya Farooq, se mugun kallo yake min irin na zamu hadun nan, Allah

kuma duka na ze yi".

Dagawa yayi ya saci kallon Farooq din, se kuwa ya samu har lokacin hararar ta yake, dan haka ya mike tare da kama hannu na na tashi muka shiga bedroom din sa.

Komai na dakin is milk in color, se curtains dake da ratsin coffee color, ko ina na dakin neat ga kamshi dake tashi me dadi da sanyi.

A can falo kuwa muna shigowa wani abokin ya Farooq me suna Haisam ya gyara zama

"Guy da gaske yarinyar can kanwar ku ce kamar yadda Man yace?".

"Hala baka ga kamanni ba?".

"Not at all, kawai dai ina son tabbatarwa ne dan yin kamun kafa da ku, Allah yarinyar tayi min naji ina son ta sosai, kuma auren ta zan yi in har kun amince min".

Dayan dake zaune tare da ya Farooq a three sitter yayi tsaki

"Haba guy, ya zaka min shigar sauri, Nima fa tayi min magana kawai ka riga ni yi".

Dariya raguwar suka saka suna fadin

"Kowa a nan tayi masa, amma tun da ya riga mu magana se mu mun masa solidarity ".

Magana ya Farooq ze yi se ga mu mun sake fitowa har lokacin yana rike da hannu na daya hannun sa kuma waya ta ce rike, wannan yasa duka suka yi shiru mu kuwa muka yi wajen kofa, ya bude tare da bani waje na fara fita shima ya biyo baya na.

Ya Farooq na ganin rufe kofar mu ya dubi abokan nasu

"Kanwa tace uwa daya Uba daya dan itace autar mu, haka kuma matar Masdooq ce insha Allah, so you guys should take your eyes off her".

Da mamaki duk suke kallon sa, ya watsa hannuwa a iska yana cewa

"Oh baku san Masdooq cousin dina bane ko, to we're cousins ba wai siblings ba".

Dukkan su mutuwar zaune suka yi dan basu taba sanin ba uwa daya Uba daya ne Masdooq da Farooq suke ba.

A can waje kuwa muna fita ya saki hannu na tare da miƙa min wayar, na karba ina Murmushi

"Thanks so much Yaya, ka cece ni daga wancan zakin ".

"Waye zakin?".

Dafe baki na nayi se kuma na saka dariya

"Kash nayi subutar baki, ai na manta dan biyun ka ne, amma wallahi ya Farooq is more like a lion saboda fadan shi, dan Allah kace ya rage ".

Juyawa yayi yana fadin

"Bari in isar da sakon ki tun yanzu ".

Zaro ido nayi tare da fadin

"Na shiga uku". Se kuma na kwasa da gudu na bar wajen, Ya Masdooq ya girgiza kai ya koma wajen jama'ar su.

Hotuna sosai muka sha abin mu, duk inda Aunty Luba tayi kuwa ina biye da ita kamar wata jela, Babyn ta kuwa me sunan Hajiya Yayah wato Mimi na hannu na naki bawa Kowa ita.

After magrib se ga sako na ya iso, na fita na karba muka cigaba da tsare tsaren mu da Aunty Luba, ana dawowa daga sallar magrib se wutar gidan gaba daya ta dauke, se ta cikin garden kawai, na dauki mic da muka tanada tun tuni na shiga calling attention na jama'a zuwa garden din da nake tsaye.

Aikuwa within minutes se ga shi an hadu, wani irin decoration me kyau muka saka masu decoration suka mana, ga katon cake kan table wanda shine sakon da aka kawo min dazu.

Gurin yayi kyau ya tsaru matuƙa, an kawata shi sosai ta yadda yayi kamar ba'a gidan ba, an jera palstic chairs jikin kowane table, haka kuma ga abinci nan kan each table a plates, each table kuma mutum biyar yake dauka.

A can high table kuwa kujeru biyu ne da suka sha ado, a kan table din gaban chairs din cake din yake, gefe da gefe flowers ne masu matukar kyau da kamshi, light na wajen na blinking multicolor haske, komai yayi perfectly as we planned.

A lokacin su Ya Salman suka karaso shi da ya Najeeb, matar ya Najeeb ma tana nan tare da mu dan yayi aure last year, yanzu haka ciki gare ta wata biyar.

Na ja gefe na kira Ya Masdooq nace masa akwai kaya a wardrobe din su kowanne dan Allah yayi convincing ya Farooq su saka su fito yanzu ana jiran su, ban tsaya sauraren amsar sa ba na kashe kiran da sauri dan kar ya fara min tambayoyi.

A zuciya ta addu'a nake Allah yasa su sako kar su bata mana tsari.

Allah kuwa ya amsa min, bayan miti ashirin na sake kiran sa, lokacin har an zazzauna, kuma cikin ikon Allah seats din sun isa, har ma sun ragu.

Se gasu sun fito sanye cikin caramel brown 3 pieces suits, fadar irin kyan da suka yi ma wallahi bata baki ne, musamman Ya Masdooq da har gyara gashin sa yayi ya sake masa style.

Se kuwa sassanyan baitin wakar home sweet home ya shiga ta shi ta speakers din da Aunty Luba tayi connecting da wayar ta, suna karasowa under thatches da aka sa seat din su kuma flowers suka shiga falling, kowa ka gani bakin sa a bude yake da fadin wow, da masha Allah saboda yadda abin yayi kyau ya dauki  hankali, a haka suka zauna seats din su gwanin sha'awa.

Ya Ahmad ne yayi Mc, duk da cewa yana makaranta muka sanar da shi tsarin amma se da ya dauki excusee ya zo for today and tomorrow, jibi ze koma, da yawan mutane ma basu yi tsammanin ganin sa ba se ga Shi kuma.

Lokacin da aka zo yanka cake kuwa da ni da Aunty Luba muka fita muka taya su yankawa, ina by side din ya Masdooq Aunty Luba by Ya Farooq, aka irga one two three aka yanka, ana gama yankawa aka sa tafi, ban jira umarnin Mc ba na ciro gutsiren cake da wuka na nufi bakin ya Masdooq, be buɗe baki ba ya tsaya kallo na, na bata fuska tare da smirking, se kuwa ya bude bakin yana Murmushi, na kuwa danna masa katon cake din, aikuwa ya bata masa gefen baki, ba'a sa hannu na rufe baki na ina dariya haka ma raguwar yan uwa, ai kuwa shima ya sa hannu ya lakato ya goga min a cheeks dina aka kuma sa dariya.

Matsawa nayi gefe na haska da mirror na goge amma se ya kuma shafe min ragowar na hannun sa, aikuwa na bata fuska na fara buga kafa a kasa, da sauri ya daga hannun sa alamun saranda, se kuwa na saka dariya nima, na gyara fuska ta a ka fara hotuna.

Wasa wasa ba'a tashi ba se after Isha, ko da aka je aka yi sallah dawowa aka yi aka ci abinci, se da Baba yace ya isa haka nan sannan aka tashi , amma fa abin ya kayatar sosai.

Ni kuwa tuni na cafe wayar ya Masdooq tun selfie da ya mana na ga wayar na da Camera, kafin kace me na hada hotuna fin dubu biyu a wayar sa, kar kuyi mamaki, maganar gaskiya ina da son hoto, ya Ahmad na cewa wai ina da cutar hoto, dan in maka hoto dubu daya zuwa biyu da kaya kala daya ba abin mamaki bane, Styles ne zan tayin su kala kala, na hankali da na hauka, haka ko daga bacci na tashi zan iya yin hoto ni ban da damuwa.

Kin bin Mama nayi nace zan kwana a gidan, duk da ba zan so hakan ba da dan ya Farooq amma saboda na tura photos dina zuwa waya ta dole na hakura, suka yi sallama suka tafi wanda itace karshen tafiya, Aunty Luba da su ya Najeeb tuni Baba ya sallame su, ragowar yan uwa ma duk yace dare yayi a tafi gida.

Ni na taya mama da house help din su Mama Ladi muka gyara gidan sannan na tafi dakin da ke kusa da na Hajiya Yayah inda nake zama in na zo kwana gidan, na cire kaya nayi wanka dan duk maiƙo nake.

Kayan bacci na saka tare da jona waya ta caji, ta ya Masdooq kuwa na cigaba da kallon hotuna na ina goge wanda be yi kyau ba, wanda da kyar nake yin hakan dan ni ban ki duk ace sun yi kyau ba.

Ina cikin haka bacci yayi gaba dani saboda tsabar gajiya, shi kuma a can bangaren Ya Masdooq na ta zuba idon ganin ta inda zan bullo ba shi wayar sa shiru, ganin dai da gaske ba kawo masa zan ba yasa yayi shirin bacci ya kwanta, se kuma ya tuna ze tura wasu files zuwa email din ma'aikatar da Baba ya sama masa aiki.

Dole ya tashi ya zura slippers din sa ya fita zuwa cikin gidan, kayan bacci ne jikin sa, riga da wandon ta three quarter, be samu kowa a falon ba dan Hajiya Yayah na wajen Baba, ita kuma Mama Ladi ta wuce dakin ta, se ya hawo steps din na bangaren Hajiya Yayah, dan shi Baba na sa na bangaren gaban gidan ne nata kuma na baya, stairs din daya ce amma akwai inda hanyar ta rabu, zuwa side din Hajiya Yayah ko Baba.

Dake yasan daki na direct can yayi, yayi knocking har so biyu shiru, se ya Murda handle din a hankali yan kallon kasan dakin, ganin light a kunne yayi tunanin ban yi bacci na se ya shiga yana furta sallama a harshen sa.

Se da ya karaso gaban bed din sannan ya lura bacci nake, ya duba bedside ko ze ga wayar sa amma bata nan se tawa dake charge, duk inda yake tunanin ze gan ta babu ita, se ya dawo bakin gadon ya zauna tare da fara kokarin tashi ne, se kuma ya ganta a karkashin hannu na ta zame.

Dan haka ya jawo abar sa, yana dannawa kaykkyawar fuska ta me ɗauke da dariya ta bayyana kan screen din, nayi kyau sosai a hoton dan ban ma san an dauka ba, Aunty Luba ce da na bawa ta dauke ni hoto tayi min shi ina magana da wata yar uwar mu, se kuma ga shi hoton yayi kyau fiye da zato.

Ya kurawa pic din idanu kamar me analysing din sa, tsayin lokaci kafin ya janye idon sa daga kan hoton ya maida kai na, ina kwance ina bacci gashi na na baje kan pillow dan ciwon da kai na ke yi yasa ban sa hular bacci ba.

Ya matso kadan tare da sa hannu ya janye min wanda ya ba zo gaban fuska ta, sedai be zare hannun ba ya bar shi kan gashi na tare da tsurawa fuska ta ido.
Ya dade a haka kana ya zare hannun sa tare da min addu'a ya shafa min a kaina yana appreciating laushin gashi na, gashi na daya daga cikin abinda yake so a wajen mace, ba dan komai ba se dan ya nitsa hannun sa ciki ya kuma dinga gyara mata.

Da kyar ya zare hannun sa daga kai na ya dauki wayar sa ya fita daga dakin bayan ya kashe min fitila, yana fita ina farkawa dan kuwa lokacin bana bacci cikin duhu, ba bacci ba ma kwata kwata bana san duhu ne a rayuwa ta, shiyasa duk yadda Mama tayi se hakura tayi ta kyale ni nake bacci na a haske, dan ana kashe fitila nake farkawa kamar dai yanzu.

Kamshin sa da naji ya karade dakin ya bayyana min shigowar sa, se na lalubi inda nake tunanin ganin wayar sa amma ban ji taba, so se na gane wayar sa ya shigo ya ɗauka.

Se da na tashi nq kunna haske sannan na sake komawa na kwanta.

Da asuba ina idar da Sallah na tashi na gyara daki na, dan ba kamar gidan Mama ba, nan hajiya Yayah bata bari Mama Ladi ta gyara min, a can kuwa me aikin mu ke gyara min, iyakaci in ci, in dafa in na so se kuma in kwanta in huta, se kuma aikin snacks dina, shima ba da san ran Mama ba sedan ganin ina so.

Ina gama gyara daki na na kunna turaren wuta kana nayi wanka na canja kaya, dan Hajiya Yayah bata daukar ana mata yawo da sleeping dress a gida, can kuwa in ban so ba se in kai karfe sha biyu zuwa ɗaya ban canja su ba, kuma dan wulakanci fa zan yi wanka, amma memakon na sa kaya se in saka wasu sleeping dress din.

Ina shiryawa na dora karamin veil a kai na na fita zuwa falon Baba gaiuwa, can na tadda ya Farouk, na gaishe su, Hajiya Yayah, Baba da ya Farouk.

Duk a takure nake ba yadda na saba ba saboda ya Farouk dake wajen, gane haka yasa Baba ya sallame shi, aikuwa se gashi na saki jiki muna ta fira da Baba, kai baka ce ba shi ya haife ni ba.

A lokacin na fada masa shagon make up da gyaran jiki da nake so a bude min, yace to za'a bude amma ba a hannu na za'a bar shi ba dan nayi yarinta, za'a bude dai da sunana, kuma nawa ne amma za'a dora masu kula da shi, ni Kuma zan iya shiga cikin ma'aikata.

Kamar na rungume Baba dan murna se dai sanin shi da Hajiya Yayah waye yasa kawai na kama hannun sa na kankame ina murna ina ta masa godiya da addu'a, Hajiya Yayah na daga gefe tana taya ni fuskar ta dauke da murmushin farin ciki...................✍️

Vote
Comment
Share fisabilillah.

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 020  [ 29/06/2024 7:36pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Oummey
Free book!!!

Ouummey 020

Page 2️⃣0️⃣

____________________Haka kuwa aka yi, Baba ya kira ya Masdooq a gaba na ya bashi umarnin nemo shago me kyau da da zama business wise a siya, take kuma amsa masa.

Farin ciki ya cika ni matuka, na tafi daki da gudu cikin jin dadi na kira Abba na sanar masa, ga dinga tsokana ta da kaga ƴar Baba ni kuwa ina ta dariya baki na ya kasa rufuwa, na kira Mama take cewa ai ta ji mu da Baba, itama ta nuna farin cikin ta, the next da na kira Ibrahim ne.

Na san zaku ce ina yake ban gayye ce shi walima ko in ce partyn su Ya Masdooq ba, na gayyace shi amma se yace min in Yi hakuri baze samu zuwa ba, yana da tafiya ranar.

Ban ji dadi ba amma na taya shi da addu'a na shiga harkoki na, wayar na ta ringing amma ba'a dauka ba, miss call uku se na kyale shi da tunanin baya kusa ne, whenever ya gani ze kira ni.

Who next zan sanarwa, guess who? Aunty Luba, if not her not who?.

Aikuwa har ma tafi ni farin ciki, vedio call ta kira ni bayan ya kashe kiran da na mata, muka

zauna muka dinga tsara yadda tafiyar da komai na shagon ze kasance, nan tayi sugessting wata kawar ta, tace tun suna school itama haka take da son makeup, yanzu haka she's way close to zama professional, sedai ita a gida take yi, so hiring her would be a good choice.

Aunty Luba na nata business din da Ya Salman ya bata jari, dan duk da ta gama school ya hana ta aiki yace baya so, se ya bata jari take business, tana shigo da duk wani high class textiles na mata, a gida take Business din se kuma online, amma yanzu tana kokarin bude shago itama.

Sedai kafin nan muka yanke shawarar za'a dinga kai kayan can, tun da waje ne na jama'a kuma manyan mutane insha Allah hakan ze taimaka ta kowane angle.

Da wannan muka yi sallama bayan ta kanga min camera kan fuksar baby Mimi na mata wasa da surutai kamar mara kai, ma aje wayar ina jin wani madaukakin farin ciki a raina.

Ina son Baba matuka gaya, shima kuma yana so na, ya dauke ni kamar koma fiye da Aunty Luba, dan yana kara wa Abba a kan ta sosai, amma ni kam asalin gata yake gwada min, wuyar ta ban furta ina son abu ba in ya duba yaga ba shi da wani illa gare ni ko will be of helpful wa rayuwa ta to ze min shi, dan yanzu haka shagon da nake zuwa aikin cake and snacks din nan ma shi ya samo min, me wajen yar abokin sa ce.

Ina ta wulla ƙafafuwa daga kwance a kan gado ina rayawa a raina shagon snacks and more will be the next after na make up, fatana Allah ya sa mana albarka kawai.

Ranar ban iya na koma baccin asuba da nake yi ba saboda murna, bayan na gama kiraye kiraye na da kuma murna ta na tashi zuwa kitchen, a can na tarar da Mama tana kokarin hada breakfast, na sa hannu muka yi tare, muna aikin muna hirar mu gwanin sha'awa, sedai fa kome nake yi cikin nutsuwa da takatsantsan nake yi gudun fadan ta, dan bata hesitating yi min fada da gyara in na kuskure, haka kuma bata bada fuskar da nake kawo raini, ba ma ni ba kowa ma bata bashi fuskar da ze kawo mata wargi ba.

A haka muka gama, ta bar min shirya dining ta wuce daki, tayi wanka ta canja kayan jikin ta sannan ta fito, lokacin nima na shiga nayi wanka, na saka A-shape na wani shaking material golden color, plain din ki ne amma yayi min kyau, na yi daurin Zahra Buhari da ya fitar da kyan fuska ta.

Ban Sa komai a face na ba se chapette amma nayi kyau matuka, a haka na fito falo muka zauna ina dannawa waya ta ina duba social sites dina na snacks and cake, da kuma na make up dina, na duba new orders da muka samu, da kuma yadda ake hailing make up dina na jiya.

Jin saukowar Baba yasa na aje wayar ina masa Barka da fitowa, ya amsa da fara'a na ja masa seat ya zauna.
Lokacin ne kuma Hajiya Yayah ta kira su Ya Farooq kan su karaso muyi breakfast.

Ita fa Hajiya Yayah a gidan ta dole ne mutum yayi breakfast lokacin da kowa ze yi, sedai in ba shi da lafiya, haka kuma ba'a mata wani zabe zaben kaza zan yi break da shi, a dafa min kaza and on kamar yadda muke yi a gidan mu.

Tun da suka shigo idanun sa na kai na, ina dagowa amsa sallamar su idanun mu suka yi locking ya kashe ni da sassanyan murmushin nan nasa, ban yi wata wata ba ni ma na maida masa, ban fa san sanda nayi din ba, tsabar kwarjini da charisma din sa yasa naji kawai nima ina son maida masa.

Suka karaso wajen ku, har kasa suka duka suka gaida su Baba, kana ya ja kujerar kusa da ni ya zauna, shi kuma ya Farouk ya zauna kusa da Baba.

Cikin dar dar na gaida Ya Farooq, ya amsa min fuksa a hade, na dawo da duba na kan Ya Masdooq na gaida shi ƙasa ƙasa, ya amsa min kamar yadda na gaida shi, se kuma ya sake kasa da murya

"Feel free, ki saki jikin ki ina nan ba zan bari ya miki komai ba".

Na lalle shi ya lumshe min ido reassuring me da su, na sauke ajiyar zuciya a hankali na shiga serving din su, ya Farooq na fara sawa se Ya Masdooq din, ita kuma Hajiya Yayah ta sawa Baba.
A hankali muke cin abinci har muka gama, aka yi hamdala kowa ya tashi zuwa nasa wajen.

Wuni guda nayi a gidan, ban tafi ba se da na tabbatar na kwashe pics dina zuwa waya ta, daga nan nayi wa su Baba sallama Ya Farooq ya dauke ni zuwa gida dan zasu je gaida su Mama.

Suna gaba shi da dan biyun da suna hirar su ni kuma ina zaune a baya ina chatting da sanyin rai na, yana yin parking a compound din mu na wuce daki na bayan na shiga na sanar da Mama dawowa ta.

Ban kuma fitowa ba har suka tafi, haka kuma cigaba da rayuwa, duk sanda muka hadu da Ya Masdooq a ko ina ne se ya bani attention din da har se an yi noticing din mu, a gaban kowa yake nuna am special to him, ni kuwa a wautata ban dauki hakan a komai ba se kula da kauna na yan uwan taka, hakan ya sa nima na ke kaunar shi sosai a matsayin favorite brother na.

Duk abinda nake so take nake kiran shi, and nan da nan zaku ga an min, sedai fa shima kamar Baba ne, komai nw bukata in har yana da illa gare ni ko ze taba kima ta base yi ba, ya san ways da yake bi da ni cikin sauki ya lallashe ni.

Haka kuma sa'i da lokaci ze hade rai ya tsaurare min, in kuwa yayi hakan to fa kome taurin kai na se dai nayi hakuri na sauka amma shi kam be barin ra'ayin sa, wannan yasa na gane daga ya yi irin haka bana ma jan maganar, nake hakura da kome ne.

Ya Ibrahim yasha min ciwon baki kan Ya Masdooq, amma na nuna masa ba abinda yake tunani bane, yaya na ne and ba taddawa zan iya rabuwa dashi, haka ya gama ciwon bakin sa ya hakura ya kyale ni.

A lokacin ne kuma yayan Abba ya same shi kan dan kanin su mabiyin Abba na sona, haka kuma a gidan sa akwai cousin din mu Ya Khalid shima yana so na, so be ce dole se a cikin su ba amma na fitar ko a fitar min da miji dan har sun fara fada da neman yin gaba a tsakanin su, duk a kaina dan haka in nayi aure za'a sami matsala.

Wannan yasa Abba ya kira ni ya zaunar da ni kan batu na da Ibrahim dan kowa ya san maganar mu tuntuni, ban boye musu ba na sanar musu yadda muka yi da Ibrahim kan haihuwar matarsa, Abba be ki ba yace amma in turo masa Ibrahim din dan ya turo iyayen sa a zo ayi magana, se a sa ko shekara ne, lokacin matar tasa ta haihu har ma baby yayi kwari se a yi bikin.

Na gamsu da bayanin Abba, dan haka ban jira komai ba na bukaci ganin sa, sedai ya bani uzurin baze sami zuwa ba, na ji ba dadi amma haka na danne na sanar da shi sakon ta waya, ya amsa da ze zo insha Allah.

Na kashe wayar batare da na jira mun yi hira kamar yadda muka saba ba, gaba daya bana jin dadin wannan sabon Ibrahim din, ya riga ya saba min da kan sa, ko yaushe he's available min, Amma yanzu ganin sa se Sa'i da lokaci, wani sa'in hatta waya ma se mu wuni ba muyi ba, ko in na kira shi ya bani excuse, in Kuma ya kira ni ba wnai jimawa ana hira ze kawo excuse ya kashe.

Se dai in na duba ai yanzu he's committed more than before, Dan haka in dai zan yi adalci dole na masa uzuri, wannan yasa nake dannewa nake hakuri.

Ya Ibrahim be zo ya sami Abba ba kamar yadda ya bukata, daga karshe ma dana kira shi se ya sanar min baya kasar, amma in yadawo ze je, wasa wasa ya dinga min wasa da hankali, ga shi ni kuma Abba na jiran ji daga gare ni, Nima se na shiga wasan buya da shi.

Ban san yadda aka yi ba Abba da yayan sa suka shirya zuwa family house din su Ya Ibrahim, suka sami iyayen sa maza da batun mu.

Sedai abinda suka fada ya matukar bawa Abba mamaki, be firgita ba se da aka kira Ibrahim din a gaban shi ya kuma maimaita irin abinda iyayen sa suka fada.
Haka su Abba suka dawo gwiwa a sage, kuma shine karo na farko da naga fushin Abba a kai na.

Karfe takwas da rabi na dare ina duba social pages dina Ina jin dadin yabon mutane kan makeup skill dina Mama ta shigo ta kira ni Abba na kira na, na kashe datar tare da saka charge na bi bayan ta.

A falon sa na same hi zaune yana zaune cikin three sitter ya dora kafa daya kan daya yana girgiza ta, yanayin zaman sa da kuma fuskar sa ze bayyana maka tsananin ɓacin ran sa.

Na shigo na gaida shi, ya kokarta ya saki fuska duk da ba sosai ba ya amsa min, na zauna kusa da shi kan kujerar kamar yadda na saba se dai yace na sauka na koma kasa, abinda be taɓa faruwa ba, dan basu damu da na zauna cikin seat ba dan suna kai.

Na sauka kasa kai na na daurewa na mamakin me ya faru?, Se kuwa naji Abba ya kira full name dina, kamar yana tantamar ko san tabbatar da suna na ne ko ba nawa ba.

"Nu'aimah Bashir".

Na dago na kalle shi sosai, se kuma na amsa da na'am, ina jin gaba na na faduwa ba gaira ba dalili.

"Ina so daga yau ki manta da yaron nan Ibrahim, bana san na kuma ganin ki da shi, kin ji me nace?".

As a good girl ya kamata na tambayi Abba dalili? Ku bani amsa Please.

Na dago a firgice kuma a gigice na dubi Abba da shima idanun sa ke kai na

"Amma saboda me yasa Abba?, Ibrahim na so na, ni ma kuma ina matuƙar kaunar sa, me yasa zaka raba mu?".

Abba tai tsai da idanun sa a kaina kamar me neman wani abu a fuska ta kafin ya jinjina kai ya maida duban sa kan Tv, se na maida duba na kan Mama wai ko ta san meke faruwa, se ta girgiza min kai alamun bata san komai ba, dan haka na sake duban Baba murya ta na rawa ina shirin fashewa da kuka

"Dan Allah Abba ka fada min me Ya Ibrahim ya maka ka fadi haka bayan kasan Irin yadda nake son sa, in ba haka ba ni Allah ba zan rabu da shi ba".

Wani Murmushi Abba ya saki wanda kana gani zaka san bana farin ciki bane yace

"Ko da kuwa ace iyayen sa sun ce baze aure ki ba?".

"To akan me zasu ce ba ze aure ni ba bayan yana so na, in Kuma dan yar su da yake aure ne ai se da ya fada mata batu na, in ban da ma na yarda ze aure ta ne?".

Zuwa wannan lokacin na gama kular da Baba dan haka a fusace ya dubi Mama

"Ki fadawa ƴar ki ta shiga hankalin ta, dan kuwa yaron da take wannan rashin kunyar a kan sa naje ni da Yaya Kabiru gidan su akan batun auren sa da ita, ganin na nemi yazo yana ta walawala yasa muka je muka sami iyayen sa, sedai ko da suka gamma sauraren mu se suka kada baki suka ce su basu ma san wata yarinya me irin sunan ta ba, haka kuma ko akwai ta to gaskiya kar mu tsaya jiran dan su dan ba aure yayi yanzu ba, kwata kwata ma yaushe yayi auren da ze kara wani, abu ko shekara ba'a rufa ba, kuma ko da ace an jima su babu tsarin auren mata biyu a family din su, daya ce kuma in mutum yayi ta sedai mutuwa dan ko rabuwa basa yi, nayi mamakin jin wannan zancen dan haka nace kar su yanke hukunci, su fara tuntubar yaron, ba su Musa ba suka kira shi a gaba na a kan ido na, amma yaron nan yace ai shi ya fada miki babu aure a gaban shi yanzu, bayan sun kashe kiran suka ce na bawa yata hakuri na dai ji me yace ko, dan haka na mata aure kar ta tsofe garin zaman jiran gawon shanu".................✍️.

Tohm, fans ga fa Ibrahim ga Aimah, ga kuma yadda Abba yayi da waliyyan sa, me kuke tunanin ze faru? Shin AIMAH zata yarda ta karbi ƙaddara ta rabu da Ibrahim ko kuwa yaya?

Vote
Comment
Share fisabilillah.

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 021 [ 29/06/2024 7:38pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Oummey
Free book!!!

______________________Abba ya kare fada with bitterness in his tone, abin ya masa zafi, fuskar sa ta nuna haka ma idanun sa.

Wani irin kallo na shiga yiwa Abba, sam ban yadda Ibrahim zeyi abinda Abba ya fada ba, taya ma ze fara, me ze sa yayi hakan bayan ya san yadda muka tsara.

Wait to ma shi Abba wa yace yaje, ai dama dole waliyyan Ibrahim suce ba aure ze yi ba, tun da dama ba zasu bari yayi aure ba yar su na da tsohon ciki, kar tashin hankali ya jawo mata wata matsalar! Na ayyana a raina.

"To amma Abba ai da baku je ba, nifa tuni mun gama tsarawa dama ba yanzu zamu yi aure ba se matar sa ya haihu, tun da kun ga ai in yayi aure yanzu da take da tsohon ciki be mata adalci ba, na san wannan ne yasa Ibrahim ya fadi haka, su ma kawunan sa haka amma ba wai dan ba zasu bari ya aure ni ba, bari ku gani, ta na haihuwa da wata biyu zasu zo neman auren".

Takaici, bakin ciki da ɓacin rai ne ya cika Abba, ya juya ya dubi Mama da fuskar ta take ba dadi alamar itama a bin ya bata mata rai.

Kafin yayi magana ta riga shi da fadin

"Nu'aimah har yanzu ke yarinya ce, annan mahaifan Ibrahim ba zasu bari ya aure ko ba, shima kuma ba shi da niyyar hakan, ban sani ba tsoro ne yasa ko kuwa soyayyar matar sa ce, amma dai tabbas baya yin ki yanzu, kiyi hakuri, na sani da zafi amma Allah ze baki wanda ya fishi".

Dariya nayi kafin kuma na bata fuska ina kallon Mama, da wannan Muryar tawa ta shagwaba da sangarta nace

"Ni dai kar ki min baki, kuma babu hakurin da zan yi dan kuwa Ibrahim ze aure ni, ji Mama har wani fada kike wai da zafi kamar irin ya taɓa faruwa da ke".

Me ya kamata Mama tayi a wannan lokacin? Ku sanar min please.

Mama ta girgiza kai kawai bata ce komai ba, na maida duba na kan Abba, baro baro nake ganin bacin ran sa amma ni ban damu ba, damuwa ta Ibrahim da aka ce wai ba ze aure ni ba

"Kar ka bata ranka Abba, let's wait for 8 months, a gaban ku Ibrahim ze zo ya nemi aure na, and please kar ku kuma cewa ze bar ni dan Allah i can loose control".

"In har kika ga kin aure shi kuwa se dai in bana raye ko kuwa kin canja wani mahaifin ba ni ba, ban taba tunanin ba ki da hankali ba nu'aimah se yau, in fada miki irin wulakancin da aka yi mana a gidan iyayen yaron nan amma ke bata haka ma kike yi ba, an wulakanta mu, an fada mana maganganu marasa dadi amma kike ikirarin auren dan su, to let me make it clear to you wallahi ba zaki taba auren Ibrahim ba".

Wani irin mikewa nayi tsaye, ina jin numfashi na na sama kamar wadda ake kokarin rabawa da numfashi na

"Wallahi se na aure shi Abba, kawai dan rashin adalci se ace ba zan auri wanda nake so yake so na ba, bayan ku kun auri wanda kuke so, to wallahi ban zan yadda ba".

Mikewa Abba yayi jikin sa na rawa yake fadin

"Ni kike fadawa haka Nu'aimah, ina fadin ba zaki aure shi ba kina se kin aure shi? To na ga yadda zaki aure shin, dan na fada miki se dai in bana raye ko ki canja wani uban".

"Allah ma yasa ina da Baba, se in koma gidan sa na san shi tun da yana so na baze ce.....".

Saukar marin da na sha a karo na farko daga hannun Abba yasa magana ta ta katse, haka kuma jina ya dauke na sakanni, yana dawowa kuwa na saki ihu da kuka, na fadi na shiga birgima a wajen, kuka nake da ihu tare da birgima janar yar shekara biyar ba sha takwas ba, Mama na zaune ta zuba tagumi tana kallo na, Abba kuwa takaici ya sa yana tsaye yana duba na cikin bacin rai, ganin abun ba na kare bane yasa ya fusata ya cisgo wayar jikin receiver, ban aune ba se jin saukar bulala na yi a jiki na, ai tuni na tashi daga birgimar da nake na fada kan Mama na kanainaiye ta ina ihu da soshe soshe, hankali tashe Mama ta shiga kare ni tana bawa Abba hakuri.

Da kyar ya hakura ya shiga nuna ni da wayar
"Wallahi aure zan miki, tun da har kin san kiyi min rashin kunya da rashin mutunci a kan namiji to kuwa aurar dake zan yi na ga karshen iskanci, ba dai ni ba, kwaffff".

Yayi kwafa ya yar da wayar ya shige bedroom din sa ya mako kofar da karfi har se da na tsora ta, Mama ce ta kama ni zuwa daki na ina kuka, fuska ta tayi kaca kaca da ruwan hawaye da majina, idanu na sun rine saboda kuka, haka kumatu na yayi jajir duk da ba fara bace ni.

Kan bed Mama ta zaunar dani ta shige toilet dina da sauri ta hađa min ruwan wanka me dumi, ta kuma dawowa ya kama ni kamar wata wadda ta haihu ko kuma taji mugun duka ko take da rauni a kafa, lallai Mama tafi kowa contributing wajen samun kai na cikin halin da na kasance

haka kuma tafi kowa nuna kyama gare ni da blaming dina da bata musu suna.

Ita ta taimaka min nayi wankan ina ta kukan sangarta da kiran sunan Ibrahim, a yadda nake wannan kukan iskancin kama ta yayi ace an samu wani tsayayyen yaci uba na la'ada ciki da waje, amma se aka samu akasi bani da wannan tsayayyen, Ya Salman ne kuma Mama ta taka masa birki, Ya Farooq kuwa bata ma bari ya matse ni saboda zafin sa.

Ta haɗa min jiki na da towel ta taimaka min na saka sleeping dress sannan ta kwantar da ni kan bed, ta ɗora kai na kan laps din ta tana aikin rarrashi da ririra ta ni, ban yi shiru ba se da ta yi min alkawarin ba zata bari a raba mu da Ibrahim ba.

Ko da ta fita kuka na cigaba yi abina ina gani ai Abba ya dena so na yanzu, ban da haka me yasa ze ce na rabu da Ibrahim, bayan ya san yadda an shaku da shi, na ke kuma so da kaunar sa tun kan na san kai na, se kawai rana tsaka yanzu ace wai in rabu da shi, kai wallahi ba zan rabu da shi ba ko me za'a yi.

Haka nayi ta tunane tunane ina hawaye, daga karshe dai na ji ina bukatar yin maganar da wani, Aunty Luba ce ta fara zuwa kai na, sedai sanin Ya Salman na gida in yaji maganar kuma shi ma goya wa Abba baya ze yi dan dama tun farko be san ya Ibrahim, se na ture ta na shiga laluba waye next, se kuwa sunan sa ya fado min, se kuwa na jawo waya ta da sauri na shiga neman number sa, idanu na dishi dishi nake gani tsabar kukan da nasha.

Ringing tayi ta gama be dauka ba, na sake kira yanzu ma be dauka ba, se na daga kai na dubi agogo, it's five minutes past eleven, ganin time be sa na fasa sake kiran ba, se kuma yanzu yayi picking.

Daga jin muryar sa zaka san daga bacci ya tashi, ban bawa hakan muhimmanci ba na fashe masa da kuka, cikin tashin hankali ya yaye duvet din dake jikin sa ya tashi zaune, gaba daya tunanin sa wani abu ne ya faru a gidan.

Da sauri ya dira daga kan bed zuwa toilet ya kuskure bakin sa sannan cikin sooting voice ya shiga kira na da sunan da shi kadai ke fada min

"Honeybun, cool down please, fada min me ya faru kin ji Barbie ta".

Ai jin haka se na kuma fashe wa da kuka kamar wanda yake tira ni, har wata jiniya nake yi dan ya tabbatar kukan nawa na gaske ne, bawan Allah duk na bi na daga masa hankali, jin na ki yin shiru na fada masa abinda ke faruwa se ya tashi ya zafi car key, waya kare a kunnen sa yake ce min

"Is okay, gani nan zuwa gidan yanzu, bari in zo in ji menene".

Jin ze fito a wannan lokacin yasa na hadiye kuka na nace ina turo baki

"To kuma se ka fito yanzu, karfe sha daya fa ya wuce".

Se ya sauke ajiyar zuciya a hankali, da wannan cool voice din nasa yace

"To Barbie ke ce kin ki yin shiru ki fada min meke damun ki, gaba daya hankali na ya tashi, gwara nazo na ji menene haka ya dagawa honeybun dina hankali".

"To zan fada maka base ka fito ba".
"I'm all ears".

Ya fada bayan ya koma bakin bed ya zauna tare da aje car key din

"Ba Abba bane.... yiiiiii...waiii....waiii baze barni......yiiiiiii....wayyo Allah na".

Kamar abin arziki na fara fada se kuma ba bige da kukan shagwaba after each word , a hankali yasa hannu ya dafe kan sa dake masa ciwo, ga bacci ga tashin hankali.

"Is okay Barbie, kina ji na, take a deeep breath, oya ina jin ki".

Kamar yadda ya fada haka na fara yi, yana irga one two har three

"Oya, yanzu ina jikin fada min menene".

"Sweetg tooth".

Na kira shi da one of the sweet names da na saka masa,

"Uhmmm".

Ya amsa min, na gyara kwanciya ta

"Ai dai kasan na ce ma na daina rashin kunya ko sweetheart?".

"Yes my honeybun".

"To ba shi nayi ba, dama fa wai Abba ne kawai ya kira ni yace min wai ba zan aura......wait, na taba baka labarin Ya Ibrahim?".

Ɗan yamutsa fuska yayi, se kuma ya girgiza kai kamar tana ganin sa

"No, waye shim is it relevant?".

"Sure, yes".

"Okay then fada min waye shi?".

"Sweet tooth, Ya Ibrahim is my boyfriend, mun shafe years tare, farko yana gidan kanin Dad din sa ne a makotan mu, matar kanin Dad din kuma kawar Mama ce, mun shaku sosai tun ina yarinya lokacin kuna school, there and then se shakuwar ta juye zuwa soyayya me tsanani, i do love him so very much sweetheart, shima kuma he do, to muna ta tare se family din shi suka ce se yayi aure, ni kuma lokacin ban gama sec school ba, na san Abba won't married me off a lokacin, se dole muka hakura ya aura cousin din sa saboda uncles din sa da suka takura, amma kafin ya aure ta he told her about me, da kuma plan din mu na aure after na gama sec school, to daga nan aka yi auren, this is to 8 months back now, yanzu haka she's close to delivering, shine yayan Abba yazo da maganar cikin cousins din mu na bangaren su an samu wasu na fada a kai na, wai su na so na, so shine Abba yace na fitar da miji, a cikin su ko a waje, and there by na tabbatar musu Ibrahim is my choice, se Abba yace ya same shi su yi magana, da na fada masa se yace Tig, but se kuma yake ta samun tight schedules, daga wannnan se wannan, se be samu yayi answering call din ba, shi kuma Abba guess what?, Hmm wai se suka tashi shi da yayan sa Baba Kabiru suka tafi family house din su Ya Ibrahim, suka fada ma iyayen s a abinda ke faruwa da kuma zabin juna da muka yi ni da shi, wai shine a yadda Abba yace wai iyayen sa sun ce ba ze aure ni ba, wai familyn su mace daya ake aura, and basa saki se mutuwa, wai in tafi in Yi aure kar na zauna jiran dan su, and kuma wai acewar Abba wai an kira Ibrahim a gaban sa yace masa wai ya fada min shi baze yi aure yanzu ba, so shine Abba yace wai in rabu da shi , ji wani rashin adalci fa, kuma dan nace ni ina son sa ba zan rabu da shi ba, and ze aure ni after matar sa ta haihu, dan kaga ai babu adalci tayi aure tana da tsohon ciki ko, shine fa Abba yace wai se dai bayan ran sa ko kuwa in canja mahaifi, shine fa nace mai ai ina da Baba ko, to zan koma can, daga fadar haka shikenan fa Abba ya mare ni, daga nan se duka da caja, kaga ai ya dena so na ko, tun da da da yake so na ai baya duka na, yanzu baka gani ba, my elegant charming skin duk yayi bruises na duka, ya bata min fata na, sweet tooth am hurt, am still hurting, it pains, yana min zafi sweetheart".

Ta karashe tana sake fashewa da kuka, dan da gaske tana jin zafi sosai................✍️.

Uhmmm, am speechless 😶, bari mu cigaba da bin labarin Aimah Romeo babar soyayya 😂.

Vote
Comment
Share fisabilillah.

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 022  [ 1/06/2024 6:26pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Oummey
Free book!!!

*ZINARIYAR MACE⚡*
*Wai shin 'yar'uwa menene matsalarki? zubewar nono, ko kuma rashin kwankwason juyawa a falo maigida ya shiririce ya manta da tibi da matan tictok, menene matsalarki ne? rashin ni'ima ko kuma mugun sanyin da ya yi miki katutu, shin rashin taushin fata ne ko kuma kuraje da tabbani,  ko bala'in ramar da ta addabeki kuma babu rashin ci ba rashin sha a gidan auranki, gwaigwayewar gashi ce matsalarki ko kuma kaushi da faso na tafin kafa da bushewar fata, kina bukatar fatarki ta yi glowing kalarki ta fita kuraje su mutu, ko kuma kina bukatar azababbun turaruka da humra tare da turarukan wuta. Na san dai kuna da yawa matan da tumbi ya yi musu karan tsaye ina nufin ya katse muku hanzarin yi wa maigida gwalli da muskuce-muskuce a falo😃 Nesa fa ta zo kusa AL-KUTUBIYYA ISLAMIC MEDICINE sun tanadar muku da nau'in magungunan da suke magance kowace irin matsala da izinin Allah. Babban burinmu shine sha'ani na aure ya inganta a samu daidaito. Muna da.*
Na gyaran nono.
Na sanyi.
Dilka tare da hadin sabulu.
Duk Wani nau'in maganin mata.
Humra turarukan wuta perfumes, original miski tahra   3in1, ciccibi budurwar kaza. Had'addun supplement irin wad'anda ba su da matsala. Maganin Sliming wato narka tumbi. Abubuwan da muke sayarwa suna da yawa, kuma babu asarar dukiya. Muna garin kano kuma muna tura kayanmu kowane gari fad'in Najeria da Nijar har ma da  kasashemn ketare. Kai tsaye a tuntu'bemu ta lambobin wayarmu domin karin bayani.
*08089965176*
*07084653262*

Ouummey 022

Page 22

__________________Shiru yayi yana saurare na har na gaji da yan koke koke na nayi shiru, jin bai da niyyar magana yasa na dan ja numfashi na kira shi cikin tantamar ko ya katse kiran ne, se kuma naga he's still on the line da na duba screen din, se na maida wayar kunne na

"Sweet tooth".

Se lokacin naji ya ja doguwar ajiyar zuciya, daga zaunen da yake ji yake kamar ana hajijiya da shi, idanun sa dake rufe ya fara budewa a hankali har ya ware su, sun canja color zuwa wani irin blue blue dan tashin hankali.

He never knew Ina da saurayi, for once ba wanda ya taba fada masa, not su Ya Salman and not even iyayen mu, nima kuma ban taba masa maganar ba se yau, me yasa rayuwa zata zo masa a haka.

Sake kiran sunan shi da nayi da sweetheart yasa ya sake sakin deep breath, kafin ya fara magana da Muryar sa da ta dishe a take kamar wanda ya yi sati yana fama da zazzafar mura

"Nu'aimahhhhh".

Yadda ya kira real ssuna na haka kuma cikin wani irin tone me bayyana zafin da zuciyar sa ke masa haka kuma a shake yasa na ji gaba daya jiki na ya mutu, na kankame pillow na amsa masa da

"Uhmmm".

Se ya sake yin shiru dan ya rasa ma me zece, gaba daya ya nemi malamai a bakin sa ya rasa, haka muka yi shiru muna sauraren shiga da fitar numfashin juna na tsayin lokaci, zuwa sannan ya samu ya dan yi controlling kan sa se ya fara magana da sanyayyar muryar sa me sama min nutsuwa,

"Is okay, na fahimce ki, ki daina kuka kin ji hakan is not good for your health, wannan maganar ba ta waya bace, kiyi hakuri ki kwanta ki yi bacci, zan zo gobe kin ji, we'll find a solution, a very good one kin ji Barbie?".

Yadda sooting voice din sa ke ratsa ni yasa na shiga gyada kai a hankali kamar yana gaba na, se kuma cikin shagwaba na da ya zame min jinin jiki na autanci nace

"Amma bana jin bacci, kai na ma ni ciwo yake yi, kuma zuciya ta ma ba dadi".

Yanzu ma naji saukar ajiyar zuciyar sa, kana cikin lallami yace

"Ki dauki Alkur'ani kiyi karatu, insha Allah zaki ji saukin komai, ki kwantar da hankalin ki and know one thing, what ever Allah planned to be must be, duk kuma abinda kika ga baki samu ba dama ba baki bane, put this at the end of your mind, what's planned to be yours must surely be, and what's not yours would never be, just pray and leave the rest to Allah, ze kawo Miki mafita Bi'iznihi".

Cuno baki nayi gaba, ni duk cikin maganganun sa ba daya da ya shige ni, ai na sani Ibrahim and I are destined to be, to kuma Meye na wani magana, bayan kawai Abba ke neman kawo matsala ga lamarin, jin nayi shiru yasa yace "kin ji?".

"Nace maka fa kai na na ciwo, ba zan iya karatun ba".

"Then ki kwanta and put earphone, I'll be reading it ke kuma ki saurara".

Ban so haka ba, amma ba zan iya masa musu ba, haka na jawo headphon na saka na koma na kwanta tare da jan blanket na lullube jiki na, a hankali cikin nutsuwa, da wannan sassanyan muryan nasa, very deep and low yayi basmala ya fara karatun sa cikin suratul Noor, kira'ar sa me matukar dadi da sanya nutsuwa ta sa na gyara kwanciya ta tare da rungume pillow a kirji na, idanu na a lumshe nake saurar sa yana karatun cikin fitar da tsantsar tajweed, a hankali nake jin nutsuwa da salama na sauka cikin raina, zuciya ta ta shiga yin sanyi kamar wadda ake kwarara ruwan kankara, nunfashi na ya shiga fita a hankali, ina ta sauraren sa cikin wani irin shauki har ban san sanda bacci ya dauke ni ba.

Daga can bangaren sa karatun yake yi cikin son samawa kan sa da kuma ita nutsuwa, idanun sa a lumshe ya ke zubo haddar sa da ka, haka kuma yake fitar da kowane baki yadda ya dace ya kuma kamata, a haka ya sauke Suratul Noor ya sake basmala ya shiga Suratul Yusuf, ba wai a jere yake yi ba, a'a, favorite surahs din sa yake karantawa yana jin sanyi da Salama na saukar masa, ya shiga sauke ajiyar zuciya a kai a kai, yana jin samun daidaituwar numfashin sa da a daxun ya ƙara gudu kakar me cutar asthma, seda ya kai karshe har yayi basmala ze fara suratul Mumin se kuka ya saurara ya gyara zaman Bluetooth din da ya makala a kunnen sa, a sannu yake jin fitar numfashin ta alamun tayi bacci, ya sauke deep breath kana ya zare Bluetooth din ya aje ya kuma kashe kiran sannan ya cigaba da karatun sa.

Se da yayi addu'a ya shafa sannan ya mike kan bed, a lokacin ne kuma duk kalaman ta suka dawo mata word by word, sun masa zafi matuka, haka kuma sun daki zuciyar sa tare da shammatar sa, ya sani yana matukar son AIMAH, tun tana yarinyar ta yake jin strong feeling a kan ta, tana kara girma abin na karuwa, dawowar su ta kusa da karshe da ya ganta ne ya tabbatar wa kan sa ya kamu da matsanancin son ta, ba kuma na lokaci daya ba, a'a tun tuni

yake ratsa shi yana sake kafa rassa da jijiyoyi a zuciyar sa, ta yadda zuwa yanzu yake jin ya riga da yayi kafuwar da tumbuke shi ko jijjige shi abu ne mara sauki, yana mata so da kaunar da be taba yi wa wata ƴa mace ba, asali ma akan ta ya fara yin so, haka kuma tun lokacin da ya fahimci soyayyar ta a ran sa be sake kallon kowace mace a mace ba, dama tun a sali shi ba me kule kule ba ne, duk da cewa mata na son sa suna bibiyar sa dan he's 100% fit for a perfect husband, amma be taba bawa kowacce dama ba, da farko karatun sa ne ya hana, daga baya kuma Aimah ce ta gina babban shinge tsakanin sa da kowace mace, dan he's the monogamous type, be da ra'ayin mata biyu a rayuwar sa, a yadda yake ganin yadda al'amuran polygamy yake kasancewa yasa yaji ko kadan be da sha'awar hakan, ga kuma kasancewar sa silent type, be da hayaniya haka kuma baya san hayaniya, haɗa mata biyu kuwa dole se an yi hayaniya, wether tsakanin su ko tsakanin ƴaƴan da zasu haifa, shi kam tsarin gidan su da gidan Auntyn sa a wajen sa is the best, daga iyayen su maza se matan, se kuma su ƴaƴan su, gidan su cike da fahimtar juna da kauna, babu zancen hayaniya balle tashin hankali, wannan shine irin fatan da yake wa kan sa, shi da matar sa da yayan da zasu haifa.

So yake karfi da yaji ya kori tunanin daga ran sa, sedai kamar ana sake tunkudo shi, karfi da yaji yaje neman bacci amma ya rasa, daga karshe da yaga yana neman yin asarar lokacin a a banza se ya tashi zuwa toilet, yayi alwala ya fito ya tada sallah, in each sujjud yana rokon Allah zabi mafi alkhairi kuma nagari gare shi da Aimah.

Se da yayi sallar subh tare da su Baba da Farooq a masallaci sannan ya dawo ya kwanta, aikuwa ya shiga biyan bashin baccin da be samu ba, be tashi ba se after 11, dadin abin ma ranar weekend ce dan Saturday ce, ya yi wanka ya shirya cikin bakin sweatpants da golden yellow T-shirt, ya gyara gashin kan sa tare da fesa turaren sa na ko da yaushe, ya haɗa da next favorite din shi 5000 doller, take kamshin ya cakude waje ɗaya ya tashi wani sabon daddadan kamshin na daban, wanda a wajen sa ne kadai ake samun sa.

Hajiya Yayah yaje ya gaisar, ta amsa tana tambayar sa wane irin bacci be haka yayi yau, ya sanar mata be samu bacci bane da wuri, tare da tambayar Baba, ta sanar masa ai ya fita tuni.

Ya so ya zauna yayi breakfast, sedai sanin Aimah na can na jiran shi yasa ya mata sallama kan ze je wajen Mama, ta bashi sako ya kai mata tare da gaisuwa.

Mama ya tadda a falo, ya gaishe ta kamar yadda ya saba cikin sabon su na da da uwa, ta amsa tana tambayar yar uwar ta, ya bata sakon Hajiya Yayah kana ya bude baki dan tambayar inda nake se gani na sako kai falon.

Sanye nake da doguwar riga baka me taushi sosai, wannan yasa ta kwanta ta lafe a jiki na tare da bayyana perfect shape dina, duk da na ga yadda rigar tayi min tun a mirrorn daki na hakan be sa na fasa fitowa a buna ba, to ai na saba, babu ruwa na da waye a wajen, waye ze shigo haka nake zama na, Mama kuwa tun ranar da ta min magana na cuna baki cik rashin dadin rai bata kara ba.

Kasancewar bana san dankwali yasa yanzu haka ma kai na a bude take, gashi na dake nade in bun yasha gyara sosai yanan ta sheki da ɗaukan ido, fuska ta kuwa na shafa powder da ya kwanta matuka da complexion din fata ta, haka kuma idanu na ya wadata da Kohl da mascara dan kuwa ina da wadatar gashin ido, gazar gazar masu daukan hankali, almond shape eyes dina na cikin most beautiful feature na fuska ta, haka kuma most attractive.

Peach lips dina na wadace da lipgloss me kyalli da danko, hakan yasa su ma suke ta shining.

Na ware kyawawan idanu na kan shi lamarin da yasa ya hanzarta janye nasa dan kuwa wasu irin mashi ne masu matuƙar dafi yaji suna fitowa daga nawa idanun zuwa nasa, ni kuwa mamaki ne yasa nayi hakan dan be kirani yace ya zo ba, haka kuma wato da ban fito ba base neme ni ba ko.

Se na karaso gaban sa cikin tafiya ta kamar ina rausaya, dan duk nayi taku se jikina gaba daya ya jijiiga kamar wata reshen bishiya, na tsaya gaban sa na shiga buga kafafu cikin sangarta da shagwaba

"Wato ma da ban fito ba ba zaka neme ni ba ko sweetheart, bayan kuma waje na kazo ba wajen Mama ba".

Na karasa ina pouting lips dina, ya dago tare da sake min silent cool smile din sa da ya wanzar da farin ciki cikin zuciya ta take, se dai a fili se na kau da kai ina cigaba da doka kafa abina kamar wata yar shekara biyar.

Mama na dariya ta mike zuwa inner parlor din ta tana fadin

"Wannan kanwar taka se kai, nidai bari naje na yi kailula, in kun san zaku fita kuma ku sanar da Binta in zaku tafi ta rufe min kofa ta".

Daga haka ta shige parlon da a cikin sa ne bedrooms din mu suke, se lokacin Ya Masdooq ya mike yayi tsaye gaba na, gaba daya se na ga na dawo wata yar guntuwa a gaban sa, ko da dama ba wani tsayi gare ni ba.

Shi kuwa dogo ne sosai irin wanda ake kira giant din nan, dan ba shi da kiba amma a murje yake, gimming da yake kuma yasa damatsan hannun sa zuwa cikin sa kadan suke a murde.

Ya sunkuyo zuwa fuska ta tare da sa hannu ya dago haba ta na dube shi, se ya balla min harara tare da dungure min kai, ya kuma janye abin sa yaa zauna kan 3 sitter.

Ina dariyar hararar da yayi na biyo bayan shi na zauna a jikin shi dan shi ɗin bana tarar zama jikin sa da taba shi, shine ma yake janye wa yake kuma taka min birki, amma gare ni bana jin komai kan hakan dan yadda na dauki su Ya Salman haka na dauke shi.

Sedai fa duk hauka na da wautata, tare da shagwaba da snagartar da nayi, ban zama mara hankali kan kiyaye kai na ba, ban taba barin Ibrahim ya taba ni ba, ko da wasa kuwa, abu daya na sani shine yana rike hannu na, hakan kuma ba mu dauke shi a komai ba, ba kuma mu kadai bane, zamani ne yazo a haka, duk da cewa babban kuskure ne amma mu a wajen mu wayewa ce, ba kuma fa niyyar wani abu mara kyau muke yin hakan ba.

Hannu yasa yana kokarin zame ni daga jikin sa, se nima na kai nawa na sake rike shi sosai, ya dube ni ta gefen fuska ya dan hade rai

"Sake ni mana Barbie".

Make masa kafada nayi ina kwantar da kai na kan kafadar sa

"Allah ina son kamshin turaren naka sosai sweetheart".

"Kuma ai na baki ko?".

"To ai a jikin ka ne yake dadi, in ba'a jikin ba ma ni ji nayi kamar wari yake".

Girgiza kai yayi jin wani sabon sharrin, se ya saka karfi ya banbaro ni da ga jikin sa

"Wato haka kike makale kowane gardi da kamshin sa yayi Miki ko?".

Da sauri na ware ido se kuma na saka dariya

"Haba sweet tooth, taya ma zaka yi tunanin nan, bayan kai ko su Ya Salman ban shigewa haka dan bama shiri da su, kai ne kawai, kuma ai kai yayana ne".

Dan ajiyar zuciya yayi se yace

"Shi kuma Ibrahim din fa?".

"Haba haba, kamar bani da hankali, Allah ban da hannu na ba inda yake tabawa a jiki na, kuma nima ban taba rungume shi ba wallahi, ko so daya".

Yanzu kam hankalin sa ya kwanta, dan ya san ta bata karya, hatta dai da rashin kunya da tsiwa, wauta da sangarta zuwa shagwaba, amma karya ba halin ta bane, dan ta san ko ta fadi gaskiya ma ba abinda ake mata, shiyasa bata ginu kan karya ba..................✍.

Vote
Comment

Share fisabilillah

Ouummey 023  [ 1/07/2024 6:28pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Oummey
Free book!!!

*ZINARIYAR MACE⚡*
*Wai shin 'yar'uwa menene matsalarki? zubewar nono, ko kuma rashin kwankwason juyawa a falo maigida ya shiririce ya manta da tibi da matan tictok, menene matsalarki ne? rashin ni'ima ko kuma mugun sanyin da ya yi miki katutu, shin rashin taushin fata ne ko kuma kuraje da tabbani,  ko bala'in ramar da ta addabeki kuma babu rashin ci ba rashin sha a gidan auranki, gwaigwayewar gashi ce matsalarki ko kuma kaushi da faso na tafin kafa da bushewar fata, kina bukatar fatarki ta yi glowing kalarki ta fita kuraje su mutu, ko kuma kina bukatar azababbun turaruka da humra tare da turarukan wuta. Na san dai kuna da yawa matan da tumbi ya yi musu karan tsaye ina nufin ya katse muku hanzarin yi wa maigida gwalli da muskuce-muskuce a falo😃 Nesa fa ta zo kusa AL-KUTUBIYYA ISLAMIC MEDICINE sun tanadar muku da nau'in magungunan da suke magance kowace irin matsala da izinin Allah. Babban burinmu shine sha'ani na aure ya inganta a samu daidaito. Muna da.*
Na gyaran nono.
Na sanyi.
Dilka tare da hadin sabulu.
Duk Wani nau'in maganin mata.
Humra turarukan wuta perfumes, original miski tahra   3in1, ciccibi budurwar kaza. Had'addun supplement irin wad'anda ba su da matsala. Maganin Sliming wato narka tumbi. Abubuwan da muke sayarwa suna da yawa, kuma babu asarar dukiya. Muna garin kano kuma muna tura kayanmu kowane gari fad'in Najeria da Nijar har ma da  kasashemn ketare. Kai tsaye a tuntu'bemu ta lambobin wayarmu domin karin bayani.
*08089965176*

*07084653262*

Ouummey 023

Page 23

______________________"Nima ki daina shige min haka, ba kyau tun da ni ba mubarramin ki bane, kuma nima bana so".

Ban ma nuna masa naji ba dan ba zan dena ba, Allah ya sani in na rabe shi wata irin nutsuwa nake ji a raina da gangar jiki na, ban da na san baze yiwu ba ai ni ban ki kullum ace ina nanne cikin jikin sa ba.

Na sake rabawa a hankali na kwanta gefen sa kai na a kafadar sa, ya juyo ya dube ni irin me nace Miki din nan, se na yi takwaf takwaf da fuska

"I always find solace a tattare da kai, dan Allah sweetheart kar ka hana ni".

Na karasa hawayen da ni kai na ban san ko na Meye ba na rolling on my cheeks, da sauri ya kai palm din shi ne tsananin taushi kamar ba hannun namiji ba ya shiga wiping min tears din

"To Meye na kukan kuma?".

Se da na turo baki gaba sannan na bashi amsa da rawar murya

"Ba kai ne ba, ka daina so na irin su Ya Farooq".

Hannu yasa ya janye kai na daga kafadar sa ya juyo gaba daya muka fuskanci juna, hannaye na cikin nasa ya matse waje daya

"Se dai bana numfashi honeybun".

Dage masa gira guda nayi dan ban fahimci me yake nufi ba

"In dai kika ga na daina son ki to sedai bana numfashi Aimah, son ki da kaunar ki a cikin jini na suke, yadda ba zan iya rayuwa ba jini a jiki na ba haka ba zan iya rayuwa ba kaunar ki ba".

Dan farin ciki fadawa nayi jikin sa na sa hannu na zagaye shi tare da kankame shi cikin jiki na, tsayin lokaci kafin na sake shi dan shi dai be rike ni ba

"Kawo min abinci, I'm hungry ban ko karya ba na taho".

Ya fada idanun sa a lumshe bayan ya jingina da headrest na kujerar, da sauri na tashi nayi kitchen ina fadin

"Ai da ka fada min da tuni na dafa ma abinci, amma ji ba ka zauna da yunwa har to twelve".

Be amsa ni ba haka nima ban jira amsar ba na shige kitchen, da sauri da sauri na shiga nema masa simple abinda ze yi breakfast.

Ina shigewa ya bude idanun sa da suka canja zuwa ja ja ja, Allah ya sani baya san ina matsawa jikin sa, shi kadai ya san yanayin da yake shiga sedai na ki fahimtar sa, yanzu kuma ga shi har ina batun ya daina so na, ban da abu na ai yadda ba'a raba hanya da jini ya sani ba ze taba iya raba zuciyar shi da kauna ta ba, dan ba karamin kafuwa na yi a cikin ta ba, daina kauna ta na nufin daina numfashin sa a ban kasa.

A hankali ya furzar da wani dan huci lokacin da zuciyar sa ta jefo masa tambayar

"To in Kuma ta auri wani ba kai ba fa?" .

Ya sake jingina sosai jikin seat, ya sani se sha wahala in aka ce ya rasa ta, ba wahala kadai ba ya san rayuwar sa ce zata shiga wani hali, wanda shi kan sa ba ze iya predicting ba yanzu, se dai so ne na gaskiya na hakika yake mata, in har bata masa so na aure, in har bata masa kauna na hada rayuwa, in har wanin sa take so dan kare rayuwa tare, ta kuma tabbatar tana kaunar sa shi ma kuma yana kaunar ta, to ze iya sacrificing wannan dimbin so da kaunar da yake mata, ba dan komai ba se dan ta rayu da wanda take so, ta zauna da wanda take s o, tayi farin ciki a tare da wanda take so, dan baya mata fatan dandanar zafi da radadin dake cikin so, shi kan sa be san shi ba, be taba experiencing ba se jiya da daddare, amma har zuwa yanzu dacin sa be bar kan harshen sa ba, me yasa ita ze mata wannan fatan.

Haka ya cigaba da tunanin yadda ze fara rarrashi kan sa, ya lallabi zuciyar sa ta hakura da son mallakar Aimah, daga yadda ta kira shi tana kuka, da irin maganganun da take fada hatta akan mahaifin ta ya nuna masa ba karamin zurfi tayi ba akan son wanda ta kira Ibrahim.

"IBRAHIM". sunan da tun jiya yake ta echoing a kunnen sa, ya ki barin shi ya huta, ya ki batik zuciyar sa ta resting, da ya tuno Aimah see kalaman ta akan Ibrahim sun fado masa , lallai kowaye wannan Ibrahim ba karamin me Sa'a bane, haka kuma ba karamin nasara yayi ba a

rayuwa.

"Tashi Kaci sweetheart, bana san kana zama da yunwa kar ulcer ta kama ka".

Be Musa ba ya bude idanun sa da ke cike fal da damuwa ya tashi ya gyara zaman sa kana ya fara cikin jallof din spaghetti da na masa da taji kayan veggies, da indomie nayi tunanin dafa masa, se na tuna ai baya ci, shine na dafa spaghetti dan tafi komai saurin dafuwa apart from indomie, na hada masa coffee me dadi se tashin kanshi yake, na kuma soya masa kwai babba na dora kan abincin.

Cikin lokaci ƙalilan ya gama dan be da wani cin abinci apart from wanda aka san matashin namiji da shi, kar kuyi mamakin jin wai na fishi cin abinci, nima har yanzu mamakin hakan nake yi.

Na kwashe kayan na kai kitchen na dawo na tadda shi yana shan ruwa bayan ya karasa shanye coffee din sa.

Na zauna tare da kama hannun sa na sarke yatsun mu tare da zuba musu ido ina ganin tsananin kamannin yatsun namu, Hajiya Yayah ta dade tana fadar yatsu na irin nasa ne amma ban taba lura ba se yau.

"Yaya kaga yatsun mu iri daya ne ashe da gaske?".

Ya kalli hannun mu da na sarke, se ya dauke kai yana dubban fuska ta, in seriousness yace

"Fada min ya kuka yi da Abba yau?".

Na bata fuska na langwabar da kai

"Nifa ban ma je gaishe shi ba yau dan ba na san mu hadu ya bata min rai na a kawai, tsakani da Allah sweetheart a labarin da na baka jiya meye laifi na ko na Ibrahim da Abba ze ce se ya raba mu?, Bayan shi ga shi ya auri wadda yake so?".

Zare hannun sa yayi daga nawa ya harde hannuwan sa a kirji,

"Gaskiya kike so na fada miki ko karya Barbi?".

Duk da gaba na na faduwar jin me ze fada amma haka na daure na furta
"Gaskiya nake so".

Ya gyara zama ya dube ni sosai duba na tsanaki, kana cikin murya ta tsaka tsaki, ita ba me kaushi ba haka kuma ba me too cool ba yace

"Baki da kunya kuma baki kyauta ba honeybun ".

Cigaba da kallon sa nayi dan san jin karshen fahimtar sa

"Baki kyauta ba ko kadan abinda kika yi wa Abba jiya, kin manta Abba mahaifin ki ne?, Wanda ya haife ki, ya kula da ke tun baki san kan ki ba, ya so ki tun baki san wace ke ba, ya kula da rayuwar ki tun daga cin ki, shan ki, da tufar ki batare da ya taba gazawa ba ko so daya, ya gatanta ki fiye da duk ƴaƴan da ya haifa, amma ace yau akan namiji zaki kalle shi ki masa rashin kunya?, Shin ko be haife ki ba be miki wannan wahalar ba ba zaki duban shekarun sa ba nu'aimah, amma kika masa tsiwa, shin kin kyauta kenan?".

Murya ta na rawa na jin abinda yace

"Amma ai Nima ina son shi sweetheart, kuma ba rashin kunya na masa ba, shine fa yace wai ba zan aura Ibrahim ba bayan ina son shi, se nace se na aure shi, shikenan fa abinda nace".

Ya girgiza kai cikin takaicin irin tarbiyyar da su Mama sukai min, su Mama are best of parent ga duka ƴaƴan su ta kowace fuska, amma a kai na sun gaza ta fuskar tarbiyya, wnada tsananin so da gatan da suka nuna min yasa nake kokarin lalacewa, haka kuma na ke kokarin fin karfin su tun da basu isa su sani nayi ba, haka basu isa hana ni nayi ba, gaskiyar Allah da yace "Al Malu wal banu na fitnah", yanzu dai kalli yadda Allah ya jarrabi su Mama da Ya daya kwaya tak, wanda in Allah be kiyaye ba ba kuma dan ire-iren su Hajiya Yayah ba ni kadai na isa kai su wuta.

"Yin sa'in sa da iyaye da basu amsar duk abinda suka fada rashin kunya ne kuma rashin tarbiyya Nu'aimah, kuma haka kika wa Abba, kin ga kuwa la shakka kin masa rashin kunya".

Na dan cuna baki kaɗan, sedai hararar da yayi min yasa take na gyara bakin

"Na san an saki a islamiyya haka kuma na san da dai kina zuwa, ban san ko da ga baya kika daina zuwa ba, shiyasa har baki san Allah yace "wala takul lahuma uffin" ba, ke ga shi ba uffin ba, musu ne kika yi da mahaifin ki, wanda bayan Allah da Manzon sa baki da wanda suka fi su daraja, ya kike tunanin Allah ze yi dake honeybun, ko baki san wuta ce makomar duk yaron da ya kasance mara biyayya ga iyayen sa ba, haka kuma duk bacin ran da suka yi kamar curse yake zama wa rayuwar ba, fada min shin akwai farin ciki da jin dadi a rayuwar wanda aka yi cursing?, The curse ma kuma na iyaye, kin san Meye kuwa tsinuwar iyaye Nu'aimah, ga kuma ya Mala'iku da zasu sake tsinkewa mutum, innalillahi wa inna ilaihi rajiun ".

Yadda ya kare maganar yana dafe kan sa irin yana jajanta min wani gagarumin tashin hankalin da ke jira na yasa na fashe da kuka hankali a tashe, kun san me? Wallahi ba wanda ya sanni sama da Ya sweetheart dina, ba kuma wanda yake iya juya ni cikin ruwan sanyi irin sa, a hankali yake sa da kai na in ji eh nayi kuskure, kamar dai yanzu.

"Ni wallahi duk ban san wannan ba, ai mu a islamiyyar mu malamin mu be fada mana haka ba, yanzu shikenan sweetheart wuta zan tafi, wuta Allah ze wurga ni, na shiga uku?".

Na fada ina sake rushewa da kuka, can kasa ya sauke ajiyar zuciyar jin dadi ganin ta ruwan sanyi ze gyara komai, se ya dago idanun sa sun yi raurau irin lallai yana tausaya min

"Amma wannan malamin islamiyyar be kyauta ba, kuma tun da har be sanar da ku ba kin ce ko?".

Da sukari na gyada kaji ina fadin

"Eh Allah ".

"Then ki kwantar da hankalin ki, alhaki a kan sa tun da shi ne be fada muku ba, amma yanzu tun da na fada miki se kije ki bawa Abba hakuri, ki masa kuka ki fada masa kin yi nadama ba zaki kuma ba, na san ze yafe miki, yana yafe miki shi kenan shima Allah ze yafe Miki tun da ai da baki sani ba".

"Shikenan in nayi haka Allah baze kona ni a wuta ba, Mala'iku ma ba zasu tsine min ba?".

"Eh, amma that's in kin nemi yafiyar Abba ".

"And I'll surely do, zan roke shi ya yafe min, kuma na san Abba na so na ze yafe min".

Gyada kai yayi alamar hakan yayi, a ran sa yana tausayin su Abba da har suka bari na san irin mugun son da suke min, gashi har ina fada, hakan kuma shine babban dalilin da ya ba ni damar yin yadda nake so.

"To amma shikenan za'a raba ni da Ya Ibrahim dina sweet tooth?".

Na fada with a breaking voice, wadda ana jin ta an san ina cikin pain.

Se ya girgiza min kai

"No, Abba baze raba ki da shi ba, tun da har Barbie ta na son shi da yawa har haka, I'll talk to Abba, zan roke shi kar ya raba ku".

"Dagaske sweetheart?".

Na tambaya with open mouth full of joy, ya gyada min kai, se kawai na sake afka masa giving him a tight hug, yanzu be bar ni ba kamar daxu, ya dago ni tare da sake min cute smile din sa, kai wallahi tun da nake ban taba ganin wanda Murmushi ke matukar yiwa kyau kamar sweet tooth dina ba, he has the cutest smile ever.

Ya mike tsaye, Nima na mike tare da riko sangalin hannun sa

"In dauko mayafi na muje musha ice cream?".

Ya kare ma shiga ta kallo ya dauke kai,

"Ki canja kaya dai gaba daya, put on abaya se ki zo mu je, and be fast, I'll be waiting for you a mota".

Da sauri na cika shi nayi daki da gudu shi kuma ya leka kitchen ya sanar da Binta fitar mu kana ya wuce cikin motar sa, nan da nan na canja kaya na zuwa abayar kamar yadda yace, sky blue color, me kyau da saukin ado, na sha high heel black shoes da purse din su, na rolling mayafin rigar a kaina na fice bayan na sha wanka da turare na.

Yawo muke je, mune joints joints muka sha ice cream ko in ce na sha, wajejen shakatawa wato Parks zuwa dai duk inda kuka san na saka farin ciki, se magrib ya aje ni gida ya wuce gidan su ko ciki be shiga ba.

Kamar kuwa yadda na masa alkwari haka na bawa Abba hakuri, wanda hakan ba karamin faranta musu yayi ba shi da Mama, sedai ban boye ba na fada musu sweetheart yace na basu hakuri, sanin Ya Masdooq nake kira da hakan yasa suka gane shi ya sani, duk da haka sun yi farin ciki tun bare Abba, da a take a wajen ya fara wasu sake sake cikin ran sa!.....................✍️.

Me kuke tunanin Abba suke sakawa?, Let's meet in comment section 😍.

Vote
Comment
Share fisabilillah

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 024  [2/06/2024 9:16pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Oummey
Free book!!!

*ZINARIYAR MACE⚡*
*Wai shin 'yar'uwa menene matsalarki? zubewar nono, ko kuma rashin kwankwason juyawa a falo maigida ya shiririce ya manta da tibi da matan tictok, menene matsalarki ne? rashin ni'ima ko kuma mugun sanyin da ya yi miki katutu, shin rashin taushin fata ne ko kuma kuraje da tabbani,  ko bala'in ramar da ta addabeki kuma babu rashin ci ba rashin sha a gidan auranki, gwaigwayewar gashi ce matsalarki ko kuma kaushi da faso na tafin kafa da bushewar fata, kina bukatar fatarki ta yi glowing kalarki ta fita kuraje su mutu, ko kuma kina bukatar azababbun turaruka da humra tare da turarukan wuta. Na san dai kuna da yawa matan da tumbi ya yi musu karan tsaye ina nufin ya katse muku hanzarin yi wa maigida gwalli da muskuce-muskuce a falo😃 Nesa fa ta zo kusa AL-KUTUBIYYA ISLAMIC MEDICINE sun tanadar muku da nau'in magungunan da suke magance kowace irin matsala da izinin Allah. Babban burinmu shine sha'ani na aure ya inganta a samu daidaito. Muna da.*
Na gyaran nono.
Na sanyi.
Dilka tare da hadin sabulu.
Duk Wani nau'in maganin mata.
Humra turarukan wuta perfumes, original miski tahra   3in1, ciccibi budurwar kaza. Had'addun supplement irin wad'anda ba su da matsala. Maganin Sliming wato narka tumbi. Abubuwan da muke sayarwa suna da yawa, kuma babu asarar dukiya. Muna garin kano kuma muna tura kayanmu kowane gari fad'in Najeria da Nijar har ma da  kasashemn ketare. Kai tsaye a tuntu'bemu ta lambobin wayarmu domin karin bayani.
*08089965176*
*07084653262*

Ouummey 024

Page 24

___________________Ban san ya samu Abba da batun magana ta da Ibrahim ba, se after three days, shima kamar kwanan baya Abba ya kira ni, ko da naje na same su shi da Mama se sweetheart.

Tun da na shigo nake sakin Murmushi ina kokarin mu hada ido, sedai tun da ya kalle ni so daya ya dauke kai ya maida kan Tv dake aiki, ganin haka se na karasa shigowa kuma direct wajen sa nayi, na zauna gefen sa har kafadar mu na haduwa.

Ban ji komai ba duk da ga su Abba a wajen se shine ya matsa a dabaran ce, na dan tabe baki ina tunanin irin halin shi, ko dai banza ai yasan ni kanwar sa ce ko.

A jimlance na musu sannu, shima kuma shi ya rada min kasa ƙasa yace na fada, Abba da Mama suka amsa kusan a tare, kana Abba ya gyara zama yana sakin Murmushi dan kuwa yaga san da yayi min magana.

A nutse ya kira suna na, na amsa tare da dagowa na kalle shi, se yayi pointing Ya Masdooq

"Yayanki ya same ni da maganar Ibrahim, yayi min maganganu masu nauyi da suka sa na sassauta zuciya ta kan batun, haka kuma na yarda na amince zan yi azumin kaffara kan rantsuwa ta, ba domin komai ba se dan na amince da bashi dama a karo na karshe kan batun ku ke da Ibrahim din, na baku seven months nan gaba yazo ya nemi auren ki, zuwa lokacin in har yadda kika fada ne matar sa ta haihu har ma baby yayi kwari, akasin haka kuma zan aurar dake out ga duk wanda hankali na ya kwanta da shi, kin amince?".

Zufa naji tana tsattsafowa a goshi na, ba dan komai ba se na kokonton amincewar da nake ciki, in na amince kuma aka zo Ibrahim be aiko ba lokacin ko aka samu wani akasi daga gidan su shikenan Abba na nufin aurar da ni ga wanda ban sani ba be sanni ba kuma wanda bana so shima   kuma na san ze zama baya so na?.

Wani tsagin zuciya ta ke ingiza ni na amince, dan ya zuwa lokacin na san Ibrahim ze aiko, ai dama plan din mu is matar sa ta haihu kuma a dan kwana biyu ko, to ai lokacin ze zama ma baby na da wajen four months fa, then why the contemplating?, Kawai na amince mana!.

Ba tare da tunani ba na amince da gurguwar shawarar wannan bangare na zuciya ta, shawarar da ta zama silar kawo mu bigiren da muke kai yau.

"Na amince".

Abba ya dube ni sosai, duba na tsanaki kafin ya sake tambaya ta

"Kin amince?".

"Na amince".

"Kin amince?".

"Na amince".

A karo na uku ne kafin ya tambayi amince wa ta ya sake jaddada min fa babu bugu babu ja da baya a gaba, kar nazo na ce ban san zance ba

"Wallahi summa tallahi ba zan yi kaffara ba a gaba, in har Ibrahim be zo neman auren ki watanni bakwai ba masu zuwa se na aurar da ke ga duk wanda ya kwanta min, just consider this as kamar ranar aure ne na sa miki, coming seven months, ban san zancen hakuri ba, ban san neman alfarma ba, shin kin amince da sharadi na Nu'aimah?".

Wannan karon ba karsashi kamar a first and second round na furta amince wa ta, se kuma da na amsa sannan nake jin anya ban tafka kuskure ba, me yasa ban nemi Abba da ya bar batun sharadi ba kawai ya karamin lokaci, sedai ba yadda na iya, bakin alkalami ya riga ya bushe!.

Abba ya gyada kai cikin gamsuwa, kana ya dubi Mama da Ya Masdooq dake zaune a falon yace

"Ina fatan zaku zama shaida kuma alkalai a nan gaba, a gaban ku na fada mata sharadi na ta amince dashi, ina fatan Allah ya zaba mana abinda yafi alkhairi ".

Da Ameen suka amsa masa se Abba yace in tashi in je ya sallame ni, Ya Masdooq na kokarin tashi Abba ya kalle shi

"Fatan kai ma ka dinga tunawa da alkawarin da ke tsakanin mu".

"Insha Allah Abba".

Ya amsa yana sunkuyar da kai, daga haka yayi wa su Abba sallama ya fita, dama ban tafi ba, ina daga bakin kofa ina jiran fitowar sa, sedai ina mamakin wane alkawari ne haka tsakanin Abba da Ya Masdooq, shi da be fiya yin alkawari ba, dan yace alkawari kaya ne, kada ka dauki abinda ka san ba zaka iya cikawa ba, haka kuma abin tambaya ne ranar gobe kiyama.

Hannun sa na riko, ya kalle ni ya kalli hannun kana ya sake maida duban sa fuska ya, na basar tare da kau da kai na gefe saboda na sani, nufin sa in sake masa hannu, ni kuma ina son rike

hannun sa, ba dan komai ba se dan palms din sa dake dauke da wani irin sanyi ko in ce dumi me dadi da ratsa jiki, dan kuwa hannun sa ba zafi gare shi ba, haka kuma ba sanyi ne ba, se ya zama dai kamar ace dumin, kuma irin wanda ban taba ji ba a hannun wani.

Tare muka zauna a three sitter a inner parlorn Mama, maimakon na sake shi se na sake dora hannu na na hagu kan namu, nace cikin mamaki

"Wane alkawari ne Abba yake tuna maka sweetheart?".

"Kin yi kyau".

Ya fada yana jan hanci na cikin bagarar da tambayar da na masa, na saki dariya ta me kyau ina bashi amsa

"Ai ka fini kyau, so da yawa fa ina tunanin in da ace kai mace ne wane irin go slow and dambe zaka dinga haɗawa a garin nan?".

Da mamaki yake kallo na, ganin be fahimce ni ba nace

"Eh mana, dan na san maza dambe da fada zasu dinga yi a kan ka da mace ne kai saboda tsabar Kyan ka, haka kuma se ka dinga hada accident saboda drivers da zasu dinga manta wa da tuki wajen kallon ka".

Dariya yayi, dariya ta sosai da na dade ban ga yayi ba, girgiza kai kawai yake amma ya kasa dena dariyar, Nima ina taya shi, idanu na kan beauty point din sa na both cheeks, ga kuma cleft din sa na haba, making him look more attractive.

"You're too funny honeybun, wait, ba wannan ba, da kika amsawa Abba, kin tabbatar hakan is the best choice and solution?".

Dan shiru nayi dan ni kaina har yanzu zuciya ta na rawa, ganin haka yace

"Look, in hankalin ki be kwanta ba muje a warware maganar ba se nan gaba Abba yace be san zancen ba".

"Ai ko mun je ma Abba ba ze saurare mu ba tun da an riga an yi sealing deal din".

Na fada a raunane, se ya sake damke hannu na da na saka cikin nasa

"See, kin san dai i always want to see you happy ko, and kin samu abinda kike so ko?, Then in hankalin ki be kwanta ba let's go, I'll plead him har se ya yadda a soke maganar tun da ai dazu dazu ne, dan nan gaba na tabbatar baze saurare mu ba".

"I know sweet tooth, na sani kai me so da kaunar farin ciki na ne, shiyasa nake kiran ka sweetheart dan ban aje ka a kusa ba cikin raina, amma kar ka damu, na amince da sharadin Abba dan na san Ibrahim na so na, he'll surely seek for my hand in marriage kafin stipulated time din, dama muma tsarin mu shine matar sa ta haihu, daga nan everything will go smoothly".

Ajiyar zuciya ya sauke tare da gyada kai ya koma ya jingina jikin headrest na kujerar, ya lumshe idanun sa tunanin God knows what, ni kuma na samu aikin kare ma fuskan sa kallo yadda ban taba yi ba.

Sweetheart, ohh ina nufin Ya Masdooq kyakkyawa ne, in nace kyau ina nufin zallar madarar kyau da kafin ka samu namiji me irin shi se ka tona dan ko ni da nake mace ba abinda zan gwada masa se kyale kyale kawai, in kuna jin sexy eyes masu sheki da maiƙo to na Ya Masdooq kat ne, hancin sa kuwa Masha Allah dogo ne, da yazo kan saman labban sa se yayi yar tukunya me kyau, bakin sa karami ne sedai labban sa na da dan tudu hakan kuma ya kara kawata su, a wajen kalan lips din sa da suke peach color ne muka yi tarayya, fuskar sa doguwa ce cikakka me zagaye da tattausan bakin gashi (saje) da ya kara mata haiba da kwarjini, sedai be tara gemu amma akwai gashi kwance a habar sa amma ba me tsawo ba, kan sa kuwa cike yake da suma me laushi da tsayi dan be cika aski ba, hakan yasa in beyi styling gashin ba yake saukowa har kan wuyan sa, in ya yi styling ne yake nannadewa ya tsaya iya keyar sa.

Ajiyar zuciya na sauke me nauyi lokacin da ya bude idanun sa cikin nawa, sedai ya dan canja kala zuwa jajajaja, wannan maikon me kama da ruwa garai garai na kwance ciki.

Shi ya janye dan ni na kasa ko kwakkwaran motsi, ya tashi tare da ɗaukan car key din sa, be min magana ba se shafa Kai na da yayi tare da sakin guntun murmushi sannan ya fita.

Se kuma lokacin na dawo hayyaci na, na fada kan kujerar ruf da cikin ina sauke numfashi a hankali, na dade a wajen sannan na tashi zuwa kitchen na debo abinci na dawo na shiga tsakura, duk da ina da cin abinci amma ba wai cikin garaje ba, a'a a nutse cikin yanga da aji nake ci.

Ina ci ne Ina kuma tunanin sweetheart, yanayin idanun sa a dazu sun tsaye min a rai, se nake jin kamar ba lafiya ba, kamar akwai abinda yake damun sa, se nayi tsam na tashi zuwa bedroom dina na dauko waya ta kana na koma wajen abincin na shiga kiran wayar sa sedai baya tafiya, wannan matar me shegen iyayi ta Company MTN na sanar da ni not reachable.

Daidai lokacin yana zaune ne can bayan gari, karkashin wata bishiya a saman pray mat din da ya dauko daga motar, gaba daya cikin tashin hankali da damuwa yake, yana dai dannewa ne da kokarin ganin yafi karfin zuciyar sa, yana san ya zama yana da control over his emotions ba wai emotions din su dinga controlling din shi ba, sedai yanan jin kamar yana neman gazawa.

Zuciyar sa ciwo take masa, ba na komai ba se na so da kaunar Aimah, ita din is very dear to his heart, zuciyar sa ta bata wani gurbi me matsayi na gaske, haka kuma faffaɗa da take jiran

Aimah ta cike, sedai da alama wannan gurbin ba ze taba cikewa ba haka ze zauna a wawake, wala Allah har ya koma ga mahaliccin sa.

Be san yadda aka yi yayi zurfi haka a san ta ba, be san sanda son ta yayi masa kamun kazar kuku ba, ta yadda yake jin rayuwar sa babu ita tamkar mutum ne ya shirya tafiya batare da ya san ina za shi ko ina ya dosa ba, wato dai babu ma'ana.

Sedai duk wannan zazzafar soyayyar da yake mata, duk wannan kaunar mara misaltuwa da zuciyar sa ke mata be sa yaji ya kasa nema mata abinda take so ba, duk kuwa da sanin samun muradin ta is reciprocal to loosing her, forever, ba dan komai ba se dan kauna ce yake mata ta gaskiya, abinda Bature ke kira true love, shiyasa ya zabi farin cikin ta over his, ya gwanmaci ganin ta cikin walwala ko da kuwa shi ze dawwama cikin kunci ne, ya zabi kwanciyar hankalin ta over his, ya tabbatar in ya rasa ta rayuwar sa zata koma ne babu wani armashi balle digon farin ciki, sedai faranta mata is his motive, dan yana san ta ne fiye da son da ya ke wa kan sa.

Seda ya ji wayar sa na kuka sannan ya daga shanyayyun idanun sa kan screen din, sunan Farooq ne ke yawo tare da pic din sa, be yi picking ba se tsaida duban sa da yayi kan time, ten minutes pass ten, baya raba dayan biyun kiran da Farooq yake masa na yaji yana ina ne, dan shi ɗin ba me yawo ba ne, daga gida da aiki shikenan, hatta abokanai Masdooq ba shi da su se na wajen aiki, ko a makaranta shi kowa yana gaisawa da shi, amma ba wani close friends, abokan Farooq ne suke zama na sa, dan na san zuciya suke su kyale shi saboda halin sa, shi baya kiran aboki, baya zuwa wajen aboki ko da kuwa abokin ze zo so dari nawa ne, ya gwanmaci ya zauna a gida ya duba ayyukan sa na office, daga nan kuma ya cigaba da research din sa, wether related to aiki ko kuma karatun Islam da har yanzu be daina neman ilimi ba.

Se ya mike tare da nade mat din, ya kwashi wayoyin sa zuwa motar sa dake gaba kadan, yana zuwa ya bude backseat ya jefa pray mat din ya zagaya ya shiga driver seat din sa, sefa yayi fastening belt tare da addu'a sannan ya tashi motar zuwa gida.

A falon su ya sami Farooq zaune rike da waya, da alama shi yake kokarin sake kira, be kula Farooq din ba ya shige ciki, ya bishi da kallo se kuma ya tashi ya rufa masa baya, riga ya samu yana cirewa dan haka ya zauna gefen bed din Masdooq

"Mun yi waya da Abba dazu".

Farooq ya fada yana kallon fuskar sa dan ganin reaction din sa, sedai be ga komai ba a fuskar se ma karasa zare rigar sa da yayi ya cilla kan sofa

"Yace min kun yi magana".

"Sure".

Ya bashi amsa yana kokarin zare dogon wandon shaddar jikin sa

"Amma me yasa kayi haka Masdooq, why didn't you consider your self first?".

Se lokacin ya tsaya da abinda yake, ya jefa wandon kusa da rigar sannan ya zauna shima yana duban Farooq................✍️.

Vote
Comment
Share fisabilillah

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 025  [ 2/06/2024 9:18pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Oummey
Free book!!!

*ZINARIYAR MACE⚡*
*Wai shin 'yar'uwa menene matsalarki? zubewar nono, ko kuma rashin kwankwason juyawa a falo maigida ya shiririce ya manta da tibi da matan tictok, menene matsalarki ne? rashin ni'ima ko kuma mugun sanyin da ya yi miki katutu, shin rashin taushin fata ne ko kuma kuraje da tabbani,  ko bala'in ramar da ta addabeki kuma babu rashin ci ba rashin sha a gidan auranki, gwaigwayewar gashi ce matsalarki ko kuma kaushi da faso na tafin kafa da bushewar fata, kina bukatar fatarki ta yi glowing kalarki ta fita kuraje su mutu, ko kuma kina bukatar azababbun turaruka da humra tare da turarukan wuta. Na san dai kuna da yawa matan da tumbi ya yi musu

karan tsaye ina nufin ya katse muku hanzarin yi wa maigida gwalli da muskuce-muskuce a falo😃 Nesa fa ta zo kusa AL-KUTUBIYYA ISLAMIC MEDICINE sun tanadar muku da nau'in magungunan da suke magance kowace irin matsala da izinin Allah. Babban burinmu shine sha'ani na aure ya inganta a samu daidaito. Muna da.*
Na gyaran nono.
Na sanyi.
Dilka tare da hadin sabulu.
Duk Wani nau'in maganin mata.
Humra turarukan wuta perfumes, original miski tahra 3in1, ciccibi budurwar kaza. Had'addun supplement irin wad'anda ba su da matsala. Maganin Sliming wato narka tumbi. Abubuwan da muke sayarwa suna da yawa, kuma babu asarar dukiya. Muna garin kano kuma muna tura kayanmu kowane gari fad'in Najeria da Nijar har ma da kasashemn ketare. Kai tsaye a tuntu'bemu ta lambobin wayarmu domin karin bayani.
*08089965176*
*07084653262*

Ouummey 025

Page 25

_____________________"kace I should have consider my self first?".

Farooq ya gyada kai, se kawai Masdooq ya mike ya karasa gaban console ya fara zare links din hannun rigar

"Ai shine abinda nayi, that's what I did Farooq".

Cikin mamaki Farooq yace

"I didn't get you".

"Aimah ce Ni din da kake magana, and I consider her first that's why I choose her happinesses as my first priority".

Karamin tsaki Farooq yayi tare da fadin

"Look guy, jokes aside, ni magana nake maka da gaske, You're the best choice for Aimah, you deserve her Masdooq, soyayyar da kake mata should not go in vain ka fahimce ni".

"Kai ne zaka fahimce ni Farooq, ban da wani farin ciki da ya wuce na Barbie, dariyar ta itace tawa, farin cikin ta shine nawa, walwalár ta itace key to mine haka zaman lafiyar ta means mine, akasin haka kuma shima yana nufin tashin hankali na, ko da kace my love for her shouldn't go in vain, ai be je in vain din ba, tun da gashi ya bani damar bata muradin ta, and kake cewa i deserve her, wannan a idon ka ne, in her eyes bata ga wannan dacewar ba dan haka Nima ban ganta ba".

"You're not serious, zan je nacewa Abba he should over look wannan maganar, sam bata yi ba".

"Zaka batawa kan ka lokaci dan till eternity zabin Barbie would always be mine, kaga kuwa hakan na nufin ina kan ra'ayi na".

Kallon shi kawai Farooq ke yi cikin takaicin sa da bacin rai, tare yake da Masdooq a inda ba su da kowa, ya fi kowa sanin irin tsananin so da kaunar da Masdooq have for Aimah, tun tali talin yarinta, tun kan ta san kanta har zuwa ta fara zama mace, se yanzu kuma da ta gama zama yaddaa ya kamata se wani ya dauke ta ba dan uwan shi da ya sha kwana ido biyu saboda ita ba?.

No! Ba ze yiwu ba, ba ze bari haka ta faru ba, wallahi in har yana numfashi Aimah have no husband other than Masdooq, ba kuma dan iya Masdooq kadai ze yi wannan fighting din ba, har da dan ita kan ta Aimahr, ya fi kowa sanin Masdooq da irin qualities din da yake dashi, duk matar da ta auri Masdooq ta samu rabin addinin ta, he can swear akan hakan, dan haka ba ze bari kanwar sa tayi loosing this precious gem din ba.

Da wannan tunanin Farooq ya ja wa Masdooq kakkarfan tsaki me tsayi sannan ya fita daga bedroom din yana masa banging kofar, duk da he's not in the mood amma se da Murmushi ya kwace masa, ya sani dan ran sa ya ɓaci Farooq yayi tsakin dan ya fi kowa sanin ya tsani tsaki, haka ma banging door, shi kuma shiyasa yayi dan ya bata masa rai kamar yadda ya tabbatar ran Farooq din a nace yake yanzu.

"He'll never understand".

Masdooq ya fada yana nufar toilet a hankali, duk wanda ze so masa kasancewa da Barbie barin shi kan sa ne, dan hakan burin sa ne na atleast over 17 years back, Amma kuma neman cikar muradi da burin sa ba ze sa ya tauye ta ba, she've the right ta zabi life partner din ta, she've the audacity tace tana san wannan bata ra'ayin wannan, ba kuma hakan ze sa ya kalle ta da wani duba ba bayan duban da ya saba mata, sedai yana tausayin kan sa, dan son Aimah be shige shi da wasa ba!.

Da haka yayi wanka ya fito ya saka kayan bacci, ko abinci be nema ba ya fada bed, se ya kai hannu ya lalubo wayar sa ya budo hoton ta, kyawawan fararen haƙoran ta a bude cikin yin dariya, haka hannun ta ya sha zanen lalle baki da ja.

A hankali ya shiga sauke ajiyar zuciya akai akai kamar wanda ya sha kuka, se kuma ya daga wayar ya kai saitin bakin sa ya sunbata, wadda sunbar ta fito daga can karkashin zuciyar sa ne.

Da hoton honeybun din sa a hannu bacci ya sace shi, maimakon wayar ta fadi se ya kankame ta a kirjin sa kamar Aimah din ce a wajen.

Hankali na be kwanta ba se da safe da na kira yace ba komai bane, kan sa ne yake ciwo lokacin, amma ynx all is good dan ya sha magani tun jiya kuma ciwon kan ya tafi.

Successfully rayuwar mu ta cigaba da tafiya, ina waya da Ibrahim haka kuma yana zuwa, tun bare da yaji abinda Abba ya fada se hankalin sa ya kwanta, ta gefe daya kuma kullum sake shigewa sweetheart nake, wanda se da muka yi fada da Ibrahim a kan shi, abinda ba mu taba yi ba kenan wato fada a iya rayuwar soyayyar mu, bar shi dai zamu samu sabani, amma ba fada irin wannan da muka shafe har wata ba me shiga harkar wani ba, kafin Ibrahim ya fara saukowaa ya neme ni, daga nan kuma aka shirya.

Ba komai ya jawo fadan ba se wata rana Ibrahim yazo zance, muna zaune a sitting room muna hirar mu gwani sha'awa, se waya ta ta fara ringing, dake wayar na kusa da shi kan Centre table yasa ya kai hannu ya dauko, se ya ga sunan sweet tooth tare da emojin love 💕 na yawo, se ya dago ya min wani kallo kafin ya daga wayar ya saka speaker ya aje a tsakanin mu.

Ni ban ma san wanda ya kira ba se da naji muryar shi yana fadin

"Barbie". Can kasa kamar wanda ya tashi daga bacci

"Uhm sweetheart".

Na amsa masa, se na dora da fadin

"Ya naji muryan ka ya sake yin low, and very cool fiye da normal, baka da lafiya ne?".

Ina jin sautin mutmushin da yayi kamar yadda na san Ibrahim ma ya ji

"Am fine baby doll, azumi nayi ne yau kin san Thursday, gashi nayi aiki da yawa na gaji shiyasa kika ji ni haka, kina gida ne?".

"Oh, har da hankali na na neman tashi my sweetheart ba lafiya, Allah ya huta gajiya, ina gida, zamu fita ne?".

"A'ah, Hajiya lashe money, ji ta wai wani za'a fita, ni kayan iftar nake so ki min".

"As you wish boss, your wish is my command".

"Allah shirya min ke Barbie, byee se na zo".

"Take care sweet, bye".

Daga haka yayi hanging call din, se na dago dan cigaba da magana da Ibrahim, se dai yanayin fuskar sa da take kirne ga kuma idanun sa da suka canja launi yasa na bude baki dan tambayar lafiya?

Amma kafin na fada din se kawai Ibrahim ya tashi ya fita Fuuuu, na bishi da kallon mamaki se kuma na tashi na bi bayan sa da sauri, amma Nana makara dan ina zuwa yana ficewa da motar sa daga compound.

Na dade tsaye a compound Ina tunanin me ya faru da ya bata masa rai amma na kasa tunawa, se na koma daki na dauki waya ta na shiga kiran sa, bawan Allahn nan se da na hada masa missed call kusan hamsin amma be daga ba, daga baya ma se ya kashe wayar, hakan ya bata min rai sosai amma na kudure se na nuna masa banbancin Aimah da raguwar yan mata.

A kwana na uku Ibrahim ya huce, se gashi ya zo, kamar kar na je se kuma na taushi kai na na fita dan sanin dalilin bacin ran sa a wancan lokacin, daga nan se in San hukuncin dauka.

Muka gama gaisawa, ya fara sako hira se na katse na jefo tambayar me na masa rannan da ya tafi ba ko sallama.

A lokacin ne yake sanar da ni wai ai ransa ne ya ɓaci, shi da yake saurayi na har yau ya Ibrahim nake kiran shi, amma gashi ina kiran cousin dina da sweet names kamar shi zan aura, wai ma tukuna in fada masa anya babu wani abu tsakani na da Masdooq, me yasa se shi na zabi ya zama favorite na bayan ga wasu.

Kai tambaoyi dai masu tunzuri, dama gashi kuma ya hadu da Aimah, nan da nan na haye na shiga sakin zance, ta inda na shiga ba ta nan nake fita ba, na nuna masa hurumin sa daban na matsayin abokin rayuwa haka hurumin yan uwa na daban, kar ya saka min ido kamar yadda ban saka masa da amaryar sa da yan uwan sa ba.

Wannan magana ya kawo cece Kuce tsakanin mu dan kuwa yace wai kawai in fito in fada masa son Masdooq nake, ban kuwa musa ba nace masa in ma haka ne ai ya kai a so shi ne, kai wasa wasa dai yar na kai ainahin fusata nace na fasa auren, yaje abin sa, ko ba shikenan ba.

Shima se ya fusata har da fada min Allah ya sa shima yana da yan uwan, ga kuma shi nan na ga gatan sa tun da yana auren daya yanzu haka ma, wannan maganar ta sake fusata ni, na shige na bar shi a nan, ina shiga gida kuma na yi deleting duka numbers din sa daga phone na, ban tsaya nan ba na shiga goge pics din sa dake waya ta, komai da ya danganci Ibrahim a lokacin se da na cire shi a waya ta.

Wanna kuma shine fadan da muka taba yi da Ibrahim har muka kwashi wata daya bama magana, baya kira na bana kiran shi, se kuma yazo ya sauko daga baya amma ni ban shirya hakura ba, a wasa a wasa muka debi wata ba abinda ke haɗa mu se kuma lokacin na hakura, shima kuma Masdooq din dai da yake fada a kai ya dauko min sannan na yafe, daga nan be kuma kallon duk wani abu da ya shafi Masdooq yayi min magana a kai ba.

****After Seven months*****

Faduwa gaba na yake yi, ba dan komai ba se dan sanin yau ne ranar da Abba ya saka mana zamu zauna a cikin wannan watan da ya kasance wata na bakwai haka kuma karshen wa'adin da Abba ya diba min.

Hankali na a tashe yake, ba dan komai se ba dan sanin ina cikin TSAKA MAI WUYA, wasa wasa abinda nake tunanin ba ze faru ba shi yake shirin tabbata.

Tuni muka tsara yadda neman aure zuwa bikin auren mu ze kasance da Ibrahim, haka kuma matar sa ta haihu an samu da namiji, watan sa hudu da rabi yanzu.

Haka kuma bayan wata daya da haihuwar ta ne na kawo masa batun auren mu, da farko kasa amsa min yayi, se daga baya ya amsa min, amma yace ze yi tafiya zuwa wani course na two months, in ya dawo iyayen sa would go and meet Abba.

Ban ji dadi ba amma na share nayi masa fatan dawowa lafiya, muka cigaba da hirar mu.

Wata biyu ya wuce na masa magana lokacin ya dawo, se ya ban uzurin auren kanwar sa, aka yi aka gama se ya fuskanci iyayen sa da magana ta kamar yadda yace wanda later na gane duk karya ce, yaudara ce irin ta da namiji.

Sedai kashegarin rabuwar mu kan ze wa iyayen sa batu na se gashi afujajan cikin tashin hankalin iyayen sa sun ki amincewa da yayi aure, a karo na biyu da na shiga irin wannan tashin hankalin.

Na tashi hankali na, na dena ci na dena sha se da naga zan kashe kai na a banza a wofi sannan dan ban bari kowa ya san halin da nake ciki ba, a tunani na abin me sauki ne, Ibrahim can convince his parent, sedai har  satin da ya wuce maganar daya ce, ba zasu nema masa aure ba dan su a familyn su mace daya ake aura, kuma ta gida.

A lokacin ne naji duk wani garkuwar jiki na ta karye, tuno alkawarin mu da Abba kuwa in nayi se kaina ya sara, ina neman jawowa kai na hawan jini a banza a wofi.

Ya Masdooq ma duk hankalin sa ya tashi, shi abin biyu ya hade masa, ga nawa sharadin ga nashi alkawarin tsakanin sa da Abba, shima har number Ibrahim ya karba yake kira yaji yaya, sedai har yau da Abba ya kira ni babu wani zance daga iyayen IBRAHIM.

Abin da ya kara tashin hankali na be wuce kuka da Ibrahim yazo yana min ba, Nima da na rasa abun yi kukan na fashe da shi, a haka ya Masdooq ya shigo ya same mu, se yaji ai mu namu wasa ne, kukan dadi muke yi, shi ta ko wane angle yana cikin TSAKA ME WUYA NE, shiyasa gaba daya ya rame kamar ba shi ba, yau kam ba ni kadai nake fargaban haduwa da Abba ba, har da shi ma...............✍️.

Vote
Comment
Share fisabilillah

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 026 [ 3/07/2024 8:02pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Oummey
Free book!!!

*ZINARIYAR MACE⚡*
*Wai shin 'yar'uwa menene matsalarki? zubewar nono, ko kuma rashin kwankwason juyawa a falo maigida ya shiririce ya manta da tibi da matan tictok, menene matsalarki ne? rashin ni'ima ko kuma mugun sanyin da ya yi miki katutu, shin rashin taushin fata ne ko kuma kuraje da tabbani, ko bala'in ramar da ta addabeki kuma babu rashin ci ba rashin sha a gidan auranki, gwaigwayewar gashi ce matsalarki ko kuma kaushi da faso na tafin kafa da bushewar fata, kina bukatar fatarki ta yi glowing kalarki ta fita kuraje su mutu, ko kuma kina bukatar azababbun turaruka da humra tare da turarukan wuta. Na san dai kuna da yawa matan da tumbi ya yi musu

karan tsaye ina nufin ya katse muku hanzarin yi wa maigida gwalli da muskuce-muskuce a falo😃 Nesa fa ta zo kusa AL-KUTUBIYYA ISLAMIC MEDICINE sun tanadar muku da nau'in magungunan da suke magance kowace irin matsala da izinin Allah. Babban burinmu shine sha'ani na aure ya inganta a samu daidaito. Muna da.*
Na gyaran nono.
Na sanyi.
Dilka tare da hadin sabulu.
Duk Wani nau'in maganin mata.
Humra turarukan wuta perfumes, original miski tahra 3in1, ciccibi budurwar kaza. Had'addun supplement irin wad'anda ba su da matsala. Maganin Sliming wato narka tumbi. Abubuwan da muke sayarwa suna da yawa, kuma babu asarar dukiya. Muna garin kano kuma muna tura kayanmu kowane gari fad'in Najeria da Nijar har ma da kasashemn ketare. Kai tsaye a tuntu'bemu ta lambobin wayarmu domin karin bayani.
*08089965176*
*07084653262*

Ouummey 026

Page 26

____________________Duk da halin da yake ciki haka ya zauna lallashin mu da kwantar mana da hankali kan ba abinda ze faru se khair insha Allah, duk abin nan fa karfin hali ne kawai yake yi dan shima in dai ka san shi kana ganin sa zaka san yana cikin tashin hankali.

Haka ya sallami Ibrahim ya tafi mu kuma muka cigaba da zama cikin zulumi, duk da ni se kwantar min da hankali yake yi tare da ja na da wasa, a haka muka yi sallar Isha mu ka cigaba da zaman jiran Abba.

Aikuwa ten minutes after that ya kira mu a tare, jiki ba laka muka nufi parlon sa, na kama hannun hannun sa na kankame dan shi ne kwarin gwiwa ta, da ace Abba ni kadai ya kira to bana jin kafata ma zata iya dauka na zuwa wajen su.

Shima be hana ni ba, a haka muka shiga ciki, Abba ya kalli hannun mu dake hade ya dauke kan sa ya maida kan Tv, fuskar sa a hade kamar ba Abba na me yawan fara'a ba.

Be wani ja zance ba bayan amsa gaisuwar mu da yayi ya dube ni tare da kiran suna na,

azabure na amsa ina zare ido hannu na na rawa, na ma kasa amsa masa se da ya sake kira na, baki na rawa na amsa masa haka ma jiki na, jin haka Ya Masdooq ya sake matse hannu na cikin nasa, hakan kuma ya taimaka wajen ara min ƴar nutsuwa.

"Allah ya kawo mu cikar wata bakwai kamar yadda sharadin mu yake, gashi kuma har yanzu shiru ba wani labari".

Na kasa magana, se girgiza kai da nake yi, fiye da minti biyu kafin na fisgo murya ta

"Abba dan Allah ka kara mana lokaci, wallahi...".

"Ai babu wannan zancen dan bakin alkalami ya riga da ya bushe Nu'aimah, Masdooq".

Abba ya tare ni tun ma kan na karasa, kana ya karashe da kiran sunan Yaya da kan sa ke duke, ya amsa a hankali, muryar sa ta sake yin sanyi fiye da baya

"Yaya makomar alkawarin mu da kai?".

"Yana nan Abba, sedai ina neman alfarma dan Allah".

Girgiza kai Abba yayi,

"Ba halin ka ba ne karanta, kar ka fara, kai din babban mutum ne da aka san ka da magana daya, kar ka canja mana, and well, am sorry to say babu alfarmar da zan iya yi maka ko ita yanzu, ku tashi kuje".

Hakuri Ya Masdooq ya bawa Abba kana ya tashi kamar wanda kwai ya fashewa a ciki idanun sa sun sake rinewa, ni kam kasa tashi nayi se da ya mikar da ni, a jikin sa na jingina ya sa hannu ya rike kafada ta jin yadda jiki na ke rawa ta yadda kafata ma rawar ta ke yi, kuma in yayi gangancin saki na faduwa zan yi, a haka muka fice wanda idanun Abba na kan mu har muka fita kana ya juyo ya dubi Mama da itama din mu take kallo idanun ta cike da wani irin fata.

"Me ke ranki game da hukunci na akan su?".

"Ni kam ina cikin matukar farin ciki da jin dadi, ko ba komai zumuncin mu ze kara karfi, Aimah kuma ta samu abokin rayuwa managarci, alhamdulillah". Mama ta fada cike da farin ciki

"Above all that, tarbiyyar ta ze gyaru, ina hango gyaruwar barakar da muka samar a tare da ita".

"Insha Allah".

Mama ta amsa Abba da ya fadi statement din sa cike da rauni, Abba ya gyara zama ya shiga kiran wayar Baba, ita kuma Mama tana kiran Hajiya Yayah.

Mukam da muka fita be sake ni ba se da ya kai ni bedroom dina ya zaunar da ni a bakin gado na, shima ya zauna gefe na, dukan mu muka yi shiru mun rasa abin fada, ni kam zamewa nayi na kwanta kan bed din ina jin zazzabi from no where na neman rufe ni, har kuma lokacin jiki na be bar rawa ba.

Mun jima a haka sannan ya dago cikin dasasshiyar murya yace

"Am sorry Barbie, I've failed, na kasa tsaya miki, na kasa baki farin ciki, am very sorry".

Duk halin da nake ciki se da na kokarta na tashi zaune tare da girgiza masa kai

"No sweetheart, ba laifin ka bane, tun farko laifi na ne da na amince, kuma manyan masu laifin iyayen Ibrahim ne da suka gaza duban mu, su ne silar komai Ya, sun kasa gane irin son dq muke wa juna, ina matukar son Ibrahim sweetheart, ji yadda zuciya ta ke bugawa, zafi take min har ina jin kamar na mutu, kuma ina so na mutum da dai a raba ni da Ibrahim".

Na kai hannun sa kan kirji na bangaren hagu wai ya ji bugun zuciya ta dake tafiya abnormally, se dai be yadda na kai din ba ya zare hannun sa daga nawa tare da janyo ni jikin sa ya rungume, wani irin runguma dake speaking irin tashin hankalin da yake ciki, Nima ban yi wata wata ba na zagaye shi da nawa hannun, a haka muna jin irin yadda zuciyoyin mu ke bugawa sa karfi da karfi, musamman tasa da nake jin kamar zata balla kirjin sa ne ta fito.

Mun dade a haka kafin ya sake ni ya kwantar da ni tare da ja min blanket ya rufe ni kana ya duka daidai saitin fuska ta yace cikin wata irin murya da ba zan taba mantawa ba

"Ko me ze faru a gaba, ko yaya abubuwa zasu kasance always know nayi iya yina, nayi dukkan kokari na wajen ganin na baki abinda kike so, wajen ganin na sama miki farin ciki batare da duba da nawa ba, no matter thee outcome ki sani Masdooq me son ki da kaunar ki ne, me fafutuka ne wajen ganin ya sama miki farin ciki da jin dadi tare da cikar buri, baze taba yin abinda ya san ze saki kuka ko damuwa ba, pls kar ki manta you're always my first priority AIMAHHHH".

Ban san dalili ba se na ji kirji na na wani irin bugu, zuciya ta na fada min something strange is about to happen, wanda ban san mene ba, me kyau ne or bad, ba zan iya cewa ba.

Ban ankara ba se saukan tattausan lips din sa na ji kan fatar goshi na, ya bani wani dogon peck me tsayawa a rai, kafin ya daga ya juya ya fice daga dakin, na bishi da kallo zuciyar ta na dokawa da wani irin yanayi da ba zan iya fassarawa ba.

Haka na kwana almost ido biyu, dan se after sallar subh sannan bacci ya kwashe ni, ban farka ba se after twelve, shima Mama ce ta tashe ni.

Tun ina zuba ido ganin wane hukunci Abba ze yi, tun ina fargabar kar ya haɗa ni da wani jama'ar yadda yacee har na daina faduwar gaba, ganin anci a week an two days shiru, be sake tada maganar ba haka nima, se na koma bakin aiki na.

Kudi Abba ya bani kamar yadda ya saba na gyaran jiki na wanda nake yi every month, yau Alhamis gobe sabon wata ze kama, na je aka min thorough gyaran jiki kamar yadda aka saba, fata ta se sheki take tana walwali, ko da na dawo Mama tayi ta koda ni, tun bare ja da bakin lallen da aka min tare da gyaran gashi, dama lalle kam ni ya zame min jiki, wani na fita sati kawai nake karawa naje ayi min sabo, wannan kuma da fitar na baya sati biyu tukuna na yi sabo, saboda ganin wata ya kusa karewa, se na bar shi nayi gaba dayaa da gyaran jiki wanda ni kaina lalle da gyaran jiki kai har gyaran gashin sun burge ni fiye da ko yaushe dan ba karya wannan karan har wani special treatment naga ana min, dan wajen kamar ma mun zama yan uwa ne da su dan Mama da Hajiya Yayah a nan ake musu komai.

Washegari Friday na tashi da farin ciki, tun asuba na tashi na shiga aikin cake da aka yi order, kasancewar ina yi a gida wani sa'in se na shiga abu na, karfe goma na gama na saka a fridge dake birthday cake ne, masu shi zasu zo su amsa har gida.

Ko da na shiga nayi wanka wani sabon gown me shegen kyau Mama ta kawo min na saka, golden ne lace din me adon black thread and stones, ban wani damu ba dan sa'i da lokaci musamman Friday Mama kan kawo min sabon kaya kamar dai yanzu, wannan yasa kaya na gasu nan ne ni kaina bana ce ga adadin su ba dan kullum a cikin sabo nake, kasancewar ya daya mace yasa Mama ke tsaye a kai na da duk wani abu da ya danganci kayan gyara na mace da na kwalliya, ga yayye na ga kuma Abba na, ga su Hajiya Yayah.

Lokacin da Mama ta kawo min shoe and veil da zan yi amfani da shi se da nayi tsalle na dane ta ina ihun murna, ba dan komai ba saboda dream shoe na ne, kwanaki na gan shi a Instagram na nuna wa Abba ina so, ya amsa min be kai ga kawowa ba aka kama masa wasu kayan sa se hankalin sa ya dauku zuwa can.

Da na wa Mama magana se tace ita ya yi tsada in dai bari Abban ya kawo min, dan takalmin da shi da purse din sa are worth 200k, da nace zan fadawa ya Masdooq ya siya min se Mama tace a'a in kyale shi yana kan aikin bude min shagon da na ma Baba magana, shi Baba ya siya shafin da aka samo ya gyara amma se yace nauyin zuba kayan aiki da kawata wajen na hannun Ya Masdooq ne.

Dole na hakura dan ai ko banza dai ina da hankali ko, na san akan wannan shagon ba kananan kudi yake kashewa ba, so se na bar maganar, se gashi kuma yanzu unexpected Mama ta kawo min shi.

Na sake ta na zauna bakin bed ina daura takalmin a kafa ta, baki ne da yasha ado da golden and black stones, high heel kamar yadda na gan shi nake kuma so, me madauri a ta baya, nan da nan na daura, se gashi kuwa cif cif a kafata, ya zauna yayi matukar kyau kamar dan ni a ka

yi shi, tun bare da kafar ke kawace da ja da bakin lalle.

Na tashi nayi tafiya akan abina rai na fess, Mama na ganin yayi ta ficewar ta, ni kuma na karasa na zauna kan dressing chair na shiga make up wa face na, nude make up nayi da ya karbi face na sosai da sosai, nayi kyau ba karya, na gyara gashi na na masa chignon se na kwantar da gaban shima in style kana na dauki dankwalin kayan tare da bakin scarf na dauri da shi kan sa abin kallo ne na shiga nadawa, kafin kace me na daura abina in steps yayi kyau yayi fadi kamar wata bride, dan ita kan ta gown din bridal style ne da aka ratsawa wani Black expensive abin din ki yaji stone yayi kyau.

Na juya na kalli kai na na sake juyawa raina cike da farin ciki, dan a rayuwa ta ina son na ga na saka kaya nayi kyau, ina burge kai na sosai da sosai, ina ganin komai yayi na dauki perfumes na shiga wankan su, kala kala se da na sa kusan kala goma kafin na hakura, na karasa na dauki purse din takalmin na jujjuya ta cike da sha'awa kana na dauki veil din na yafa a kafada ta ta bari daya, na dauko waya ta da Ya Masdooq ya siya min kwanakin baya iphone 13 na karkace na shiga kwasar selfies, daga karshe na fita zuwa gaban console din falo na shiga yi ta mirror.

Daga karshe na bi Mama parlo din ta na saka ta min masu kyau sannan na karba, ban yi wata wata ba nayi updating Instagram page na, tun kan na fita na fara ganin ruwan likes and comments, ban tsaya ba na fice zuwa watsaapp na tura wa Ya Masdooq da Ibrahim da Ya Ahmad da Aunty Luba se kuma na dora status, kana na ka twitter and Facebook handles dina suma duk na saka.

Tun kan na aje text din Ya Masdooq ya shigo, exerggerating how cute, beautiful and adorable I look, bayin Allah kun san me, wallahi i love Ya Masdooq tuntuni kawai yarinta yasa a lokacin na kasa fahimta balle na gane.

Ina gama karanta nashi kafin na masa reply se ga text din Ibrahim, amma ban tsaya dubawa ba se da na gama ma sweetheart reply, and guess what ban wani ji farin cikin yabon da Ibrahim yayi min ba kamar na sweetheart.

Ina kokarin aje wayar bayan na gama amsa phone call din Aunty Luba se ga alert a bank account dina, ina dubawa 100k ne from Ya Masdooq, ko da na kira shi se cewa yayi kudin kwalliyar ya biya, a sake siyan sababbin kayan kwalliyar da za'a dinga yi indai zan dinga yin irin wannan kyan.

Kasa magana nayi se kawai "you're always the best and you'll forever be" da nace masa, daga haka yayi min juma'a kareemah ya kashe wayar.

Ko da Abba ya fito ze tafi masallaci haka ya dinga yabon kyan da nayi, shima yayi kyau sosai, looking very responsible a cikin farar Babbar rigar sa da ta sha aiki da ruwan kasan zare cikin ɗinkin aska biyu, kun san me? Abba na dan gayu ne, wayyayye da ya san ta kan kaya da

wanka, ya iya saka hula wallahi, da sauri na matsa kusa da shi nace Mama ta mana hoto, ai kuwa ta mana guda uku masu kyau, se kuma muka yi selfie mu duka, sannan na feshewa Abba pray mat din sa da turare na rako sa compound, se kuma ga motar Ya Masdooq ta shigo gidan, se Abba ya tsaya be shiga mota ba..................✍️.

Vote
Comment
Share fisabilillah

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 027  [ 3/07/2024 8:03pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Oummey
Free book!!!

*ZINARIYAR MACE⚡*
*Wai shin 'yar'uwa menene matsalarki? zubewar nono, ko kuma rashin kwankwason juyawa a falo maigida ya shiririce ya manta da tibi da matan tictok, menene matsalarki ne? rashin ni'ima ko kuma mugun sanyin da ya yi miki katutu, shin rashin taushin fata ne ko kuma kuraje da tabbani,  ko bala'in ramar da ta addabeki kuma babu rashin ci ba rashin sha a gidan auranki, gwaigwayewar gashi ce matsalarki ko kuma kaushi da faso na tafin kafa da bushewar fata, kina bukatar fatarki ta yi glowing kalarki ta fita kuraje su mutu, ko kuma kina bukatar azababbun turaruka da humra tare da turarukan wuta. Na san dai kuna da yawa matan da tumbi ya yi musu karan tsaye ina nufin ya katse muku hanzarin yi wa maigida gwalli da muskuce-muskuce a falo😃 Nesa fa ta zo kusa AL-KUTUBIYYA ISLAMIC MEDICINE sun tanadar muku da nau'in magungunan da suke magance kowace irin matsala da izinin Allah. Babban burinmu shine

sha'ani na aure ya inganta a samu daidaito. Muna da.*
Na gyaran nono.
Na sanyi.
Dilka tare da hadin sabulu.
Duk Wani nau'in maganin mata.
Humra turarukan wuta perfumes, original miski tahra 3in1, ciccibi budurwar kaza. Had'addun supplement irin wad'anda ba su da matsala. Maganin Sliming wato narka tumbi. Abubuwan da muke sayarwa suna da yawa, kuma babu asarar dukiya. Muna garin kano kuma muna tura kayanmu kowane gari fad'in Najeria da Nijar har ma da kasashemn ketare. Kai tsaye a tuntu'bemu ta lambobin wayarmu domin karin bayani.
*08089965176*
*07084653262*



___________________Ni kuwa tuni na bawa Abba daddumar sa na nufi motar da sauri, bangaren driver ba bude ina kiran sunan shi, se na ja baya da sauri ganin ya Farooq, na fara zare ido dan na san se yayi min bala'i amma ga mamaki na se ya sake min mutmushin da yasa kamannin mu suka fito, rashin sabo ya sa da sauri na shiga gaishe shi, ya amsa min se na ja baya ina kallon daya side din da Ya Masdooq ya fito.

Ina son in je wajen shi amma ina tsoron ya Farooq, se na juya zan koma wajen Abba se kuwa ya kira ni

"Barbie".

Na kalle shi se ya min alamar na zo, da kuwa sauri na nayi wajen shi, ina zuwa tun kan na gaishe shi ya katse ni da fadin

"Kin yi kyau".
Se na samu kai na da lumshe ido cikin farin ciki da jin dadi, ban san me yasa ba in dai ya yabo ado na se in dinga ganin kyan adon fiye da baya ko da kuwa na san nayi kyan.

Tare muka jera zuwa wajen Abba batare da na iya gaishe shin ba, muna zuwa Masdooq ya tsaya gefen Abba bayan ya duka har kasa ya gaida shi, ya sa na tsaya gefen Abba bangaren hagu ya ciro wayar sa ya bawa Ya Farooq yace yayi mana photo, aikuwa ya mana masu kyau biyu, Abba na matsawa na matsa jikin Ya Masdooq na bawa Ya Farooq waya ta cikin dari dari nace ya mana pics, na zata ze zage ni yace na raina shi se naga kawai ya karba bakin sa dauke da mutmushi yayi mana har biyar se ya miko min.

Da zasu tafi se na karbi wayar Ya Masdooq nace zan tura pic din da aka mana da Abba se yace nima in tura masa wanda aka yi mana mu biyu da kuma photos dina masu yawa, na amsa shi na karba na koma cikin gida su kuma suka tafi masallaci.

Ina zaune a falo ina turawa se ga sallamar Aunty Luba, na tashi na rungume ta ina ihu se kuma na karbe Mimi dake hannun ta, kuka zauna muka bude sabon fejin hira tare da Mama da ta fito.

Ranar kin yin girki nayi nace nayi gayu, suna ta tsokana ta se Aunty Luba ce tayi, ana saukowa masallaci se ga Abba da tawagar ƴaƴan sa maza, abin mamaki se gashi suna kiran na taso muzo muyi photo, abin daure kai duk hoton da za'a yi se an yi da ni da Ya Masdooq, kuma a tsakiya ake samu, a'a a jima kadan mana, ba se ga Baba da Hajiya Yayah ba, haka ka yi ta dauke dauken pic, dake dama dabi'a tace se ga shi ban ko gaji ba, ana gamawa da iyaye suka shige suka bar mu muna tayi, mune har garden.

Kuma ko da na riƙe ya Masdooq be kalle ni yada yake yi da ba, se ma sake riko ni jikin sa da yayi muka yi ta pics, har da wanda ya duko yayi pecking goshi na, style kala kala, kuma jiki na be taba cakuduwa da na wani namiji ba ko da ba Ya Masdooq din be irin na ranar.

Ko da aka gama pic nan muka yi zaman mu a garden leaving su Mama a cikin gida, ana gama abinci me aikin mu da ta su Hajiya Yayah da aka taho da ita su suka dinga bi suna rabawa, nan cikin garden din muka ci abincin, ba mu fito ba se da aka kira Asr, mazan suka tafi masallaci, mu matan muka yi ciki.

Ni, Aunty Luba da matar ya Najeeb Aunty Labiba muka yi sallah a daki na, Hajiya Yayah kuma na dakin Mama, su Abba sun fita suma.

A dakin muka yi zaman mu bayan mun yi sallah, gaban mu cike da snacks da juices muna ta hira, suma mazan suna bangaren mazan gidan sun baje a parlo suma snacks da juices kala kala a gaban su a wadace.

Gathering din be tashi ba se after magrib, suna dawowa daga sallah Ya Salman ya dauki Aunty Luba suka tafi, Baba dama su suka fara wucewa da Hajiya Yayah, se Ya Najeeb da Aunty Labiba, Ya Ahmad kuwa dama tun Asr ya koma school, dan yana da exam Saturday morning.

Ya saura ni da Mama da Ya Masdooq, shi kam yace se yayi dinner ze tafi, aikuwa yana dawowa daga Isha tare muka yi dinner dashi da su Abba a falon Abba dan nan muke dinner kullum,

sedai In bazan yi tare da su ba in bana jin cin abinci da wuri.

Sallama yayi wa su Abba suna ta masa addu'a da shi albarka, ban jira ance na raka shi ba na tashi na bi bayan sa kamar yadda na saba, a bakin kofa na samu yana jira na, yau shi ya rike hannu na da kan sa muka fita zuwa main falo, muna shiga main falo ya jawo ni ya rungume kan sa akan gashi na, na sa hannu na zagaye shi ina lafewa cikin faffadan kirjin sa.

Minti kusan uku muka yi a haka kafin ya janye yana kallon fuska ta da na dago ina kallon shi nima, se ya sake min kyakkyawan murmushin sa yana fadi cikin daddadar muryar sa

"Na dade ina son jin kamshin turaren gashin ki, yana min dadi sosai, and alhamdulillah yau na shaka to my satisfaction kuma yafi kamshi a jikin gashin ki".

Mutmushi nayi me kyau nace

"Ni kuma sajen ka ke burge ni sosai sweetheart, how I wish zan iya tabawa".

Da murmushin da ya kasa barin fuskar sa ya kama hannaye na duka biyu ya kai each side na face din sa placing them on kwantaccen sumar wajen Idanun sa on my face looking straight into my eyes, a hankali na lumshe nawa eyes din dan ba zan iya jurar cigaba da kallon cikin idanun sa ba, dan wasu irin abubuwa nake hangowa manya masu wuyar fassaruwa, a hankali ya sake hannu na leaving them kan kuncin sa yayinda nake jin kaifin idanun sa a fuska ta, idanu na a rufe har lokacin nan bata fuska nace

"Ni wallahi ka dena kallo na, ai da zaka shinshina gashi na se da ka rungume ni dan kar na kalli fuskar ka shine ni kake kallo na, wannan idanun naka masu kaifi na piercing dina".

Dariya yayi, a karo na biyu na ga dariyar sa wanda ta yau ma ta fi ta rannan karfi dan yanzu duka bakin sa a bude yake, a sace sace na bude idanu na na shiga kallon sa, dariya na masa kyau matuka, hakwaran sa na kara ma dariyar armashi.

"Tom nima ki rungume ni se ki shafa abin ki".

"Tab to in na rungume ka ai face din ka bayana ze yi facing, ta ina zan shafa, kawai ka rufe idon ka".

Be ja ba yace "okay na rufe".

Se da na leka fuskar sa sosai na tabbatar ya rufe idon sannan na tsurawa sajen ido, Allah ya sani yana matukar burge ni, haka kuma na dade ina son taba wa ko dan naji laushin gashin dan idanu na na nuna min zasu laushi sosai.

A hankali kamar me tsoro na fara motsa hannaye na dake kan kuncin sa ina shafa gashin

wajen, kalmar yadda nayi zato kam yana da laushi, taushi and salki duk a lokaci daya, a sannu nake shafawa se kuma can na maida hannu na daya keyar sa in da gashin wajen yayi kwance lamban cikin style din da yayi masa, ai jin laushin gashin da yadda hannu na ke lumewa ciki se na maida dayan ma, nice har da cire masa hular kan sa ina yamutsa gashin, a hankali ya shiga tafiya damu bayan ya sakalo hannun sa kugu na har muka kai jikin bango ya jingina, nikam kamar me neman wani abu da aka boye a gashin sa haka na dinga yamutsa masa shi, gaba daya ba lalata style din da yayi, se da yaji abin nawa ba na kare bane sannan ya daga hannayen sa ya riko nawa tare da fito su daga kan sa, ya kuma bude idanun sa da na sa ya rufe.

Waro ido nayi ganin yadda color din idanun sa suka dan canja

"Kan ka na ciwo ne? Naga idan ka ya canja kala".

"Bacci kika sa na fara ji da wannan susan naki, daga kuma saje se ki koma kai, dubi yadda duka kika lalata min gashi".

Na dan langwabar da kai ina karamar dariya

"Allah gashin ne ya kira ni, ga laushi kaman na mace, da kyar ma fa in be fi nawa laushi ba, watarana dai zan maka kitso a gashin nan, kuma fa kyau ze yi".

Harara ta yayi yana fadin

"Kice kawai kin shirya mai da ni dan daudi".

"Allah ya tsare, to kai ai ko na maka kitso ba zaka yi kama da yan daudi ba da jikin ka irin na cikakkun maza ne".

Na fada ina sake duban sa tun daga kafar sa zuwa kan sa, Ya Masdooq na da tsayi sosai dan duk yafi yayye na tsayi, haka kuma ba shi da kiba amma a murje yake kuma daga damtsen hannun sa zuwa cikin sa a murde yake saboda gimming, yana da six packs abs wanda ke bayyana in dai ya saka kananan kaya.

"Uhm, fada min yaya jikin cikakkun maza yake?".

Ni ban san ma ya akai na fada masa haka ba, dan ban san yadda zan masa bayani ba, se kawai na daga hannu na nuna dantsen sa

"Ai nan din ka a murde yake ba irin na mata ko yan daudu ba".

Mutmushi yayi tare da dauke hulan sa daga kai na ya dora a kan sa, ya tsuguno yayi pecking kunci na tare da rungume ni kadan ya sake ni

"Bye".

"Safe drive, and take care pls".

Gyada min kai tayi ya juya ya fita na bishi da kallo baki na a tale da murmushi.

Se da ya fita daga falon sannan na juya zuwa ciki, wanka nayi na canja kaya zuwa na bacci na kwanta kan bed na shiga duba handles dina ina ganin irin likes and comments da na samu tare da shares, ina kuma bin comments ina karantawa, wasu nayi likes wasu comments.

A haka har kusan goma se na kashe data na tashi zuwa falon Abba, na musu saida safe na dawo na kwanta, gajiyar dake jikina yasa take bacci yayi gaba dani, bacci me cike da wasu irin mafarkan da a lokacin ban gane ba, se washegari da Abba yake sanar da ni abinda na ji kamar tatsuniya ko wata hikaya.

Washegari na tashi bana jin jiki na sosai, ba wai ban da lafiya ba, a'a amma dai haka kawai naji jiki na yayi min nauyi, and bana jina cikin farin ciki, ga faduwar gaba da nake fama da ita ko yaya na motsa.

Nayi duk wani abinda ya zama al'adar rayuwa ta kafin na tafi karyawa tare da su Abba, wanda Mama ta shigo kira na yafi so a kirga ban iya tashi ba se yanzu da na daure.

Kamar kullum muka karya cikin farin ciki duk da dukan su sun lura ba ni da walwala, I'm just faking it.

Muna gama karyawa na mike dan tafiya se Abba ya tsayar dani yace in jira shi ya karasa, na nemi sitter na zauna tare da ɗaukan remote na canja channel daga news din da Abba me kalla zuwa animation dan ina son shi, sedai ga mamaki na bana ma gane me nake kalla, hankali na ya tafi inda nima ban sani ba.

Abba na gamawa suka dawo falo tare da Mama, suka zauna irin yadda suka saba a gaban mu, Abba cikin three sitter, Mama cikin one sitter kusa da shi.

Abba ya karkata ya fiddo wasu kudi ya aje a gefen sa, kana ya kira sunana, na amsa masa se yace in matso kusa.

Na tashi na komq gefen sa na zauna se ya dauki kudin ya mika min, na kalli kudin gabana na faduwa haka kawai, though Abba ya saba bani kudin kashewa amma se nake jin wannan wani iri.

"Na mene ne Abba?".

"Karba tukuna".

Na sa hannu na karba, ya sa hannu a aljihu ya fiddo wata diamond necklace karama me kyau tare da earing din ta shima ya miko min, wannan karon ban tambaya ba kawai na sa hannu na karba ina juya ta, tayi kyau sosai, na dago na dubi Abba cikin neman karin bayani

"Sadakin ki ne, na daura miki aure a jiya juma'a cikin sahalewar Ubangiji, na zaba miki miji nagari da ya dace dake, wanda insha Allah ina da yakinin in har kika kwantar da hankali kika nutsu kika zauna ba zaki taba samun damuwa da shi ba".

Wani irin dam daram dam haka naji saukar kalaman Abba, Aure kawai nake ta maimaita wa cikin rai na, Abba ya daura min aure, Abba ya daura min aure, shine abinda ke maimaituwa cikin rai na, tsayin lokaci kafin na kada baki nace

"Kamar aure naji kace ka daura min ko Abba?".

Cikin tabbatarwa Abba yace

"Ba kama bane Nu'aimah, aure ne na daura miki a jiya da mijin da ya dace da ke".

Aikuwa se na daddage na fasa ihu, ihu ba na wasa ba, na dau hannaye na duka biyu na dora a ka ina kiran na shiga uku na lalace

"A'a Abba, dan Allah dan Annabi kar ka min haka, ka ji kai na ka tausaya min kar kayi min auren dole, wallahi bana san shi ko waye, shima kuma na san baya so na, dan Allah Abba kace wasa kake, wayyo Allah na na shiga uku na lalace, wayyo Abba ya daina so na".

Hankali kwance batare da damuwa da ihun da nake ba Abba yace

"Inaaa, ko a mafarki ba zan taba aura miki wanda na san baya san ki ba, mijin ki yafi kowa kaunar ki, ya fi kowa son ki kamar yadda na tabbatar yana miki son da ko kan shi baya yi wa, dan haka ki kwantar da hankalin ki, wanda yake son ki na aura miki".

Se na tsayar da kuka na take, har da sauke ajiyar zuciya jin malaman Abba, amma dan na kore shakku se nace

"Abba Ibrahim ka aura min? Dan na san shi ne me so da kauna ta".

"Ko daya, wanda ya fi Ibrahim kaunar ki na aura miki, wanda nake da yakinin soyayyar ki ba zata taba gushewar daga ran sa ba har mutuwa".

Cikin mamaki, fargaba da wani irin curiousity na tambayi Abba waye shi, dan bana zatan akwai wanda ze taba fin Ibrahim so da kauna ta, dan hakq na kagu naji waye wannan da Abba ke fadi.

Kamar saukar aradu, kamar tashin BOM haka naji muryar Abba na amsa kuwwa a kunne na lokacin da ya ambaci

"MASDOOQ".................✍️.

To Allah ya kawo mu lokaci ya kawo mu, yau dai an daura auren Masdooq da Aimah 💃💃💃💃💃💃💃💃💃💃

Ta zama ta zama ta zama, ta zama matar Masdooq 😂😂😂😂😂.

Ya kuke tunani, shin Aimah zata karbi Masdooq matsayin miji?, In har ta karbe shi to Meye silar rabuwar su?

In kuma baya karbe shi ba yaya kuke tunanin lamarin ze kasance???

Mu hadu a comment section!!!.

Vote
Comment
Share fisabilillah

Ouummey📚✍️.

Ouummey 028 [ 4/07/2024 7:13pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Oummey
Free book!!!

*ZINARIYAR MACE⚡*
*Wai shin 'yar'uwa menene matsalarki? zubewar nono, ko kuma rashin kwankwason juyawa a falo maigida ya shiririce ya manta da tibi da matan tictok, menene matsalarki ne? rashin ni'ima ko kuma mugun sanyin da ya yi miki katutu, shin rashin taushin fata ne ko kuma kuraje da tabbani,  ko bala'in ramar da ta addabeki kuma babu rashin ci ba rashin sha a gidan auranki, gwaigwayewar gashi ce matsalarki ko kuma kaushi da faso na tafin kafa da bushewar fata, kina bukatar fatarki ta yi glowing kalarki ta fita kuraje su mutu, ko kuma kina bukatar azababbun turaruka da humra tare da turarukan wuta. Na san dai kuna da yawa matan da tumbi ya yi musu karan tsaye ina nufin ya katse muku hanzarin yi wa maigida gwalli da muskuce-muskuce a falo😃 Nesa fa ta zo kusa AL-KUTUBIYYA ISLAMIC MEDICINE sun tanadar muku da nau'in magungunan da suke magance kowace irin matsala da izinin Allah. Babban burinmu shine sha'ani na aure ya inganta a samu daidaito. Muna da.*
Na gyaran nono.
Na sanyi.
Dilka tare da hadin sabulu.
Duk Wani nau'in maganin mata.
Humra turarukan wuta perfumes, original miski tahra   3in1, ciccibi budurwar kaza. Had'addun supplement irin wad'anda ba su da matsala. Maganin Sliming wato narka tumbi. Abubuwan da muke sayarwa suna da yawa, kuma babu asarar dukiya. Muna garin kano kuma muna tura kayanmu kowane gari fad'in Najeria da Nijar har ma da  kasashemn ketare. Kai tsaye a tuntu'bemu ta lambobin wayarmu domin karin bayani.
*08089965176*
*07084653262*

Ouummey 028

Page28

___________________Sabida tsabar  rudewa da tashin hankali gaba daya se na manta Masdooq sunan sweetheart ne, se na tafi yawon tunanin waye Masdooq, a ina Abba ya san shi har yake yabon shi haka har kuma ya iya daukar ƴa guda ya bashi.

Da na kasa tunowa se na shiga tambayar Abba, shi da Mama se suka kalle ni cikin mamaki

kafin Abba ya sanar da ni Masdooq dai nawa, dan Hajiya Yayah da Baba.

A lokacin ne na shiga asalin tashin hankali, kawai tunani na yadda zamu yi zaman aure da sweetheart, mutumin da nake matuƙar so da kauna a matsayin Wa na, kallan wanda muke CIKI ƊAYA nake masa, kallan wanda muka zauna mahaifa daya muka sha mama daya, ta ina zan fara rayuwar aure da shi, inaaaa, hakan ba ze yiwu ba, ba zan yadda ba kuma ba ze taba Kasancewa ba.

"Naji na yarda ka aura min duk wanda kake so, gurgu ko makaho kai ko almajiri ne na yarda, amma dan girman iyayen ka Abba kar ka haɗa ni zaman aure da Ya Masdooq, wallahi ba zan iya ba, yayana ne fa, Abba kallan wanda muka fito ciki daya nake masa wallahi, dan Allah Abba ka dube ni ka dubi makoma ta".

Na fada cikin gunjin kuka, ni yanzu na yadda ya aura min kowaye, ko ba Ibrahim ba ne, amma ban da Ya Masdooq, ban da shi, ba kuma dan na tsane shi ba, se dan ba zan iya ba.

"Wannan shine iya zabin da zan iya miki, gatan da zan iya miki kenan a gidan duniya, dan haka kiyi hakuri ki maida komai ba komai ba, Masdooq yayan ki ne, amma ba wanda kuke ciki daya ba, dan haka babu inda aure ya haramta a tsakanin ku, so ki tashi kije ki sake tunani, ya sanki kin san shi, zan iya cewa kina cikin wanda suka masa makurar sani, dan haka bana tunanin zaku sami matsala Insha Allah ".

Daga haka Abba ya tashi ya shige bedroom din sa, leaving me helplessly crying a falon, Mama ta zo zata kama ni amma naki, na kwace hannu na na tashi ina layi da burarin kuka na fice, dan ai da hadin bakin ta aka yi komai, ba yadda za'a yi ace Abba yayi lamari irin haka bata sani ba, shine ta rufe ni bata gaya min ba tun da wuri in nemo mafita, se yanzu da abu ya kwabe zata ce zata wani rike ni.

Ina shiga bedroom dina na saka lock na zube nan bakin kofar na cigaba da kuka, birgima kuwa ba kalar wadda ban yi ba, murya ta kam se da ta fashe ranar saboda ihu.

Hankalin Mama ya tashi ta taho bakin kofar ta shiga bugawa tana kiran sunana da fadin in bude sedai ko saurar ta ban yi ba, daga baya da ta takura min se na shiga yi mata rashin kunya da tsiwa

"Ni ki kyale ni, kawai zaki zo ki wani takura min da kiraye kiraye bayan da hadin bakin ki aka cuce ni, da sanin ki aka zalunci rayuwa ta, dan kawai an haife ni, ai dai da aka haife ni ba halitta ta aka yi ba, kuma kuma ai ba auren dole aka yi muku ba, amma dake ni an tsane ni shine za a aura min wanda bana so, to wallahi bana yi, ba zan yi auren ba, se dai ku gaji ku sa ya sake ni, babu inda zani ehe...yiiiiiii".

Rashin kunya sosai na shiga zubawa Mama, amma hakan be sa tayi fushi ta bar wajen kofar ba, lallashi na take yi na bude ta shiga, ita tsoron ta Allah tsoron ta kar na cutar da kai na.

Ranar wuni guda nayi ina abu daya, ba ci ba sha se kuka, se da aka yi magrib na ji da gaske ciki na neman hadewa yake da bayana saboda yunwa, ga yan hanji na da nake jin sun tattare waje ɗaya sannan na shiga toilet na sha ruwa me dumi, wai ni Aimah ce da shan ruwan toilet, saboda na ɗorawa raina wahala, wai kar na bude kofa Mama ta shigo.

Daga nan se na bude fridge na kwashi snacks, inda Allah ya taimake ni kenan dan ina ajiyar su, naci na sha da drinks, na dasa sabon kuka da ihu, ban yi shiru ba se da wani munafukin bacci ya sadado ya dauke ni, ranar ko sallar Asr, magrib da Isha ban yi ba.

Washegari da safe na dasa sabo, sedai ganin kamar ba'a damu ba yasa na shiga fashe fashe, duk wani kayan glass na dakin se da na fashe shi, mirror, perfumes da show glasses komai se da na fasa, asarar da nayi bata kanan kudi bace.

Aikuwa se gashi cikin ikon Allah na tashi zuwa toilet nayi fitsari na dawo na taka wani katon piece na glass ɗin mirror, ya kuwa shiga ƙafan sosai, tsabar razana da ganin yadda jini yake flowing ban san na saki azababben ihu ba, ga kuma azaba dake ratsa ni, hankali a tashe Mama dake zaune falo cikin tashin hankali, ta kira Hajiya Yayah ta sanar mata kenan ta ji ihu na, ta taso da gudu dan ina jin takun ta tazo tana buga ƙofar, se dai ba zan iya tashi ba, ga shi se kuka nake ina kiran wayyo Mama wayyo kafa ta, jini na ze kare, wannan ya kara tayar da hankalin mama, ga windows na kama duka nayi locking din su ta ciki.

Duk ihun kiran na bude da Mama ke yi ban ko yi kokarin mikewa ba, har naji muryar ta na rawa alamun kuka, se kuma lokacin naji muryar Hajiya Yayah, wannan da ba wasa a ciki, in a commanding tone tana fadin na tashi na bude kofar nan.

Haka na tashi na tsaya kan kafa daya, na dauki mukullin dake cikin pocket din skinny jeans din jiki na na daddafa zuwa window na bude na jefa musu, har rige rigen dauka suke yi, Allah yasa Mama ta cafe suka matsa wajen door din suka yi unlocking.

Salati Hajiya Yayah ta saki lokacin da ta ga yadda na maida dakin, kamar wanda irin aka yi fadan cikin Film din India a ciki, komai ya watse a inda na wurga shi, glasses ta ko ina a kasa a farfashe, haka kaya na na wardrobe duk na watsar kan bed zuwa kasa.

Da kyar ta iya tsallakowa ta kama ni, cin takatsantsan ta fitar da ni daga dakin tare da zaunar ni kan kujera, se lokacin suka lura da irin jinin da na zubar nake kan ma zubarwa dan har lokacin jini be daina rushing out ba, gashi kwalban na ciki har lokacin, a gigice Hajiya Yayah ta dau phone din ta ta shiga kiran Ya Masdooq.

In less than ten minutes ya karaso, shi kan sa hankalin sa ya tashi ganin girman kwalbar, be tsaya jiran su ba ya dauke ni gaba ɗaya zuwa mota ya sani a backseat, Hajiya Yayah ta shiga baya Mama kuma gaba, ya tashi mota muka fice zuwa asibiti leaving house help din mu kadai, at the same time Mama na kiran number Abba dan ta sanar masa.

Muna zuwa aka karbe ni da sauri, sedan aka min anesthesia sannan aka zare kwalbar, duk da haka ban fasa jin zafi da radadi ba dan jini na na da karfi be karbi allurar sosai ba.

Se bayan an fito da ni zuwa wani dakin sannan Abba da ragowar brothers dina suka karaso, dukan su hankalin su ya tashi ganin irin girman wajen da kwalban ya shiga, an gyara an yi dressing, sedai suna jin yadda komai ya faru har aka samu broken glasses q daki na gaba daya ran su ya ɓaci suka shiga fada, ta inda suka shiga ba ta nan suke fita ba, daga ƙarshe se kawai na fashe da kuka ganin ma ba su damu da ciwon da naji ba se fada suke min.

Hajiya Yayah ce ta dakatar da su tace bata son haka, su bar ni naji da abinda ke damu na mana, se kuma lokacin Ya Masdooq ya shigo, yaje ya siyo magunguna da alluran da aka prescribing, yana shigowa na maza na rufe ido kamar ina bacci, dan ko ganin shi bana san yi.

Gaba daya yayi bakikirin a idanu na yau, haushin sa nake ji, kamar na je na shake shi, sedai hakan ba ze yiwu ba.

Ina jin shi ya karasa gaban gadon da nake kwance yana min sannu amma nayi banza kamar da gaske bacci nake, Hajiya Yayah dake gefe na tace masa bacci nake yi, se ya aje ledan magungunan ya koma kusa da su ya Salman.
Nayi mamakin dalilin ta na goya min baya da sunan ina bacci dan ta san ba baccin nake ba, dan yana tafiya da na bude ido se cikin nata, ta min mutmushi ta cigaba da shafa sumar kai na da take yi, kun san abin haushi, ko kunya fa ban ji ba, se ma dadi da naji ganin alamun da alama zata fahimce ni ta san bana san auren nan, dan haka na kudure ban zan koma gida ba, ita zan bi dan in samu in sanar mata ta sa a raba auren nan da yake neman zame min alakakai.

Kwana na daya a asibiti aka yi discharging din mu, kamar yadda na kudura kuwa na makale wa Hajiya Yayah nace ita zan bi, Abba be hana ba amma ya sanar min tariya ta is in five days coming.

Da wannan tashin hankalin muka karasa gidan ta, tun cikin mota nake ta rusar kuka kamar wadda iyayen ta suka mutu, tana ta lallashi na a hankali, ya Masdooq na gaba yana jin mu, sedai bece komai ba.

Muna zuwa ta kama ni zuwa dakina na gidan da yake a gyare se tashin kamshi yake, ta zaunar da ni bakin bed tayi ta lallashi kana tace bari taje ta dora wa Baba abincin dare, dan lokacin shida da minti biyu, se da ta tambaye ni akwai abinda nake so nace babu sannan ta tafi.

Tana fita na kwanta daga zaman da nake, idanuna da suka kumbura na cigaba da zubar da hawaye, gaba daya raina a kuntace yake, zuciya ta zafi take min, gaba daya komai na duniya baya min dadi, a haka naji wannan daddadan kamshin nasa na kai wa kofofin hanci na ziyara, ban dauka shi ɗin bane, na bar shi as iska ne ya kwaso shi daga falo ya kawo min, dan duk inda ya zauna se ya bar kamshin sa.

Se da na ji yana ta karuwa da yin karvi ga iskar da nake shaka sannan na bude kumburarrun idanuwa na na sauke a kan sa daidai lokacin da yake zama a gefe na ta wajen ciki na, ina ganin haka na matsa da sauri har ina fama ciwona, na kuma juya masa baya, cikin muryar da kana jin me ita zaka san yana cikin damuwa yace

"Kar muyi haka dake Barbie, Please listen to me kiji me zan ce".

Maimakon abin da ya roka se kawai na dau pillow na danne fuska ta alamun bana san jin muryar sa, ya zuba min ido cikin rashin dadin rai, zuciyar sa na masa ba dadi, haka kuma hankalin sa a tashe, sedai ya rasa yadda ze min.

Ya dade zaune a wajen be tashi ba, Nima kuma ban cire pillown ba har se da aka kira magrib ya tashi ya fita, se lokacin na janye pillown daga fuska ta duk na yi zufa saboda zafi, na juya tare da hararar kofar kamar itace shi kana na ja tsaki.

A lokacin gaba daya neman kaunar da nake masa nayi na rasa, se wani kululun haushin sa da ya tsaye min a zuciya, gani nake da hadin bakin sa aka yi komai, dan kawai a raba ni da farin ciki na, duk da na san struggling din da muka sha tare akan batun Ibrahim amma se zuciya ta take fada min duk yaudara ce.

Haka na cigaba da yi masa, naki yadda mu hada ido, na ki saurarar sa, da ya shigo waje zan rufe ido, duk kuma maganar duniya da ze yi bazan amsa ba, haka in ya takura min se in sa kuka, ranar da aka yi gaban Hajiya Yayah se ta rufe shi da fada, ta inda ta shiga ba tanan ta ke fita ba, daga karshe ta Kore shi da kada ta kuma ganin shi kusa da ni tun da bana so, yanayin da ya fita a ciki yasa naji kamar tausayin sa a raina, se kuma take na kwabi kai na, shi ba abin tausayi bane indai za'a hada baki da shi a raba masoya.

Shaidan na sake tunzura ni da yin bore, dan ganin nake is an abomination zaman aure da yayana, dan shi da Ya Salman a lokacin gani nake ba maraba a waje na, to akan me za'a aura min yayana ciki daya, inaaa baze yiwu ba.

Da haka na sake daura damarar ba zan karbi auren nan ba, dole ya sake ni, dan bana ma san Ibrahim ya san wannan batun, tun dama yana cewa soyayya muke ina ga yanzu yaji an daura mana aure, na san kawai gani ze yi nice na aure shi da son rai na, shiyasa dole ma na dage na kashe auran nan batare da ya sani ba, ta yadda zamu yi auren mu hankali kwance.

Ina kwance ba kafa amma gaba daya na gama tsara yadda zan ruguza auren nan, jira nake kawai kafa ta ta karasa warkewa daga nan na aiwatar fa aiki na.........................✍.

Vote
Comment
Share fisabilillah

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 029  [ 4/07/2024 7:14pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Oummey
Free book!!!

*ZINARIYAR MACE⚡*
*Wai shin 'yar'uwa menene matsalarki? zubewar nono, ko kuma rashin kwankwason juyawa a falo maigida ya shiririce ya manta da tibi da matan tictok, menene matsalarki ne? rashin ni'ima ko kuma mugun sanyin da ya yi miki katutu, shin rashin taushin fata ne ko kuma kuraje da tabbani,  ko bala'in ramar da ta addabeki kuma babu rashin ci ba rashin sha a gidan auranki, gwaigwayewar gashi ce matsalarki ko kuma kaushi da faso na tafin kafa da bushewar fata, kina bukatar fatarki ta yi glowing kalarki ta fita kuraje su mutu, ko kuma kina bukatar azababbun turaruka da humra tare da turarukan wuta. Na san dai kuna da yawa matan da tumbi ya yi musu karan tsaye ina nufin ya katse muku hanzarin yi wa maigida gwalli da muskuce-muskuce a falo😃 Nesa fa ta zo kusa AL-KUTUBIYYA ISLAMIC MEDICINE sun tanadar muku da nau'in magungunan da suke magance kowace irin matsala da izinin Allah. Babban burinmu shine sha'ani na aure ya inganta a samu daidaito. Muna da.*
Na gyaran nono.
Na sanyi.

Dilka tare da hadin sabulu.
Duk Wani nau'in maganin mata.
Humra turarukan wuta perfumes, original miski tahra   3in1, ciccibi budurwar kaza. Had'addun supplement irin wad'anda ba su da matsala. Maganin Sliming wato narka tumbi. Abubuwan da muke sayarwa suna da yawa, kuma babu asarar dukiya. Muna garin kano kuma muna tura kayanmu kowane gari fad'in Najeria da Nijar har ma da  kasashemn ketare. Kai tsaye a tuntu'bemu ta lambobin wayarmu domin karin bayani.
*08089965176*
*07084653262*



___________________Sosai Hajiya Yayah ke kula da ni, komai ina zaune ake min, bana komai da kai na ban da shiga toilet da cin abinci, Baba ma kullum se ya shigo duba ni so uku a rana, haka kuma se ya tambaye ni me nake so, duk abinda na fada haka za'a kawo min, ko ma ban fada ba se ya siyo wani abu da ya san ina so ya kawo.

Iya gata Baba yana gwada min, shiyasa nake kokonton canjin sa a kai na yanzu.

Ya Masdooq kuwa tun korar da Hajiya Yayah ta masa be sake shigo min daki ba, one among the amazing and beautiful facts about him kenan, biyayya, yana da matukar biyayya ga iyayen sa har ma dasu Mama, da wuya, kai zan ce ban ma taba jin ya maida wa daya daga cikin iyayen mu magana ba, komai suka ce sedai yace to.

Kwana uku da dawowar mu na fara taka kafata, a kwana na biyar kuwa na warke sumul, ranar a na i gobe tariyar da Abba yace, sedai abinda basu sani ba shine sedai wata amaryar ta tare ba Aimah ba.

Daren washegarin da zan tare zaune nayi na ki bacci, duk da haka kuma na saka alarm kar ma bacci ya sadado ya cuce ni, aikuwa haka aka yi, bacci ya dauke ni ban sani ba, amma dan albarkan alarm dina ya tashe ni, dake kuma na saka abin a raina kadawa biyu yayi na farka.

Nan da nan na tashi na dauko karamar handbag dina da na zuba duk wani abu da na san zan bukata, ATMs dina kudi, ID card da wayoyi na, a hankali na gama karewa dakin kallo ina

tabbatar na dauki komai da na tsara tafiya da shi, se na fito cikin sanda, a irin wannan lokacin ne na san su Ya Masdooq da Baba ke fita Masallaci, Hajiya Yayah kuma se an yi kiran biyu take tashi ta tashe ni, dan haka na san yanzu tana bacci, Baba kuma da su suna masallaci, me gadi kuwa Sarkin bacci ne na san zan iya ficewa yana can yana baccin sa kamar gawa.

A sadade na sauko daga stairs, na karewa falo kallo to make sure ba me gani na sannan na fita zuwa compound, aikuwa kamar yadda na zata ina zuwa bakin gate babu kowa, megadi yana can bacci a daki with assurance din ai ya sa sakata, ajiyar zuciya na sauke cikin jin dadi da farin cikin komai ya tafi daidai.

Na saka hannu na zare sakatan da ya saka, duk da girman ta amma ba me kara ba ce sosai, so na zare ba wani dar, kana cikin kwarin gwiwa na ja karamar kofar jikin gate din zan fita, se kuwa idanu na cikin nasa.

Ya shiga bina da kallo cikin mamaki dan ya ma kasa magana, ni kuma gaba daya fuska ta ta hade cikin takaici da bacin ran yadda se da na zo gabar hango farin ciki sannan plan di na ze ruguje, cikin kokonto ya kira sunana

"Honeybun?".

Ya fada kamar dai be yadda ni din ce tsaye a gaban sa ba, se na dago cike da tsiwa na batare shi tare da murguda masa baki

"Nu'aimah ne sunana ni ehe".

Se ya kuma daskarewa a tsaye, ganin haka na raba ta gefen sa da tunanin kawai na fice se na fyalla da gudu abu na, faffaɗan hannun sa yasa ya riko damtsen hannu na kam, na dago cike da rashin kunya sedai ganin yadda fuskar sa ke hade yasa na hadiye yawu mukut, na kasa cewa komai se dukar da kai da nayi, yana ganin haka ya shiga jan hannu na zuwa cikin gida, dama yana sani ya hade rai dan ya san in ya zauna yin lakwa lakwa zamu bata lokaci ne kawai dan ba lallashi zan ji ba.

Daga masallaci ya taso ya taho bayan ya katse nafilar da yake yi jin cikin sa na juya meaning yana bukatar ziyartar toilet, ashe rabon ba zasu wahala neman ta da sunan ta gudu bane, se gashi ya ci karo da ita.

Ganin muna komawa ciki yasa idanu na cika da kwalla, bana san auren nan na fada, na nuna a aikace , me yasa ba zasu bar ni ba?, Me yasa ba zasu kyale ni ba? Ana dole ne eye!.

Be tsaya ba se da ya kai ni har bedroom dina, ya sake min hannu bayan mun shiga, kana ya dube ni a kausashe, idanun sa jawur na bacin rai, cikin Muryar da ban taba jin shi da ita ba, dan ko yana da ita be taba amfani da ita a kai na ba yace

"Wallahi summa tallahi in kika sake yunkurin fita daga gidan nan da sunan guduwa se kin raina kan ki,  in kina ganin wasa ne then give it a try".

Ya fada tare da juyawa ze fita, se kuma ya dakata tare da juyowa giving me a look da yake tabbatar min da duk abinda ya fada.

Yana ficewa na fada kan bed na shiga kuka, kuka me cin rai, me yasa ne wannan auren ke neman zame min karfen kafa?, Eh mesa?!

Shi kam yana fita ya tsaya ya jingina da kofar yana maida numfashi, tashin hankalin da ya shiga na ganin ta zata gudu at that time of the dark ya fi tashin hankalin tunanin ze iya rasa ta da ya shiga baya, jama'a guduwa fa zata yi, zuwa inda bata sani ba, dan bayan su da dangin Abba bata da kowa da zata ce zata tafi can, gidan su Salman kam ba ma zata fara kusantar su ba, dangin Abba ma na goyon bayan auren, su ma ba zata je gare su ba, then ina zata je?.

"Wajen Ibrahim!".

Wani side na zuciyar sa ya fada masa, wani daci ya ratsa harshen sa da bakin sa, se ya girgiza kai, ai da hankalin ta, ko banza tasan ita matar aure ce, ba zata je wajen saurayi ba da auren sa a kanta, to ina zata je?!.

Ya tambayi kan sa amsar da bashi da ita, se ya ɗaga daga jikin kofar yana jiyo sautin kukan ta, ban da kofar irin masu kwarin nan ne, haka kuma ginin gidan me aminci ne da ba abinda ze hana Hajiya Yayah jiyo ta.

Kafar sa a nauyaye kamar ba zata iya daukan sa ba yake takawa zuwa part din su, be taba zaton haka lamarin ze zama ba, tun farko ma dan ba yadda ze yi ne yasa ya masa alkawarin Abba, a kokarin sa na neman sa ma mata abinda take so, be yi tunanin dagaske shi wancan din ba ze fito ba, se gashi komai ya juye yadda baya tunani.

A yadda suke da fahimtar juna da ita ya zata zata bashi dama su zauna, ya zata zata tsaya ta saurare shi, se gashi ta shayar da shi mamakin da be taba tunani ba, ta mai da laifin komai kan sa shi kadai, bayan in ma yana da laifin to itama tana da shi, shi ya amince da alkawari ita kuma ta amince da sharadi, so be kamata ta ji haushin sa ba.

A hakq ya karasa, yayi abinda ya kai shi, ya sake alwala ya koma masallaci, kafin nan kuwa se da ya tashi megadi yayi masa gargadi sannan ya wuce.

Ana idar da Sallah yayi azkhars din sa be zauna tilawa ba kamar yadda ya saba, ya tashi zuwa gida bayan ya cewa Baba da Farooq cikin sa na ciwo.

Ba wani ciwo da cikin ke masa, damuwa ce ta masa yawa, da yake so ya zauna yayi tunanin mafitar hakan, ya dade a haka kafin yayi coming up da idea din da yake ganin ita zata fisshe

shi.

Nikam ko da gari ya waye idanu sun kumbura sun yi suntum tsabar kuka, ga rashin bacci da ban yi sosai ba, Hajiya Yayah hankalin ta ya tashi gani na, se karya na mata nace na fadi ne a toilet ganin yadda ta tsura ni se na fada mata me yasa ni kuka, gashi ita ba irin Mama bace balle na fada mata abinda na ga dama, dan ko maganar aure da nayi mata cewa tayi

"Mahaifin ki ya rantse ya sake ratsewa in dai shine ya haife ki to a duniya babu namijin da ze aurawa ke in ba Masdooq ba, nayi nayi da shi se hakuri kawai yake bani da fadin ya riga ya gama magana, har Baba na dauka na kai wai ko ze shawo kan sa sedai ban san me ya fada masa ba shima ya koma goyon bayan sa, Nu'aimah ni da Maman ki ma duk muna san auren nan, sedai gare ni in har zan samu hanyar raba ki da Masdooq zan yi tun da na lura ba kya san shi, sedai babu, da ace tuntuni na san ba kya ra'ayi wallahi da ban bari an daura auren nan ba, sedai yanzu ba yadda zan yi, dan Abban ki yace muddun kika tunzura Masdooq ya sake ki sedai ki nemi wani uban ba shi ba.
Ina fada miki wannan ne dan in roke ki ki kwantar da hankalin ki ki nutsu kiyi hakuri kin ji, ko ba dan kan ki ba ko dan ki farantawa mu iyayen ki, ki sani babu dan da ze yi biyayya ya tabe a rayuwa, haka kuma duk dan da yace bijirewa iyaye ne halin shi wallahi ba ze taba samun solace ba a rayuwar sa, na san Masdooq, na san kuma kema kin san shi, in har kika kwantar da hankalin ki wallahi se kin yi alfahari da auren shi, ki daure kin ji Nu'aimah, na sani da zafi amma insha Allah dadi da sanyi ne ze baibaye wanann zafin ya kuma maye gurbin sa".

A lokacin shiru nayi na rasa abin fada, bana san auren kuma nasihar ta be sa naji zan iya hakuri ba, duk da ta wani bangaren na san maganar ta gaskiya ne, zan shedi Ya Masdooq a ko ina a fadin duniya cewa duk macen da ta aure shi tayi Sa'a, sedai ni ban taɓa hango shi matsayin miji na ba, har kuma yanzu haka, kuma na san har gaba ba zan hango ba, shiyasa nake neman hanyar rabuwa dashi ido rufe, amma ko bayan ba auren na sani zamu cigaba da zumuncin mu kamar yadda muka saba.

Se na samu baki na da fadin

"Kuma fa baya so na Hajiya Yayah, Nima ba shi nake so ba".

Yar dariya Hajiya Yayah tayi jin wata wautar tawa kuma

"In jiwa yace miki baya son ki? Ai bana jin kaf duniya akwai da namijin da yake miki ko da kwatankwacin son da Masdooq yake miki".

Se da na dan tura baki gaba na sakalci nace

"To ai ba so na yan uwan taka ba, so na soyayya fa nake nufi".

"Kowanne iri kike nufi nima shi nake nufi Aimah, in kina son tabbatar da gaskiyar zance na se

kin bashi dama, na tabbatar zaki ga ita wannan soyayya da kaunar da nake fada miki".

"To ai amma ni bana son shi irin wannan soyayyar".

Yanzu kam sosai tayi dariyar

"Give it a try, ki bashi dama, na san kema zaki so shi, in kuma har nan da shekara daya baki ji kina son shi ba na tabbatar miki zan raba auren".

"Da gaske Hajiya Yayah?".

"Da gaske Aimah ta".

Se na fada jikin ta ina dariya, itama ta rungume ni ta na farin ciki.

Da na gama tuno yadda muka yi, se wata zuciyar tace to in gwada shawarar Hajiya Yayah mana?, Tun da har tayi alkawari, and shekara daya ai kamar yau ne ko, lokacin ma ze zama Ibrahim yayi settling issues din sa da iyayen sa, kin ga yana saki na se naje na auri abin kauna ta.

Take naji nayi na'am da wannan shawarar, tun da duk abinda nake tunanin zan yi nayi ba ci, bari na gwada wannan, shima in be yi ba ko na samo mafi kyan solution then se na canja.

Da wannan tunanin na dan saki raina, har aka gabatar fa wunin biki, camara man ya zo yayi mana pics sosai, har da ya Masdooq da yau yasha wanka da dark Ash din shadda, taji ɗinkin babbar riga itama dai kamar ta ranar daurin auren mu da aka shammace ni, takalman sa zuwa watch din sa duk silver color ne, yayi kyau matuka gaya, dan haka na dinga satar kallon sa.

Ban tashi raina kai na da shiga tashin hankali ba se da na tabbatar da gaske dai na zama matar Ya Masdooq, lokacin da motocin daukan amarya suka yi dafifi a compound din Hajiya Yayah.

Abokan ya Farooq ne duka suka yi wa ya Masdooq abokai, dama tuni Hajiya Yayah ta sa nayi wanka, ta bani wani soft gown na wani yadi me bin jiki dan roba ne na saka milk color se ta dauko coffee lafaya ta nada min ita, kai na daure da milk scraf, nayi simple daurin ture kaga alkhairi (dan bana ce tsiya ba😂).

Nq yi kyau sosai, nayi amfani da milk handbag and shoes, na sani ya zuwa yanzu kun san takalma na duka heels ne dan in ban da a toilet da kuma bedro slippers ba na amfani da flat shoe.

Turare kuwa na sha shi kamar me, dan har se da yazo yana hawa min kai, Hajiya Yayah ta riko ni a hannun ta zuwa wajen Mama dake zaune a falo cikin jama'a yan uwa, nasiha aka ce tayi min sedai tace ai ta san Hajiya Yayah ta gama fada min komai, ita sedai tace Allah ya bada

Sa'a, daga haka Hajiya Yayah ta kama ni zuwa compound, ban ko kalli Mama ba bale wai irin na yi kukan rabuwa da Ita, se da muka je wajen motocin Hajiya Yayah ta sani cikin wadda za'a dauke ni sannan na fashe da kuka tare da fitowa na rungume ta, da kyar aka banbare ni daga jikin ta aka maida ni motar, daga nan kuma se gidan Ya Masdooq.

Na san me karatu ze iya gajiya da labarina na baya ko, sedai kuyi hakuri, ya zama dole na bada labarin haukan da nayi, wauta da saki na dafen da nayi wa rayuwa ta, na saki cikakken reshe me karfi da karko na kama ganyen da tun kan aje ko ina ya tsinke ya tika ni da kasa, ta yarda ya bar ni da raunin da ya jawo miki da dama wa rayuwa ta, da har yanzu basu warke ba.

Kar ku gaji masu karatu, ku cigaba da bina a labari na, insha Allah ba zaku yi danasani ba!...................✍️.

Vote
Comment
Share fisabilillah

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 030  [ 5/07/2024 5:44pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Oummey
Free book!!!

*ZINARIYAR MACE⚡*
*Wai shin 'yar'uwa menene matsalarki? zubewar nono, ko kuma rashin kwankwason juyawa a falo maigida ya shiririce ya manta da tibi da matan tictok, menene matsalarki ne? rashin ni'ima ko kuma mugun sanyin da ya yi miki katutu, shin rashin taushin fata ne ko kuma kuraje da tabbani,  ko bala'in ramar da ta addabeki kuma babu rashin ci ba rashin sha a gidan auranki, gwaigwayewar gashi ce matsalarki ko kuma kaushi da faso na tafin kafa da bushewar fata, kina bukatar fatarki ta yi glowing kalarki ta fita kuraje su mutu, ko kuma kina bukatar azababbun turaruka da humra tare da turarukan wuta. Na san dai kuna da yawa matan da tumbi ya yi musu karan tsaye ina nufin ya katse muku hanzarin yi wa maigida gwalli da muskuce-muskuce a falo😃 Nesa fa ta zo kusa AL-KUTUBIYYA ISLAMIC MEDICINE sun tanadar muku da nau'in magungunan da suke magance kowace irin matsala da izinin Allah. Babban burinmu shine sha'ani na aure ya inganta a samu daidaito. Muna da.*
Na gyaran nono.
Na sanyi.
Dilka tare da hadin sabulu.
Duk Wani nau'in maganin mata.
Humra turarukan wuta perfumes, original miski tahra   3in1, ciccibi budurwar kaza. Had'addun supplement irin wad'anda ba su da matsala. Maganin Sliming wato narka tumbi. Abubuwan da muke sayarwa suna da yawa, kuma babu asarar dukiya. Muna garin kano kuma muna tura kayanmu kowane gari fad'in Najeria da Nijar har ma da  kasashemn ketare. Kai tsaye a tuntu'bemu ta lambobin wayarmu domin karin bayani.
*08089965176*
*07084653262*

Ouummey 030

Page 30

____________________Karfe takwas na dare kowa ya watse se Aunty Luba kawai da Ya Salman ze tafi da ita in yazo, tun tana lallashi na ta dadin rai har ta gaji ta zuba min ido, kuka nake yi kamar wadda aka kawo kabari ko kuwa gidan yankan kai ba wai gidan Ya Masdooq ba, Aunty Luba ta zuba min idanun ta da suka canja kala, ranta baya mata dadi ganin yadda nake kuka akan auren dan uwan ta, kar ku manta jini daya fa ba wasa ba, gashi ni kuma sakara ba na boye kin auren a gaban kowa hatta kuwa mahaifiyar sa Hajiya Yayah, can Aunty Luba ta sauke ajiyar zuciya ta kamo hannu na da suka sha jan lalle da baki tun last week, kuma dake ba

wani aikin ruwa nake ba zanen yana nan tar kamar jiya aka yi shi

"Mun taso tare karkashin kulawar uwa daya kuma uba daya dake Little, mun nuna miki gata da so da kauna, tun bare Mama da Abba, haka kuma Baba ma ba'a barshi a baya ba, Ya Masdooq ya soki tun kina kankanuwa, a lokacin dan gidan su babu yarinya mace, su Ya Salman duka sun so ki sun kauna ce ki kuma sun yi wahala dake, ni kuwa kallon ki nake da idanu biyu, daya kanwata mafi soyuwa a rai na, na biyu ƴata abar alfahari na duk da kuwa ban ci na haife ki ba dan shekara bakwai kawai na baki, amma yarda da so da kaunar dake tsakanin mu yasa ke kan ki kan kirani Little Mom, Hajiya Yayah na kaunar ki duk da ita bata miki irin yadda mu muke miki, duk wannan so da kaunar da muka shafe shekara da shekaru muna gwada miki ace abu daya yaa gagare mu samu daga gare ki Aimah?, Ba fa rayuwar ki muka roki ki bamu ba, ba kuma wani sashe na jikin ki ba, rokon mu kawai ki kwantar da hankali ku zauna lafiya da dan uwan ki, yayanki kuma mijin ki a yau, wanda kin fi kowa sanin shi, kina cikin wanda zasu ba da shaida akan shi a karba ba tare da kokonto ba, amma hakan yana neman ya gagara, jibi yadda kike kuka kamar wadda aka saka cikin kabari tare da bakin kumurci ba wai amaryar da aka kawo gidan angon da ke son ta da kaunar ta ba, fada min, shin Ya Masdooq na da wani mugun hali mara kyau wanda mu bamu sani ba da ya hana ki karbe shi matsayin miji?".

Ban amsa ba se fama goge hawaye da nake da dayan hannu na, maganaar gaskiya babu wani hali mara kyau da Ya Masdooq ke da shi, ba shi da makusa ta bangaren halitta balle hali, kwata kwata ba shi da aibu da ze hana a zauna da shi matsayin miji, hasalima duk macen da ta same shi matsayin abokin rayuwa ta gama dace kuma ya kamata ta godewa Allah, ni kawai matsalar shine bana son shi, bana mishi so na aure, soyayya da kaunar dake tsakanin mu ta yan uwan taka ce, so na aure Ibrahim kadai nake yi wa, me yasa ba zasu gane ba!.

"Ki fada min matsalar kida auren nan Aimah, wallahi in har dalilin ki me karfi ne I'll back you, zan tsaya tare da ke yar uwa ta har se na ga an raba ki da shi, ni ban damu da shi ba, ban damu da ya yake ji ba, ke ce concern dina, ke nake bukatar ki samu kwanciyar hankali da nutsuwa, shiyasa nake son jin menene matsalar dan taya ko magance ta".

Jin wannan bayanin daga little Mom se na samu sauki har na rage kuka na zuwa kuma ya tsaya gaba daya ina sauke ajiyar zuciya, se na sa hannu nq dage lafayar da aka ja ta rufe min kai, na dubi Aunty Luba da kodaddun idanuwa na

"Baya so na little Mom, Nima bana san shi, taya ya zaman aure ze yi yiuw a haka, Ibrahim kadai nake wa son aure, kaunar mu da sweetheart kauna ce ta yan uwan taka ta jini ba wai ta soyayyar aure ba".

"Shine kawai matsalar?".

Se na daga mata kai ina jin dadin ta fahimce ni ita

"Ko kin san lokacin da akai auren mu da Ya Salman nima bana masa son aure Aimah?".

Da mamaki nake kallon ta dan ban taba sanin haka ba, irin yadda ta amsa zancen auren lokacin da aka zo mata da shi a wancan lokacin yasa kowa yake tunanin dama itama tana san Ya Salman din, daga nan kuma aka yi shirye shirye aka yi aure batare da ta bada kowace matsala ba, se ma farin cikin ta da take nunawa, ya kuma yanzu zata zo tace min wani bata son shi, kuma tayi tunanin na yadda?.

"Kwarai bana masa son soyayya lokacin da aka zo da batun yana so na da aure, sedai na zauna na yi nazari sosai, Ya Salman ba shi da wani hali na banza, ba shi da nakasu a halittar shi, haka kuma na san shi ya san ni, tun a gida muna da fahimtar juna da shi, haka kuma shi yana so na so irin na aure, to me yasa ba zan aure shi ba, me nake nema a wajen mijin aure da shi ba shi da shi?, Soyayya?, Na sani zan so shi in muka zauna, halayen sa da soyayyar da yake min zasu farauto soyayya a raina, karin dadi shine kullum ze dinga tunawa shi yace yana so na ba wai nice nace ba, haka kuma sanin ni ba wani so nake masa da ban ba ze sa ya kasance kullum tunanin yaya ze faranta min, ta ya ze kyautata min har ya samu soyayya ta, akasin in na auri wanda nake so, dole ze dinga min wasu abubuwa da tunanin ai dole zan yi hakuri da shi tun da ina son shi ina son zama da shi, ba lallai ya zama akwai uzuri a tsakanin mu ba, ba kuma lallai ya kasance na san halayen sa kamar yadda na san na baban Mimi ba, ba kuma lallai  e mu fahimci juna yadda muka fahimta da baban Mimi ba, dan shekaru kusan ashirin da muka yi muna tare a gida daya kafin aure babu wani hali na mu da zamu boyewa juna, yin wannan tunanin yasa na karbi tayin auren sa willingly, and kalle ni a yanzu, ban taba danasani ba, bana kuma fatan nayi ta, kwanciyar hankali da jin dai nake ciki, duk da akwai sabani da dole se an samu, amma fahimtar juna mu yasa bamu fiya samun sabanin ba, in muka samu ma baya mana wahalar warwarewa, haka har yanzu baban Mimi hankalin sa na kai na ne, tunanin sa a ko yaushe shine ya faranta min rai, ya kiyaye bacin rai na, ya sanya dariya da farin ciki a saman fuska ta, shin ya kike tunani in ba shi na aura ba?, Bana tunanin zan samu ko da kwatankwacin sa a tattare da wani namijin, kuma har gobe ina godewa Allah da iyaye na, dama fadar Allah da Manzon sa ce duk wanda yayi biyayya ga iyayen sa base tabe ba.
Aimah, irin wannan rayuwar nake miki kwadayi a tattara da Ya Masdooq, shiyasa nake cikin tashin hankalin kar ki biyewa zuciya ki yi mana asara, dan ban ce miki in kin rabu da shi ba zaki sake aure ba, se dai zan rantse miki samun mazaje irin namu yanzu wahala suke, wuya suke, haka kuma kina sake wa kika yi sake wallahi wata ce zata dafe shi, kuma ban fada Miki lallai ne ya sake waiwayar ki ba, dan yanzu mata ba sa wa maza rikon wasa, kowaccen mu kam muke rike abin mu, sanin akwai dubbai dake jiran su a waje, Little mistake zamu yi ya zame mana tashin hankalin rayuwa".

Lallai yau Aunty Luba ta shayar da ni mamakin rayuwa ta, wai duk wannan soyayyar, duk wannan lelen dake tsakanin su da Ya Salman ashe ba auren soyayya suka yi ba?, Kai anya in yarda da hakan, amma kuma na fi kowa sanin little Mom bata karya, musamman tsakanin ni da ita, komai tana fada min iya gaskiyar ta ne, dan ta kan ce bata da wadda ta fini, nice ita itace ni, dan haka ba abinda zata boye min, ko menene kuwa.

"Amma ai little Mom ke ai Ya Salman yana san ki, shi kuwa da ni da shi duk bamu san juna".

Wani murmushi Aunty Luba tayi, ta gyara zama sosai ta fuskance ni, ganin haka Nima na sake bata hankali na

"Waya fada miki?, Waye yace miki Ya Masdooq baya san ki?, To ko waye ya fada wallahi na rantse Miki karya yake, asalin soyayya Ya Masdooq yake Miki, so irin me saka mutum ya zama tamkar bawa, me wahalar da ruhi da rayuwa shi Masdooq yake Miki Aimah".

Karo kusan na biyar kenan ana fadin min Masdooq na so na, farko Abba, then Mama, then Hajiya Yayah, yanzu kuma ga Aunty Luba, na rasa ta yadda suke gane hakan, bayan ni ban taɓa ganin wannan son ba, be kuma taba fada min da bakin sa ba, sedai maganganun Aunty Luba na karshe suka jefa ni cikin wani irin nazari da tunani har ban san sanda ta wuce ba, shi kuma ya shigo.

"Kiyi tunani kiyi nazarin rayuwar ki da Masdooq, yadda ya fifita ki akan kan sa, yake baki duk lokacin da, yake kashe abubuwa masu muhimmanci saboda na ki uzurin, burin ya faranta miki a ko yaushe, irin kallon da yake miki duk sanda kuke tare, fafutukar sama miki farin ciki a cikin kowane hali, yaba wa komai da ya dangance ki da kuma bawa duk wani abu da ya dangance ki muhimmaci, daga karshe kiyi duk yadda zaki yi ki nemi diary din sa ki karanta, na sani daga ranar ba zaki sake kokonton rashin soyayyar Masdooq gare ki ba, Nima ba bani yayi ba, Ya Farooq naji yana maganar diary din cikin fada, lokacin da yayi tsaye wajen ganin ya tabbatar kin auri Ibrahim, dan samun farin cikin ki batare da duba da nasa ba".

Muryar sa da naji daf da ni, da warmness din hannun sa cikin nawa shiya dawo dani cikin duniyar zahiri, na dago na kalle shi a hankali, idanun sa na kai na, daga ta cikin idon sa damuwa ce kwance zokar da ta rufe tarin farin cikin da yake ciki, se na samu kai na da kare masa kallo ganin yadda ramar sa ta bayyana.

Ya rame kam musamman a idanun mutanen da suka san shi sosai iri na, sedai har yanzu fa wannan gayun na nan, dan sanye yake da Black shaddah, ɗinkin jamfa, yayi kyau sosai haka fuskar sa look fresh, da alama daga wanka be shafa mai ba, sumar sa da nake so da sajen sa sun sha gyara, se na samu kai na da furta

"Ka rame sweetheart".

Se da na sake dagowa na kalle shi jin irin kakkarfar ajiyar zuciyar da ya sauke, ya lumshe idon sa a hankali yace

"Dan Allah, na roke ki ki daina azabtar da ni da fushin ki Barbie, yana cutar da ni yana sani cikin damuwa, na hada ki da Allah ko meye kiyi min amma ban da fushi, ba zan iya jurewa ba, satin nan ji nake kamar kaina ze buga saboda tashin hankali, kiyi min wannan alfarmar kin ji Barbie?".

Ya ilahi wallahi se na ji kamar na fashe da kuka, looking at how painful and pitiful he is se na ji kwata kwata ban kyauta ba, me yasa nayi haka, shin Ya Masdooq ya cancanci haka daga gare ni?, The answer is capital NO.

Hannu na dake rawa na daga na riko nasa, murya ta ma na rawa na shiga bashi hakuri

"Am sorry sweetheart, ka yafe min dan Allah, ban san what come over me ba da nayi hakan, kawai naji ina jin haushin ka ne shiyasa na ki maka magana, bana san na bude baki na fada maka abinda be dace ba, in nayi hakan ba zan taba yafe wa kai na ba, hankali na kuma ba ze taba kwanciya ba dan in na fada maka kalaman fa basu dace ba they'll continue hurting me, day by day har lokacin da ban sani ba, shiyasa na kulle baki na na kuma nesan ta da kai, ban san hakan ze dame ka ba, am sorry, terribly sorry please ".

Be iya yace komai ba se janyo ni da yayi jikin sa ya kankame, zuciyar sa na bugu abnormally, ni kaina na san ba daidai zuciyar sa ke bugu ba, ina rungume jikin sa maganganun Aunty Luba na sake dawo min, se na dan zame daga jikin sa cikin son jin gaskiya daga bakin me ita, ban kula bugun da zuciya ta ke yi ba, na irin amsar da zata fito daga bakin sa na dube shi, yana rike da hannaye na idanun sa akan fuska ta

"Ranar da Abba yace ya zaba min kai ya fadi wata kalma da nake kokonto, haka ma Mama ta maimaita, se Hajiya Yayah, yau ma kuma Aunty Luba ta fada min haka dazu, ina cikin shakku da babu inda za'a fitar da ni face nan, kuma kai ne kadai zaka kore duk wani kokonto dake raina, shin dagaske ne KANA SO NA YA MASDOOQ?, soyayya irin ta aure ba ta yan uwan taka ba?".

Zan iya cewa na ga sanda numfashin sa ya tsaya a kirji sa kafin kuma ya cigaba da in and out, ya tsira min kaifafan idanuwan sa yana min kallon da ke ratsa jinin jiki da tsoka ta, ya sa hannu ya tallafo fuska ta ta kowace side ya matso da tasa daf da tawa, tsayin lokaci muna kallon kallo tare da musayar numfashi wnada nake jin na wa na barazanar katsewa daga kirji na, tsayin lokaci kafin ya ambaci suna na da wata irin murya da so daya na taba jin ta daga gare shi , ban iya amsawa ba se idanu dana lumshe ina jin kamar hawaye na forming a ciki, be yi magana ba se da ya sake tallafo fuska ta har hancin mu na haduwa waje ɗaya lokacin kuma na sake ware idanu na da suka tara hawayen da ban san na menene ba cikin nasa

"I have noticed that with you, I smile more often, I anger a little less quickly, the sun shines a little brighter, and life is so much sweeter.  For being with you takes me to a different place called love. I started beliving in LOVE when for the first time I cuddle you in my chest few minutes you're born, very tiny in my arms, yet very amazing, my heart kept skipping in my chest crying out very loud, telling me you're my soulmate, my missing rib, and My forever.
Ever since my heart has never beat unless with your name, never sat without thinking about you, awake, eating, walking, asleep and in every condition I never stopped thinking about you, and the thought of you become my company driving away my boring time and keeping me Happy.

Barbie I love my life because it gave me you I love you because you are my life!!!".......................✍️.

Vote
Comment
Share fisabilillah.

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 031 [ 5/07/2024 5:45pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Oummey
Free book!!!

*ZINARIYAR MACE⚡*
*Wai shin 'yar'uwa menene matsalarki? zubewar nono, ko kuma rashin kwankwason juyawa a falo maigida ya shiririce ya manta da tibi da matan tictok, menene matsalarki ne? rashin ni'ima ko kuma mugun sanyin da ya yi miki katutu, shin rashin taushin fata ne ko kuma kuraje da tabbani, ko bala'in ramar da ta addabeki kuma babu rashin ci ba rashin sha a gidan auranki, gwaigwayewar gashi ce matsalarki ko kuma kaushi da faso na tafin kafa da bushewar fata, kina bukatar fatarki ta yi glowing kalarki ta fita kuraje su mutu, ko kuma kina bukatar azababbun turaruka da humra tare da turarukan wuta. Na san dai kuna da yawa matan da tumbi ya yi musu karan tsaye ina nufin ya katse muku hanzarin yi wa maigida gwalli da muskuce-muskuce a falo😃 Nesa fa ta zo kusa AL-KUTUBIYYA ISLAMIC MEDICINE sun tanadar muku da nau'in magungunan da suke magance kowace irin matsala da izinin Allah. Babban burinmu shine sha'ani na aure ya inganta a samu daidaito. Muna da.*

Na gyaran nono.
Na sanyi.
Dilka tare da hadin sabulu.
Duk Wani nau'in maganin mata.
Humra turarukan wuta perfumes, original miski tahra  3in1, ciccibi budurwar kaza. Had'addun supplement irin wad'anda ba su da matsala. Maganin Sliming wato narka tumbi. Abubuwan da muke sayarwa suna da yawa, kuma babu asarar dukiya. Muna garin kano kuma muna tura kayanmu kowane gari fad'in Najeria da Nijar har ma da  kasashemn ketare. Kai tsaye a tuntu'bemu ta lambobin wayarmu domin karin bayani.
*08089965176*
*07084653262*

Ouummey 031

Page 3️⃣1️⃣

___________________Hawayen da ban san na meye ba suka shiga tsere kan kunci na, baki na ya shiga bari amma na kasa cewa komai, har lokacin kuma idanun mu na sarke cikin na juna, in na rantse ba zan yi kaffara ba a wannan lokacin hatta zuciya ta se da ta tsaya da beating, agogo ya tsaya da bugu, lokaci da komai ya tsaya da tafiya, babu abinda yake motsi a lokacin face Aimah and Masdooq, only the two of us.

Na shiga lumshe ido na very slowly, se kuma lokacin zuciya ta ta dawo da bugu, se tsalle take a kirji na looking for something I knew not, sassanyan harshen sa ya sauka kan kunci na wiping away my tears, na kankame hannun sa batare da na san nayi ba, haka kuma take tears din suka kame kamas, yana kai wa saitin ido na ya sunbace idon cikin wani irin soyayya me karfi da tsafta, ya hade fuskar mu, goshin mu kan na juna, hancin sa kan nawa, lips din sa na brushing nawa haka muna exchanging breath,

"Barbie, If you ask me about love, I can’t answer you but if you ask me who I love, the answer is you and will always be, life can give us lots of beautiful persons, but only one person is enough for a beautiful life, and you're my that one person, stay in my life, forever Barbie, will you Please????".

Jin da gaske numfashi na na neman daukewa yasa na fisge jiki na tare da juya masa baya, hawaye na bin kunci na daya bayan daya, ina jin shi ya sake matsowa ya kwantar da kan sa a

baya na batare da ya sake cewa komai ba, haka muka yi shiru tsayin lokaci, ina jin hucin numfashin sa dake sauka a baya na, har se da na ji na saisaita nutsuwa ta, nasa hannu na daga kan sa a hankali na saukaa daga  bed din gaba daya, se lokacin muka sake hada idanu, na sunkuyar da nawa da sauri dan se na ji ina jin nauyin sa a yau, kunyar hada ido nake da shi, shi kuma kamar ya fahimta se ya sauko shima ya tsaya gaba na tare da rike hannu na

"Wil you pls try giving 'US' a chance?, I promise you won't regret it".

Kai na na kasa na bude baki nace

"It's not like I don't love you sweetheart, Allah ya sani ina son ka ina kaunar ka, but a matsayin yaya na not my husband, the love I have for you ba na soyayyar aure bane, wannan Ibrahim nake yi wa, but Please give me some time, ka bani lokaci nayi digesting all that happened, yanzu ji na nake blank and empty , komai sabo nake ganin shi, ina bukatar lokaci nayi tunani and decide our fate, sedai I promise you khair insha Allah".

Gyada kai yayi alaman ya fahimta, se ya sake ni ya shiga toilet, ya dan jima sannan ya fito, lokacin na koma na zauna bakin bed,

"Ga ruwan wanka nan na hada miki, take your bath, I'm coming".

Daga haka ya fita, na raka bayan sa da kallo cikin tunani, kafin kuma na aje komai a gefe na shiga rage kayan jiki na sannan na shiga toilet.

Har na fito be dawo ba, se na buɗe wardrobe da su Aunty Luba suka min jeren kaya na, sedai to my utmost surprise komai na ciki sabo ne, elegant and classy, na shiga bin kayan da kallo cikin mamaki dan nidai na san ba'a min lefe ba, ko da yake ba na ce ba dan ba'a sa ni a cikin komai da ya shafi auren ba kamar ba aure na ba.

A hankali na koma bangaren sleeping wears, suma dai gasu nan birjik kala kala kaman zasu yi magana, kowacce gwanin sha'awa, na rasa ma wadda zan dauka, daga karshe na dauko wani pink color riga iya cinya da wandon ta da yake tsayawa daidai tsayin rigar.

Na saka tare da yin wanka da turare kamar yadda na saba, na gyara gashi na na saka hulan bacci kana na saka pink socks da ke tare da kayan na kara karfin AC na kwanta tare da jan duvet na rufe jiki na, tsayin lokaci ina so na yi bacci amma tunani ka sun cika min kai, a haka ya shigo ya same ni, shima yayi wanka ya saka kayan bacci sa farare, yayi kyau sosai, ya tako zuwa bakin bed ya zauna tare da duba na

"Tashi muci abinci kafin ki kwanta".
Batare da na dube shi ba na ce

"Na koshi, Hajiya Yayah bata bari mun taho ba se da ta zauna ta sa na ci abinci sosai, sedai ko

zuwa da safe".

"Har milk din ba ze iya shiga ba?".

Hannu na sa na shafa ciki na dake a cike da gaske nace

"Allah am full sosai".

Se ya gyada kai, kana ya tashi dauki ledojin da se lokacin ma da ya dauko su na san a she da su ya shigo tun dazu ya aje, dan dai yanzu be shigo da komai ba.

"Okay, kin yi addu'ar bacci?".

"Nayi".

Duk da na fada masa nayi se da ya sake min wata ya shafa min a kai na da kafafu na sannan ya fita yana cewa good night.

Wannan daren ni da shi zan iya rantse wa ba mu runtsa ba se bayan sallar subh, ni dai in an tsira Ni ba zan iya cewa ga tunanin da nake ba, sedai na san har lokacin ina cikin shock din jin wai ya Masdooq na so na.

Washegari na riga shi farkawa, na tashi na yi wanka na sa kananan kaya, half gown da ta kama ni iya gwiwa se skinny jeans da ya tsaya min a idon sawu, kafa ta cikin bedroom slippers na fito kai na ba dankwali se dai gashi na ya sha gyara, na shiga kitchen na hada mana breakfast dan da yunwa na farka, nan da nan na gama na kai dining, Ni na taso shi yayi wanka ya zo muka karya, be fita ba se da baki suka fara zuwa, sedai zaman shiru da danne dannen waya muke.

Haka muka cigaba da kasancewa har bayan wata daya , lokacin ya sake tuntuba ta batun bamu chance, sedai har lokacin ban shirya ba, ga tunanin Ibrahim da kan fado min rai sa'i da lokaci, se nace masa shikenan na yarda we're now husband and wife, but bana san wani affair ya shiga tsakanin mu, w e should just continue fa mu'amala kamar yadda muke yi lokacin kafin a mana aure, har zuwa lokacin da zan ji yes am comfortable and ready for married life.

Duk da fuskar sa ta nuna rashin dadin jin haka amma be ki ba ya amsa min, daga nan muka koma normal rayuwa kamar da, sweetheart and his Barbie kuma honeybun, a wannan lokacin ne zance mun yi farin ciki duk cikin zaman auren mu, sedai shima be yi wani lasting longer ba, guguwar da ta tumbuke auren gaba daya ta sako kai.

Kullum tare muke gyaran gida, muyi girki abin mu dan baya bari na ko ina nayi kafar sa na bina, haka ze kama min muyi girkin, yayi shara nayi mopping, ya gyara bed na share dakin, komai da kuka sani na aikin gida tare muke yi hatta kuwa da wanke wanke, ya saba na dauraye ko na saba ya dauraye, wankin mu kuwa shi yake yi da machine se a ba me guga ya goge, a lokacin

rayuwar mu su very perfect, ya tsokane ni muyi ta fadan wasa, mune dambe da kokaye kokaye, daga haka har ya fara samun audacity na kissing dina, the first time fa hakan ya faru na nuna naji haushi, sedai a boye nayi enjoying, ya bani hakuri yace base kara ba, the second and the rest kuwa duk ban wani damu ba, daga baya ma wataran nike kissing din shi, tafi tafi tun muna kwana separately har wata rana da nayi ciwon kai ya kwana daki na shikenan muka cigaba da kwana tare rungume da juna, sedai babu abinda ke faruwa bayan rungumar.

Wata biyu muka yi cikin wannan farin cikin plus wata dayan baya, making three month, nace masa zanje gida, be hana ba dan baya hana ni duk abinda nake so in dai babu wani matsala, shi ya kai ni da kan sa bayan ya tsaya a supermarket yayi wa su Mama tsaraba me yawa, bayan duk wata se ya siya kayan abinci ya kai musu kamar yadda yake kaiwa gidan Hajiya Yayah, ya kuma bawa Mama kudin kashewa yadda dai yake wa Hajiya Yayah.
Ranar Abba da Mama bana jin akwai wanda ya kai su farin ciki, kamar yadda Mama tace wai se ranar hankalin su ya kwanta dan kullum suna cikin zulumin jiran jin wani abu ya faru daga gare ni, Mama na ta farin cikin gani na tana ta yabon yadda na kara kyau na sake murjewa, fata kamar ka taba jini ya fito duk da ba fara bace ni, Abba ma se ina ka saka ka cire yake dani, ashe duk wannan sa albarkar ba ze dore ba.

Duk da yace in jira shi in ya tashi aiki yazo mu tafi amma se ban tsaya ba dan ina son zuwa gidan Aunty Luba, fa na fada masa kuma yace ba yanzu ba, dan haka karfe uku na wa su Mama sallama da sunan na tafi gida na wuce dan zuwa gidan aunty Luba, sedai kafin na karasa se na tsaya a wani supermarket dan siyawa Mimi tsaraba, kamar azal, na gama siyan komai na je wajen biya ina jiran na gaba na ya biya se kawai na ji an kira suna na, with the Muryar da ko cikin bacci nake na san waye me ita, IBRAHIM ne!.

A darare na gaida da shi, sedai na lura da uban ramar da yayi ba kyan gani, duk ya susuce kamar ba shi ba, cikin tausayi nake kallon shi dan ko be fada ba na san rashi na ne yasa haka, gaba daya zuciya ta tayi rauni, nace Ibrahim kai ne haka?, Se hawaye ya fara min zarya, shima idanun sa suka cika da kwalla, ganin ana kallon mu yace muje gefe.

A nan yake sanar da ni irin tashin hankalin da yake ciki na rasa ni, yanzu haka saboda yadda har ciwo ya kwanta a kan so da kauna ta matar sa ma tayi yaji ta koma gida, sedai shi be damu ba, ni ce kawai a ran sa, komai na sa ya tsaya saboda rashi na, yana kuka yake fada min tare da tuhuma ta me yasa zan ci amanar sa, me yasa na kasa hakuri ya rarrashi iyayen sa naje nayi aure, gashi daga baya iyayen sa sun amince ni kuma babu ni.

Kai wasa wasa gaba daya Ibrahim be bar ni ba se da ya tayar min da tsohon mikin da na samu na yaka, na ringa jin soyayyar sa na dawowa sabuwa a raina, a binka da shaidan ji nayi ma yanzu nafi son sa a kan da, na dube shi with wet eyes

"Ibrahim in na kaso aure na na fito zaka aure ni?"

Amsar da ya bani tasa na ji nauyi se dai ban damu ba tun da bani da wata matsala a lokacin

"In har be taba taba ki ba Aimah, dan kin san ina da tsananin kishi a kan ki".

Gyada masa kai nayi, ta haka ya gane ba a binda ya shiga tsakanin mu, nan kuwa ya tunzura ni kashe aure na with the promise of aure na a cikin watan tun da ban da idda.

Lokacin da na koma gida ko gidan Aunty Luba ban je ba, gaba daya kai na ya juye, tunani na ya jirkita, ba abinda nake gani se Ibrahim da cikar burin mu na auren juna.

Ko da ya Masdooq ya dawo ya kasa gane min, na canja kamar ba ni ba dan ko sallamar sa ban amsa ba, ya tambayi me yasa na dawo ban jira shi ba nace haka na ga dama, ya tsaya ya zuba min ido cikin tunani, se kuma ya bani hakuri ya wuce daki, sedai be shige ba na ja masa tsaki, abinda ya fi tsana, ya tsaya yayi shiru kafin ya bude kofa ya shige bedroom, tun daga ranar kuma zaman mu ya lalace, rashin kunya da rashin mutunci kala kala nake wa Ya Masdooq, yayi yayi na fada masa me ya kawo wannan matsalar, amsar ta kawai ni ya sake ni, yayi yayi in bashi dama mu shawo kan matsalar naki, gaba daya hankalin sa ya tashi, na saka shi cikin damuwa, ya rame kamar ba shi ne watan baya yake cikin kwanciyar hankali da kibar sa ba, da na ga dai ba shi da niyyar saki na da wannan abin da nake se ya koma in yana bacci se in cika ruwa in je in kwara masa, na masa so biyu ana uku da ya zabura kamar wani zaki se nayi baya da gudu, dan na firgita, zata na duka na ze yi, daga nan na dena zuba masa ruwa, amma fa duk wani abu da na san yana so se na lalata, hatta kaya haka nake dauka na kona ko na yaga, wani kuma na bayar, wulakanci kala kala amma be taba fadawa kowa ba, se watarana da Aunty Luba tazo ta ga na yayyaga masa kaya kala kusan bakwai, yana tsaye rike da kayan ya kasa magana, idanun sa sun kada sosai, ni kuwa na rike kugu ina ga zuba rashin kunya ta, ranar Aunty Luba har fa kukan ta kan in taimaka in rufa musu asiri in yi hakuri amma na murje ido nace mata nifa ba zan iya ba, kawai ya sake ni, ganin bana ganewa yasa ta je ta sanar da Abba da Mama, se ga su, lokacin kuwa yana kwance kan doguwar sofa ni kuma ina one sitter Ina ta fitsara, ya dauki pillow ya dora a kunnen sa, daga dakin sa muke muka dawo nan, tun da na gane yana rufe dakin se na kwashe duka mukullayen gidan na boye, aikuwa ranar Abba se da ya kusa karya ni, ya kuma kira Ya Salman da Ya Farooq da Ya Najeeb ya fada musu, yace kuma duk na kuma wulakanci ya Masdooq ya zane ni, in ba ze iya ba ya kira su Ya Farooq su ci masa uba na, haka suka tafi suka bar ni cikin tsamin jiki ga zagin da Mama tayiyyi min, na ji haushi ganin har da Mama a mari na ita da ta tsani a dake ni, me makon nayi sanyi se na sake hayewa, bawan Allah shi yayi jinya na na kwana biyu, ina ta masa rashin kunya amma be kula ni ba, har da su Allah ya isa na masa, to na masa mana indirectly tun da nace masa ban yafe ba, wai a haka fa yana min kwarjini, fa ban san iya iskancin da zan yi ba, shi kuwa ban san me yasa yake kyale ni ba.

Ina warkewa na dasa iya shegе, da ina girki na dashi na aje masa a kitchen, yanxu se na dawo se in yi nawa daban shi in cika yaji ko gishiri a nasa, da ya gane se ya daina ci sedai ya girka, shima na taso bala'i se ya daina girkawa se dai ya siyo daga waje, shima in yayi sake ya shiga wanka na gani se na lalata, ko ta ina na hana bawan Allah sakat, gashi shi ne iya yawo ba, haka ze dawo gidan ya kwanta yana sauraren iskanci na.

Mama da abin ya ishe ta taje ta samu Baba da maganar, se Hajiya Yayah tace yarinta ce, kuma tun farko laifin su ne da suka min auren dole, shi dai Baba yazo har gida yayi min nasiha.

Kamar naji kwana biyu shiru, se da Ibrahim ya kira waya ta da ban san inda ya samu number ba dan sabon sim Ya Salman ya canja min lokacin auren mu, nan ne lamura suka sake tabarbarewa, ya zama ina fita in je wajen shakatawa mu hadu da Ibrahim, ya Masdooq be taba sani ba se watarana da muka hadu yaje tattaunawa da wasu abokan kasuwancin sa, ya gan mu muna zaune muna hira se dariya muke, ranar ne naga asalin bacin ran sa, dan maruka uku yayi min da na dawo, ya koma kuma se ya kulle ni in ze tafi aiki, in ya dawo ya bude.

Ranar da ba zan taba mantawa ba, ya dawo daga aiki ina daki, jin shiru ban tare shi da bala'i ba yasa da yayi wanka ya shigo duba ni, ni kuma na fito daga wanka kenan sanye da karamin towel da ko kan cinyoyi na be gama sauka ba, ban san ya aka yi ba se tsintar kai na nayi a jikin sa yana kissing dina cike da kwarewa, kasancewar da ya saba min da haka kuma nima nayi missing hakan se na bashi hadin kai batare da sani na ba, ban tashi ankara ba se da na ji ni on bed babu towel dina a tare da ni, all that follows kuwa be yi dadi ba, na sha kuka iya kuka kamar raina ze fita, Allah ya isa kuwa ban san adadin da na masa ba, shi kuwa se faman lallashi da lallaba na yake, be bar lallashi na ba se da na ambato bawa Ibrahim kai na da na san haka zata faru, nan ne ya dauke wuta, daga nan be kuma lallashi na ba, ya dai gyara min jiki na wanda ta karfi yayi hakan dan naki bari ya taba ni, mugayen alkaba'ai ba wanda ban masa ba, se da ya samo weak point dina, cewa ze kara min abinda a lokacin na tabbatar in ya sake mutuwa zan yi.

Daga nan ya dan sami freedom na wata daya da rabi, se kuma rashin lafiya kamar ba zan rayu ba, ko da ya dauke ni zuwa asibiti se ga batun ciki, ai kuwa dan tashin hankali suma nayi, ya rude likitoci suna rude, ko da na farfaɗo kuka kawai nake bana iya magana, shi kuwa cikin farin ciki yake, ya kikkira gidajen mu ya sanar mana, Aunty Luba tazo gida washegari tana ta lelena, dake laulayi nake sosai yasa kullum in Ya Salman ze tafi aiki se ya sauke ta a nan tana kula da ni, Ni kam cikin raina tunanin yadda zan yi da cikin nake, dan ban manta sharadin mu da Ibrahim ba, ban da jaraba ace daga yin abu so daya se ciki, wannan wane irin bala'i ne ni Aimah.
Daga karshe dai na kira Ibrahim na sanar masa Masdooq yayi min fin karfi kuma ga ciki ya bullo, Ni kaina duk sanda na tuna wannan jakancin da nayi ji nake kamar na shake kai na, Ibrahim yayi ta min bala'i kamar wadda ta samu cikin zina, daga karshe ya kashe wayar sa, hankali na ya tashi, kullum cikin kira da text nake, se bayan kwana uku ya kira ni ya ban umarnin zubar da cikin, daga nan duk yadda za'a yi na kashe auren cikin wannan watan zuwa na gaba, da sauri na amsa kamar wadda yayi wa asiri.

Aikuwa tun daga ranar kullum se na maimaita wa Masdooq se na zubar da cikin, tun yana daukan wasa nake har hankalin sa ya fara tashi sanin zan iya, a kokarin sa na samar da tight security se ya sanar da Aunty Luba ikirari na tare da sanar da ita dan Allah ta dinga samin ido tun da dai ba za yiwu ya zauna ba zuwa aiki ba....................✍️.

Vote
Comment
Share fisabilillah.

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 032 [ 5/07/2024 5:47pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Oummey
Free book!!!

*ZINARIYAR MACE⚡*
*Wai shin 'yar'uwa menene matsalarki? zubewar nono, ko kuma rashin kwankwason juyawa a falo maigida ya shiririce ya manta da tibi da matan tictok, menene matsalarki ne? rashin ni'ima ko kuma mugun sanyin da ya yi miki katutu, shin rashin taushin fata ne ko kuma kuraje da tabbani, ko bala'in ramar da ta addabeki kuma babu rashin ci ba rashin sha a gidan auranki, gwaigwayewar gashi ce matsalarki ko kuma kaushi da faso na tafin kafa da bushewar fata, kina bukatar fatarki ta yi glowing kalarki ta fita kuraje su mutu, ko kuma kina bukatar azababbun turaruka da humra tare da turarukan wuta. Na san dai kuna da yawa matan da tumbi ya yi musu karan tsaye ina nufin ya katse muku hanzarin yi wa maigida gwalli da muskuce-muskuce a falo😃 Nesa fa ta zo kusa AL-KUTUBIYYA ISLAMIC MEDICINE sun tanadar muku da nau'in

magungunan da suke magance kowace irin matsala da izinin Allah. Babban burinmu shine sha'ani na aure ya inganta a samu daidaito. Muna da.*
Na gyaran nono.
Na sanyi.
Dilka tare da hadin sabulu.
Duk Wani nau'in maganin mata.
Humra turarukan wuta perfumes, original miski tahra 3in1, ciccibi budurwar kaza. Had'addun supplement irin wad'anda ba su da matsala. Maganin Sliming wato narka tumbi. Abubuwan da muke sayarwa suna da yawa, kuma babu asarar dukiya. Muna garin kano kuma muna tura kayanmu kowane gari fad'in Najeria da Nijar har ma da kasashemn ketare. Kai tsaye a tuntu'bemu ta lambobin wayarmu domin karin bayani.
*08089965176*
*07084653262*

Ouummey 032

Page 32

____________________Aunty Luba ma ta dinga lallashi, hadisai da ayoyi babu wanda bata ja ba amma be sa na ji zan fasa kudiri na ba, hankalin ta itama ya tashe yake da zulumi, a haka har sati uku na fara jin sauki, ranar da Aunty Luba ba ta zo da wuri ba na fadawa Ibrahim, se ya kawo min wani magani ya bawa gateman wai in ji yaron office din oga dan kar yaji wani iri, ni kuwa dama na san da tsarin, aikuwa maimakon biyu da aka ce a sha ni hudu na sha, shiyasa kafin awa daya na rikice da ciwon mata, daga nan kuma se bleeding, lokacin Aunty Luba tazo ta same ni cikin wannan halin, ta kira shi ta sanar masa hankali a tashe, shima Allah ne kawai ya kawo shi lafiya, ya kwashe mu se asibiti, a can aka sanar masa cikin ya zube kuma maganin zubar da ciki me karfi na sha haka kuma doze off, ranar ni kaina na tausayawa ya Masdooq dan kuka yayi da idanun sa, be taba sanin tsanar da nayi masa har ta kai haka ba, sedai ban dashi da ni da Aunty Luba ba wanda ya san maganar, dan ya roke ta kar ta fadawa kowa.

Kwana biyu nayi aka sallame ni, ya kwashe ni zuwa gida, Aunty Luba ta dena min magana, ta daina sake min fuska, zata dai taimaka min har nayi sati na gyagije, daga nan bata kuma zuwa ba, ban damu da bacin ran ta ba dan a gani na bayan dan uwan ta ta goya, daga nan muka koma gidan jiya, sedai yanzu ko kallo na baya yi, hade ran da yake yasa nake ganin kwarjinin sa, da yawa iskancin da nayi da na kasa ci-gaba wa, cikar wata daya da sati Ibrahim ya kira ni yana ta min masifar me nake jira ne, aikuwa na sake rikicewa, komai ya tabarbare, wannan karon har takardun kadarorin Masdooq nake salwantarwa, kudi in ya aje in yaga in zube masa

ko in kona, abinci haka zan hada masa wani da wani, baya san yana duka na shiyasa ya rasa ya ce yi da ni, karon farko da ya kai karata wa Abba, Ya Salman da Ya Farooq se da suka sumar dani amma a banza, Hajiya Yayah bata taɓa tambayar me ke faruwa ba duk da tana lure da yadda yake cikin damuwa yake kuma rama, ita da Baba karkari su zaunar da shi su masa nasiha, nima in naje nasiha da hannun ka me sanda ne tsakanin mu amma ban taba kulawa ba, kwana uku da yi min dukan su Ya Farooq na dau fetur din inji na jika duka falon na dauko ashana zan kunna se ga Aunty Luba, tana kuka tana roko na amma baki, fada nake kawai gara na kashe kai na, a cikin haka Ya Masdooq ya dawo, dan yana office amma gaban sa na ta faduwa, shiyasa kawa yaji gwara ya dawo gida ya ga lafiya dan hankalin sa be kwanta ba,.

Idanun sa suka yi jajir kamar an watsa barkono, zuciyar sa na tafasa nna ganin irin kiyayyar da nake masa yaga na kunna ashanar zan jefa ya tare ni da fadin

"Na sake ki saki daya Nu'aimah Bashir".

Ina jin haka na kashe ta hannu na na yarda duka kwalin, na durkushe a wajen, duk da ni na nemi sakin amma na girgiza, wani bangaren na zuciya ta tashi hankali ne zokar, wani bangaren kuma murna nake yi, haka nake jin kamar ana danne bangaren tashin hankalin, Aunty Luba ma zubewa tayi tana kuka tana fadin

"Kin cuce mu Aimah, kin cuci kan ki, kin cuci kan ki".

Na dade a wajen sannan na tashi zuwa bedroom dan daukan kaya na tafi, daidai kofar bedroom din sa dake be rufe kofar ba naji yana fadin

"Ka sha ce min na hakura da auren Aimah, ka sha fada min me yasa ba zan bar ta ba tun da ba iya kadai ce mace ba, a wancan lokacin ban amsa ka ba, amma a yanzu ina tabbatar maka na bar Aimah, na bar Nu'aimah, har abada ni MASDOOQ na bar Aimah Farooq".

Se naji zuciya ta ta buga da karfi, nadama na neman lullube ni amma na ture ta da karfi da yaji na shige daki na ina fadin ai ni na fara barin ka, bari kuma na har abada ehe.

Da haka na kwashi kaya se gida, aikuwa na ga tashin hankali dan kwallo Abba ya dinga yi dani har waje yace ba zan zauna a gidan sa ba, dake bani da kunya se na tafi gidan Hajiya Yayah, ta min nasiha ta shigar ni daki na, Baba kuwa shima kamar ze doke ni kafin ya kyale ni, ban san ya akai ba dan ban kuma ganin Ya Masdooq ba, amma na ji ya tafi India, ban tashi shiga tashin hankali ba se da Ibrahim ya sanar da ni ba ze taba aure na ba, ya sa na kashe aure na ne dan ya rama yaudarar da nayi masa, wai na yaudara shi nayi aure shi ne ya dauki fansa, ya sa na zubar da ciki na, na kashe aure na kuma ya ci amana ta, se kuma lokacin na dawo hayyaci na har na dinga tunanin me ya hau kai na na yi duk wannan diban albarkar, amma na rasa ganewa.

Abba be yarda na koma gidan sa ba se bayan shekara daya ada Ya Masdooq ya dawo, dan

kuwa Abba yace in wani abu ya sami Ya Masdooq ta dalili na wallahi ni da shi har abada, haka Mama da taguwar yan uwana su Aunty Luba da ya Salman duk basa kula ni, kowa ya tsane ni, Baba da Hajiya Yayah kawai ke kula ni, shima Baba sama sama kawai.

Se bayan dawowar sa naji wai an aura masa Sa'adah tun sati biyun rabuwar mu, an mai huce haushi shi kuma ya gudu, kamar yadda naji Hajiya Yayah na fadawa Aunty Luba, dawowar sa ne abokin sa kuma kanin likitan da ya kula dashi ya sanar musu ciwon zuciyar sa, aikuwa wannan ya kara kaimin tsana ta a zuciyar yan uwa na.

Da kyar da nasiha Baba ya shawo kan Abba na koma can, zaman ba wani dadi dan ba me kula ni, Abba da kyar yake amsa gaisuwa ta, Mama kuwa se daga baya ta fara amsawa, kullum cikin habaici take min wai yana Masdooq ya samu mata ta kwarai me tarbiyya me son sa, dan kuwa Sa'adah na kula dashi.

A duk sanda ta ambaci Sa'adah zuciya ta ciwo da daci take yi, ban san ina son Ya Masdooq ba se a wannan tsukin, so ba na wasa ba da ya sa nake kishin sa, duk sanda Mama tayi hirar Sa'adah ranar kwana nake kuka, ba na komai ba se na nadama, da nayi hakuri na zauna a gida na da tuni ina can ina farin ciki abi na, da be kara aure ba, da tuni har yanzu yana kashe ni da salon soyayyar sa, na cuci kaina cuta mafi muni.

Ganin in na zauna nima ciwon zuciyar ze kamani yasa na kira Baba na kwantar da murya da fadin ya nema min alfarma wajen Abba ya bar ni na fara zuwa shago na na make up, wanda na manta ban fada muku ba satin tarewar mu Baba ya damka min mukullin, an gama komai se fara aiki, sedai abubuwan da suka biyo baya yasa ba'a fara din ba, yanzu kuwa na dauki damarar mai da kai wajen sana'a ta, cikin ikon Allah yana tambaya Abba yace shi ba ruwan sa, ko me na ga yayi min a rayuwa nayi ba ruwan sa, duk da ban ji dadin amsar ba haka na shirya na fara fita, sati daya ina cuku cukun yadda komai ze kasance, taimakon da Allah yayi min sarkar sadaki na dake hannu na, ita na siyar dake me tsada ce na karbi manyan kudi na karasa bukatuna, duk da komai na kayan aiki Ya Masdooq ya saka min kuma masu tsada da quality, wannan yasa ma'aikata kawai na nema na zuba, ka na basu albashin su tun lokacin dan su ji dadin aiki, haka kuma na sake kara wasu kayan mayuka da na kwalliya, zuwa kayan saloon dan nayi 30% discount a watan farkon fara aiki.

Aikuwa wannan discount din ya jawo kin customers matuka, nan da nan guri ya bunkasa, dake Baba se da ya duba fuskar kasuwa sannan ya kama min ko in ce ya siya min wajen.

Kafin kace me guri ya daukaka, se gashi na bude wajen yin snacks a kusa da shi, da wasa na fara se gashi Allah ya sa masa albarka, wajen kwalliya na duk inda kayi zaka ji sunan "Asaimah touches and beauty saloon".

Ni kadai na san ma'anar Asaimah, sanin duk inda Masdooq yake daidai yake da Assadiq yasa na dauko As din farkon sunan Assadiq, se na hada da suna na Aimah, making Asaimah, zuwa lokacin kam ba zan iya fada muku irin karfin da so da kaunar Masdooq a raina ba, se dai na

sani na banza nake yi, MASDOOQ ya riga yayi min nisa, naji ma labarin wai ya dauki matar sa zuwa India sun je ganin likita, daga nan kuma ya cigaba da hutun amarci, duk a bakin Mama nake ji cikin habaice habaicen ta, ranar da naji kwana nayi da zazzaɓi da ciwon kan da kuka ya sa min, zuciya ta kuwa kamar na cire na jefar ko na huta da zafin da take min, kishi nake yi da Sa'adah ba kadan ba wadda tuni na san tana san miji na, amma jakanta be bari lokacin na iya rike mijin ba, gashi nan na yar ita kuma ta dafe.

Sedai duk yadda na kai ga son sa da kaunar sa ban taba nunawa ba, dan nasan in Mama ta gane na shiga uku, dama gashi har a jarida aka buga labari na ina neman kashe kaina da kona gidan miji na saboda rashin so, ban san waye yayi ba, har kuma kawo yanzu ba'a san wanda yayin ba, sedai zuciya ta ta dade da amincewa Ibrahim ne, na kuma ja masa Allah ya isa ba adadi, dan kuwa babu damar na fita se an nuna ni, Hajiya Yayah da Mama ma na jaza musu, haka yan uwa na, dan har da hoto na da cikakken sunana aka buga, se da kyar su Ya Salman suka samu aka kashe maganar, wanda hakan na cikin dalilin dada tsana ta da suka, kuma ban ga laifin su ba na cancanci hakan dan ni kaina na tsani kai na.

Dawowar su daga India suka dawo da cute baby da Sa'adah ta haifa a can, ranar suna yarinya taci sunan Mama, ban iya zuwa ko Barka ba saboda kunya, shi kuwa tuni ya watsar da komai, dan yana zuwa gaida su Mama , sedai daga na ji Muryar sa zan shige daki dan fahimci ranakun zuwan sa se na daina zaman falo, dan ranar farko da ya ganni wallahi be nuna ya san Allah yayi tsiron wata halitta ba a wajen, hakan ya sanyayyar min da gabbai, ya kuma karamin son sa, dan yayi kyau, ya murje alamun kwanciyar hankali, babu wannan fargaba da damuwa, bare ramar tashin hankalin da na ja masa.

A shekara ta uku da mutuwar aure na ne na hadu da Habeeb, ba wani son sa nake ba amma haka na kawo shi wajen Abba dan na gaji da zaman gidan tsakanin Abba da Mama ina ganin tsanar da suke min, wata biyu aka saka bikin, sedai ana saura sati biyu waliyyan sa suka zo wai an fasa, mahaifiyarsa tace ba zai aure ni ba bayan ina ikirarin kashe maza, abin nan yayi wa Abba ciwo ba kadan ba, ashe yasa maganar a ran sa, yana ta ciwo ba wanda ya sani, na kuma haduwa da Jameel, shi tun kan lamari yayi nisa aka fasa, amma an sa rana se dai sati daya da sa ranar Babar sa tazo tayi cin mutuncin ta son ranta a gidan mu, wai dan ta ba ze auri mara tarbiyyar ba makashiya, a lokacin ne ciwon Abba yayi tsananin da aka sani, aka tafi asibiti, nan aka gano hawan jini da damuwa ne suka masa yawa.

Wata daya yayi a asibiti aka dawo gida, ya sani gaba da nasiha yana fadin ya yafe min, nayi kuka kamar zan mutu, na roki abba gafara ya yafe min, tun daga lokacin kuma tare muje cin abincin dare da safe, duk da Mama ita har lokacin bata sauko ba.

Watan Abba biyu a gida jiki ya kuma rikicewa aka koma asibiti yayye na na kula ni lokacin amma sama sama, kwanan sa biyu a asibitin yana rike da hannu na Abba yake fadin

"Duk cikin ƴaƴana Allah ya jarrabe mu da matsanancin son ki ni da Maman ku Nu'aimah, soyayyar da ta kai har mun yi sake wajen tarbiyyar ki, ta yarda har komai da faru cikin rayuwar

ki ya kasance, sedai bana fushi da hakan dan na yarda ƙaddarar ki ce kuma tamu ce, jarrabawa ce daga Allah da baya barin me imani Babu ita, sedai ina rokon ki da girman Allah a karo na karshe dan na san ba lallai na tashi ba, a duk sanda MASDOOQ ya huce daga fushin da yake yi ya waiwaye ki kar ki juya masa baya, ina rokon ki da kar ki kullace shi dan masoyi ne na gaskiya gare ki, ko da ace fushin zuciya yasa ya aikata wani abu a gare ki ina nema masa yafiya tun yanzu, NU'AIMAH ina son Masdooq saboda yana son ki, ina kuma addu'a da fatan Allah ya sake hada ku zama, ya sa ku kasance abokan rayuwar juna har a aljanna".

A lokacin kuka kawai nake, kukan so da kaunar mahaifi na, kukan kaico da nadama mara amfani, kukan tsanar kai na da na kasa farantawa wannan bawan Allahn rai, yana kwance a sickbed amma ni ce a ran sa, ni ce a zuciyar sa, me zan yi ni kuwa na biya Abba a rayuwa ta?

Se na kamo duka hannayen sa cikin nawa, har lokacin ina kuka nace

"Nayi maka alkawari Abba, na amsa maka, wallahi ko me Masdooq ze min a gaba na yafe masa, ka yafe min Abba na bijire maka da nayi, ka yafe min dan girman Allah, kuma ka dena cewa zaka bar mu, ina rokon Allah ya aura maka rayuwa ka kalle mu ni da Masdooq karkashin inuwar aure Abba na".

Duk da ina jin idanun yan uwa a jiki na da na san harara ce da mugun kallon jin abinda na fada amma ai bata tasu nake ba, ta Abba na nake yi da yake mutmushin farin cikin kalamai na, ya shafa kai na yace

"Allah yayi Miki albarka ya ya baki zuri'a ta gari yayi miki mafificin zabin abokin rayuwa, hakika naji dadin wannan alkawari naki, ina kuma rokon Allah ya baki ikon saukewa".

Haka Abba yayi wa sauran yan uwa na nasiha har Aunty Luba, dan tana tare damu kamar mahaifin ta ne, ko da yake ai Abba mahaifin ta ne kamar yadda Baba yake mahaifi na.

Kwana biyu da wannan maganar Abba ya rasu, Abba ya tafi ya bar mu, na sha kuka, na rude, na shiga tashin hankalin da na ke tunanin ko Mama ba zata fini jin mutuwar nan ba, ba dan komai ba se dan shakuwar mu da kuma guilty conscience da yake damu na na rashin faranta masa rai har ya mutu, se kuma ran sadakar bakwai ga sabon zance wai bakin ciki na ne ya kashe Abba, ban san ya akai aka fara zancen ba se ga zance a bakin yan unguwa da mutan gari, nice har social media, Abu kamar ana rurawa maganar wuta musmaman kasancewa ta sannanniya, se gashi wanda be san labari na ba da yanxu ya sani, na sanu na samu daukaka amma negative daukaka.

Na zama mujiya a unguwa da gidan mu, dan Mama ma tace ai gaskiya ne bakin ciki na ne ya kashe Abba, yan uwa na da dama ba su gama sauka daga dokin fushin su ba suka sake hayewa dan naja musu magana, duk in da suka yi nuna su ake ai yayye na ne, abin dai babu dadi.

Hajiya Yayah kawai ke tare dani a lokacin, tattarowa tayi gaba ɗaya zuwa gidan mu ta tare a waje na, dan tayi tayi na bita naki, bana san ganin Sa'adah kamar yadda nake boyewa Masdooq, in har kuma zan je gidan ta haduwa da su dole ne.

Se da aka yi wata daya sannan ta koma, bayan ta bani shawarar komawa islamiyya, na ji dadi kuwa dan damuwa ta min sauki, a nan Allah ya haɗa ni da Malam Huzaifa, mutum na gari da bayan Masdooq babu wani namiji da naji dadin mu'amala da shi, mutum me ilimi da sanin ya kamata, shi ya fara fahimtar sihiri Ibrahim yayi min bayan ya saurari labari na, ya dage da bani azkhars da kuma rubutu da tofin ayoyin karya sihiri, haka ya kawo min hayaki na su habbatus Sauda da su ganyen magarya, cikin ikon Allah tun da nake amfani da su nake jin kamar ana kwakkwance min zuciya ta da nake jin ta a daddaure, be tsaya haka ba ya dage min wajen karatu, se gashi cikin kankanin lokaci na kusa hada sauka, abinda da ko ixu biyar me kyau bani da shi, ga kuma litattafan addini da ya tsaya min nake yi, se gashi Allah ya albarkace ni da samun ilimi a dan kankanin lokaci na wata shida, se kuma ya bijiro da zancen son aure na, ban ki ba na amsa masa, aka yi komai da ya kamata, shine fa a ranar daurin aure aka samu wanda yaje gidan su ya sanar da iyayen sa wace ni, wannan karon ba mahaifiyar ce ta ki ba, mahaifin sa ne, shine fa aka daura da Masdooq a karo na biyu batare da na sani ba, Huzaifa ya rubuto min dogon text message da ban hakuri, sedai ban rike shi ba, na kuma fahimce shi, na kuma yi fatan hakan ya zama mafi alkhairi, bayan na gama karanta text din sa ne cousin Dina ta shigo a rude tana fadin an daura auren kamar yadda kuka ji a farkon labarin, wannan shine ainahin wacece ni Aimah.

Na sauke numfashi a hankali bayan na gama na baby labari na, nace ina dafe da mara ta

"Na sani na yi wauta, nayi hauka, nayi rashin hankali duka, amma shin laifin duka nawa ne baby?".

Shiru ban ji baby yayi kicking ba, se hankali na ya tashi, murya ta ta shiga rawa

"Kai ma kana fushi da ni ko baby, kai ma ka tsane ni?, Me yasa ba zaka min adalci ba kai ma?, Please in har ba ka tsane ni ba do kick".

Shiru babu kick, se na kuma marairaicewa ina shafa ciki na

"Please baby, please ". Na fada ina fashewa da kuka, kamar abin almara se ga kick sosai da har se da naji zafi, se gashi ina dariya same time ga hawaye na rolling down my cheek, na saka hannaye na duka kan ciki na cikin farin ciki da tsananin soyayyar sa................✍️.

Vote
Comment
Share fisabilillah

Ouummey 📚✍.

Ouummey 033 [ 6/07/2024 7:34pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍ Oummey
Free book!!!

*ZINARIYAR MACE⚡*
*Wai shin 'yar'uwa menene matsalarki? zubewar nono, ko kuma rashin kwankwason juyawa a falo maigida ya shiririce ya manta da tibi da matan tictok, menene matsalarki ne? rashin ni'ima ko kuma mugun sanyin da ya yi miki katutu, shin rashin taushin fata ne ko kuma kuraje da tabbani, ko bala'in ramar da ta addabeki kuma babu rashin ci ba rashin sha a gidan auranki, gwaigwayewar gashi ce matsalarki ko kuma kaushi da faso na tafin kafa da bushewar fata, kina bukatar fatarki ta yi glowing kalarki ta fita kuraje su mutu, ko kuma kina bukatar azababbun turaruka da humra tare da turarukan wuta. Na san dai kuna da yawa matan da tumbi ya yi musu karan tsaye ina nufin ya katse muku hanzarin yi wa maigida gwalli da muskuce-muskuce a falo😃 Nesa fa ta zo kusa AL-KUTUBIYYA ISLAMIC MEDICINE sun tanadar muku da nau'in magungunan da suke magance kowace irin matsala da izinin Allah. Babban burinmu shine sha'ani na aure ya inganta a samu daidaito. Muna da.*
Na gyaran nono.
Na sanyi.
Dilka tare da hadin sabulu.
Duk Wani nau'in maganin mata.
Humra turarukan wuta perfumes, original miski tahra 3in1, ciccibi budurwar kaza. Had'addun supplement irin wad'anda ba su da matsala. Maganin Sliming wato narka tumbi. Abubuwan da muke sayarwa suna da yawa, kuma babu asarar dukiya. Muna garin kano kuma muna tura kayanmu kowane gari fad'in Najeria da Nijar har ma da kasashemn ketare. Kai tsaye a

tuntu'bemu ta lambobin wayarmu domin karin bayani.
*08089965176*
*07084653262*

Ouummey 033

Page 33

______________________Dariya nake hakwara na a waje, ina ta shafa mara ta kamar me shafa baby, kaunar sa na sake ratsa ni.

"I know ko kowa ze kini ban da kai baby na, na sani ko ban samu adalci a wajen kowa ba ban da kai, i knew I've wronged your Dad and my family, I've cheat him, nayi masa abinda be kamata ba, but ai ba duka ba ne laifi na ko? Starting with Mama, eh mama has the right to be angry with me tun da ta fada min abu naki ji, ta roke ni na bijire, na saba umarnin ta na bakanta mata, amma kafin nan ai suna da laifi ko?, Ba'a raine ni kan nema in rasa ba, ba'a koya min cewa a rayuwa akwai samu akwai rashi ba, samu kadai na sani ni, kome nake so yi min ake tun daga yarinta har girma na, me yasa kuma se daga baya za'a ce min akwai abinda zan iya rasawa, bayan na san na samu duk abinda nake so, shima kuma a lokacin ina ganin in na dage zan samu?.

Bayan wannan, ilimin addini na a lokacin is not that much, bana san zuwa islamiyya kuma Mama ta goya min baya, Ya Salman da yake kokarin ganin ya tsaya a gare ni Mama ta katange tsakanin mu, ban manta irin tijarar da Mama tayi masa ba, a lokacin se da ya zama na in nayi masa magana harara ce amsa gare ni saboda bacin rai, kafin ya dawo ya saki ya cigaba da bin mu da addu'a kawai. Ya Farooq ma da ya dawo da karfin sa ya tsaya kan tsawatar min daga karshe har gidan Mama ta hana shi shigowa, Ya Najeeb ma haka, tsakani na da Ya Ahmad ne kawai bata shiga ba saboda shi me sanyi ne gare ni, tsakanin mu nasiha ce kawai.
To me yasa kuma daga baya zata ke ganin laifi na, bayan tushen komai ya faro ne daga gare su?.

Abba, Allah ya jikansa da rahama ba zan iya cewa wani abu a kan sa ba, na yafe masa ya yafe min, duk da cewa alkhairan sa sun fi komai yawa gare ni, be sangarta ni kamar Mama bq dan shi be san bana zuwa islamiyya ba, haka duk da baya min fada ko duka amma yana min nasiha, cikin nasiha yake fada min abinda yake so na yi da wanda yake so na bari, se dai ya sabar min da komai nake so ze yi min ko ze siya min, har yau ban daina kukan so da kauna tare da kewar Abba na ba, na san duk da yana raye da ba'a banzatar da ni haka ba, ko kowa ze

yi fushi da ni ban da shi, Allah ka jikan sa ka rahmata masa kasa aljanna ce makomar iyayen mu baki daya".

Na karshe ina fashewa da kuka, wannan maganar da nake yi ba karamin raunata zuciya ta take yi ba, abu ne da ya dade ya jima a raina na kuma rasa wa zan furta wa, ko da Huzaifa ya kasance malami na kuma ya san wacece ni ba wai yana nufin komai kuma da ke faruwa ina fada masa bane, daga labari na ban kuma sanar da shi komai da ya dangance ni ba, ba shi kadai ba, kowa ban sanarwa ba, na bar abin a raina ne tsayin wannan lokacin ina fama da nauyin sa, yau daya da na rage se nake jin na samu sassauci kadan na nauyin da zuciya ta ke dauke da shi, haka nauyin da nake jin tayi min q kirji na shima ya ragu.

Se da na sha kuka na na koshi, wanda da ace hawaye na karewa a idon mutum to da na jima babu sauran digon ruwa a idanu na saboda kukan da nake yi a kwanan nan.

A hankali na yunkura na mike, saboda nauyin cikin a cinya ta da kafafu na nake jin sa, shiyasa tashi da tafiya su ke ban wahala.

Wardrobe na bude na jawo gwangwanin madara Nido, cikin sabuwar siyayyan da Ya Masdooq yayi min na watannan, dan yanzu duk wata yake kawo min siyaya, indomie, kayan tea, kwai, Bama, bread, snacks, custard, cornflakes, cooking oil, juices, ruwan gora da gas dina dan karami, shiyasa ban da matsalar abinci ko yunwa, abinci me nauyi ne kadai ake kawo min daga wajen Sa'adah, wanda lokuta da dama Bama ci nake ba, saboda tun ganin madara se naji babu abinda nake so kamar madarar, shiyasa se na hada da bournvita ko milo na yi ta shan kaya na, wataran ma madarar ce kawai se na saka ma ta suga kamar dai yadda nake kokarin yi yanzu.

A dan bowl me madaidaicin girma na hada na sakan tea spoon na dauko ruwa da bread na koma bakin bed na zauna, yau kam bayan na gama hada madarar cikin bread na dinga zuba madarar a tsakiyar bread ina cin abi na, kun san me, da ruwa na dinga kora shi, babu damuwar sanyin sa balle, kai ciki masu gari.

Haka na cinye abu na cikin dadin rai, na shanye ragowar ruwan kana na jingina da headrest na bed din ina sauke ajiyar zuciya, se da naji daidai sannan na tashi zuwa toilet nayi wanka, a cikin sababbun kayan da Masdooq ya kawo min, wanda na san ba nawa bane na gida, kuma kana kallon su kaga sababbi, an musu ɗinkin buba dukkan su se guda biyu da aka yi gown, ban san me yasa yasa aka yi musu wannan ɗinkin ba amma ni kam godiya nake wa Allah dan ina jin dadin saka su in sake, ragowar kaya na na nan duk sun min kadan, abayas dina kwai nake sawa cikin dadin rai.

Yanzu ma bubu daya na dauko na saka, na dauki hula cikin nawa na saka a kai na sannan na koma gaban gas dina, iloka nake son yi da albishir, shiyasa na cire katon hijab din da ba'a raba ni da shi ko yaushe, naje na sakawa bedroom dina lock duk da na san babu me shigo min.

Nan na gwaggwafe zaune gaban gas da katon ciki na kai kace ya kai watan haihuwa ne alhalin

yanzu muke cikin wata na bakwai, nan da nan nayi albishir dina na juye kan plate bayan na shimfida leda, se na maida tukunyar cikin haɗa iloka ta, itama se gashi nayi successfully, na juye itama akan different plate shima na sa leda, ina son albishir din ya sha iska kafin na yanka so se na fara yayyanka iloka ta na bar ta nan kan plate din, baki nq yayi dumu dumu da mai saboda yadda nake ta dandane a ilokar, na sha kusan kwata tun wajen yankawa.

Se da na bude kofar bedroom din na fita falo na dauko juice na dawo na aje sannan na shiga toilet dan wanke jiki na, se kuma naji bari kawai na yi wanka dan zafi nake ji, haka nake fama kwana biyu da jin zafin nan, se in Yi wanka so uku so hudu a yini, shiyasa ban fiya rabuwa da mura ba.

Ina cikin toilet din na ji an bude kofar bedroom din an shigo, nayi kasake cikin son jin waye, se naji shiru babu wani motsi, nace cikin daga murya

"Waye?".

Kamar ba za'a amsa min ba dan har na bude baki xan kuma tambaya se na ji that masculine voice of his, husky and deep, yet very low yace

"Ni ne".

Se da gaba na ya fadi, baby ya juya a ciki na, zuciya ta kuma ta cigaba da bugawa da karfi da karfi, tunani nake kawai me ya kawo shi daki na, na sani baya shigowa se after Isha, shima daga bakin kofa yake tsayawa mu gaisa se kuma asuba, shima gaisawa ce daga bakin kofa, yanzu kuwa daga sautin inda Muryar sa yake se nake jin kamar yana a wajen bed na ne, ko kuwa close to that area.

Ba wannan me tashin hankalin ba, cikin jiki na ne! Dan kuwa hijab dina na kan bed ban shigo da shi ba, in kuma na fita da iya rigar jiki na se ya gan ciki na dan yayi girma sosai har fiye da girman watannin sa.

Se nayi shiru cikin tunanin mafita, daga karshe na yanke ba zan fita ba har ya gaji ya ya tafi, se na sake danna kofar a hankali na kara mata sakata bayan lock din da ke jiki kana na koma na cigaba da wanka na, ko da na gama se na daura towel sannan na maida riga ya, na samu toilet seat dina na zauna dan it's very clean.

****Masdooq*****

Zuba ido yake ya ga ta fito amma shiru, ya duba wrist watch din hannun sa yaga har 20 minutes ya wuce da shigowar sa dakin, ya tabbatar ko kee take yi yaci ace ai ta gama, to me ta zauna yi?.

Ten minutes ta kara mata kafin ya tashi zuwa bakin toilet din yayi knocking, wani zabura nayi

har se da mara ta ta amsa jin knocking din da na tabbatar shine, se kuma na koma na zauna ina dafe wajen tare da cije lips dina, jin shiru ban yi responding ba yasa ya sake kwankwasawa, na kalli kofar ina runtse ido gaba na na dukan uku uku, ya sake yin na uku duk ban amsa ba.

Jin haka se yace

"Me kike yi ne a toilet din har kusan awa daya baki fito ba?, Kina lafiya kuwa? Is everything alright?".

Na lumshe ido cikin jin dadin kulawar sa gare ni, sedai ba zan iya bude kofar ba, se nayi gyaran murya kana nace cikin murya ta da kuka ya dusar kadan

"Ina yin abu ne".

"Is everything ok?".

"Uhm".

Na ce masa, se ya sake cewa

"Zan yi tafiya for two weeks, ga kudi nan na aje miki kan bed, ki rike a hannun ki ko wani abu ze taso, and anjima za'a karo Miki kayan amfani, make sure baki zauna da yunwa ba dan bana san Allah ya kama ni da hakkin wani, dan na san addini daidai gwargwado ina kuma kokarin yin aiki da sani na".

Yana fadar haka ya juya yana kallan bangaren wardrobe dina, a lokacin kuma ya lura da plates biyu dake dauke da iloka da albishir, se ya matsa wajen ya sa hannu ya dauki iloka bibiyu albishir din kuma ya gutsira dan ban yanka ba, ya san su yana kuma so, tun shekarun baya da muna good times na koya masa shan su, har yazo ya fini dan madara yake kawo wa purposely yace na mana tun a gida.
Se da ya lumshe idon sa lokacin da zaki da gardin madarar albishir din ya ratsa harshen sa, ya saki mutmushi batare da ya sani ba, wato har yanzu ina nan da kwadayin da ya sanni, shiyasa madara yake riga komai saurin karewa a siyayya na, Hmm Allah ya shirye ni.

Da wannan tunanin ya juya ya fita bayan ya sake kallon kofar toilet din.

Se da naji fitar sa na kuma bude kofa a hankali na leka na tabbatar ya fita sannan na fito, da sauri kuma na je na saka lock kana na dawo na zauna kan bed bayan na dauko plate din abu na na zauna na yanka albishir din, se kuma naga an gutsira wanda na san shi ne, yo ai na san shi kamar yadda ya san ni ko, se na kalli ilokar itama se na ga ya diba, a raina nace da na san in ze iya karbar abin hannu na da na yi masa da yawa ya tafi da shi.

Na zauna na sha abu na sosai kana na gicciye bacci, hankali na a kwance sanin kofa ta a rufe

take.

Ban tashi ba se da aka kira magrib, na sake wanka nayi alwala na yi salla a zaune dan ruku'i da sujjada na bani wahala sosai saboda nauyin cikin da kuma tokare ni da yake yi, ina idarwa na cigaba da zama cikin yin tasbih kamar yadda na saba da karatu har aka kira Isha na tashi nayi.

Daga nan kuma na dora da aikin da ya zame min wajibin manzil, wato tunani, indai na zauna babu abin yi da ya wuce shi, ban ankara ba har after 11 ina wajen, kafata da ta sage ta dawo da ni hayyaci na, na mike ta daga tankwashewar da na mata sannan na dubi lokaci, zaro ido nayi cikin mamakin yadda aka yi ya tafi da gudu haka, seda kafa ta ta saki sannan na lallaba na haye bed, ko da nayi addu'ar bacci na shafa baccin be zo ba har aka kira sallar asuba, dama na kwana biyu ina fama da wannan rashin baccin, amma bani da wanda zan fadawa, haka nayi sallah sannan na koma na kwanta, kamar ko da yaushe ban kara minti biyar ba bacci ya kwashe ni.

Nice ban farka ba se after eleven, na tashi na yi wanka a daddafe, na gyara iya gado na dan yau bana jin dadin jiki na ko kadan, kaina ciwo jiki na ciwo, wanda ban san inda zan nuna takaimai yake min ciwo a jikin ba, ko ina kawai jin sa nake ba daidai ba.

Yau ruwan tea kadai na sha da na kuzawa madara da bournvita, ko bread ban hada dashi ba, ina gama sha na koma na kwanta, kamar wasa se kuma ga zazzabi gaf gaf gaf.....................✍️.

Vote
Comment
Share fisabilillah

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 034  [ 06/07/2024 7:35pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Oummey
Free book!!!

*ZINARIYAR MACE⚡*
*Wai shin 'yar'uwa menene matsalarki? zubewar nono, ko kuma rashin kwankwason juyawa a falo maigida ya shiririce ya manta da tibi da matan tictok, menene matsalarki ne? rashin ni'ima ko kuma mugun sanyin da ya yi miki katutu, shin rashin taushin fata ne ko kuma kuraje da tabbani,  ko bala'in ramar da ta addabeki kuma babu rashin ci ba rashin sha a gidan auranki, gwaigwayewar gashi ce matsalarki ko kuma kaushi da faso na tafin kafa da bushewar fata, kina bukatar fatarki ta yi glowing kalarki ta fita kuraje su mutu, ko kuma kina bukatar azababbun turaruka da humra tare da turarukan wuta. Na san dai kuna da yawa matan da tumbi ya yi musu karan tsaye ina nufin ya katse muku hanzarin yi wa maigida gwalli da muskuce-muskuce a falo😃 Nesa fa ta zo kusa AL-KUTUBIYYA ISLAMIC MEDICINE sun tanadar muku da nau'in magungunan da suke magance kowace irin matsala da izinin Allah. Babban burinmu shine sha'ani na aure ya inganta a samu daidaito. Muna da.*
Na gyaran nono.
Na sanyi.
Dilka tare da hadin sabulu.
Duk Wani nau'in maganin mata.
Humra turarukan wuta perfumes, original miski tahra   3in1, ciccibi budurwar kaza. Had'addun supplement irin wad'anda ba su da matsala. Maganin Sliming wato narka tumbi. Abubuwan da muke sayarwa suna da yawa, kuma babu asarar dukiya. Muna garin kano kuma muna tura kayanmu kowane gari fad'in Najeria da Nijar har ma da  kasashemn ketare. Kai tsaye a tuntu'bemu ta lambobin wayarmu domin karin bayani.
*08089965176*
*07084653262*

Ouummey 034

Page 3️⃣4️⃣

____________________Zazzabi me zafi ya rufe ni har jiki na na rawa, ga ni ba ko paracetamol a daki, ni kadai kamar mayya haka nake fama babu wanda ya san halin da nake ciki, a haka na

wuni har magrib kafin na ji saukin sa, na tashi nayi wanka da ruwan zafi da kyar dan jiki na ba karfi, ga yunwa dan bayan tea babu abinda ke ciki na wuni guda.

Da dafa bango na fito daga toilet din na zauna bakin bed ina maida nunfashi, tsayin lokaci kafin na ja jiki zuwa gaban wardrobe ba ciro wata bubu din na saka, na fesa turare cikin karfin hali dan se na ji dakin gaba daya kamar yana tashi tashi.

Ban iya yin sallah ba se da na dafa indomie biyar na dora mata kwai hudu soyayye na cinye ta tas da zafin ta tana tururi, se da na jira ta fada min sannan na tashi nayi sallah.

Ban koma bed ba se da na yi Isha, duk da haka na cigaba da zama na dan na san ko na hau bed ba bacci zan iya yi ba, tunqnin shago na yau nake yi da ya kusan shekara a rufe, dan tun rigimar aure na da Habeeb na garkame shi ban kuma waiwayar sa ba, ma'aikatan sun yi zarya gidan mu har sun gaji nace se daga baya tukuna zan neme su, suma da suka lura ba ni da niyyar budewa se ba su sake nema na ba.

Na sani da abubuwa ba su sake rikicewa ba da tuni yanzu ba wannan maganar ake ba, na sani da shago na ya shiga cikin manyan shagunan kwalliya da ake ji da fadin su a garin nan.

Yau ma se after subh na samu bacci, ina farkawa na karya se zazzaɓi ya dawo, ban samu sauki ba se after magrib, daga ranar kuma se abin ya zama daily routine, in dai har zan karya shikenan zazzaɓi ze taho, ba ze tafi ba se bayan magrib.

Ban taba fadawa kowa ba, duk da ma bani da kowan da zan fadawa din, haka na cigaba da rayuwa, ga zazzabi ga ciwon kai, ga kuma wataran in ji kirji na yayi min nauyi, se gaba daya tsoro ya rufe ni, na dinga tunanin mutuwa zan yi, ba wai mutuwar nake tsoro ba a'a in mutu ban haife baby na ba, ina son ko da zan mutu ya zama baby na yazo Duniya, ta yadda zan tafi hankali kwance da sanin na bar me min addu'a.

Wannan tsoron se ya sake haddasa min damuwa, ya zama kullum cikin kuka da tunani na ke, ciwon kai kuwa ba ya taba bari na, safe rana da dare cikin sa nake ga kuma ƙarin zazzabi, duk se na fige na lalace na rame se katon ciki a gaba, dama ba wani aikin kirki nayi ba, ci ne ya buda ni.

Sati biyu kamar yadda yace yayi ya dawo, kafin nan kuwa yaron office din su ya kawo min irin siyayyar da yake min, ya bayar me gadi ya kawo falo Hindi kuma ta kawo min.

Hajiya Sa'adah na nan na abin da ta ga dama, rowar abinci tana nan tana yin shi se dai ko a jiki na wai an tsikari kakkausa, shi kam Masdooq har yanzu be mata maganar horan yunwar da tayi min ba a baya, ya zuba mata ido yana fahimtar ta, irin fahimtar da be yi mata ba a baya.

Sedai ya sanar da ita kar ko da wasa ya sake ganin kafar ta a daki na, haka kumq duk abinda ze min babu ruwan ta a acikin be shafe ta ba, that's in tana san cigaba da samun farin ciki da

kwanciyar hankali daga gare shi.

Abin da ya kawo maganar shine bayan mun dawo daga hospital yaje yayi min siyayyar nan se ta tare shi da kissar me yasa ze min wata siyayya daban bayan muna da komai a gida, se yace mata kawai dan baya san fitina na, se kuwa tace ita dai bata ji dadi ba sai hakan kamar yana neman nuna fifiko ne tsakanin mu, wai dama ai ita ta san har yanzu yana so na waye waye, shine fa ya bude mata wuta.

Gaba daya se ta tashi hankalin ta lokacin, ita a son ranta kar ya kula ni, kar ya damu da ni da duk wani abu da ya shafe ni, sedai abin da bata sani ba shine ba wai so bane yasa yake min duk abinda yake min, kawai bin umarnin Allah da son sauke hakki ne, amma maganar so a lokacin ai babu ita, da dai shekara biyar baya ne wannan ba zan musa ba.

Ko da ya dawo ban gan shi ba ranar dan dawowar dare yayi, so na bar shi as gajiya ne ya hana shi shigowa, tun da asuba nayi ta zuba idon ganin sa, ba wai dan na san ze kula ni ko kuma zan samu wani abu daga gare shi ba, se dan kewar sa da kewar motsin sa da nayi.

A duk ranar kwana na kwanan farin ciki nake yi saboda sanin yana tare da ni, ko da ba'a kusa dani sosai ba amma ba a nesa da ni can haka ba.

Ina son miji na, in kaunar sa a raina, irin soyayya da kaunar da wani mahaluki ne taba samu ba daga gare ni, son shi da kaunar shi yasa kwata kwata duk abinda ke faruwa bana ganin laifin shi, wanda a zahiri ma haka ne ba'a iya waje na bane, duk wanda yaji labarin mu ya san Masdooq ya ma yi kokarin sake zama dani, cikin kuma kulawa irin haka, bana tunanin in ba shi bane wani en ze kula da ni lokacin da bana iya yi wa kai na komai, saboda tsana iya ta duniya babu wadda ban gwada masa ba, wuka ce kawai ban dauko na sa masa a wuya ba, amma ai nayi alternative tun da na kusa kona mu gaba daya.

Har gari ya waye ranar ban koma bacci ba saboda san ganin sa, wannan ya kara min ciwon kai na, sedai ban damu ba, in as much as zan gan shi to duk wani ciwo daga baya ne.

Sedai gaba daya wunin be neme ni ba be nemi inda nake ba, damuwar hakan ta karawa zazzaɓi na karfi, ranar se bayan Isha na samu kai na, idanu na sun yi zuru sun yi loko saboda ciwo da rashin bacci, na rama salloli na kamar yadda yanzu ya zame min wajibi saboda zazzabin baya min da sauki, ko hannu bana iya dagawa in yazo, ga na yau da yazo da sabon salon kwankwatsar jiki, se in ji kamar ana daddaka min jiki na da tabarya.

Se da ya kwana biyu sannan ya shigo, lokacin kuwa na gama fidda rai, na gama yardar wa kai na ba ni da sauran gurbi a rayuwar Masdooq face biyayyar iyaye, se na sake jin son baby na a raina, sanin bani da kowa se shi.

Idanu na a kasa muka gaisa kamar yadda muka saba ya tafi, se ga siyayya again ranar ya karo, na yi godiya da kalma biyu

"Na gode".

Daga haka ya fita se kuma wata asubar duk da ranar a daki na ya kwana, haka rayuwa ta cigaba da tafiya, ciwo na damu na amma na kasa bude na fada ko da paracetamol ne a samo min.

Na yi wani irin haske kamar mara jini a jiki, haka kullum sake ramewa nake saboda danuwar da na sawa raina, hatta cin abinci na ya ragu, se kuma Allah ya yaye min zazzabin after a month and week, ciki na ya sake fitowa sosai saboda girma, haka yanzu da yawan abu da rarrafe nake yi saboda yadda mikewa da tafiya ke wahalar dani, cikin gaba daya a cinyoyi na da kafafu nake jin sa, yanzu watan ciki na takwas da sati biyu.

Ban taba zuwa awo ba, ba'a taba duba lafiya ta ko ta cikin a wani asibiti ba, hasalima wata na kusan biyar ban leka ko falon gidan ba bare in fita, fata ta tayi kyau se sheki da ɗaukar ido take yi na jin dadi da Hutu, se dai rama ce ya bata kyan da nayi dan ana kallo na ake ganin ta, dan ma hijab na suturta ni.

*****AUNTY LUBA*****

A hankali ta zauna kusa da shi, gaban ta na dukan uku uku, ta rasa ma ta ina zata fara, abu ne da ya katange ta daga shiga, ya saka mata iya limit din ta, yace kuma a nan yake so ya tsaya.

Rashin madafa yasa ta kasa cewa komai, se ta bige da kiran sa zuwa yin breakfast, Ya Salman ya juyo ya dubi matar sa cike da so da kauna

"Tashi muje, Allah yayi miki albarka".

Cikin jin dadi ta amsa da amin kana suka wuce wajen dining, a can suka tadda Mimi da Lily kamar yadda suke kiran second born din Aunty Luba, asalin sunan ga na gaskiya NU'AIMAH ne, sunan da Aunty Luba ta zaba wa Babyn ta bisa zabin da Ya Salman ya bata, lokacin da ta sanar da shi sunan da ta zabawa yar su ya dade yana kallon ta, cikin wani irin yanayi, ya sani yana son Nu'aimah, ba shi kadai ba ma dukkan su yan uwan ta na son ta, sedai a yau ya sake yarda Luba da Masdooq na wa Aimah irin son da su basa mata, ba wai yana nufin sun fi su son ta ba ne, su suna iya fushi da ita saboda bacin rai, amma lubabatu bata taɓa fushi da Aimah nan, despite all that happened da kuma abinda tayi wa dan uwan ta, duk da a zahiri tana nuna fushi wa Aimah, sedai a badini tana azabtuwa da hakan, babu ranar Allah da zata fito ta fadi Luba bata ambaci sunan Aimah sama da so biyar ba, har yau tana kuka da ƙaddarar Aimah, ze iya cewa ita take kishin Aimah lokacin da ita take can tana hauka, dan in be manta ba lokacin da aka aura wa Masdooq Sa'adah kukan da tayi ba kadan bane, a cewar ta a jira Aimah ta gane kuskuren ta a maida musu auren su mana, shine za'a aura masa wata, seda Hajiya Yayah ta zauna tayi fada tayi nasiha kafin ta danni ranta ta karbi Sa'adah, duk da kuwa kasancewar ta itama yar uwar ta kuma cousin me irin matsayin Aimah.

Da ta ji Masdooq ya gudu saboda auren bata wani damu ba, hasalima se taji kamar tana farin ciki, se da ta nutsu tayi tunani ta auna hakan a kan ya ko Aimahn Tata tukuna taga rashin dacewar ace tayi farin ciki, shine karo na farko da ta tausaya mata, bare da ya dauki har shekara cirr ya gujewa sabuwar amarya, a wani bangare kuma tayi farin cikin sanin har lokacin Masdooq na san yar uwar ta, tana kuma addu'a da fatan Allah ya daidaita su.
Haka kuma ta dauri aniyar tausar Masdooq da ma duk wani me fushi da Aimah, sedai Salman na sanin kudirin ta ya saka mata katangar karfe da duk abinda ya shafi Aimah

"In har ni mijin ki ne da yake da cikakken iko a kan ki kika kuma yarda da hakan to na umarce ki da zare hannun ki daga duk wani abu da ya shafi Nu'aimah, haka kuma ban miki izinin kiran ta ko zuwa inda take ba, in har kika yi hakan batare da sani na ba Allah ya na kallon ki kuma kin san me hakan ke nufi".

Ranar ba irin kuka da magiyar da bata masa ba amma yaki saurarar ta, daga karshe ya mata warning me karfi kan kawo masa duk wani batu kan Aimah, hakan kuma ya dade yana damun ta duk da tayi biyayya, wannan yasa lokacin da ta zabi sunan Aimah matsayin na yar ta be yi mata musu ba ya saka mat, sedai ya hane ta sanar da Aimah kamar yadda ya gargadi duk yan uwan sa, duk abin nan fa Ya Salman ke yi ba wai baya son Aimah bane, sedai yana kokarin ganin sun nuna mata wani side na rayuwa, ta yadda zata farfaɗo ta dawo cikin hankalin ta, sedai a kokarin sa na son yin gyara wa rayuwar kanwar sa be san ya sake yin wani gibin bane.

Kwanciyar Mama a asibiti ya tada musu hankali ganin kamar zasu rasata yadda suka rasa Abba, shiyasa out of consciousness suka kira ta suka yi mata maganganun da suka yi, a ran sa yana jin zafin kasancewar ta kaddarar su duka.

Shi da kan sa yace lilly za'a ke kiran Aimah karama wadda Aimah babba da Lilly ta san ta, har kawo yanzu kuma bata san ainahin sunan ta ba, a fili yake son Lilly sedai shi tashi soyayyar bata sa ya kasa tsawata mata ba, amma fa Daddy's favorite ce.

Ajiyar zuciya Aunty Luba ta sauke da ta sa Ya Salman kallon ta, tun dazu ya lura tana cikin damuwa haka akwai Magana a bakin ta, sedai ya bar shi zuwa su gama cikin abinci, suna karasawa yace Mimi ta kama hannun Lilly me shekara uku su tafi playroom din su, cikin jin magana yarinyar ta kama kanwar ta suka tafi.

Se lokacin ya maida hankalin sa kan matar sa da ya kuma lura ta koma tunanin da take, ya kira ta cikin sunan da se suna su biyu kadai yake fadar sa

"Zuma ta".

Sedai ga mamakin sa bata ji shi ba, ya sake kiran ta amma har yayi na uku bata ji ba, se ya koma kusa da ita ya jawo ta jikin sa, se lokacin ta dago ga kalle shi da idanun ta da suka tara hawaye, cikin damuwar da ya samu kan sa na ganin ta cikin wannan yanayin yace

"Menene?, Me yake damun ki har yake saki cikin zurfin tunani har haka Luba?".

Tana buɗe baki ta fadi abinda be yi tunani ba saboda yadda tsabar biyayyar ta gare shi tun da ya hana bata kuma marmarin tsallake umarnin sa ba

"AIMAH".

Sunan ya fito tare da saukar hawaye daga idanun ta zuwa kan kuncin ta, ya tsira mata ido cikin rashin abin cewa........................✍️.

Se kuma Allah ya kai mu ranar Litinin da rai da lafiya, daga haka ni da Aimah muke cewa ayi weekends Lafiya ❤️💝😍.

Vote
Comment
Share fisabilillah.

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 035 [ 8/07/2024 9:02pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Oummey
Free book!!!

*BOJUWA HERBAL'S & SCENTS*

*Suna kawo Saiwowin sanyi da suke dagargaza sanyin mara da na jijiya.*
*Haka nan suna kawo Saiwowi daban daban daga Chad da Sudan, kuma marasa illah*
*Saiwowin tsumi*
*Saiwowin dahuwar kaza/tattabaru*
*Saiwowin matsi gangariya*
*Original gadalin mata*
*Ƴaƴan gadali na asali*
*Original gumba*
*Tsumin Saiwowi*
*Tsumin kwakwa da Dabino*
*Igiyar alkairi*
*Zumar goran tula*
*Hakkin daka na musamman na asali*
*Bayan haka suna dafa kazar amare da masu jego da ma uwayen gida*.
*Akwai bridal package*
*Mai jego package*
*Ƴar gata package*.
*Dukkan kayan kuma available ne for pickup or immediate delivery.*
*A Kano nake amma kuma nationwide delivery ne*
*Ku tuntubi Surayya Halin yau a wannan lambar dan samun naku cikin musulmin farashi*
*08032773332*
*Iyah Basiru na gaisuwa*😅

Ouummey 035

Page 35

___________________"Shin ban hane ki kawo min batun ko da Abinda Ya shafe ta bane Luba?".

Bata share hawayen ba take bashi amsa, duk da dukan da gaban ta ke yi amma bata fasa ba, baze yiwu a cigaba da wannan abin ba, sam babu adalci a lamarin nan, ko da kuwa bata kyauta ba amma ai bata cancanci haka ba, da soyayya da jawo wa a jika ne zata gyara, amma abinda suka yi ai kara tabarbara lamari ze yi.

"Idan da gaske ba kwa san jin ko da batun da ya shafe ta ne se ku tsaga jikin ku ku cire jinin ta da yake yawo a jijiyoyin ku, haba mana baban Mimi, wannan abin naku babu adalci, sam wallahi".

Tsananin mamaki da al'ajabi yasa Ya Salman kasa cewa komai, se kallon ta da yake yi kamar wata sabuwar halitta, abu ne da be taɓa faruwa ba cikin tsawon zaman auren su, kai tsawon rayuwar su ma tun suna gida, Luba me biyayya ce, bata da tsayayya balle rashin kunya, shiyasa yanzu abin ya girgiza shi.

Duk da ganin yadda maganar ta ta dake shi be sa ta fasa ba, dan ta kudiri niyyar Insha Allah se ta kawo karshen wanann rashin adalcin da suke wa yarinya karama, kuma in har tayi nasara a kan sa kamar tayi ne akan sauran, dan Kasancewar sa babba yasaa duk sauran maganar sa suke ji bayan ta Mama.

"Ku duba fa, Aimah yarinya ce karama, ko ba komai ai ta cancanci a mata uzuri dan akwai kuruciya a tattare da ita lokacin, aside that ga gata da sangartar autanci da kuma kasancewar ta tilon ya mace cikin maza hudu, kuma ko da su Mama su ka kasance iyayen mu ai yan adam ne, ajizai ne masu iya yin kuskure, dan haka ma su Mama ba su tsallake ba, sun yi nasu ajizancin a kan tarbiyyar Aimah, wajen kokarin gwada mata kauna da soyayya se suka zarme idanun su suka kulle, sukai mata raino akasin wanda suka mana, dan haka har da wannan ajizancin nasu cikin kasancewa dalilin ƙaddarar Aimah, so be kamata ace ita kadai zata yi taking blame din ba, mu ma da namu laifin, dan haka se mu tsaya mu hadu gaba daya mu gyara, ba wai mu wofintar da ita ba, yau da ace Abba ze dawo rayuwa ya ga yadda kuka wulakanta rayuwar ƴar sa mace tilo kuna tunanin ze yi farin ciki da ku, ko ze yi alfahari da ku? In kuna tunanin haka ne to kun yi kuskure, muna rokon ƴaƴa maza a farko ne dan su tsaya wa kannen su a rayuwa, wajen tarbiyya, wajen kula da dabi'u da halayya, da kuma tallafar su a wajen da sukai rauni, in har basu kasance masu aikata haka ba kenan meye marabar su da mata, masu gajeren tunani, marasa dogon tsinkaye da kuma yanke hukunci cikin fushi?, Tabbas babu wani banbanci, dan Allah baban Mimi ku sake tunani, dan Allah".

Ta karashe tana rushewa da kuka, ta dade tana auna irin yanayin da ze iya kasance Aimah ke ciki a yanzu, sedai duk yadda ta auna se taga kamar be kai yadda take ba, tun ranar da taje tausar Sa'adah shekara daya ba wata biyu baya, ta shiga ta fito batare da neman Aimah ba duk da sanin tana cikin gidan, haka kuma ta tabbatar taji ta zuciyar ta ke cikin rashin dadi, ko da Sa'adah ta kasance yar uwar ta me irin matsayin Aimah a musulunce amma a zuciyar ta matsayin nasu varies, in ta rantse ba zata yi kaffara ba tana jin Aimah a ran ta fiye da Masdooq, dan bayan kasancewa jini daya a kwai shakuwar shekaru goma sha shida tsakanin su, ta ya to ba zata damu ba, taya hankalin ta ze kwanta?, Ba zata iya ba, ba zata cigaba da jurewa ba, dole zata yi fighting, for Aimah's sake, and Insha Allah she'll win it.

"Ban san yaushe kika fara ketara umarni na ba, amma na yafe miki, ina kuma rokon Allah ya yafe miki".

Daga haka Ya Salman ya bar table din, har ransa maganganun ta sun taba shi, sosai ba kadan ba amma ba ya san ya nuna mata, shi kan sa hankalin sa ya dade da komawa gare ta, tsoro da fargabar rasa mahaifiyar su da kuma fushin da be gama hucewa daga kirjin su ba ya tunzura su suka yi abinda suka yi, yanzu kuma kunya ce ta sa yake jin nauyin su neme ta, se kuma sanin

waye Masdooq, ko da fushi ya sani ze kula da ita, ba zata tozarta a hannun sa ba.

****Masdooq****

Yau kwanan sa biyu da zuwa kasar France, aiki ne ya kawo shi kuma tun ranar da suka zo suka shiga meeting kan batun da ya tara su, jiya ma sun yi, yau kuma suna hutawa ne.

Tun tashin sa sallar asuba ta fado ran sa, tunanin sa me take yi a lokacin, duk da a irin wannan lokacin in ya shiga ya kan same ta ne kan dankwalin ta da ta maida abun sallah tana yin nafilfili, wani abu da be san ta da shi ba a baya wato tsayuwa ga addini, kai addinin ma gaba daya be kama mata jiki ba, dan se da ya dinga yaki da ita kan tashi sallar subh, haka kuma karatun Alkur'ani da su tasbih zuwa nafila ba ma ze iya cewa ya taba gani tana yi ba a zaman su na baya, se gashi a yanzu ya ga wannan canjin wanda ba karamin faranta masa yayi ba.

Ya sauke ajiyar zuciya yana tuhumar kan sa kan dalilin da ze ke tunanin ta, sedai iya binciken sa ya kasa gano dalilin, ya dai san yana jin wani tight connection tsakanin zuciyar sa da ita, se yak jin kamar akwai wani abu me girma da ya daure zuciyar sa zuwa ga tunanin ta, a bin da baze ce ga shi ba.

Abu ne da ya fi karfin ya kira shi da soyayya, dan ya san feeling din soyayya kamar yadda ya san na denial, se kawai ya ture batun da karfi tun da ya kasa gane meye, ya zaro wayar sa ya danna kiran Sa'adah.

Yana daga tsaye jikin railern karfe a saman hotel din da ya sauka, iska me sanyi na ratsa shi, jikin sa sanye da white blazer maballan ta duka a bude, ta ciki kuwa ko shimi babu, ya harde kafafu yana kallan gari, muryar sa ta shiga kunnen sa tana masa sallama

"Ameen waalaikumussalam warahmatullah".

Ya amsa ta cikin daddadan muryar sa, Sa'adah ta lumshe ido cikin jin karin so da kaunar sa,

"Kuna lafiya? Ya gidan?".

"Muna Lafiya kalau ni da princess, dazun nan ta ishe ni da maganar Daddyn ta".

Mutmushi me kyau ya samu gurbi kan lips din sa har dimple din sa ya lotsa, yana da san yara da yawa, shiyasa har yau in ya tuna Aimah ta masa asarar baby se yaji yana jin haushin ta, ciwon ya dawo masa sabo haka ma radadin, zubar da cikin was abun da tayi ya bata masa rai ya jefa shi cikin damuwa fiye da komai, yau da ace bata zubar masa da ciki ba da baya jin ze rike ta a rai har haka, duk da ya san dama Allah be yi me zuwa duniya ba ne amma ya kasa manta wa.

"Daddy missed her too, a shafa min kan ta in ta dawo".

"Insha Allah, ya aikin?".

"Lafiya kalau, har mun fara abinda ya kawo mu".

"Allah ya bada Sa'a".
Haka suka cigaba da hira da Sa'adah, har sun yi sallama ya kasa daurewa se da ya furta abinda yake ta kokawar dannewa,

"Aimah fa? Tana lafiya?".

Shiru Sa'adah tayi kamar bata kan wayar har se da ya daga wayar da ga kunnen sa ya duba, ganin tana kan call din har lokacin se ya maida yace cikin karamin sauti

"Hindu taje ta duba min ita yanzu".

Daga jin yadda yayi maganar ta san ba wai ra'ayin ta yake neman ji ba umarni ne, dan haka se ta daga wayar daga kunnen ta ta kashe, sefa ta hadiye abinda ya tsaye mata a makoshi sannan ta kwalawa hindu kira, da sauri ta zo ta zube gaban ta cikin kujerun falon da ta ke zaune, yanzu ma da kyar ta iya fada mata taje ta gano Aimah in lafiyar ta.

Ta shiga ta tadda ta a zaune tana shan tea, se ta fita taje ta sanar da ita lafiyar ta kalau.

Ta daga wayar da niyyar kira yafi so biyar amma ta kasa kiran, cikin haka kiran sa ya shigo, ta daga tare da sanar da shi lafiyar ta kalau, be ja maganar ba yayi mata sallama ya kashe kiran dan daga muryar ta ya gane abun ya motsa.

Har yau yana mamakin Sa'adah, taba kishin Aimah fiye da kowace mace a kan sa, be san me yasa ba, sedai abinda bata sani ba shine bata gaban Aimah, dan ko da tun auren su na farko bata taɓa kawo masa batun Sa'adah ba, ya dai san itama ba ta yin ta kamar yadda ya san Sa'adah ma bata yin Aimah.

Tun daga ranar be kuma tambayar ta Aimah ba, in ya kira suka gama gaisawa ze kashe, duk dare kuma ze kira landline din dakin hindu dan jin yaya Aimah take, itama tun da ta gane kullum ta shiga dakin zata duba ta dan sanin amsar da zata bashi in ya kira.

Sa'adah bata taba sanin abin da ke faruwa ba har ya gama kwanakin da ze yi ya dawo, ya dawo da zazzaɓi shiyasa ya kwana ya wuni kafin ya iya samu ya leka ta.

Kullum ya shiga da asuba in ya balle ta se ya ga kamar akwai abinda ya canja a tattare da ita, sedai kuma ya kasa ganewa, amma dai idanun sa na fada masa this is not the normal Aimah da ya sani a baya, tayi haske haka kuma fuskar ta ta rame, amma se ya bar shi as Hasken na zama waje ɗaya ne, shi kuma ranar na damuwar da ke ranta ne, dan shi da ya santa yana

ganin damuwar kwance a idanuwan ta, he choose to ignore it ne dan ya san maybe yana tambaya tace tana bukatar saki, shiyasa ya share kamar be gani ba.

One bitter truth da ya sani amma yake masa wahalar accepting is the fact that Aimah ba zata taba son shi ba, bata so shi a baya ba a yanzu ma ba zata so shi ba, duk da ya fadawa kan sa he's over her Amma har yanzu rashin kaunar ta a kan shi na sukar shi, a duk san da ya ware lokaci yace yayi tunani kan zaman ta a gidan sa a yanzu se ya ciwon sa ya motsa, shiyasa ya hakura kawai da tunanin, ya bar wa Allah komai q hannun sa yake tafiyar da rayuwa da ita a duk yadda tazo, ya na san sama mata wajen zama cikin gidajen sa, sedai yin tunanin gyara mata gidan kan sa na tuna masa tarin kiyayyar ta gare shi, haka kuma ya sani yana yin yunkurin hakan se ta dakatar da shi da wani aiki ko kalaman da zasu tunatar da shi tsabar da tayi masa.

Yau satin sa uku da dawowa, yau kuma wata tafiyar ta taso masa, sedai ba outside kasar ba ne, so kwana uku kawai ze yi ya dawo, ya shiga kamar wancan lokacin ya mata sallama sedai yau kan pray mat ya same ta, sanye da hijab din ta da ya haddace shi saboda indai ze same ta kwana biyu da shi yake yadda ta, a gurguje ya mata sallama ya fita saboda ya kusa makara, yana iya missing Flight din shi, saurin da yake yasa be lura da yadda ta sake ramewa ba da kuma cije cijen lips din da take yi cikin ciwo ba, karfe sha daya jirgin su ya daga.

******

Kwana biyu kenan ina fama da ciwon baya da cinya, yanzu ko tashi ma bana iya yi, satin Ya Masdooq uku kenan da dawowa, yau ya shigo ya min sallama ze sake tafiya, cikin ciwo nake dan cinya ta ba karamin kwankwatsa take min ba, amma dake sauri yake se be kula ba, ko kuma ya kula ya dai share ne ban sani ba, na raka bayan shi da kallo lokacin da yake fita daga dakin hawaye na zubowa daga idanu na, ni kadai na san yadda nake ji a jiki na, rashin wani da zan fadawa ciwo na na kara min zafin ciwon, yanzu da ze bar garin sena ji zuciya ta ta sake karyewa, dan na san ko mutuwa zan yi a dakin nan ba wanda ze sani saboda yadda dama iya nan nake rayuwa ta balle a damu dan ba'a ganni ba, wala Allah se na rube na fara wari kafin a san babu ni.

A kwana biyun nan cikin tunanin Mama nake, so nake na gan ta, so nake na sata cikin idanu na, na rike hannun ta na nemi gafarar ta ko na dace a wannan karon ta dube ni, ban san me yasa nake jin kamar lokaci na yayi ba, amma zuciya ta na fada min mutuwa zan yi, dan ciwon da nake ji ban taba jin irin shi ba.

Haka na ke zaune cikin ciwo, ga ciki rididi a gaba, ga ba wani makusanci a kusa, duk lokacin da hindu zata shigo kuwa ina kokarin dannewa kar ta gane dan bana san idanun kowa a kaina har zuwa lokacin da Allah ze kawo min baby na duniya yadda ba yadda za'a yi da shi tun da na riga na haifa.

Yau ne Ya Masdooq ze dawo indai kwana biyun ze yi kamar yadda ya fada da yana aje min

kudi, yau din kuma na tashi da wani irin ciwo da ya ninka na baya nesa ba kusa ba...................✍️.

To fa, ga Aimah cikin ciwo, ga ba kowa a kusa, Allah ya kawo miki dauki Aimahr mu🥺🥺.

Vote
Comment
Share fisabilillah

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 036  [ 8/07/2024 9:05pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Oummey
Free book!!!

*BOJUWA HERBAL'S & SCENTS*
*Suna kawo Saiwowin sanyi da suke dagargaza sanyin mara da na jijiya.*
*Haka nan suna kawo Saiwowi daban daban daga Chad da Sudan, kuma marasa illah*
*Saiwowin tsumi*
*Saiwowin dahuwar kaza/tattabaru*
*Saiwowin matsi gangariya*
*Original gadalin mata*
*Yayan gadali na asali*
*Original gumba*
*Tsumin Saiwowi*
*Tsumin kwakwa da Dabino*
*Igiyar alkairi*

*Zumar goran tula*
*Hakkin daka na musamman na asali*
*Bayan haka suna dafa kazar amare da masu jego da ma uwayen gida*.
*Akwai bridal package*
*Mai jego package*
*Ƴar gata package*.
*Dukkan kayan kuma available ne for pickup or immediate delivery.*
*A Kano nake amma kuma nationwide delivery ne*
*Ku tuntubi Surayya Halin yau a wannan lambar dan samun naku cikin musulmin farashi*
*08032773332*
*Iyah Basiru na gaisuwa*😅

Ouummey 036

Page 36

___________________ciwo ne da tun da uwata ya haife ni ban taba jin irin shi ba, ga wani irin ruwa da yake bin jiki na wanda na fara ganin shi tun shekaranjiya, sedai ban bashi wani muhimmanci ba, ji nake kamar zan mutu, ga ba mataimaki a kusa, nishi kawai nake cikin zafin ciwo, idanu na a warwaje saboda azaba.

****Aunty Luba***

Yau da farin ciki ta tashi, jiya da dare ta samu tayi convincing Ya Salman, da kuka da magiya da komai kafin ya amince mata taje gidan Aimah, ya fada mata Yes ya san sun yi kuskure sedai kunya fa nauyin Aimah yake ji shiyasa suka kasa neman ta all this while, amma taje, da daddare ze tattaro sauran duk su zo a zauna ayi magana su kuma nemi yafiyar ta komai ya wuce.

Da wannan farin cikin Aunty Luba ta kwana, ta kuma tabbatar wa Ya Salman dan kuwa ta shayar da shi soyayya me matukar tsayawa a rai.

Ko da ta gama shirya wa se ta dauko tsarabar da take son kaiwa Aimah, tsaraba ce ta kayan gyara, kayan kankara mutunci fa kima a idanun megida, kamar kowace mace Aunty Luba ma na siyan kayan mata, na kara niima da kuma na gyaran jiki, sedai ba kowane kara zube take siya ba, a waje ɗaya take yin siyayyar ta, wajen SURAYYA, shima dan ta yadda da ingancin

komai ne, ta gwada ta samu kyakkyawan result shiyasa ta rike ta hannu bibbiyu.

Bata manta yadda aka yi ta santa, makociyar ta Maman Ilham ta haihu ta shiga yi mata Barka, a nan ta samu yan uwan Maman Ilham din, da ke sun san juna sosai aka gaggaisa aka shiga hira, a nan ne suka zo kan hirar kishiya, Aunty Salma yayar Maman Ilham na bada labarin kishiyar ta, ana ta raha se aka zo batun kayan mata da take amfani da su dan gyara da yasa me gidan ta har lokacin itama yake yayinta

"Ai Maman Mimi duk macen da ta zauna tsura yanzu ita taso, mazan nan namu na yanzu se da gyara wallahi, to kana gyaran ma ya ka cika balle ka zauna ka saki baki, shiyasa kin ganni nan bana sanya wajen kula da kai na, ba wai nace mata ku haukace ne wajen shaye shayen magungunan da baku san da me aka hada su ba, kuje ku dinga karbo abinda ze cutar fa lafiyar ku ba, no, komai akwai na gargajiya me kyau da da kan ki zaki duba ingredients din sa ki ga yadda aka hada shi wanda in kina so kema zaki iya yi da kan ki sedai dan wasu abubuwan da zasu yi wuyar samuwa, atoh kin ganni nan nan tikee fruits hannu bibbiyu haka kuma kayan wajen SURAYYA, shiyasa wani wulakancin ko an so kawo maka shi dole a fasa".

Aunty Luba ta gyada kai tace

"Haka ne Aunty Salma, Ni ina taso in samu wajen siyan ire iren kayan gyaran nan duk da nima ina amfani da fruit daily, sedai tsoron irin hannun da zaka fada ya hana ni wallahi".

Aunty Salma ta gyara zama

"To kuwa ki kwantar da hankalin ki, i recommend SURAYYA HALIN YAU for you, in dai kayan gyara sadidan kike nema kin samu, tana dafa kazar amarya, Saiwowin dahuwar kaza, Saiwowin sanyi daga Chad, Saiwowin tsumi, Saiwowin matsi maganin niima, Original gadalin mata, Ƴaƴan gadali na asali, Original gumba, Tsumin Saiwowi, Tsumin kwakwa da Dabino, Igiyar alkairi, Zumar goran tula, Hakkin daka na musamman na asali, da sauransu duka zaki samu a wajen ta, kayan ta masu inganci ne, babu cutar wa ko kadan a cikin su and at very affordable price, ga number ta, 08032773332 chat her up ko ki kira ta, Allah Maman Mimi se kin gode min daga baya".

"Aikuwa yanzu ma zan kira ta, Allah dai yasa a garin nan take?".

"A garin Kano take, sedai tana pickup and nationwide delivery, ko a ina kake za'a iya tura maka, na fada miki zafa ki gode min, just ki tanadi kyautar da zaki min bayan kin yi amfani da kayan".

Aunty Salma ta karashe da tsokana tana dariya, Maman Ilham na mutmushi tace wa Aunty Luba

"A dai bi a hankali kar a ruda min dan uwa da yawa, bana san na ga ya zama mijin Hajiya atoh".

Aunty Luba itama ta harare ta cikin wasa

"Aikuwa yanzu ma na daura damara, mara kirki, ashe babu amana a zaman mu, all this while kin san akwai irin wannan kayan masu inganci amma ko da wasa baki taba fada min ba, yanzu ma if not Aunty Salma ta fada ba zan sani ba".

Dariya Maman Ilham tayi

"Wallahi ba haka bane, kawai dai kin san lamari irin wannan se a hankali".

Hararar ta Aunty Luba tayi aka cigaba da hira, ba'a tashi ba kuwa se da ta kira SURAYYA HALIN YAU, suka gama magana ta biya har kudin delivery, ita kuma ta tabbatar mata gobe gobe kayan ta zasu iso.

Kamar yadda suka yi kuwa kashegari aka kawo mata su, bata yi sanya ba kuwa ta shiga amfani da su yadda aka fada mata, a daren ranar kam ta tabbatar da ingancin kayan SURAYYA HALIN YAU, shiyasa nan da nan bata yi sanya ba wajen siyawa Aimah, itama ta gyara kamar yadda ta gyara, ta kuma samu makamin yako soyayyar ta back a zuciyar Masdooq, sedai kuma bata samu kai mata ba saboda dokar Ya Salman, ta kulle ta aje da alkawarin kai mata duk san da taci nasara akan Salman ya yarje mata zuwa, haka kuma tana wa kowa da kowa recommending kayan SURAYYA HALIN YAU, ta gwada ta tabbatar shiyasa take son yan uwa mata su amfana, ga duk me bukata ga number wayar ta nan, 08032773332, Aunty Luba tace duk wanda ya gwada se ya gode mata kamar yadda ta godewa Aunty Salma.

Cikin farin ciki ta danna ledar a jaka bayan ta dawo daga tunanin da ta tafi, ta fita zuwa compound ta shiga motar ta ta fita, ita kadai zata dan yara na makaranta.

Tana tafe ranta cike da dokin ganin yar uwar ta, gefe daya kuma fargabar irin karbar da Aimah zata mata dan ta san zuwa yanzu itama tayi fushi da su.

Tana yin parking a compound din gidan ta ji gaban ta na wani irin faduwa, fargaba da tsoro mara tushe suka rufe ta, sedai ta alakanta hakan da tsoron reaction din Aimah, se tayi addu'ar komai ya zo da sauki kana ta fito daga motar ta dumfari cikin falon.

****Masdooq****

Tun da ya sauka daga airport kirjin sa ke dukan uku uku, ya dinga jin faduwar gaba ta ba gaira ba dalili, yana jin fargaba mara tushe, haka kawai yake jin gidan sa ba lafiya ba, shiyasa ya tare mota a hanzar ce zuwa gida, tun a gate yake tambayar gate man lafiya dai ko, shi kuma ya tabbatar masa lafiya kalau, duk da haka hankalin sa be kwanta ba se da ya shiga gidan ya ga Sa'adah da princess lafiyar su lau.

Har ya sauke ajiyar zuciya se kuma sunan ta yayi ringing a kan sa tare da wata muguwar

faduwar gaba da se da ya dafe kirjin sa dan ji yayi kamar zuciyar sa zata fado, se kuma ya cire hannun ya nufi dakin ta da gaggawa yana ambatar sunan ta da karfi amma har ya kai kofar dakin bata amsa ko daya ba.
Da wani irin karfi ya tura kofar ya shiga da gudu yana jin tabbas ba lafiya ba, ile kuwa se ya same ta duke a jikin bed tana jujjuya kai jikin ta duk ya jike da zufa da gani tana cikin tsananin ciwo, se kuma wani ruwa da ya gani yana bin kafafun ta, cikin dimuwa da tashin hankali ya riko ta yana kiran sunan ta a rude, daidai lokacin Aunty Luba ta shigo falon.

Da ita da Sa'adah gaba ki daya suka yi dakin cikin fargaba jin yadda yake kiran sunan ta yana kiran ta buɗe idanun ta, daidai suna shiga shi kuma yana birkitota daga kifawar da tayi, haka kuma direct idanun Sa'adah suka sauka kan katon cikin Aimah da yayi kasa sosai a yau.

Wani irin poster tayi cikin shock me karfi da ya daskarar da ita a wajen, shi kam be ma lura ba se da aunty Luba tace

"Innalillahi, Ya Masdooq haihuwa ce fa, kama ta muje asibiti, wai dama tana da ciki ne har ya kai haihuwa bamu sani ba?".

Se lokacin ya kalli cikin, cikin tunanin akan wa ne Luba ke magana, se yayi arba da ciki him gaban Aimah, se da yayi baya kamar ze fadi saboda al'ajabi, mamaki, firgici da rudewa da suka sake shi duka a lokaci daya.

Ganin yadda nake wani irin nishi da yunkuri yasa Aunty Luba jijiiga shi tana fadi cikin tashin hankali

"Ka kama ta muje asibiti Ya Masdooq, tana cikin wahala dan Allah ka muje asibiti kar ta mutu".

Kamar wanda aka yi wa allura se ya shiga kokarin cicciba ta, amma saboda ciki da yasa na yi nauyi da kyar ya iya dauka ta zuwa compound, a motar Aunty Luba ya sani seat din baya shima ya shiga, Aunty Luba kuma ta shiga waje driver ta ja muka fita, Sa'adah dai can aka bar ta cikin shock din da har lokacin be sake ta ba.

Ni kam muna tafe ina salati da kiran sunan Allah, azaba ce nake ji ta ko ina, cinya ta kuwa kamar in balle ga daga jiki na nake ji, haka bayana kamar ana buga min guduma, ba abinda nake face juya kai da kiran Allah, duk na ruda ya Masdooq, se riko ni yake yana min sannu da yin duk addu'ar da tazo bakin sa, se ambatar Aunty Luba tayi sauri yake, gani yake kamar bata sauri bayan tana ganin halin da nake ciki.

A haka muka kai wani nearby private hospital, Aunty Luba ta shiga da gudu ta kira nurses, lokacin da suka zo bakin motar da bed din daukan marasa lafiya tuni Ya Masdooq ya fito da ni daga cikin motar, lokacin na fara fita hayyaci na dan bana gane wanda ke kai na sosai.

Haka aka dora ni aka nufi labour room da ni da sauri, duk yadda nurses da likitan dake kai na

suka yi na kasa haihuwa da kai na, wai babyn bae gama juyawa ba, an so juya shi kuma abu ya faskara, ga shi na riga na gama galabaita dan sati daya kenan ina nakuda ni kadai a daki ba wanda ya sani, dole doctor ya fita dan sanar da family na abinda yake akwai na son yi min CS, daga fitar likitan kuma ban kuma sanin me ya faru ba.

****Masdooq & Aunty Luba****

Tun da aka shiga da ita suke cikin tashin hankali musamman Masdooq, se kai da kawo yake ya kasa tsayawa waje ɗaya, hankalin sa in yayi dubu to a tashe yake, gaba daya kuma kan sa a kulle yake, gani yake abin kamar a mafarki.

Aunty Luba ma ta kasa zaune ta kasa tsaye, se Safa da Marwa take tana addu'ar Allah ya sauki yar uwar ta lafiya, gaba daya ta manta da ya kamata wai ta kira wani daga iyayen su ta sanar musu, ita dai fatan ta kaiwa a fito ace ta sauka lafiya.

A cikin wannan halin doctor ya fito daga labour room ya same su, da sauri duk suka nufe shi suna tambayar ta sauke, se ya sauke ajiyar zuciya yace

"Kasancewar ya dade tana labour kafin a kawo ta so ta jigata matuka, haka kuma Babyn be gama juya ba wanda mun yi iya yanda zamu yi a gyara mata amma ya gagara, dole akwai bukatar a yi mata aiki a ceto ran ta da na Babyn, dan if she continues like this there's tendency na rasa ta ko Babyn ko ma gaba dayan su".

Wani irin kallo ya Masdooq yake masa kafin cikin ihu yace

"To me kake jira da ba zaka mata aikin ba, ko so kake se ta mutun kuzo kuna faɗin you're sorry?, Wallahi duk matata ta rasa ranta ko wani abu ya faru da ita se nayi Shari'a da ku, I'll sue you guys if something bad happened to my wife, kaji na fada maka".

Doctor be damu da ihun da Masdooq ke masa ba se paper da ya mika masa yace yayi signing, cikin fushi ya warci paper ya yi signing din hannu na rawa, doctor na karba ya wuce office din sa dan shirya wa aikin bayan ya bawa nurses umarnin su shirya Aimah.

Cikin mintina uku doctor ya fito shirye ya wuce dakin theatre wanda tuni an gangara Aimah kan bed an shige da ita, nan jinin Masdooq da Aunty Luba ya sake tsinkewa, zulumi da fargaba suka sake samun wajen zama a zuciyar su.................✍️.

Jama'a Aimah zata haihu ga shi abu yazo da tangarda🥺🥺, shin babu nurses, midwives and doctots ne a gidan nan, kuzo ku mata CS ku bamu babyn mu mana, Aimah Allah ya sauke ki lafiya 🥺🥺.

Vote
Comment
Share fisabilillah.

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 037  [ 9/07/2024 8:38pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Oummey
Free book!!!

*BOJUWA HERBAL'S & SCENTS*
*Suna kawo Saiwowin sanyi da suke dagargaza sanyin mara da na jijiya.*
*Haka nan suna kawo Saiwowi daban daban daga Chad da Sudan, kuma marasa illah*
*Saiwowin tsumi*
*Saiwowin dahuwar kaza/tattabaru*
*Saiwowin matsi gangariya*
*Original gadalin mata*
*Ƴaƴan gadali na asali*
*Original gumba*
*Tsumin Saiwowi*
*Tsumin kwakwa da Dabino*
*Igiyar alkairi*
*Zumar goran tula*
*Hakkin daka na musamman na asali*

*Bayan haka suna dafa kazar amare da masu jego da ma uwayen gida*.
*Akwai bridal package*
*Mai jego package*
*Ƴar gata package*.
*Dukkan kayan kuma available ne for pickup or immediate delivery.*
*A Kano nake amma kuma nationwide delivery ne*
*Ku tuntubi Surayya Halin yau a wannan lambar dan samun naku cikin musulmin farashi*
*08032773332*
*Iyah Basiru na gaisuwa*😅

Ouummey 037

Page 3️⃣7️⃣

____________________Suna nan tsaye ciki ciki cikin tashin hankali, lokacin kuwa da za'a auna jinin Masdooq ya dade da hawa, hawan ma irin na wuce hankalin nan, zuciyar sa kuwa bugun da take ya zarce ka'ida, ya dunkule hannayen sa cikin juna amma duk da haka rawar da suke yi bata buya ba, ga zufa da ta jika shi sharkaf kamar wanda aka kwarawa ruwa.

Awa day shiru, biyu shiru ba'a fito ba, wannan ya kuma dugunzuma hankalin su, izuwa yanzu jiri yake ji, kamar gurin na juya masa, yace cikin shakakkiyar murya,

"Rike ni Luba".

Aunty Luba da itama ke cikin tashin hankali ta ji maganar sa kamar daga sama, ta juyo da sauri ta kalle shi se ta ga idanun sa a kulle haka kuma kamar yana tangadi, se ta rike shi da sauri ta taimaka masa zuwa seats a bayan su ta zaunar da shi itama ta zauna.

Yau ita ta karbi girman ta dinga lallashin sa da kalaman karfafa gwiwa, tana fada masa all will be fine, Aimah zata haihu lafiya insha Allah.

A nan suke cigaba da zama har another thirty minutes kafin red light dake blinking a kofar theatre room din ya koma green, indicating an gama komai, se duk suka mike cike da zulumin labarin da za'a basu, a lokacin nurse ta fito rike da baby cikin showel, dake tun da zasu shiga da ita nemi kayan haihuwa Aunty Luba tace babu amma in akwai wajen siyarwa cikin asibitin se a siyo, se nurse din ta mata kwatancen wani mini supermarket nan gefen su, shine fa ta fita ta siyo aka basu.

Cikin fara'a nurse din ta kara so gare su ganin yadda duk suka yi tsaye kamar wasu gumaka, tace cikin fara'a

"Congratulations Mr Masdooq".

Be iya amsawa ba se Aunty Luba ce ta karbi Babyn da ake mika masa tana amsawa da

"Thanks Madam".

Nurse din ta gyada kai ta wuce, bata iya bude Babyn ba saboda tambayar da Masdooq yayi mata

"What about NU'AIMAH?, How's she?".

Aunty Luba ta juya da sauri dan tambayar nurse din sedai cikin rashin Sa'a tayi wani wajen, se ta kalle shi cikin rashin abin cewa, daidai lokacin da another nurse ta fito itama rike da another baby cikin showel, shi be ma lura ba dan hankalin sa na kan doctor din dake tahowa, Aunty Luba kuwa Babyn da ake mikawa ne idanun ta ke kai, tunanin ta na bata abinda take kokarin karyatawa, se kuma Muryar doctor ya gasgata mata shi

"Congratulations Mr Masdooq, the theatre was a successful one, an samu nasarar cirowa matar ka twins, a baby boy and a girl, congratulations 🎉".

Ai daga ita har shi se suka daskare a tsaye, hannun Aunty Luba dake rike da baby ya shiga rawa, ga maza ta kankame showel din ranta nayin fari tass, zuciyar ta na kara gudun garin ciki.

Cikin rawar baki tace
"Doctor...w..whi..ch".

Se kuma ta kasa hada sentence din saboda joy, gane abinda take son tambaya yasa doctor saukaka mata ya bata amsa da nuna mata na hannun ta
"The baby boy din ne babba, and the baby girl kuma karama".

"Wai dagaske kake doctor?, Ta haihu? Kuma lafiyar ta kalau? Kuma yara biyu?, Haka kace?".

Doctor yayi nodding kai in affirmation, shima fuskar sa dauke da fara'a me nuni da farin cikin sa

"An yi mata aiki successfully, an ciro mata baby boy and a girl, abin farin cikin kuma duk suka cikin koshin lafiya a yanzu, ana gyara ta ne kafin a kai ta dakin Hutu".

Se kawai gani suka yi Masdooq ya zube a floor din wajen, not minding the dirt and everything ya yi sujudus shukur, kana ya dago idanun sa kaca kaca da Hawayen farin ciki, Aunty Luba na taya shi da nata Hawayen, ta kankame Boy din a kirjin ta,

"Can I see her doctor, tell me I can, please".

"For sure you can Mr, amma what about the  cute baby girl, an bar min ita ne?".

Se lokacin Masdooq ya sauke idanun sa kan showel din hannun doctor, ya matsa da sauri ya mika masa hannu, likita ya dora masa ita cikin kulawa daidai ana turo Aimah a gado za'a kai ta dakin Hutu, se Masdooq ya matse yar a kirjin sa ya bi bayan su da sauri Aunty Luba ma ta mara masa baya leaving behind doctor a tsaye dake bin su da kallo yana Murmushi.

Se da aka gyara mata kwanciyar ta tare da daura mata ruwa kana nurses din suka congratulating din su suka fita daga dakin, da sauri Masdooq ya matsa ya zauna daidai kan ta tare da dora hannun sa a kan ta da wuyan ta feeling her temperature, ko da yaji daidai se ya mai da hannun sa kan gashin ta yana shafawa cikin tausayi, kauna da wata irin soyayya me girma,  fuskar ta tayi fayau, ramar ta ta fito sosai se kuma haske da ta kara.

Aunty Luba ma na zaune gefen kafafun ta, ban da mutmushi babu abinda take yi, musamman ganin yadda Masdooq ya zubawa fuskar Aimah ido yana kare mata kallo kamar be taba ganin ta ba, alhalin Babyn da aka bashi ko bude ta be yi ba balle ya ga ya take, matar sa kadai yake gani a yanzu dan ko Babyn hannun ta be kalla ba be kuma tambayi shi ne macen ko namijin ba.

Se da ta gaji taga dai be da niyyar kallan yaran sannan tace

"Barkan mu Yaya, Allah ya raya mana yan biyu bisa turbar addinin Musulunci yasa masu jin kai da tausayi ne, Allah ya albarkace su ya albarkaci rayuwar su ya bawa Maman su lafiyar shayarwa, Allah ya tashi kafadun ta".

Se lokacin ya dago ya dubi Aunty Luba

"Ameen lubabatu, Ameen, Ameen, Nagode sosai".

Se tace

"Yaya baka kalli yaran ba, duba mana da wa Babyn hannun ka da wa take kama? Allah yasa da Aimah ne".

"Macen ce a hannu na?, Indai ita e Amin, Allah yasa ta kwaso kamar Barbie, she'd have been the most beautiful baby girl I've seen bayan my honeybun".

Cikin wani irin excitement Luba ke kallon shi, hearing these two names daga bakin sa na nufin komai ya wuce, kamar be taɓa faruwa ba, hakan na nufin Aimah ta dawo matsayin ta na baya a rayuwar Masdooq har ma da zuciyar sa she pray Allah yasa hasashen ta ya zama gaskiya, da bata san irin murnar da zata yi ba.

Shi kam kama showel din da Babyn ke ciki yayi ya yaye a hankali exposing the baby's face, wow Masha Allah, i exclaimed.

"Fatabarakallah Ahsanul Khaliqeen, Masha Allah".

Ya Masdooq exclaimed saboda ganin tsabar Kyan Babyn, Aunty Luba ma da ta matso se fadi take

"Masha Allah, subhanallah, so cute, Ya Masdooq kalli tsabar kyau a nan wajen".

Be iya amsa Luba ba se kallan Babyn da yake kamar ze hadiye ta bakin sa a tale da genuine smile, murmushin da ze iya rantse wa rabon sa da irin shi shekaru biyar baya, wani irin so da kaunar Babyn na ratsa shi, tare da karin karin soyayya da kaunar mahaifiyar da ta kawo ta duniyar gaba daya.

Ya dade yana kallan ta kafin ya sunkuya ya sumbaci forehead din ta da cheek din ta, kana yayi mata kiran sallah a kunnen ta, a hankali ya mika wa Luba ita tare da karbar baby boy din hannun ta, shima tubarkallah kamar yar uwar sa, kyau iya kyau a wajen, shima haka yayi pecking both cheeks and forehead din sa kana ya masa kiran Sallah.

Se lokacin Aunty Luba ta tuna ai ya kamata ace sun sanar da gida, se ta kalli Masdooq

"Yaya are you with your phone?, Ya kamata mu sanar da su Hajiya Yayah, ka san Yaya dole su yi mamaki in suka ji maganar nan, Nima nayi mamakin ganin ya da ciki dan ban taba sanin da shi ba".

"A'a, ba waya a jiki na".

Ya bata amsa in brief, shi kan sa har yau ya kasa digesting samun cikin, baya doubting kasancewar ƴaƴan nasa dan yafi kowa sanin wace ita, tun a zaman su na farko da ta yiyyi kuskuren fita batare da izinin sa ba be yi doubting cikin sa bane, balle wannan da ya san ba inda take fita, mamakin sa shine yadda aka yi ta iya zama da ciki a gidan batare da ya sani ba duk da yana shiga inda take so biyu a kowace rana, har kuma ta iya jure duk wani lalurar da cikin ya zo da shi duk ita kadai, lallai she's indeed very brave, ita din jaruma ce, ya sara mata a kan hakan, sedai kuma yana jin ba dadi yadda ace yana da rai da lafiyar sa amma ta sha wannan wahalar ita kadai, be san yaya ƴaƴan sa suka kasance ba acikin ciki, haka itama wace wahala ta sha duk be sani ba, ita kadai ta jure komai, dole tausayin ta ya rufe shi.

Ya dago ya sake maida duban sa kan fuskar ya, bakin gashin idanun ta sun kwanta gwanin sha'awa, haka kuma cikakkiyar gashin girar ta baki sidik yayi gwanin burgewa.

A hankali ya duka zuwa fuskar ta, forgetting akwai Luba a dakin ya kai bakin sa kan goshin ta

yayi kissing, a very deep and sincere kiss from his heart, ya dade kafin ya daga yana sake kallan idanun ta, ya lumshe nasa ya dora lips din sa kan nata ya bar shi haka without kissing kuma be daga ba.

Aunty Luba ta share hawaye farin ciki ta matsa gefe ta kwantar da babyn hannun ta ta nufi kofa, se da ta kai bakin door din sannan ta fada masa tafiyar ta

"Ya bari na duba motar in handbag dina na ciki na dauka na kira, in kuma baya ciki zan je gida na sanar da Hajiya daga nan na taho da abin da ake bukata".

Be dago ba daga yadda yake ya bude bakin sa lips din ta na shiga cikin nata

"Okay, drive safe and take care".

Daga haka Aunty Luba ta fita, fuskar ta a washe da murna da farin ciki, ji take kamar ta taka rawa ko tayi ta tsalle tana ihu har se an san tana cikin farin ciki, ganin hakan ba ze yiwu ba se yake tafe tana ta nanata kalmar alhamdulillahil laziy biniimatihi tatimmus salihat, har ta fita harabar hospital din, ko da ta duba babu handbag din, se kawai ta shiga motar tare da yi mata key tayi reverse ta fice.

Not long ta kai gidan Masdooq, bata shiga ciki da motar ba tayi parking a waje ta shiga ciki dan hado kayan bukata, a falo ta tadda Sa'adah zaune a hannun kujera lost in thought, jin sallamar Aunty Luba yasa ta dago kamar a firgice, without knowing abinda take yi ta karasa gaban Aunty Luba da sauri har kamar zata fada mata asking her,

"Wai da gaske ciki ne da ita Aunty?, Ko wata cutar ne da ita me sa kumburin ciki?, Ko kuwa dai nice na fara hauka shiyasa nake ganin ciki a jikin ta?".

Se da ta ja baya kafin ta dubi Sa'adah sosai, ganin yadda take a rude se ta kama hannun ta zuwa kujerar dining ta zaunar da ita kana ta dauko ruwa me sanyi ta buɗe tare da miƙa mata, amma se ta kasa kaiwa bakin ta ta sake maimaita wa Aunty Luba tambayar da ta mata,

"Ki sha ruwa tukuna se muyi magana".

Was the answer da Aunty Luba ta bata, bata sake musu ba kuwa ta kai ruwan bakin ya ta shiga sha da kana kalla kasan ba'a san ran ta tasha ba.

"Nima I was shocked da na ga ciki a jikin ta dan all this while be taba fada min ba, da alama ke ma baki sani ba duk da kuma gida daya, nayi mamaki gaskiya, sedai abinda yafi daɗaɗawa shine ta haihu, though CS ne amma komai Lafiya alhamdulillah, an ciro mata babies biyu, a boy and a girl, congratulations kin yi ƴaƴa".

"How?, Taya ya, kuma ƴaƴan har biyu?, No it can't be, ba gaskiya bane, base yiwu ba, ba ze

zama gaakiya ba, ke ma na sani wasa kike ko Aunty Luba?".

Cikin mamaki Aunty Luba take bin ta da kallo, yadda duk ta bi ta rude tana mqganganu kamar wadda a ka ce mata Aimah tayi cikin shege?, Though dole tayi mamaki amma kamar abin na neman wuce limit.

Se kawai tayi gaba tana ce mata tana zuwa ta wuce dakin Aimah, kayan wardrobe din ta watso kan bed gaba daya tana neman kayan da zata tafi mata dashi, sedai gaba daya kayan se ta gan su wani iri, na farko dai ba guga ga kuma kodewar da suka yi.

Da kyar ta samo guda biyar, shima cikin abayas din da ya siyo mata ne ta zuba a wani leda dan babu karamar luggage balle ta zuba, ta duba ta rasa abin dauka kuma se kawai ta fita tana raya koma me ake nema a siya a can.

Gidan Mama ta fara zuwa, se ta tadda bata nan, so se ta juya zuwa gidan Hajiya Yayah, ko gama parking me kyau bata yi ba tayi cikin gidan da gudu tana kwallawa Hajiya Yayah kira..................✍️.

Hurayyy💃💃, it's a baby girl and a boy, congratulations team Aimah, congratulations to the entire BA KOWANE SO BANE FANS❤️😍💃.

Vote
Comment
Share fisabilillah.

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 038  [ 9/07/2024 8:39pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Oummey
Free book!!!

*BOJUWA HERBAL'S & SCENTS*
*Suna kawo Saiwowin sanyi da suke dagargaza sanyin mara da na jijiya.*
*Haka nan suna kawo Saiwowi daban daban daga Chad da Sudan, kuma marasa illah*
*Saiwowin tsumi*
*Saiwowin dahuwar kaza/tattabaru*
*Saiwowin matsi gangariya*
*Original gadalin mata*
*Ƴaƴan gadali na asali*
*Original gumba*
*Tsumin Saiwowi*
*Tsumin kwakwa da Dabino*
*Igiyar alkairi*
*Zumar goran tula*
*Hakkin daka na musamman na asali*
*Bayan haka suna dafa kazar amare da masu jego da ma uwayen gida*.
*Akwai bridal package*
*Mai jego package*
*Ƴar gata package*.
*Dukkan kayan kuma available ne for pickup or immediate delivery.*
*A Kano nake amma kuma nationwide delivery ne*
*Ku tuntubi Surayya Halin yau a wannan lambar dan samun naku cikin musulmin farashi*
*08032773332*
*Iyah Basiru na gaisuwa*😅

Ouummey 038

Page 3️⃣8️⃣

______________________Hajiya Yayah na zaune tare da Mama dake rusa mata kuka se ga muryar Luba na kwala mata kira, ta kalli Mama da ta sa hannu da sauri tana share hawayen ta kana ta tashi ta fita Mama ma ta bi bayan ta dukan su cikin zulumin abinda ze saka Luba yin irin wannan ihun kiran.

A falon sama suka hade da ita, ko kafin su bude baki su tambaye ta se kawai tayi wani dan tsalle ta fada jikin su gaba daya, ta saka hannu ta rungume su dan abin ya zo mata a daidai samun su da tayi tare.

Gaba dayan su cikin fargaba suke tambayar ta Lafiya? ta saka dariya ganin yadda duk suka tsure, se kuma hankalin su ya kwanta jin dariyar ta, hakan na nufin ba wani abu mara kyau bane ya faru.

Hajiya Yayah ce ta janye jikin ta tana fadin

"Ji min wani rashin hankali, me haka zaki zo kina abu kamar wata karamar yarinya, duk kin sa hankalin mu ya tashi?".
Batare da ta saki Mama ba ta dago tana dariya

"To kuwa hankalin ku ya kwanta, wannan babban gagarumar abin farin ciki ne da ze girgiza ku, shiyasa nima na kasa danne nawa farin cikin".

"Ba mu musha daughter, har kin sa na kagu naji".

Shiru tayi ta ja baya tana kare musu kallo, kana tace cikin karamin sauti

"Nu'aimah ta haihu, dazu aka mata aiki aka ciro yara biyu, namiji da mace".

Gaba daya se suka kame, kamar babu jini a jikin su, kamar bata ji ba Hajiya Yayah tace

"Me kika ce?".

Aunty Luba ganin reaction din su se taja hannayen su zuwa kan sofa ta zaunar da su kana ta zauna a ta gaban su
"Wallahi Aimahn mu ce ta haihu Mama, nima ban san tana da ciki ba dan be taba fada min ba, se kawai zuwa nayi na tarar da su tana nakuda shi kuma duk ya rikice, abin mamaki har Sa'adah ma bata sani ba se yau din, can na baro ta cikin mamaki itama".

Shiru suka yi duka kowa na assimilating zancen, basu ankara ba suka ji Mama ta fashe da matsanancin kuka, duk se hankalin su ya koma kanta, Hajiya Yayah ta shiga lallashi ita kuma Aunty Luba tana tambayar ta me ya faru, cikin kukan take cewa

"Me na aikatawa yarinyar nan Luba?, Me ya tunzura ni har haka?, Shin ita ba yar Adam bace me iya yin kuskure?, Me yasa na manta hakan, ace ta dauki ciki tsayin watanni tara tayi fama da shi amma babu kulawar uwa?, Tun kwanakin baya nake mafarke mafarke da ita amma fushin zuciya ya hana ni neman ta, yanzu da ace mutuwa tayi a wajen haihuwar shikenan sedai a zo a fada min ta mutu?, Wayyo Allah na ni Safiyya, me nayi haka?".

Hajiya Yayah ma cikin damuwa tace

"Ba iya ke kadai ce kika yi kuskure ba har da ni Safiyya, tun ranar da na kai yarinyar nan gidan

ta ban kuma zuwa na duba ta ba, hasalima so daya kawai na ganta a tsayin shekara ba wata biyu na auren su shima nan gidan suka zo, Allah ya sani ban rike ta akan komai ba haka ban yi da niyya ba, na bar su ne dan su sarara, na kuma basu space din da zasu fahimci juna ne, ashe ban sani ba hakan kuskure ne babba, da ace ina zuwa duba ta da na ga cikin jikin ta, amma shi ma da laifin sa, me yasa baze fada mana tana da ciki ba, wannan ai raini ne babba".

Ita dai Aunty Luba shiru tayi musu, a ranta tace gwara ta kyale su su gane kuskuren su, musamman ma Mama dan in ta rantse ba zata yi kaffara ba hukuncin ta se ya fi na kowa jijjiga Aimah, kasancewar shakuwar su da ita ba ta wasa bace.

Se da ta ga abin nasu ba me karewa bane ana ta koke koke da nadame nadame sannan ta mike

"Ni dai zan koma asibitin dan babu komai na bukata a can, se kun taho".

"Wane irin banzar magana ce wani se mun taho, dama mun san asibitin ne da zaki fadi haka, ni jira mu muje jor, tashi Safiyya".

Tashi Mama tayi har lokacin tana sharar hawaye, Hajiya Yayah ta daga waya ta kira Baba sedai bata ce masa ga abinda ke faruwa ba ta dai ce zata asibiti dubiya, be ja ba yace a dawo lafiya.

Haka suka dunguma cikin motar Aunty Luba, a hanya ta tsaya ta siya fruits da yawa se kayan maltina, drinks da ruwa, se kuma sabon tea flask me Dan girma, kayan tea da sauran su, se kuma ta shiga baby's world, wani katon shagon saida kayan yara ta siya kayan babies da yawa shima, unisex da kuma kowa na gender din shi, ta siya feeder, zam zam , dabino da milk din babies wato formula.

Kusan cika booth tayi da kaya sannan ta karasa da su asibitin, se da ta nemi taimakon cleaners suka kwashi kayan zuwa dakin da take bayan ta fada musu room number din.

Su Hajiya Yayah tuni suka yi gaba tun lokacin da suka ji room number din, sedai sun kasa shiga saboda guilty conscience, har Aunty Luba ta karaso ta tadda su, da mamaki ta kalle su se kuma ta bude dakin ta shiga da sallama, Ya Masdooq dake zaune bakin gadon ta gefen da yaran suke ya dago ya amsa mata, se kuma suka biyo bayan ta jiki a sabule.

Da sauri ya mike yana musu sannu da zuwa, suka amsa shi cikin jin kunya duk da shi be nuna komai ba, dukan su hannu na rawa suka dauki baby daya daya, kowacce ta tsurawa na hannun ta ido cikin tasbih ga Allah, Mama ta kasa shiru ta dago ta kalli Hajiya Yayah tace

"Yayah dubi ki gani, kamar Aimah tana jaririya ko?, Banbancin su farin fatar Masdooq da suka dauko".

Ta fada bakin ta a washe da farin ciki, so da kaunar ƴaƴan na ratsa ta

"Ai kamar tayi kaki ta tofar, haske kawai zasu nuna mata, se gashin kai da Aimah zata dan fi baby girl din nan".

"Ba ni ita Yayah, karbi sabon megidan ki".

Mama ta fada tana mikawa Hajiya Yayah baby boy din ita kuma ta karbi girl din, kamar yadda Hajiya Yayah ta fada kuwa haka ne, duhun sumar ka kawai Aimah zata fi yarinyar, se take jin kamar Aimahn ta ce a yarinta, ta kankame yarinyar kamar ance mata za'a kwace ta, kwallar nadama, danasani da tarin kaunar yaran na sauka bisa kuncin ta.

"Allah ya raya su ya musu albarka, ita kuma Allah ya kara mata lafiya ya bata lafiyar shayarwa".

Hajiya Yayah tayi addu'ar tana shafa kan Babyn dake hannun ta, itama tana jin kaunar su a ranta kwatankwacin kaunar da take wa mahaifi da mahaifiyar su,  se kuma ta dubi Masdooq

"Ta farka ne tun bayan da aka yi aikin?".

"A'ah, ai ba'a dade ba, be fi awa daya ba, likita kuma yace da bukatar ta samu Hutu sosai".

"To Allah ya tashe ta lafiya".
Da Amin suka amsa se Masdooq ya dubi Aunty Luba yana cewa

"Kayan da aka shigo da su na san ke kika siyo ko?, Nawa ne?".

Ta girgiza kai tana dashare baki

"Wannan welcome din twins kenan daga Mommyn su, na sani cewa zaka yi zaka biya, to ba kai ko Aimah na wa ba, ƴan biyu na nayi wa".

Se yayi yar dariyar da tun daga Dady zuwa yanzu bata taɓa barin bakin sa ba yace

"Kin fadawa su Salman?".

"Oops, kaga na manta, bari na kira nuna musu albishir, kuma dukkan su se sun bani ladan wannan kyakkyawan surprise din".

Daga haka ta zaro wayar ta daga handbag din ya da ta dauko a dakin Aimah ta shiga kiran su, Ya Salman ta fara kira, sedai be yi picking ba so se ta masa text kawai ta fita zuwa number Ya Najeeb.

Lokacin yana zaune a falon sa yana kallon ball, wasa ake yi da club ɗin sa da manyan abokan dabin su, wato real Madrid and Barcelona, gaba daya hankalin sa ya dauku da fatan club ɗin sa

su doke opponent din, ganin hankalin sa ya karkata gaba daya ne ma yasa Aunty lateefa matar sa tashi ta ka bedroom tana gyaran kayan ta, dan ta san ko ta zauna ba acknowledging din ta ze yi ba.

Cikin haka ne kiran wayar Aunty Luba ya shigo, se kawai ya danna reject dan baya san duk wani abun da ze dauki hankalin sa har ayi wani abu be sani ba, a karo na biyu kiran ya kuma shigowa ya sake rejecting, yana kokarin sa wayar a airplane mode ne kiran ya kuma shigowa for the third time, duk da be so ba haka ya daga, ze fada ta da fada ta riga shi da fadin

"Ya Najeeb ina ta kiran ka na maka albishir kana rejecting call na, duk da surprise ne ba zan tsaya ja ba, Aimah ta haihu muna hospital, an samu twins".

Se ga Ya Najeeb da mikewa tsaye instead of kishingiden da yake

"Aimah.. Aimah..wace Aimahn?".

"Nu'aimah dai ta mu Yaya, kai ma kayi mamaki ko?, Gaskiya ne fa dan gamu nan a unicare hospital, mun samu macw da namij".

Se ya zabure tsaye,

"Wai kina nufin Aimah ta, Aimah tawa fa ta haihu, to taya Ke kika sani?".

"It's a long story Yaya, bari na sanar da Ahmad, bye".

Daga haka ta katse wayar ta bar shi da waya a kunne baki sake, da sauri kuma ya shiga bedroom yana fadin

"Wai kin ji Nu'aimah ta haihu, an fada Miki?".

Lateefa dake jera kaya ta dakatar ya dago ta dube shi, duba irin na tsanaki se kuma tace

"Wace Aimahn?".

"AIMAH tawa fa, kuma yan biyu wai, i was shocked, very shocked".

"To ai ba abin mamaki bane tun da saura wata biyu ta shekara a gidan, ko kuwa kuna tunanin ba ƴaƴan mijin ta bane?".

Zaro ido Najeeb yayi yana jin wani irin ɓacin rai da fusata a kan maganar lateefa

"Are you in your sense lateefa, ko kun fara hauka ne, how dare you zaki danganta yar uwa ta da banzar magana irin wannan?".

Lateefa ta dago ta dube shi ta sakar masa mutmushi

"Oh, ai na zata ita din yanzu ba yar uwar ku nace, tun da iya sani na kun riga kun zare ta a cikin ku ko, then why the anger?".

Se fa ya ja wani mugun tsaki me tsayi kafin cikin fusata ya shiga nuna ta da yatsa

"Ko ma meye tsakanin mu ne ina ruwan ki da zaki kawo wannan banzar maganar?, Ko an gaya miki ban san darajar yan uwa na bane?, For the first and last time kar ki kuma danganta yan uwa na da mummunar kalma, if not wallahi ba zata ma na dadi ba ni dake, bullshit kawai".

Yana fada ya fice daga dakin yana banging mata door din, ta daga kafadu alamun oho dai fuskar ta dauke da murmushi, seda ta tabbatar ya wuce daga wajejen bedrooms din ta dauko wayar ta ta shiga kiran Aunty Luba, se taji line busy dan haka ta aje, after 3 mins ta sake kira, se gashi ringing daya ta daga, cikin farin ciki da fara'a tayi wa Aunty Luba Barka kana ta ce ayi extending congratulations din ta to Masdooq, se Aunty Luba ta bashi wayar saying ai gashi a kusa.

Cikin mutunta juna suka gaisa da Masdooq tayi masa Barka ya amsa kana suka yi sallama ya maida wa Aunty Luba wayar ta.

Ya Farooq da shi ne Aunty Luba ta kira lokacin da lateefa taji wayar ta busy be kara minti talatin ba ya karasa, yana shigowa idanun sa suka fada cikin na Masdooq, se ya tafi da sauri suka rungume juna suna congratulating themselves, after like two mins sannan ya matsa wajen babies din, tun da ya dauke su yake santi kamar ya hadiye, fadi yake dole ma Masdooq ya nishi baby girl din, shi dai dariya yake masa kawai a ran sa yana fadin ai ko Hajiya Yayah da Mama ba ze iya bawa wannan baby girl din ba, replica din Aimahn sa ce, no dole shi zai raine ta, cikin so da kauna tare da tarbiyya me kyau, ya sani zata na ɗebe masa kewar Maman ta musamman in ya tuna daga gare ta take.

Haka Farooq ma ya tare, ya kira matar sa saddiqa ya fada mata, itama kuwa da hanzarin ta ta karasa, suna mugun son yara sedai har yanzu shekaru biyu da auren su Allah be basu ba, yanzu kuwa da suka ga wadannan jin su suke kamar nasu, shi ya kama macen ya kankame ita kuma ta dauke namijin, Hajiya Yayah da Mama na gefe suna kallon su se murmuhsin farin ciki kawai suke.

Can ajima se ga Ya Najeeb da lateefa da da kyar ya jira ta yana ta kumbure kumbure, ita dariya ma ya bata, ashe dai suna son Aimahn suka banzatar da ita, tana sane ta fadi abinda ta fada dan bata masa rai dan itama ya bata mata yadda ya share ta ya tafi kallon ball.

Ya Salman da yayi receiving text din Aunty Luba lately se gashi wajejen magrib, be yarda ba se

da aka dora masa yan biyun duka a hannun sa a tare, ya kuma dubi Aimah dake bacci har lokacin bata farka ba, kan ta kan cinyar Masdooq da ya tare a dakin dan ban da Sallah ba abinda ke tayar da shi, gaba daya ya manta da rayuwar wata Sa'adah a gida, Bama ita kadai ba komai ma ya manta a lokacin ban da Aimah da Babies din sa, se wadanda ke gaban sa, su kuma ganin su ke sa shi tuna su.................✍️.

To ga fa family gaba daya ya hadu a dakin Aimah, kowa ya garzayo, ya kuke tunani zata kasance, Mee ze faru in Aimah ta farka ta gan su a tare da ita?, Shin zata yi farin cikin addu'ar ta ta karbu ne ko kuwa akasin haka???

Vote
Comment
Share.

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 039 [ 10/07/2024 8:27pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Oummey
Free book!!!

Allah yayi wa ƴar uwar mu marubuciya Rahma Rufa'i na lele rasuwa, dan Allah yan uwa a sa ta cikin addu'o'in ku da bakunan ku masu albarka, Allah ya jikanta da Rahma yasa ta huta, Allah yasa aljanna ce makomar ta, mu ma wallahi yasaa mu yi kyakkyawan karshe yasa mu cika da imani, Ameen.

*BOJUWA HERBAL'S & SCENTS*
*Suna kawo Saiwowin sanyi da suke dagargaza sanyin mara da na jijiya.*
*Haka nan suna kawo Saiwowi daban daban daga Chad da Sudan, kuma marasa illah*
*Saiwowin tsumi*
*Saiwowin dahuwar kaza/tattabaru*
*Saiwowin matsi gangariya*
*Original gadalin mata*
*Ƴaƴan gadali na asali*
*Original gumba*
*Tsumin Saiwowi*
*Tsumin kwakwa da Dabino*
*Igiyar alkairi*
*Zumar goran tula*
*Hakkin daka na musamman na asali*
*Bayan haka suna dafa kazar amare da masu jego da ma uwayen gida*.
*Akwai bridal package*
*Mai jego package*
*Ƴar gata package*.
*Dukkan kayan kuma available ne for pickup or immediate delivery.*
*A Kano nake amma kuma nationwide delivery ne*
*Ku tuntubi Surayya Halin yau a wannan lambar dan samun naku cikin musulmin farashi*
*08032773332*
*Iyah Basiru na gaisuwa*😅

Ouummey 039

Page 3️⃣9️⃣

____________________Suna nan zaune likita ya shigo yace musu ba'a san hayaniya, is either suyi shiru ko su fito waje, haka suka tsuke bakin su dan kam kowa baya san fita ya bar dakin.

Se da magrib tukuna mazan suka tafi sallah, matan kuma suka yi a daki, se kuma a wajen nurse din dazu suka ari pray mat dan Aunty Luba bata hado da shi ba, su Ya Salman na dawowa da suka ji haka Ya Najeeb ya bawa Aunty Luba key din motar sa yace taje akwai pray mat biyu da ya aje a ciki saboda sallan juma'a ta dauko su, haka kuwa aka yi, ta maida wa nurse tata ta mata godiya.

Aunty Luba ce ta koma gida saboda yara da se da Hajiya Yayah ta tuna mata ta bar su a school ko daukar su ba'a je ba, Allah ma yasa se six o'clock ake tashi, tana zuwa kuwa ta tarar driver ya aje su gidan Maman Ilham, ta shiga ta musu godiya ta kwaso su, tayi girki ta musu wanka ta canja musu kaya ta sake kwasar su zuwa hospital.

Se karfe tara Hajiya Yayah ta kora su, da kyar Aunty Luba ta hakura dan cewa tayi ita zata kwana a wajen ta, shi kam me gayya me aiki yana jin su yayi fumfurun fus abin sa, be ce a zauna ba be ce kar a zauna ba hasalima be nuna ya ji su ba.

Aka gama Ya Salman ya tarkata Aunty Luba da yara suka wuce, ya Najeeb da Aunty lateefa, Ya Farooq da Aunty saddiqa, Ya Ahmad dama be karaso ba saboda ba'a garin yake aiki ba.

Ɗaki ya rage daga Hajiya Yayah se Mama da Ya Masdooq, Hajiya Yayah ta dago zata yi magana kenan kira ya shigo wayar ta, ta daga ta duba se ta saki murmushi ta daga tare da yin sallama, aka amsa mata daga can tare da tambayar ta inda take, ta bada amsa da asibiti.

Mama ta kalle ta da tambayar ta waye, ƙasa ƙasa tace mata Baba ne.

"Wai waye a asibitin da kika kai dare har haka a can, ko kuwa kin manta da ni ne?".

"Ina ni ina mantawa da wannan dattijon arzikin, sirikar ka kuma yar ka ce Allah ya sauke lafiya".

Dan shiru yayi se kuma yace

"Sa'adah na da ciki ne dama?".

Hajiya Yayah ta girgiza kai kamar yana ganin ta

"Ba ita ba, dayar yar uwar ta ta ce".

Unbelievably Baba yace

"Kina nufin Nu'aimah ce ta haihu?".

Seda ta saki mutmushin da yaji shi ta cikin wayar
"ita dai Baban Aimah, yau Allah yayi ka samu jikoki daga gare ta".

Dake a da can takan kira shi da baban Aimah saboda kaunar dake tsakanin su.

Se Baba ya kara rike wayar da kyau

"Jikoki?, Biyu ne kenan ko uku ta haifa?".

"Biyu ne, aboki da mata".

"Kai Masha Allah, Masha Allah, alhamdulillah, wane asibiti ne, ya sunan sa?".

Baba ya tambaya cikin shauki, ba bata lokaci Hajiya Yayah ta sanar masa, yace gashi nan zuwa.

Tana aje wayar ta dubi Masdooq da ya jingina da jikin gadon ya lumshe idanun sa,

"Ya kamata kaje gida kayi wanka ka huta, kaga yau ka dawo daga tafiya akwai gajiya ga kuma Sa'adah, Safiyya zata zauna da Nu'aimah".

A hankali ya bude idanun sa sanin da shi take tun da babu wani namiji a dakin se shi, da gaske a gajiye yake, Sa'adah kuma ya manta da ita wallahi se yanzu da Hajiya Yayah ta ambaci sunan ta, amma duk da haka ba inda ze je ya kwana bayan matar sa da ƴaƴan sa na kwance a nan wajen daban, base iya ba dan ko ya tafi ma hankalin sa ba kwantawa ze yi ba, Hutu kuma ba ze taba samuwa ba kwanciyar hankali ba.

"No Hajiya, zan kwana wajen ta, gobe in kuka zo se in koma gidan".

Hajiya Yayah ta hade rai ganin ze kawo mata wargi, dama ita ko nonsense ce

"Kai bana son shashanci, nace ka tashi ka tafi ko, in ka zauna a nan ita kuma Sa'adahn ka bar ta ita kadai saboda rashin hankali?, Ka tashi ko se ranka ya ɓaci?".

Nan da nan idanun sa suka marairaice, abinda ba halin sa ba yake kokarin yi wato musu da iyayen sa, sedai ba yadda ze yi, baze iya bane

"Please Mama ki bawa Hajiya Yayah hakuri, Allah ko na koma gidan hankali na baze taba kwanciya ba, kin ji Mama na?".

Mama ta dube shi da mutmushi akan lips din ta wanda yake direct daga zuciyar ta, tun da can tana son Masdooq sosai saboda nutsuwar sa, biyayyar sa da kuma uwa uba ya dauke ta mahaifiya ne iya sa shi yayi me hana shi ya hanu, ga kuma ƙari ya so gudan jinin ta da ta fi so fiye da duk ƴaƴan ta, Allah ya sani tana son zama wajen Aimah, sedai zata hakura ko dan Masdooq, dama tana cike da fargabar yadda Aimah zata kalle ta in ta farka din, so se ta dubi Hajiya Yayah

"Ayi masa hakuri ya kwana wajen matar sa Yayah, ita kuma daughter Sa'adah se in tafi da ita gida mu kwana abin mu".

Hararar ta Hajiya Yayah tayi se suka hade hannaye waje ɗaya alamar pleading, se da ta sake

hararar su gaba daya sannan tace

"Ni babu ruwa na fa, ya dai san waye baban sa ko, to ku kuka sani".

Dariya yayi dan yau fa kome ze faru ba ze kwana a gida ba, amma dai yana bukatar wanka, so kafin Baba yazo su kuma su yafi ze je yayi wanka ya canja kaya, se ya taho da abin shimfida ma.

Ya tashi bayan ya sauke kan Aimah a hankali kamar wanda ke aje kwai yace

"Bari naje gida nayi wanka na taho da kayan shimfida".

Cikin murmushi Mama ta masa adawo lafiya, ita kuwa Hajiya Yayah kau da kai tayi, har ranta tana farin cikin soyayyar Masdooq ga Aimah, sedai akan wannan maganar kwanan ba kowa ne ze fahimci Masdooq ba, shiyasa tace ya koma ya kwana a gida tun da yana da wata matar, amma tun da shi da babar sa sun yi insisting ai shikenan, in zasu wuce gida sa biya ta tafi da Sa'adah, ba zata bar Mama ta tafi da ita ba kar ace ta cuce ta ta bar miji a wajen yar ta ita kuma ta tafi da ita.

Da haka ya fice su kuma suka cigaba da hirar su ƙasa ƙasa har Baba ya karaso, bakin sa ya kasa rufuwa saboda murna, se daukar Babies din yake yi, ya dauki wannan ya aje ya dauki wannan, ya musu kiran sallah shima kana ya shiga yi tofa musu addu'o'in tsari a gaba daya jikin su, a karshe kuma ya rungume baby girl din yana tsokanar Hajiya Yayah da cewa shi fa yayi sabuwar mata.

Masdooq ya kashe motar tare da fitowa a gajiye, duk da a nutse yake be yi loosing coolness din sa ba amma kana kallan idanun sa zaka hango tsantsar gajiya da bacci, a sannu yake taku har ya shiga gidan.

Da Sa'adah ya fara cin karo zaune cikin two sitter, gaba daya she looks disturbed, wannan gayun da gyaran duk babu shi, yadda ta saba tayi masa kwalliya ta gyara gida yau duk be samu ba, shi da ya lura sosai ma se ya ga kamar tayi kuka, dan idanun ta sun yi jajir haka kasan su ya kumbura.

Ya zauna cikin seat a hankali yana fadin "wasshh".

Sa'adah na zaune har lokacin bata ce masa komai ba, ba sannu da zuwa ba kawo ruwa ba komai, tana dai zaune tana bin shi da ido.

Se da ya dan huta kana ya dube ta

"Sannu da gida wife".

Bata amsa ba ta cigaba dai da kallon sa, hakan look very weird gare shi, se ya maida hankali gaba daya kan ta yace

"Is everything ok?".

A dishe muryar ta ta fito, can kasa tattare kuma da wani irin daci da har shi kan sa yana iya jin sa cikin sauti da yanayin fitar kalaman ta

"Da gaske ne ta haihu?".

Ya gyada mata kai yana nazartar ta

"Kuma yan biyun da aka ce?".

Yanzu ma kai ya gyada mata

"Duka mata?".

Se yanzu ya girgiza mata kai, yace

"Mace da namiji".

Se kawai ji yayi Sa'adah ta rushe da kuka, kuka me amsa sunan kuka ba wai kukan wasa ba, yayi tunanin kukan farin ciki ne se da ya lura sosai ya lura sam babu abinda ya alakanta kukan ya da na farin ciki, in ya kula da kyau kukan da take yi kamar tana fitar da wani daci ne da ya dankare a cikin cikin ta da kirjin ta

"Shikenan ta kwashe komai, ta samu komai ta raba ni da komai, ni na tashi a tutar babu, bani ga tsuntsu bani ga tarko, innalillahi wa inna ilaihi rajiun".

Tsai yayi yana duban ya, yana neman fassara kalaman ta, sedai ya kasa ganewa dan haka ya basar ya tashi ya koma seat din da take ya riko ta zuwa jikin sa yana lallashin ta

"Is okay please, tana cikin koshin lafiya fa, haka ma yaran, i know you're worried ko wani abu ya same su ko, to ba abinda ya faru kin ji".

Ya sani ba kukan da take yi kenan ba, se dai ya zabi ya nuna be gane ba, yana ganin girman Sa'adah, baya san tayi abinda ze taba wannan kimar tata da yake gani.

"Ba na kukan ko ta na lafiya ko bata lafiya, bana kukan ƴaƴan da ta haifa lafiyayyu ne ko akasin haka, ina kukan makoma ta a gidan nan ne, a wajen ka da ka riga kasan matsala ta, ga shi yanzu ka samu me magance maka wannan matsalar, ni kuma na sani se yadda Allah yayi dani a gidan nan".

Ta fada cikin rishin kuka, wanda suke tahowa tun daga kasan ran ta

"Me ye kike fada haka Sa'adah?, Kin san tuntuni na san matsalar taki, na kuma san yadda zan magance ta amma na zabi zama dake a haka, na zabi binne matsalar a cikin raina batare da na sanar da ko fa iyaye na ba, duk dan na kwantar miki da hankali ki yadda a kowane yanayi zan rayu dake, me yasa yanzu kike taso da maganar abinda ya wuce?, Me yasa kike neman sa min damuwa a daidai lokacin da ya kamata na kasance cikin farin ciki?, Shin ban yi adalcin da na cancanci Barka daga gare ki ba?".

"Duk wannan a da ne, yanzu kam da maganin matsalar ya zo hannun ka na tabbatar ba zaka sake adalci a gare ni ba, a da ma rashin uwa ne yasa kayi uwar daki, yanzu tun da ga uwa ta zo ita uwar daki me ye amfanin ta?, Shi yasa gaba daya ba na kaunar ta cikin rayuwar mu, na sani shigowar ta tsakanin mu na nufin tozarci gare ni da tagayyara, shoyasa hankali na ya tashi tuntuni, ina kokarin fin karfin zuciya ta ne gudun yin abinda zan dawo ina danasani, amma yanzu kam komai ya kare min, ba ni da sauran madafa ni Sa'adatu".

Ya ma rasa abin cewa gare ta, se ya zuba mata ido yana kallo kawai, daga karshe ya hadiye rashin jin dadin sa ya shiga rarrashin ta, sedai duk yadda yaso taki yin shiru, daga karshe se ya canja salon lallashin amma duk ta tankwabe, se kawai ya tashi ya wuce bedroom leaving her a falon, to Mee kuma ze yi mata, shi kam ya yi iya kokarin sa amma taki, ya ze yi in be kyale ta ba.

Wanka yayi da ruwan dumi ya saka kaya marasa nauyi na bacci, ya janyo jakar da yake amfani da su in tafiya within kasar ne ya zuba kaya marasa nauyi na zaman gida da na bacci, kana ya dauki bargo manya biyu fa abin rufa marasa nauyi guda biyu tun da zafi ake, komai da ze bukata se da ya haɗa shi waje ɗaya, ya janyo trolley ya zuba ragowar kayan da yake bukata da bargunan da abin rufan, a nan inda ya bar ta ya tadda ta, ta dena kukan ta zuba tagumi idanu sun mata jajir.

Tana ganin fitowar sa ta mike tsaye tana kallon sa cikin rashin fahimta, ya aje trolley din ya karasa gare ta

"Zan je na koma wajen su a asibiti, akwai abinda kuke bukata?".

"Ban gane zaka koma wajen su ba, yau fa ka dawo daga tafiya, and throughout kana wajen ta, yanzu kuma ka dawo ka sake ce min zaka koma?".

"Ko na zauna a nan hankali na baze kwanta ba Sa'adah, har na taho bata farka daga baccin allurar da aka yi mata ba, taya zan iya zuwa gida na kwanta in bar yarana a can kuma hankali na ya kwanta?".

"Tun yanzu ka fara?, Ba ma zaka bari zuwa gaba ba, tun yanzu?".

Ɗan bata rai yayi dan kan sa har ya fara ciwo

"Ban fahimci ma'anar ki na tun yanzu ba, me ye aka yi yanzu din?".

"Eh ma'ana ta gashi nan a fili, tun yanzu daga haihuwar ta har ka fara nuna banbanci, dama har yanzu kana son ta kake min pretending you don't, me yasa, nace me yasa Masdooq?".

Shi kam yau be san abinda ya shiga kan Sa'adah take misbehave haka ba, be san wannan side din nata ba, dan abin da take yi yanzu ko lokacin da ya auri Aimah karo na biyu bata yi ba...............✍️.

Vote
Comment
Share fisabilillah

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 040 [ 10/07/2024 8:31pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Oummey
Free book!!!

*BOJUWA HERBAL'S & SCENTS*
*Suna kawo Saiwowin sanyi da suke dagargaza sanyin mara da na jijiya.*
*Haka nan suna kawo Saiwowi daban daban daga Chad da Sudan, kuma marasa illah*
*Saiwowin tsumi*
*Saiwowin dahuwar kaza/tattabaru*

*Saiwowin matsi gangariya*
*Original gadalin mata*
*Ƴaƴan gadali na asali*
*Original gumba*
*Tsumin Saiwowi*
*Tsumin kwakwa da Dabino*
*Igiyar alkairi*
*Zumar goran tula*
*Hakkin daka na musamman na asali*
*Bayan haka suna dafa kazar amare da masu jego da ma uwayen gida*.
*Akwai bridal package*
*Mai jego package*
*Ƴar gata package*.
*Dukkan kayan kuma available ne for pickup or immediate delivery.*
*A Kano nake amma kuma nationwide delivery ne*
*Ku tuntubi Surayya Halin yau a wannan lambar dan samun naku cikin musulmin farashi*
*08032773332*
*Iyah Basiru na gaisuwa*😅

Ouummey 040

Page 40

__________________"Na taba ce miki na daina son ta, ko na taba fada miki yanzu bana son Aimah?, Me yasa kike neman complicating issues ne?".

Kalaman sun doke ta matuka, sun kuma shige ta yadda bata taɓa zata ba, bakin ta ya shiga rawa kamar wadda aka tsoma a kankara

"Kana son ta ke nufi?, So kake kace min kana son ta har yanzu?".

"Ban taba ce miki bana san Aimah ba balle ki titsiye ni da maganganu haka, this is unlike you Sa'adah, na roki da Allah kar ki canja, kar ki kawo matsala cikin rayuwar auren mu".

Gaba daya hankalin ta baya kan pleading din da yake mata, abu daya kunnen ya ya jiye mata kuma akan shi take magana dan haka ta dora

"Despite a that happened in the past?, All the heartbreak, all the denial, amma kake son ta har yanzu?".

Se da ya sha mur ganin tana neman kawo masa wata maganar banza

"Koma me ya faru a bayan is none of your business, Abu ne da ya shafe ni ni da Aimah, babu abinda ya shafe ki balle ya kawo sunan ki ciki, and am warning you for the first and last time, kar ki sake, kar ki ƙara, kar ki kuma yi min katsalandan cikin rayuwa ta, in zaki yi magana da ni kiyi ta abinda ya shafe ni ni dake amma ba ni da Aimah ba, na Shata miki layi ina kuma umartar ki da ki kiyaye tsallake shi, in ba haka ba tabbas zaki kuka da idanun ki".

Daga haka ya wuce ya dauki trolley din sa ya ja ya fice fuuuu, ta bata masa rai, wallahi ta bata masa rai, be taba zaton haka daga gare ta ba, a yadda yake ganin ta ya kuma dauke ta gaba daya ta baro wallahi.

Ran sa a bace ya saka kayan a backseat ya koma gaba ya ja motar ya fice daga gidan, bayan ya gargadi gateman kan ya saka ido sosai a kuma kula sosai.

Yana daukar hanyar asibitin ya dinga jin wani farin ciki na tahowa from nowhere yana washe duk wani ɓacin ran da Sa'adah ta cusa masa, ya dinga jin dokin ya karasa ya yi tozali da fuskar ta da ta cute babies din sa.

Yana yin parking ya nemo cleaners suka taya shi kwasar kayan  zuwa dakin, yana shiga su Hajiya Yayah suka mike tana ta mishi fadan ya bar su a daki bayan ya san dare yayi, har sun kai bakin kofa ya dakatar da su da fadin

"Ehm ina ganin ba se an je an dauki Sa'adah ba, na yi magana da ita tace zata kwana a gida kawai, kuma na wa gateman magana kan ya kula, so ina ganin ba damuwa insha Allah".

"Ko ba tace ba ai ba inda zata je daukar ta, ina tun da ai kana yin tafiya kuma ta zauna ita kadai ko, bana san shashanci fa".

Baba ya amsa yana ficewa daga dakin, su Mama suak rufa masa baya.

Ba su kai Mama gidan ta ba, gidan su suka wuce da ita dan dare yayi, dana kuma ita kadai ce a ciki se matar gateman da shi da suke zaune a boys quarter.

Sa'adah baki sake ta bi Masdooq da kallo har ya fice, gaba daya se ta sake jin komai ya rushe mata, komai ya kare mata, se ta sake rushewa da kuka tana kiran ta shiga uku, a daren ta kira mahaifiyar ta Aunty Hauwa ta sanar mata, ta lallashe ta da kyar kan zata kira Baba da safe, yanzu dare yayi amma baza ta yarda da wannan rashin adalcin ba.

Ranar saboda ɗorawa kai masifa a nan zaune a falo ta kwana, da kyar ta gyangyada, amma bacci dai me sunan bacci ranar Sa'adah bata samu yin shi ba.

Ana yin sallar asuba ta tashi ta yi ta dawo falo ta zauna ta zuba wa kofa idanu, so take ta ga shigowar sa da kuma yanayin da ze shigo a ciki, ita gaba daya ma kan ta ya cushe, yaushe har Aimah da Masdooq din suka samu privacyn yin wani abu da ze samar da ciki?, Tun jiya take tunanin nan amma har yanzu ta kasa hango mata yadda lamarin ya faru.

To ko dai dama ita suke rainawa hankali komai lafiya yake tsakanin su?, Amma kuma ace har da kowa da kowa aka yi shirin?, Kai ba haka bane, akwai dai wani abu, amma ta ya zata gano komai?!.

Tana zaune har karfe bakwai amma ba alamar Masdooq balle shi kan sa, se kawai ta shiga yin hawaye, rashin adalci ze mata kenan, jiya ya tafi ya kwana da matar sa amma yaki zuwa ya duba ta har yanzu?, Kenan ita tata ta kare ko me?, Dama saboda rashin matar sa ya karbe ta, yanzu kuma da gata yaya kenan zata kasance??

Da kyar ta daga jikin ta da ya mata nauyi ta shiga daki, ko da ta kalli kan ta a madubi da sauri ta kautar da kan ta saboda yadda ta koma, se kuma ta shiga tunanin a haka ta tsaya gaban Masdooq jiya?, Hasbunallahu, ya aka yi ta kwafsa haka?.

Tun da indai ta san zata hadu da shi se ta gyara ta ɗan yi makeup, ba dan komai ba se dan sanin wace matar sa wajen kyau, in bata gyara ta nutsu ba ta tabbatar ba ze taba kallan ta ba, yo in ba ƙaddara ba me mata kamar Aimah me ze tafi kalla wajen wasu matan?.

Ko ita da take mace ta kan kasa dauke ido kan Aimah, ba wai kwalliya ba wuyar ta tayi wanka ta sa kaya ta fito, to ko hasidin iza hasada ba ze ce bata yi ba, balle kuma ta zauna ta tsara wannan kwalliyar tata me mai da ita kamar wata hurul een, ga jiki Masha Allah ko ina a cike bulbul, mace iya mace a sura da siga, ga kuma fuska, shiyasa tun da aka yi auren su bata taba yarda tsaya a gaban sa tsurar ta, se tayi kwalliya ko yaya, ta kuma nemi kayan gyaran jiki ta dinga yi, hankalin ta be kwanta ba se da taga jikin ta ya ciccike daidai gwargwado, se ta dakata ganin cikar na neman canja fasali.

Wanka ta shiga tana jawa Aimah Allah ya isa da ta sa yau daya Masdooq ya ganta a ita din ta, maybe ma yana can yana kakabin dama haka take.

Shi kuwa Masdooq shimfida yayi a sofar dake dakin, ya sake ninka bargo ya sa cikin karamin bed din da aka kwantar da yaran bayan ya dauke su, kana ya maida su bayan ya tofe su da addu'a ciki da bai, ya dade yana kallon su kamar ya hadiye, da kyar ya iya hakura ya mike ya koma wajen Aimah, itama yayi mata addu'a ya shafa mata a fuskar ta zuwa wuyan sa, itama haka ya bata lokaci wajen kare mata kallo, seda dayan dare ta buga sannan ya tashi ya koma sofar bayan ya kulle dakin ya kuma tofe ko ina da addu'a.

Without hesitation bacci ya dauke shi dan ya gaji matuka, yana bukatar baccin dan be samu yi ba tun yana can tafiya saboda hankalin sa da be kwanta ba.

Kiran sallar asuba a masallacin new ya farkar da shi, ya tashi ya zauna zuwa lokacin da bacci ya sake shi, ya juya wuyan sa da yake jin ya kage masa saboda yanayin kwanciyar da yayi dan kujerar tayi masa kadan kasancewar shi dogo sosai, se ya tashi zuwa toilet din, ya tsaya ya kare masa kallo, a wanke yake amma hankalin sa be kwanta ba, se ya kwashi toilet wash ya shiga sake wankewa, tas ya wanke shi sannan yayi wanka tare da alwala bayan ya ciro shower gel din sa da toothbrush din sa a jaka, yana fitowa ya shirya cikin jallabiya ruwan kasa ya shimfida sallaya ya tayar da nafiilfilun sa, cikin kowace sujjada yana romawa ƴaƴan sa rayuwa me albarka kan tafarkin gaskiya, haka kuma yana rokawa mahaifiyar su lafiya me dorewa da ikon kula da tarbiyyar su, kana ya dora da normal Du'as din sa.

Ana kiran sallar biyu ya fita zuwa masallacin cikin hospital din yayi jam'i, shima se da ya nemi nurse ya bar ta wajen su, a gurguje yayi tasbih din sa ya taho dakin yana tafe yana azkhars din sa.

Hankalin sa be kwanta ba se da ya gan shi a gaban su, ya dudduba su duka ya tabbatar lafiya sannan ya zauna, kamar jira kuwa boy din ya shiga kuka cikin yar karamar muryar sa ta jarirai, ya dan zaro ido awkwardly, shi fa ya ma manta jarirai na kuka wallahi, dan tun haihuwar su zuwa yanzu so biyu kadai sukai kuka, shima jiya ne lokacin su Hajiya Yayah da Luba na nan, su suka kula da su, amma kamar ya lura da ruwan zam zam ta haɗa da dabino ta zuba a feeder ta basu, se ya tashi da sauri zuwa inda aka aje feeder din ya dauko, ya zo ya dauki baby boy din se kuma ya rasa ta yadda ze fara, cikin ikon Allah se ga nurse ta shigo duba Aimah, fa sauri ya kira ta yana sauke ajiyar zuciya, ita ta karbi Babyn ta bashi ruwan, ta dauki macen da itama ta farka amma bata kuka ta bata, kana ta ce zata turo wata tazo ta musu wanka.

Haka kuwa aka yi, ta turo another nurse ta musu wanka aka shirya su cikin kayan su iri daya unisex, sun yi kyau se tashin kanshin turare suke yi, kana cleaners suka shigo suka share dakin nurse din ta sa masa turare, se da aka gama komai hankalin sa ya kwanta ya sauke ajiyar zuciya tare da yiwa nurse din Godiya.

Ashe dai kula da Babyn ba sauki gare shi ba kenan, yanzu if not nurses din nan sun taimaka da ya ze yi, lallai ko baya so dole ya bari mace ta zauna da ita tun da shi ba sanin komai yayi ba.

Bakin gadon babies din ya sa kujera ya zauna ya rike mitsi mitsin hannayen su yana kallon su, suma idanun su a bude tarwai suna kallon haske, ji yake kamar ya hadiye wadannan kananun halittu.

Muslim Muna ya budo cikin wayar sa ya shiga karatun Alkur'ani daga zaunen da yake gaban su, kamar kuwa suna saurara suka yi zuba masa ido duk da ba shi da tabbacin shi ɗin suke kallo, a haka yayi Suratul bakrah, Ali Imran zuwa Nisa'i, lokacin gari ya fara haske sosai se yayi addu'a ya shafa.

Not long se ga Aunty Luba da katon food flask da tea flask, gaisawa kawai suka yi ta shiga hada masa tea, ta zuba masa pepper soup din cat fish, ta haɗa masa da yam balls ta aje masa a gaban sa.

"Ya Masdooq ga breakfast, na sani ba lallai murna ta bar ka ka ci abinci jiya ba, Please ka daure Kaci sosai, i did it purposely saboda kai".

Da Murmushin kauna yake bin Aunty Luba, shi dai dan uwa wato daban ne, ji bi yadda ta fahimci be ci abinci ba, ta kawo kuma ta ke roko da lallashin sa yaci, abinda ko Hajiya Yayah bata masa, sedai Mama, se ya gyada mata kai

"Thank you lubabatu, Allah ya albarkaci zuri'ar ki ya cigaba da zaunar da ku lafiya da mijin ki, I'm proud of you dear sis".

"Anything for you Yaya, ko ba komai ina taya Aimah kula da kai ne tun da yanzu ba zata iya ba".

Murmushin da ya saki yanzu har yafi na dazu, itama ta lura da haka, dama ka ta fada ne dan ta sake tabbatar da hucewar sa kan yar uwar ta, ya kuma tabbatar har gobe Masdooq ba ze taba daina son AIMAH ba in dai da numfashi a kirjin sa, never!.

Tana masa hirar kayan yara da ta gani a wajen wata kawarta har ya cinye komai da ta zuba masa, ta dube shi da kallon tausayi, da alama tun jiya da ya dawo be saka komai a cikin sa ba.

Karfe takwas da rabi su Hajiya Yayah suka karaso, a can gida kuma Aunty Hauwa ta kira Baba, suna can suna kashe nasu boss din ta waya.

Wuni guda dakin baya rabo da yan uwa da abokan arziki yan Barka, wannan ya shiga wannan ya fita, sedai har magrib Aimah bata farka ba, kai tun da aka kwantar da ita bata ko motsa ba se da nurses suka motsa ta, wannan ya tashi hankalin su Hajiya Yayah, kar Masdooq yaji labari.

Be tsaya sanyin jiki ba yayi office din likitan, se kuwa ga su sun dawo tare, aka tura ta aka fita da ita zuwa dakin gwaje gwaje, awa biyu kafin aka fito da ita, zuwa lokacin kam duk sun galabaita da zulumi, duka suka rufu akan likitan da tambayoyi, sefai be amsa ba ya bawa Masdooq umarnin biyo shi, ba Masdooq kadai ba har da su Ya Salman suka bishi, dan se da Ya Farooq ya tallafe shi saboda ya kasa bin likitan dan tsoron jin me ze ce........................✍️.

Vote
Comment
Share fisabilillah

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 041  [ 11/07/2024 8:26pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Ouummey
Free book!!!

Ouummey 041

Page 4️⃣1️⃣

___________________"Am sorry to say yar uwar ku na fama da depression".

Dr ya fada yana zuba musu ido dan ganin reaction din su, sedai kamar ba su fahimta na dan duka shi suke kallo ba ko kiftawa

"Aikin da aka mata was a successful one, so a ka'ida ya kamata ace ta farka tun jiya dan alluran baccin da aka mata ba me karfi nace, so ganin har yanzu bata farka ba yasa muka yi running mata series of tests, only to find out that tana fama da depression, and she's at second to the final stage, dan a binciken mu bata dade da shi ba, sedai ya shige ta da karfi ne, da alamar duk damuwar da ta assasa mata ciwon ba kara bace, se kuma shi wannan depression din ya hadu da ciwon nakuda yaso ya taba mata ƙwaƙwalwa, cikin ikon Allah hakan be faru ba amma ta shiga mini coma shiyasa har yau bata farka ba, after being examined by a neurologist ya sanar mana ba zata yi exceeding tomorrow ba zata farka Insha Allah, sedai ba wai dole ne se ta farka a goben ba, she's just suppose to be".

Tun da ya fara bayani Yaya Ahmad da ya karaso yau ya kwantar da kan sa kan table cikin

kunar rai, Ya Masdooq kuma ya sunkuyar da kai, the other three kuwa idanun su duk sun kada na tashin hankali.

Dr yayi rubutu a takarda ya tura musu gaban su

"These are the medications da muke bukata now, akwai bukatar a siyo su yanzu".

Hannu ya Masdooq ya mika ya dauki papern ya tashi ya fita daga dakin yana layin tashin hankali kamar wanda ya shawu, gaba daya kan sa ya kulle kwakwalwar sa ta kasa ma yin wani tunani, shi dai yana tafe ne kawai amma he's feeling empty and blank a kwakwalwar shi, yana tafe mutane na ta kallon shi saboda yadda yake hada hanya har ya kai pharmacy din asibitin ya siyo komai ya juyo.

A dakin da aka canja mata ya tadda su Ya Salman da su Hajiya Yayah duka sun rufu kan Aimah, Aunty Luba kuka take yi da kana gani zaka san a dame take, ya Ahmad ma sa'i da lokaci yana kai handkerchief ya share idanu haka ya Najeeb, Ya Farooq da Ya Salman kuwa idanun su sun yi jajir har fiye da na masu kukan, Hajiya Yayah da Mama ma kuka suke , duk taurin ran Hajiya Yayah da taji me likita ya fada se gata tana zubar hawaye riris, balle Mama da se da Ya Farooq ya tare ta saboda baya da tayi zata fadi.

Masdooq ya samu gefe daya ya aje ledar magungunan ya koma jikin bango ya kifa kan sa, only God knows what's going on in his mind, be san adadin lokacin da ya dauka a haka ba, shidai ya san an dafa shi tare da juyo da shi, daga nan shima se kwasar shi aka yi.

Wannan ya dada daga hankalin su, Mama se kuka take yi tana fadin duk ita ta ja komai, da bata yi fushi da Aimah ba da bata shiga damuwa har ta haddasa mata ciwo haka ba, hankalin su be yi kololuwar tashi ba se da yaran suka fara kuka, Dr yace a hada musu madara a basu, amma fir sun ki karbar madarar, anyi anyi sun ki karba, har allurai aka musu amma sun ki karba, daga karshe Dr yace sedai ayi pumping breast milk din into feeding bottles se a gwada basu a gani.

Aunty Luba ce tayi, aka wanke breast din, nurses suka yi sterilizing feeding bottles din sannan aka yi, cikin ikon Allah se kuwa gashi sun karba, yadda suke sha da sauri will define how hungry they're, ba wanda be share kwalla ba dan tausayin su se baban su dake kwance shima ana fama akan shi dan ciwon zuciyar sa ne ya tashi.

Daga Mama har Hajiya Yayah ranar a asibitin suka kwana, Ya Farooq ma ya kwana wajen Ya Masdooq.

Washegari Ya Masdooq ya farka sedai cikin ciwo yake, se Drs suka sake masa allurar bacci dan ya samu ya huta, bugun da zuciyar sa yake ya zarce ka'ida and abun na neman zama out of control, dole ana bukatar ya huta bugun zuciyar sa yayi stabilizing.

Maimakon farim ciki da suke ciki shekaranjiya se ga shi abu ya juye zuwa damuwa, kowa ka

gani zuciya ba dadi, Aunty Luba na zuwa ta dauki babies din tayi feeding duk da ba ma su nema ba, amma se gashi sun karba suna ta sha, hakan yayi showing ba wai basa jin yunwa bane kawai ba su da rigima ne, and a wannan part din they resemble Masdooq me, dan kuwa Aimah na yarinya akwai kuka da karadi.

Cikin zulumi suka wuni yau har Masdooq da yana farkawa daga baccin dolen da likitoci suka sa shi ya shiga masifar shi a kyale shi ba abinda ke damun sa kar a kuma dura masa wata allurar baccin, yadda ya dage dole yasa suka hakura amma sun ce ba zasu sallame shi ba se sun ga yadda jikin ya kaya, suna fita daga dakin ya rufa musu baya zuwa dakin da Aimah take, a can aka cigaba da jiran farkawar ta tare da shi.

Ba abinda ya fi fargaba saurin karar da mutum, dan har gara Masdooq ace yayi rashin lafiya, ragowar kuwa sun rame sun yi zuru zuru kamar su ma din majiyata ne, Sa'adah tazo lokacin da yana bacci, bata zauna ba ta musu jaje tace zata gida itama bata jin dadi.

Ganin yanayin ta yasa Hajiya Yayah tausaya mata dan da gaske ba wanda ze kalle ta be dauka bata da lafiya ba, se suka yi mata fatan sauki gaba daya, Mama ta sa Ahmad ya mai da ta gida.

Karfe shida na magrib Dr ya shigo ya sake duba ta ya fita, bayan ya musu bayanin in har ta wuce yau bata farka ba to akwai yiwuwar ta shiga cikakkiyar coma, in Kuma haka ya faru to tashin ta fa se sanda Allah ya rubuta, wannan ya sake dugunzuma hankalin su, gaba daya zuciyar su babu dadi, hankalin su kuma a tashe, zulumi da fargaba ke girma ya lullube su, kowa addu'a kawai yake yi internally Allah ya tashe ta ya takaita musu wannan tashin hankali, karfe takwas nayi kuwa duk suka rufu a kan ta, kowa ido a zare, jira suke yi ko yaya ta motsa.

Har karfe tara Aimah bata motsa ba, zuwa lokacin zuciyoyi da yawa sun karaya, Masdooq da yake jin zafin zuciyar a cikin kirjin sa dole ya aika Ahmad pharmacy ya siyo masa magungunan sa, wanda ya manta rabon da ya sha saboda ciwon ma ya dena tashi, se ga shi cikin kwana biyu komai ya rikice shine har da kwanciya a sickbed.

Duk da ya sha maganin kamar be sha ba, karfe goma Hajiya Yayah ta yi wa su Ya Salman batun tafiya gida, sedai kukan da Aunty Luba ta rushe da shi yasa ta dakata da maganar tana duban ta, se kuma ta koma lallashi duk da itama hawaye take yi, Mama kuwa ta ma daina magana se dai ido, abinda ke going a ranta Allah ne kadai ya sani.

Suna can suna fama da Hajiya Yayah dake kora su, shi kuwa hankalin sa na kanta, ko blinking ba yayi dan gani yake yana kiftawa zata motsa, cikin ikon Allah kuwa se ya ga hannun ta ya motsa, ya yi tsai ya sake tsura wa hannun ido, se ya sake ganin ya motsa, yanzu kuwa ya tabbatar ba idanun sa ke yaudarar sa ba, da gaske ne ta motsa din, zuciyar sa tayi wani tsallen murna a kirjin sa, bakin sa ya shiga rawa yana nuna ta da hannu

"Ta motsa, ta tashi, wallahi ta motsa".

Jin haka se suka yo kanta gaba daya, sedai su ba su ga ta motsa din ba, dan hannun ya koma ya kwanta yadda yake, duka suka dago suka kalli Masdooq da yake fadin

"Na gani fa, hannun ta ya motsa, har ya daga yatsan ta, wallahi ta motsa".

Ya fada da karaya cikin muryar sa idanun sa na cikowa da kwalla, da girman sa be taba kuka ba se akan Aimah, duk wani kukan sa a kanta ne dan yanzu ma ji yake hawaye na neman hanyar fitowa daga cikin idanun sa.

"Aikuwa ta motsa, ku kalla ku ga kafar ta na motsi, ku kalla".

Aunty Luba take fadi tana Hawayen farin ciki, aikuwa sun gani dan sosai kafafun ke motsi, se ga dariyar farin ciki a fuskokin su Mama dake hawaye, kowa alhamdulillah ya ke kira, shi kuwa tuni ya fice kiran Dr.

Dole suka fita likitoci suka shiga duba ta, ba su dade ba suka fito, Dr dake in charge din case din ta yace

"Alhamdulillah, she's out of danger yanzu, sedai case na depression din ta wanda wanan wani case ne shima daban, so Insha Allah nan da ten minutes zata farka fully".

Dukan su alhamdulillah suke kira ana congratulating each other, Dr yace kar su shiga tukuna su bari after eight minutes tukuna, dan motsin su da surutan su ze iya rikita peace din brain din ta.

Nan kan seats dake waje suka zazzauna, Hajiya Yayah ba ta sake musu maganar tafiya gida ba dan ta san ma ba wanda ze saurare ta, ta bar shi as in ta farka suka gani hankalin su ya kwanta sa tafi.

Seven minutes after suka koma dakin, a lokacin motsin ta ya tsanan ta indicating zata iya farkawa any time.

Kowa na san zuwa wajen ta sedai kuma fargaba from nowhere ta rufe su, duk suka yi tsiru har zuwa lokacin da ta daga hannun ta da kyar ta dafe kan ta tare da fadin

"Wasshh".

Masdooq da Aunty Luba suka karasa da sauri suna fadin

"Sannu".

Bata amsa ba se yamutsa fuska da tayi tare da kokarin bude idanun ta........

*********

A hankali na shiga bude idanu na da naji sun min nauyi, ga wani dan yaji yaji da naji suna min, da kyar na bude eyes na, se kuma bana gani sosai a e dishi dishi, ga kuma zafi da naji ciki na na min.

Dishi dishi nake ganin inuwar mutane a tsaye a kai na sedai ba zan iya gane su waye ba, da murya ta da ta dishe nace

"Waye a nan?, Please ka ma ni na tashi, me yasa bana gani sosai?, Ciki na na min zafi.

Gyaran murya MASDOOQ yayi ya sa hannu yana kokarin komar da ni kwance, yace cikin sooting voice

"A'ah, koma ki kwanta kin ji, bacci kika yi sosai shiyasa ba kya gani amma a hankali idanun zasu washe".

Kamar na san Muryar da ke magana, sedai ban gama predicting din ta a kwakwalwa ta ba, se kawai nace

"Ciki na zafi".

"Akwai ciwo ne a gurin, shima ze warke, okay?".

Se a lokacin brain dina ya harba min sunan sa , ya kuma tuno min muryar sa tun a shekarun baya wanda har yanzu be canja ba, se maturity da ya karawa muryar armashi, na yi shiru zuciya ta na bugu, kwakwalwa ta na min ringing abinda yace na wai ciwo ne a ciki na, yaushe na ji ciwon?, Kuma a ciki?, Tsaya INA CIKI NA?.

Tambayar tayi ringing a kai na, se na zabura cikin tashin hankali, amma be bar ni ba ya maza ya sa hannayen sa masu taushi ya tare ni

"Da ciwo a jikin ki Barbie, Please ki kwanta kar ki fama kin ji".

"Ina baby na, Masdooq ina baby na, ina ka cire min baby na ka kai shi, dan Allah na roke ka kar ka raba ni da baby na, ba ni da kowa fa se shi, ka bani baby na dan girman Allah, wayyo Allah na na shiga uku na lalace".

Na fada ina sake zabura musmaman da na shafa ciki na na ji wayar babu komai, komar da ni yake yi yana yi min magana se dai bana ma fahimtar me yake cewa, jin sa ma bana yi, baby na kawai nake kira.

Ganin abun na neman rikicewa se su Mama suka matso wai su kwantar min da hankali, maimakon hankali na ya kwanta se na sake firgicewa, shikenan sun dauke min baby, zasu

kashe min baby, zasu wullar da shi a can wani waje da ba zan sake ganin sa ba.

Yin wannan tunanin se na haukace musu gaba daya, na sa hannu na toshe kunnuwa na dan bana san jin ihun da muryoyin su ke yi cikin kaina, na shiga ihu ina kiran baby na, ga yunkurin sauka daga gadon da nake yi dan guduwa daga gare su da kuma fita neman baby na, gurin aikin da yake danye se ya fara jini, murya na rawa Masdooq dake rike da ni ina fincike fincike yace

"Lubabatu kira likita, yi sauri kar ta cutar da kan ta, Mama kalli gurin aikin jini yake yi, innalillahi wa inna ilaihi rajiun".

A guje Aunty Luba ta fita daga dakin Ya Farooq ya rufa mata baya, Mama ta ɗora hannu a ka ta fashe da kuka tana maganganu, echoing din Muryar ta na shiga kunnuwa na da wani irin sound me karfi mara daɗi, hakan ya kuma sake birkita ni na shiga dambe da hannayen Masdooq da ke rike dani fuskar sa jike sharkaf da hawaye......................✍️.

Vote
Comment
Share fisabilillah

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 042  [ 11/07/2024 8:27pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Oummey
Free book!!!

*BOJUWA HERBAL'S & SCENTS*
*Suna kawo Saiwowin sanyi da suke dagargaza sanyin mara da na jijiya.*

*Haka nan suna kawo Saiwowi daban daban daga Chad da Sudan, kuma marasa illah*
*Saiwowin tsumi*
*Saiwowin dahuwar kaza/tattabaru*
*Saiwowin matsi gangariya*
*Original gadalin mata*
*Ƴaƴan gadali na asali*
*Original gumba*
*Tsumin Saiwowi*
*Tsumin kwakwa da Dabino*
*Igiyar alkairi*
*Zumar goran tula*
*Hakkin daka na musamman na asali*
*Bayan haka suna dafa kazar amare da masu jego da ma uwayen gida*.
*Akwai bridal package*
*Mai jego package*
*Ƴar gata package*.
*Dukkan kayan kuma available ne for pickup or immediate delivery.*
*A Kano nake amma kuma nationwide delivery ne*
*Ku tuntubi Surayya Halin yau a wannan lambar dan samun naku cikin musulmin farashi*
*08032773332*
*Iyah Basiru na gaisuwa*😅



___________________A haka Dr ya shigo ya tadda mu, ganin lamarin yayi karfi ya sa da sauri ya fita se kuma ya dawo bayan sa nurses na biye da shi, yana zuwa ya karbi wata allura a hannun dayar su yayi min, saboda yadda nake a gigice ban ko ji shigar allurar ba se zafin maganin da na ji, a hankali jiki na ya shiga mutuwa haka karfin da na sa na ta raguwa har ya zama jiki na ya saki a hannun Ya Masdooq.

Ya saki ajiyar zuciya ya maida ni kwance tare da gyara min gashi na da ya barbaje kanq ya dubi Dr

"Dr me yake faruwa haka, se wasu abubuwa take yi kamar wadda ke hauka, dan Allah kar ka ce min ƙwaƙwalwar ta ta tabu, wallahi ba zan iya dauka ba, pls Dr".

Dr ya sauke ajiyar zuciya ya dafa kafadar Ya Masdooq

"Ka kwantar fa hankalin ka aboki na, all will be well insha Allah, sedai fada min ya aka yi hakan ya faru, i mean yaya komai ya kasance bayan farkawar ta?".

Komai da ya faru Ya Masdooq ya sanar masa, yayi shiru yana kallo na, se yace ya Masdooq ya matsa masa, be ja ba ya matsa gefe Dr ya matso wajen fuska ta da hawaye ke gangara ta gefen idanu na, ba allurar bacci suka min ba saboda zata iya haifar min da matsala tun da da kyar aka samu na tsallake siradin fadawa coma, allurar kashe jiki suka yi min dan in dai na fighting din da nake, saboda dinki na ze iya budewa, hakan kuma ze jawo matsaloli sosai.

"I know kina ji na ko Nu'aimah?".

Dr ya fada da wannan muryar ta su da suke kwantar wa da mara lafiya hankali,

"In kina ji na just blink your eyes".

Ya fada sanin bq zan iya yin komai da jiki na ba se after thirty minutes dan ba me karfin yayi min ba.

Kamar yadda yace nayi blinking idanu na tare da kokarin bude baki na, "ina baby na?". Shine tambayar da nake son masa amma baki na yayi nauyi

"Kina son ganin Babyn ki ne?".

Dr ya tambaya bayan ya gama kare min kallo, da sauri na dinga blinking alamun eh, se yayi mutmushi yace

"Za ki ga Babyn ki, but only if you promise you won't fight".

Yanzu ma da saurin nake masa blinking saying I agree with my eyes, se ya juya ga su Ya Masdooq,

"Daga bayanin da ka yi min na fahimci tana cikin firgici rashin ganin cikin jikin ta ko in ce Babyn ta, haka kuma akwai tsoro tattare da kalaman ta da kuma idon ta, da na nazarci komai da ka fada se na gane tana cikin tsoron ganin ku, am sorry da abinda na fada, but yess a firgice take da ku, kamar tana tunanin zaku cutar mata da baby, shiyasa take wannan ihun da fadace fadacen, sedai wannan duk tunani na ne, ba wai lallai ya zama haka ba, na riga nayi mata allurar kashe jiki balle na ji ta bakin ta, amma in th next thirty minutes zata sake ta, I'll be here with you guys, three minutes before the time zaku yi hakuri kuyi excusing din mu, ina nufin zaki fita waje dan na samu nutsuwar ta na san Meye damuwar, together with me will be two nurses ga su nan da muka shigo yanzu, hope hakan is okay?".

Masdooq da da yake jin ba inda zashi ya bar wani kato da matar sa su biyu a daki when she's not in her normal Sense se hankalin sa ya kwanta jin da nurses biyu, so se ya daga wa Dr din kai, damuwa cunkushe a ran sa, yanzu in ya zama su din ne Aimah take tsoro bata kuma san gani me ze faru?.

Zuciyar sa na hakalto masa abinda ka iya faruwa sedai yana korewa dan baya jin ze iya yadda da hakan.

As Dr planned, three minutes to the time suka fita gaba daya jiki a sanyaye, Ya Masdooq ne na karshe, kuma ko da yaje bakin kofar se da ya juyo ya kalle mu kafin ya hadiye yawu ya fita, sedai be je da nisa ba, jikin kofar ya ja ya tsaya in case of cases.

A ciki kuwa minti talatin din bata cika ba da minti daya na ji karfin jiki na ya dawo, duk da ba kamar dazu ba amma haka na fara kokarin mikewa zaune, wadannan nurses din biyu suka rike min hannu amma se na shiga kokarin kwace wa ina zare ido, nifa ba su Hajiya Yayah kadai ne bana san gani ba, gaba daya mutane ne suke bani tsoro, bana san ganin kowa a kusa dani, not har ma a taba ni.

Zasu sake riƙe ni bayan na kwace Dr ya daga musu hannu, se suka ja gefe kadan suna kallon mu.

"Sannu Nu'aimah, me yake damun ki yanzu?".

"Baby na, ina baby na yake?, An cire min baby na an gudu da shi".

Na fadawa Dr ina rushewa da kuka instead of amsa masa tambayar sa, se yasa hannun sa kan bakin sa yana cewa

"Shhhh, babyn ki kike son gani ko?".

Da sauri na dora hannu na kan baki ina gyada kai, se ya juya ya dubi nurses din yana cewa

"Ku kawo su".

Se kuma ya juyo waje na

"Shikenan?".

Da sauri na gyada masa kai, se ya sake zuba min ido yace

"To bari na kira su Mama su shigo, da su Ya Salman ko?".

Ambaton sunan nan biyu kadai ya sa na firgice har fiye da dazu, na shiga girgiza kai ina cewa

"A'a, a'a, kar su zo, Ni bana so suzo, zasu kashe baby, zasu duke Ni, ya Salman yace ze kashe ni, kar su zo, zasu kashe baby ma, Mama tace bata so na, ba zata so baby ba ma, zata dake shi, zata kashe shi....".

Dr da ya sunkuyar da kai yana ta bubbuga hannun sa a cinya yana sauraren na ya dago

"Shikenan, ba zasu zo ba, ba zasu kashe baby ba, amma uhm..uhmmm..uhmmm"

So yake ya tuno sunan da yaji ana kiran Hajiya Yayah sedai ya kasa, se yace

"Shi Farooq ai ba ya kashe baby ko?".

"Kowa yana son kashe baby, kowa yana duka na, zasu kashe ni su kashe baby ma, kowa baya so na, kar su zo, bana so, nace bana so, bana soooo".

Na kwalla ihun da se da nurses din suka firgita haka ma Babies din suka farka daga baccin da suke yi tare da tsanyara kuka, nurses din suka kankame su suna lallashi, daga waje kuwa ihu na yasa duk suka firgita suka mike tsaye.

Kukan yaran ya shiga kunnuwa na ya shiga kutsawa cikin jini na yana kurdawa cikin ƙwaƙwalwa ta, se na dakata da ihun da nake na juya bangaren da nake jin kukan, se idanu na suka sauka kan first nurse tana rike da abu a showel.

Baki na da hannu na na rawa na daga ina nuna ta batare da na kalli Dr ba nace

"Ba..b.a..bbbb...bbyyy?".

Gyada min kai yayi yace da baki

"Babyn Nu'aimah".

Ai se na sake zabura zan tashi, wannan karan ba na fada ko neman kare kai ba, na neman kwace baby na da nake gani hannun wata, bayan na san zata cutar da shi ne, dan haka nake ganin kowa a wannan lokacin.

Se ta riga ni ta karaso da sauri ta mika min shi, na rike bayan Dr ya daga min gadon ta yadda na dan kishingida, da sauri na finciki Babyn a hannun ta, ya kuwa fashe da kuka, se na maza na kankame shi ina hararar ta , dama na san cutar da shi zata yi, gashi nan ta sa shi kuka, Dr dai na zaune yana kallo na.

Ban lura ba se da na fama dinki na da har lokacin yake tsattsafo da jini kadan, ban damu da

zafin ba se dai na dan runtse ido, na yi kasa da babyn a hankali cikin takatsantsan na bude a hankali, se na zaro ido ina kallon shi ganin kamar nice ai a cikin showel din, se na shiga taba hannayen sa yan kananu, na kalli na wa da suka yi babba, se na koma kan bakin sa, dan mitsitsi kamar ba ze budu ba, se na kai hannun na taba nawa, haka nayi tayi, kome na taba nasa se nayi comparing da nawa, daga karshe kuma nayi dariyar da fa taho da hawaye na rungume shi

"Ina son ka baby na, ina son ka sosai, ba zan bari kowa ya taba ka ba, ba zan bari Ya Salman ya dake ka ba, ba zan bari Mama ta ce bata son ka, baby sun ce basa so na, sun ce sun tsane ni".

Na fara maganar in seriousness like q protective mother, se kuma ba karashe da kuka, abin na taba min zuciya, a cikin kowane hali bana manta yadda suka ce sun tsane ni sun kuma yafe ni a cikin su.

A cikin kukan da nake na ji aan aje min abu a cinya, na sa hannu da sauri zan ture Dr ya riga ni da fadin

"Another baby na, shima na Nu'aimah".

Se nayi sak, a kuma slow motion na kalli showel din, iri daya da na hannu na, se na kalli na hannu na na kalli Dr, ya tabbatar min ta hanyar fadin

"Twins ne ba baby daya ba".

A haka rike da baby boy din na kai hannu na riko macen, ganin hakan ba ze yiwu ba se na kwantar da namijin a kirji na, ita kuma na saka hannu biyu na dagota na jingina ta da jikin baby boy din, kamar me tsoro na yaye showel din, se ga cute baby face din ta which is a replica of mine ya bayyana, a yanzu kam baki na bude gaba daya saboda mamaki, dan girl din tafi kama da ni, komai da komai.

"Laaaah, it's a baby girl".

Na fadawa kai na, se na karasa warware showel din na shiga kare mata kallo, irin kallon da ake cewa na kwakwaf haka nake mata, hatta yatsun hannun ta irin nawa ne, se na kafarta da na lura suna da tsayi, nawa kuma ba su da tsayi sosai.

Se na dubi Dr da yar damuwa

"Yatsun kafarta masu tsayi, ni nawa ba tsayi". Na fada ina motsa kafata, Dr yayi yar dariya

"Maybe na baban su suka gado, dan baby boy din ma haka nasa yake, and su farare ne ke kuma ba ki da haske".

Nan da nan na hade rai, na harare shi nace

"Su ba su da Baba, only Ummu gare su, Ni".

Se Dr ya gyada kai yace

"Haka ne, na manta ne".

Ban sake kula shi ba na kankame su gaba daya a kirji na, suma kuma kukan da suke duka se ya dauke, se wawure wawure da suke yi a fatar kirji na.
Dr ya dubi nurses din da ke tsaye suna kallon komai alamun su je, shima ya mik yayi kofa, ban lalle su ba duka har suka fita.

Se da suka fita na sauke ajiyar zuciya na sauke baby boy din kan cinya ta haka ma macen na jera su ina kallo, haka nake so, na ji ni Ni kadai a waje, ba tare da kowa ba, dan na san za'a cutar min da baby na ne, Ni kuma bana son haka.

A can waje, Dr na fita ya Masdooq dake jingine jikin bangon wajen ya dago da sauri yana kallon su, hannun sa kawai Dr ya kama ya wuce gaba, se kuma ya dakata ya juyo ya kalli su Hajiya Yayah da suka nufi dakin da nake

"Kar wanda ya shiga in ba haka ba zata sake birkicewa".

Daga haka ya cigaba da jan Ya Masdooq, se sauran ma suka bisu, Ya Masdooq ya zama kamar wani mutum mutimi, bin sa kawai yake yi.

Office din sa ya shigar da shi ya zaunar kan seat shi kuma ya zagaya na sa seat din ya zauna, seda ya bude wata folder yayi rubuce rubuce a ciki sannan ya dago ya dube su, daidai su Mama ma na shigowa, se ga Baba da shima ya kira waya Dazu Hajiya Yayah ta sanar masa akwai matsala, Dr ya mike ya bawa Baba another seat, ragowar kuwa na tsaye.

Seda ya zauna sannan ya dube su one after the other, kana ya sauke ajiyar nunfashi

"Ya Salman, da kai da Mama me kuka yi wa yarinyar nan da zafi har haka?, Dan jin sunan ku kadai na lalata duk wata nutsuwa da aka samar mata, wace irin illa kuka yi wa ƙwaƙwalwa da tunanin ta haka?".

Ya Salman da Mama suka daga suna kallan shi, Mama kamar cikin firgici tace

"Kuskure ne Dr, fushin zuciya ne duk ya sa muka yi abinda muka yi, amma wallahi ba dan Bama san ta ba, duk cikin ƴaƴana nafi son Aimah Dr".

Dr ya gyada kai yace

"Well, koma mene ya faru gaskiya ta dauke shi da girma, haka kuma ya taba ta sosai ta yadda ya taba kanta, ya sanya mata tsoron ku da tunanin in dai kuka kusance ta to cutar da ita ne zaku yi".

Se yayi shiru kadan kafin ya dago ya sanar da su duk yadda suka yi da ita a dakin, gaba daya hankalin su ya tashi bare ma Masdooq jin wai tace ƴaƴan ta basu da Baba

"I think for now dole zaku hakura da zuwa asibitin nan while she's awake, dan yin hakan ze dinga dawo mana da aiki baya, dan yanzu haka ɗinkin ta yana bukatar dubawa saboda jini da yake, ban taba bane dan bata damar samun nutsuwa da kwanciyar hankali, so I recommend da kuyi hakuri da zuwa wajen ta har nan da sati biyu, zuwa lokacin insha Allah ɗinkin ya fara warkewa, and taba bukatar therapy, dole zata ga therapist dan dawo da ita hayyacin ta da yin yaki da depression din dake damun ta".

"Amma ai ni zan iya zuwa ko Dr?".

Dr ya kalli Masdooq, ya dan yi mutmushi

"Komai ze yi daidai aboki na, ka dan yi hakuri kajiii".

Sunkuyar da kai yayi zuciyar sa na masa zafi, kan sa na wani irin ciwo

"Nifa Dr?".

Aunty Luba ta tambaya da karyayyiyar murya

"Kowa da kowa ne ze dakata da zuwa, she'll be under our care, and I assure you she's safe with us, munq da nurses sosai masu kyau, za'a kula da ita da Babies din Insha Allah, ku dai ku cigaba da taya ta da addu'a".

Daga haka kowa yayi shiru, aka rasa me abin cewa se da Baba yayi gyaran murya yace

"Ku tashi muje".

Mikewa suka yi duka ban da Masdooq da ya sake dagowa cikin rauni gwanin tausayi

"Ba zan iya ganin su ba Dr kafin mu tafi?".

"Kayi hakuri amma ba zasu ganu ba yanzu, sedai zan sa a canja mata daki zuwa me glass a kofa, se ka dinga zuwa kullum kana kallon su, ka kwantar da hankalin ka please, everything will fall into place, it's just a matter of time".

Da haka Ya Masdooq ya hakura ya bi su Baba, be iya jan mota ba se ta Farooq ya shiga, suna tafe babu me iya cewa komai har suka kai gidan Masdooq, ya bude kofa ya sauka, se lokacin Farooq ya fito ya dafa shi cikin kokarin danne nasa damuwar ya bashi sooting words, shi dai gyada kai kawai yayi ya shiga guda, su kuma suka wuce.

Ranar se da ya sha magungunan sa kafin ya ga wayewar gari, saboda yadda ciwon sa ya tashi da karfin gaske, ga Sa'adah baya gidan dan da ta fita zuwa asibitin dazu daga can gidan Hajiya Yayah tayi..................✍️.

Vote
Comment
Share fisabilillah

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 043  [ 12/07/2024 8:11pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Ouummey
Free book!!!

Ouummey 043

Page 4️⃣3️⃣

__________________Tun daga ranar ba wanda ya sake shigowa inda nake a cikin su, ni dai na ga an canja min daki, ban damu ba dan ina kankame da ƴaƴana a kirji na aka tura ni a kan bed

zuwa dakin.

Nurse Vanessa, wata Christian ita ke kula da ni da Babies di na ita da sister Husna, itama nurse ce, se Dr da kan shigo sa'i da lokaci ya duba ni.

Masdooq kam kullum yana zuwa, da asuba da kuma dare wajejen 12pm, duk yazo se a nannada kaya suyi kamar baby a sa a showel dina da nake dora hannaye na, ni a nawa wautar na danne su yadda ba wanda ze zo ya dauke min, se a kai masa yaran office din Dr, wanda saboda Masdooq yake zuwa kullum by 11:30pm.

A haka yayi naming din su, the baby boy sunan Abba, wato Muhammad Bashir, macen kuma NU'AIMAH, wato suna na.

Ba wanda yayi expecting haka daga gare shi, kowa zato yake ze saka sunan Aunty Luba, Hajiya Yayah ko Mama ne, se gashi ya bada mamaki.

Hatta yan Barka da ke zuwa gida wajen Mama da Hajiya Yayah in suka ji sunan yarinyar se sun sake nanatawa kafin su share, a cikin iyayen mu kuwa ba wanda yayi masa maganar me yasa yayi haka.

Ya Farooq dai ne ya dube shi ranar da suka je office din tare, ranar da ya sakawa yaran suna

"Me yasa zaka saka sunan Aimah? Bayan ga sunan iyayen mu da suka fi cancanta ka saka?". Ya Masdooq na cigaba da kallan Babyn yace

"Bana tunanin akwai sunan wanda ya fi nata cancanta da yarinyar nan, ko ka manta ita kadai ta raini abar ta taɓa ciki batare da taimakon kowannen mu ba, har kuwa da ni da nayi cikin?, Ka san wahalhalun da ta sha yayin zama da cikin, all the pains, the agony and the sleepless nights, all the tastelessness, abubuwa da yawa da ba mu sani ba, ta gama tazo haihuwa ta wahala, aka yanka cikin ta aka ciro Babyn, sannan take kan shayar da ita daga jikin ka kace bata yi deserving a sa sunan ta ba?, Beside all this alƙawari ne nayi in dai na haifi ƴa mace kuma na mata huduba da kai na to tabbas sunan ta Nu'aimah, se kuma God so kind ya sa Babyn ta zama her replica, what would I asked more?".

Cikin tausayi, mamaki da al'ajabin irin soyayyar nan Farooq yace

"Kana nufin after all abinda tayi maka a baya ko da bata dawo gare ka ba se ka haifi ƴa da wata matar ka saka mata sunan ta?, To what about princess? Me yasa ita kasa sunan Mama?".

"Ban taba rike Barbie a raina ba, ko da so daya kuwa, Allah ne shaida tun ranar da na furta mata saki rana bata fitowa ta fadi dare yayi gari ya waye batare da na ambatar wa ubangiji ya yafe wa Aimah ba, dan Nima na yafe mata, Farooq zaman mu da Aimah a wannan auren ba zama ne irin na kowane ma'aurata ba, na yi mata abubuwa da dama, na hana ta serving dina

abinci, daga karshe na hana ta dafa min abincin ma, bana kwana tare da ita a same bed, duk da cewa ban taba daukar kwanan ta na kai wa Sa'adah ba, hakan ne ma ya kawo rabon yaran nan dan na shiga matsuwa sosai kuma ya zamto a ranar kwanan ta, i can't go to Sa'adah dole na daure komai na samu nutsuwa da ita, after that babu abinda ya kuma hađa mu, ban matsar ta balle na san matsalar ta, seda ta kai ta kwanta a asibiti na kwana uku saboda yunwa, se kuma lokacin na gane nayi sakaci akan hakkin ta na ciyarwa, and from then ban kuma dauke ido daga kan abincin ta zuwa lafiyar ta ba, ban san me yasa ta zabi boye min tana da ciki ba, na dai lura daga baya kullum na shiga duba lafiyar ta zan same ta sanye da hijab ne, na tambayi kai na hijab din na meye, se kuma zuciya ta ta raya min tana kokarin killace jikin ta ne dan kar ya bani sha'awa har nace zan yi wani abu da ita, wannan tunanin yasa na daina kare wa jikin ta kallo, sedai na kan kalli fuskar ta sosai dan gane akwai ciwo tattare da ita ko da bata furta ba ko kuwa babu, ashe ciki ne da ita, and ban gane ba se ranar da na dawo daga tafiya na samu tana nakuda muka taho asibitin nan,hmmmmm".

Ya sauke ajiyar zuciya ya dago ya dubi Farooq da ya tsura masa ido, se ya lumshe nashi ya cigaba

"Na sani zaka iya jin haushi na, sedai ko me nayi ina da dalili Farooq.
Kaga na farko batun girki, na hana ta serving dina ne saboda ba zan iya jure kusancin mu batare da na ji wani abu a raina game da ita ba, a duk sanda tayi kusa da ni soyayyar ta karuwa take a raina, ni kuma ina kan kokarin ganin na koyawa raina danne son ta ne dan na lura yana cikin abinda bata so ganin soyayya daga gare ni.
Se batun hana girki gaba daya, yi tunani a karan kan ka, shin saddiqa bata sake samun soyayya daga gare ka duk sanda kake cin abincin ta?, Shin baka jin karin soyayyar ta in kana cin abincin da ka san da hannun ta ta sarrafa shi purposely saboda kai, wannan yasa na kasa jurewa, dan maimakon na iya daure danne son ta se yake neman tumbatsa fiye da da ta yadda ze zama out of my control, shiyasa na hana dan zaman lafiyar mu both, and one more thing, na sani ba'a san ran ta take dafa min ba, tana yi ne saboda tursasa kan ta yin biyayya ga su Mama, Ni kuma duk abinda na san ze zama takura gare ta ina raba ta dashi ko da ni zan cutu, wannan shine dalili na na sakin ta tun auren mu na farko.
Se batun kwana, wannan ba se na fada ba ma na san ka fahimce ni, I can't sleep with her in the same room as my legally wedded wife, the one I love most sannan na iya dauke ido a kan ta, no ba zan iya ba, aside that kuma ta nuna bata bukatar hakan daga gare ni tun auren mu na farko, irin yadda komai ya faru da reaction din ta a wancan lokacin ba ze bar ni na sake forcing din kai na gare ta ba, se kuma rabon yaran nan da yasa dolen dole na karya alƙawari na, shima kuma ganin hawaye a idanun ta bayan faruwar komai ya tuna min wani abu mara dadi da ya wuce a wancan lokacin har ya sa na kasa daure bacin rai na na ja tsaki na fita, daga lokacin ban kuma matsa mata ba, se kuma batun rashin lafiyar ta da bani da masaniya se da na gan ta a sume, daga lokacin kuma na đorawa kai na shiga duba ta da asuba da dare ko da kuwa ba girkin ta bane, alhamdulillah a sani na dai bata rasa komai ba, se kuma batun ciki da na fada maka ban san komai a kai ba".

Yana dasa aya Farooq ya jawo shi jikin sa ya rungume, cike da tausayin dan uwan sa, tausayi

ba kadan ba, shi kuma ƙaddarar sa kenan, jarrabawar da Allah ya masa kenan ta so da kaunar wadda bata son shi, ya tuno dubban matan da ke rububin sa tun a da suna karatu, in kyau ne da yawan su sun fi Aimah, in diri ne wasu sun dame ta sun shanye, in gayun ne ma haka, in kuma class ne da yawa wallahi Aimah ba zata tsaya in da suke ba, amma duk da haka, a duk kan su Masdooq be ga wadda yake so ba, zuciyar sa bata zabi kowa ba se Aimah, wadda be tsinci komai a son ta ba se wahala, ga shi nan har yanzu fama yake.

"I thought zaka ji haushi na ne Farooq, why the opposite reaction?".

"Saboda na fahimce ka, na san ka ciki da bai, na san abinda zaka yi da niyya da akasin shi, komai da ya faru wasn't your fault, kafin aje ga ƙaddara kayi ne da farar niyya, wajen ganin ka faranta mata ka guji bacin ran ta, to me yasa zan ji haushin ka bayan ban ga kuskuren ka ko daya ba?".

Ya Masdooq ya lumshe ido tare da jimke hannun sa

"Ai ban fada maka kuskuren ba ne Farooq shiyasa ba ka gan shi ba".

"Banq kuma son jin shi, yadda na san ba zaka dauki wuka ka yanka kanka dan cutarwa ba na sani ba zaka yi wa Aimah komai dan mugunta ba, so kuskure in ma kayi ai we all are humans and bound to make mistakes, Abu daya zaka yi, in ta nutsu ka nemi gafarar ta, that's all, okay?".

Be amsa ba se sake rungume Farooq da yayi, ya kwantar da kan sa a jikin sa yana jin tashin hankalin da yayi kwana da kwanaki a cikin sa na bajewa, zuciyar sa da har yau bugun ta ne daidai ta ba ya dinga saisaitawa,

"Na gode Farooq, na gode for understanding me, na gode for believing in me, Nagode for everything brother".

"Ka dinga tunawa always, am your brother and not Aimah's, I'm the most closet to you, you can always count on me, okay?".

Gyada kai Masdooq yayi yana jin son dan uwan nasa a ran sa, ya dade da sanin ciki daya ne kawai ba su fito ba amma ko wanda suka kwanta mahaifa daya ba lallai su fada musu kauna da fahimtar juna ba.

Daga haka suka bada Babies din aka maida su, su kuma suka wuce gida.

Ba wnada yace komai da aka ji sunan baby girl Nu'aimah, se Aunty Luba da tace ya kamata a samo nicknames masu dadi a saka musu, duk an yarda da hakan se kuma aka dakata tuno ita fa uwar gayyar ko sunan gaskiyar bata san an saka ba balle nickname, a yadda wannan Aimahn ke birkice tsaf zata ce ita ba hakka sunan yaranta yake ba.

Da haka lokaci ya cigaba da tafiya, cikin ikon Allah da tsarin sa se gashi har mun yi sati biyun da likita ya diba mana, dake ina samun kulawa ciwo ba ya kame tas, har zaren ya fara sassautawa, yara kuwa kullum suna kankame a jiki na, nurse Vanessa ce ta koya min yadda zan yi breastfeeding din su, dan an yi batun cigaba da pumping nace a'a, na fi son su sha da kan su, kwana biyar aka yi ana koyon kafin na iya, shima ba wani cancan ba, se a hankali hannu na ya fada.

Abinda na lura shine, handsome ya fi cutie hakuri, dan haka nake kiran su, ba wai tana rigima ba ne, a'a ta dai fi shi kulafuci na, dan ko ya na aje ta yanzu zata fara wuwwula ƙafafuwa tana tabe baki amma ba wai kuka take yi ba, though nurse Husna tace wai ni na sabar musu da riko a hannu kuma a jiki na tun da kullum ina kankame da su, hatta wanka ban yadda a je toilet a musu, a gaba na ake kawo ruwa a musu, wannan kuma aikin Husna ne, dan ita Vanessa goge musu jiki take da wiper, tace ba su yi kwarin a dinga musu wanka ba.

Wankan ma a sirrence Husna ke yi, shima da kyar tayi convincing dina, shima se da tace ai in ba'a musu jikin su ze dinga ciwo, shine fa nake bari.

Ranar da aka yi na farko kuwa baki cutie na kuka se na ce kawai a bar wankan a bani ƴata, Husna na dariya se da ta karasa wankan, aikuwa har da hawaye na ina taya baby na kuka.

Tun daga lokacin ban hana ba saboda yadda naga ranar sun yi luff suna ta bacci cikin jin dadi.

Dr ya shigo dazu da safe ya duba ni yake cewa

"Masha Allah, guri yayi kyau, se sallama ko Maman twins?".

Na gyada kai dan yanzu magana ma wahala take bani, kamar ba Aimah me kaudi da karadi ba

"To za'a bani handsome ko cutie?, Wanne za'a bani?".

Zaro ido nayi without considering ai wai wasa yake, be ankara ba yana ma handsome wasa yaji na kai hannu na rike dana, ya juyo ya kalle ni sedai be yi mamaki ba dan ya san yadda nake akan yaran, se ya sakar min shi yana murmushi

"Wato ba dai za'a bani ba ko Mom twins?".

Da sauri na gyada kai, yo ana zaune kalau ina wani batun na bashi baby na, nifa ko nurses da suka fara min sagarabtun zuwa ganin yaran bana yadda na bayar, makale kaya na nake yi, ayi ayi na ki bayar wa, akwai ranar da na birkice musu na dinga ihu da doke doke, tun daga lokacin Dr yace kar wadda ta kuma shiga dakin in dai ba Vanessa ko Husna ba, suma da kyar na fara yadda da su, musamman akan yara na.

Da daddare allura Dr yayi min ta bacci, ya kira Masdooq kan yazo yau da wuri dan ya rubuta

min sallama, a haka kamar matatta aka saka ni cikin mota, tunanin sa ina ze kai ni tun da dole akwai bukatar a dinga kula da ni, tuna yadda nayi akan Mama yasa yayi tunanin kai ni gidan Hajiya Yayah, se ya wuce dani can, a hannu ya dauke ni zuwa dakin da nake zama, ya kwantar da ni tare da kwantar da yaran a gefe na, Hajiya Yayah da Mama se ranar suka sake ganin yaran, suka kalle su cikin kwanciyar hankalin da da ina farke ba ze samu ba, ranar Mama a nan ta kwana, Sa'adah kuwa dama washegarin komawar su gida Hajiya Yayah ta sa ya Farooq ya maida ta gidan ta.................✍️.

Vote
Comment
Share fisabilillah.

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 044  [ 12/07/2024 8:13pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Oummey
Free book!!!

Ouummey 044

Page 4️⃣4️⃣

____________________Yau fa a ke yin ta!.
Washegari da safe ina farkawa na ganni in a different environment, the first thing that came to my mind was my children, cikin tashin hankali na shiga neman su, se ga su na gani a gefe na covered with a very soft duvet, na yayime su a cikin cover din na makale su q kirji na, na shiga bin dakin da kallo ina zarar ido.

Ina a haka ya bude kofar ya shigo, na daga kai na dube shi, duba na sosai da sosai, se kuma na sunkuyar da kai na hawaye na flowing out zuwa kan kunci na.

Se yanzu na gane, ya dawo da ni gida ne, amma kuma ai nan ba daki na bane, jin shiru be dago ba se na kalle shi a kaikaice, yana tsaye ya tokare kofa da bayan sa hannayen sa zube a aljihun sa yana kallo na, se na sake sa hannu na rungume yara na, na sani zuwa yayi ya fada min baya son su, may be ma yace ze kwace ya je ya yar, tun da da nace bana san haihuwa da shi shima yanzu tun da baya so na na san zuwa ze yi ya yar min fa yara.

Yin wannan tunanin se na sake kankame se har se da cutie ta motsa tana yin kuka, na kalle ta da sauri dan in akwai abinda na tsana a duniya to kukan su ya biyo bayan shi a yanzu dai, se na dan sassauta tare da dagowa na kafe shi da ido, se lokacin kuma ya shiga takowa zuwa gare mu, wanda duk takun nake jin sa a cikin raina yake kuma tafiya tare da bugun zuciya ta.

Da ya tsaya a bakin gadon kuwa se na ja baya da sauri ina makalewa jikin headrest na bed din idanu na a zare cikin tsoro, se ya zauna a hankali a bakin bed din, kamar ina jira kuwa ni kuma na sauka da sauri na matsa na makale jikin bango, bugun da kirji nake yi kuwa na san har shi ya gani dan be buya ba.

"Calm down Aimah, am not here to harm you, not our children".

Duk da ya fadi haka ban zauna din ba, dan ban yarda da shi ba, na san yadda ya dena so na, na kuma san yadda dole zece se ya rama abinda na masa, duk da a yanzu ban dauki komai da yayi min matsayin ramuwa ba, sedai fushi kamar yadda Abba yace, da kuma so na da ya daina yanzu.

"Wallahi na rantse miki da girman Allah ba cutar da ku zan yi ba".

Ko a halin hauka nake ba depression ba naji wannan kalaman daga gare shi zan yarda balle yanzu, ku san wani abu, na fa san Ya Masdooq irin sani da fahimtar da ban da Ya Farooq bana jin akwai wanda ya san shi ya fahimce shi kamar ni, na san waye shi akan rantsuwa, dan be cika yin ta ba ma, in kuma yayi to be meant it.

Se na gyada kai alamar na yadda, ajiyar zuciyar da ya saki kuwa se da naji ta, ya bubbuga min gefen sa tare da cewa

"Seat, please seat let's talk".

Na kalli wajen da ya nuna na kalle shi, se kamar me tafiya kan ruwa na shiga takawa a hankali naje can nesa da inda ya nuna na zauna, abin dariya har lokacin yaran na hannu na na hade su a cakude na rungume kamar wasu kayan wanki, Sarkin hakuri handsome shiru abin sa duk da na san matsar da nayi masa na takura shi, amma cutie kuka take yi ƙasa ƙasa har lokacin.

"Saurare ta, ki rage tsaurin rikon da kika musu, shi ke sa ta kuka".

Kamar doluwa se na kalle ta, na kuma sassauta rikon da na mata, se kuwa tayi shiru tana yamutsa karamar fuskar ta, abin ya bani sha'awa se nima nayi tare da taba kuncin ta na murmusa, murmushin da ya bayyana hakora na.

Irin yadda ya kura mana ido yasa na ji kallon shi a jiki na, na dago a darare na kalle shi, se na samu kuwa idanun nasa na kan mu kamar yadda nayi zato, se na maza na ja showel din cutie na rufe mata fuska ni kuma na bata tawa fuskar.

Se ya dan yi murmushi kadan sannan yace

"Na sa musu suna".

"Suna?".

Nayi magana da shi for the first time, ya gyada kai in affirmation

"The Babies, I've named them, Muhammad Bashir the boy, and NU'AIMAH the baby girl".

Fuskata ta haska da mamaki, farin ciki and confusion at the same time

"Kana nufin handsome sunan Abba na, and cutie suna na?".

Yanzu ma kai ya gyada yana kallon cikin idanu na

"Allah ya maka albarka Abba na, Allah ya jikan Abba na, i missed you Abba na, kai kadai ke so na dama, se kuma ka tafi ka bar ni, yanzu kuma Allah ya dawo min da kai, i promise to be q good girl Abba, na sani zaka yarda da ni ko?, Ka sani NAYI NADAMA ko?".

Na fada ina rungume handsome a kirji na, hawaye Masu zafi na saukowa kan kunci na, da gaske nake nayi kewar Abba na, na yi kewar kulawa da kaunar sa a gare ni, ban iya na kyautata masa ba har ya bar duniya.

"I was never a good girl to you Abba, I disobeyed you always, I never listened to you, but that was before, I'm now a changed girl, I've changed Abba, I've changed to a better person, for you and for myself, me yasa zaka tafi ka barni a lokacin da na fi buƙatar ka Abba?, Me yasa?, Duniyar babu dadi da babu kai, duk wani so da kauna akasin naka gaibu ne, karya ce Abba, ban gane hakan ba se bayan baka nan, ka dawo duniya kazo ka ga Aimahn ka, ka zo kaga yadda na canja, zan saka farin ciki Abba, zama yarinya tagari, dan Allah ka dawo, ka dawo Abba na roke ka".

Nake fadi cikin marayan kuka mara sauti sedai me kona zuciya da ruhi ne, zuciya ta matsewa take yi kamar ana cure min ita waje guda, ban san ni ba komai bace se da Abba ya bar duniya, ban san bani da komai da kowa ba se da ya gusa, duk wani so da kauna yayi fading, ya bi iska ya watse kamar be taba wanzuwa ba.

"Abba duniya ta min zafi, kowa ya guje ni, babu me so na, yan uwana sun ce basu bani, Mama ta tsane ni, Masdooq ya dena so na, Baba ya juya min baya, Hajiya Yayah na kasa gane mata, me yasa Abba?, Me yasa?, SABODA BABU KAI".

Irin kukan da nake yi a lokacin da irin yanayin da kalaman ke fitowa tun daga karkashin zuciya ta cike da rauni zuwa kan harshe na cike da daci ya isa ya sa me tausayi zubar da kwalla, kamar yadda ya kasance ga Masdooq, idanun sa sun yi ja na tausayi da tashin hankali, he's feeling guilty,  feeling din laifin da be san yaushe yayi sa ba yake jin yana mamaye shi, ya matso a hankali ya dafa kafada ta, ina dagowa na kalle shi da  Watery eyes dina

"Ban dena son ki ba Aimah, Mama bata.......".

Kafin ya karasa nayi wancakali da hannuwan sa na ce cikin ihun dake expressing bitterness dina

"Karya kake, karya ne, kowa baya so na, kowa baya kauna ta, Abba na ne kadai me so na, shine kadai me kauna ta, ka bar ni na fada masa yazo ya dauke ni daga duniyar nan, ka bari in sanar masa su waye ya bar ni a cikin su, na tsani rayuwa, na tsani kowa, mutuwa nake so, mutuwa kadai".

Da sauri ya duka ya tare yaran da ke shirin faduwa saboda yadda na mike a haukace, a kan bed ya kwantar da su, ya komo waje na, bubbuga kai na nake a garu ina fadin

"I want to die, Ina so na mutu, mutuwa nake so nayi, Abba ka zo ka ɗauke ni mu tafiyar mu, Ya Salman yace se ya kashe ni, Mama tace ta tsane ni, kowa baya so na, gwara na mutu, maybe in na je lahira zan yi farin ciki, Abba take me with you, a tare da kai na san zan samu so da kauna, kaji Abba na".

Ta baya ya riko ni, kafin ma yayi magana na hankade shi

"Nace ka kyale ni, ka kyale ni mana, ko kai maye ne?, Se na mutu, wallahi se na mutu, Abba na zan bi, se na je wajen shi ".

Ihu da maganganun da nake yi yasa su Hajiya Yayah shigowa a rikice, ta karaso da sauri ta riko ni tana fadin

"Calm down, kwantar da hankalin ki Nu'aimah, yi shiru Please ".

Juyowa nayi na ture ta itama kamar Masdooq se idanu na suka fada cikin na Mama dake tsaye tana zubda hawaye, na yi tsalle baya da sauri har ina kokarin fadawa kan wata ƴar flower vase, Masdooq ya tare ni da sauri, se nq fincike hannaye na da ya rike na koma bayan sa ina fadin

"Ka gani ko, gata nan, ka gan ta, tazo ta kashe ni, dama sun ce se sun kashe ni, gata nan ta zo, ka ce ta fita, ta fita dan Allah kar ta kashe ni, kaga ina da Babies, kar ta kashe ni".

Ina rirrike da rigar sa nake fadin haka, gaba daya ya zama stranded, ya ma rasa me ze yi, ni kuma se ihun ya fada mata ta fita nake yi.

"Mama pls...".

Be karasa ba na daka wani wawan tsalle na dane gado, ba dan komai ba se dan ganin Hajiya Yayah tana kokarin daukar min yara, ina zuwa na ture ta, Allah yasa bata bada nauyi ba da se ta fadi, ni kuma na kifa kan yaran gaba daya

"Se dai ku kashe ni, ba zaku cutar min da yara ba, zan kare su daga gare ku, sedai ku min komai amma ba zaku cutar min su ba".

Ya Masdooq da ya firgita dan yadda na fada kan yaran zan iya ji musu biyo, ya kalle su da rawar murya

"Dan Allah Mama ku fita, Hajiya Yayah dan Allah ku je, in baku fita ba ba zata daga yaran nan ba, kuma zasu iya jin ciwo, Please ".

Ya karashe hawaye na zuba a idanun sa, karo na uku kenan, gaba daya yana neman zama me rauni akasin jajirtaccen da yake a da, lallai soyayya bata da adalci, haka kuma ba karya bace, so na gaskiya kuma daban ne.

Ba wadda ta sake cewa komai suka juya suka fita, Mama da gudu ta karashe fita tana toshe bakin ta, Hajiya Yayah kuwa sharar hawaye take, suna fita ya taho wajen mu yana kokarin daga Ni

"Is okay, sun tafi, na kore su, ba wanda ze taba mana yaran mu, ba wanda ze cutar da su, zamu kare su, at all cost, ko?".

"I'll protect them, with every fiber of my beinnnggggg".

Na karashe fada ina fadawa kan su gaba daya saboda sumewa da nayi, a gigice ya shiga kokarin daga ni, ya janye yaran ya kai su bed din su na yara dan an riga an shirya dakin, kana ya dawo kai na, komai da yake yi a gigice yake yi, ya haura saman bed ya shiga tattaba ni yana kiran in tashi, amma inaaa, na riga na sume.

Da sauri ya sauka ya bude fridge ya dauko goran ruwa ya bude ya zuba min a fuska, nayi numfashi so daya nayi shiru, se ya jefar da ruwan da sauri ya haow gadon ya tallafo face na ya hade bakin mu, iska ya shiga hura min wato mouth to mouth resecution, cikin ikon Allah se gashi na karba, na ja numfashi me tsayi se kuma na shiga tari, ya tashi ya kuma dauko ruwa yazo ya samin a baki, dake ina bukata nan da nan na shanye, na koma nayi yaraf kan bed din jiki na ba karfi.

Ya zauna kusa da ni tare da riko hannu na, na daga ido na kalle shi a galabaice

"Yaarrrraanaaa".

Daga haka na sake sumewa, yanzu kam fadin irin halin da yake ciki karya ne, dan alkalami ba ze iya rubutawa ba, be kuma bi takan yaran ba ya sabe ni zuwa downstairs ya fita compound ya saka ni a mota, har ya shiga ze tayar se kuma ya fasa ya fita ya koma ciki, yaran ya kwaso yazo ya zauna, da kyar ya dauko su dan ba a nutse yake ba, yana zama ya kwantar da boy cikin seat din gaba, cutie kuma a kan cinyar sa ya rike ta da hannu daya.

A haka yayi driving har zuwa asibiti, ya fita ya wa nurses magana aka kawo bed aka dauke ni, nurse Vanessa da aka shigo da ni a gaban ya ta karbi cutie a hannun sa shi kuma ya dauko handsome.

Few minutes Dr yayi a dakin da aka kwantar da ni ya fita, a office din sa ya samu Ya Masdooq zaune rike da handsome a hannun sa ya zuba tagumi

"Kar ka damu Mr man, ba wani abu me girma bane, ta firgita ne ga kuma damuwa da rashin abinci a cikin ta shiyasa ta sume, amma ina ganin tafiya da ita gida wajen su Mama is not a solution, ina ganin why not ka samu wani waje haka da babu su kuma ba zasu dinga zuwa ba?, Tun da bata son ganin su, kuma yawan firgicin nan ze dinga sa ta suma, haka kuma yawan suman shima ze iya taba lafiyar kwakwalwar ta".

Shiru yayi yana cigaba da sauraren Dr da shawarwarin da yake ba shi, se da ya nutsu sosai sannan ya yanke hukunci, be yi kasa a gwiwa ba ya daga waya ya kira ta, gwara Aimah ta koma can, he can't risk her mental health, duk da ya na san ganin yaran sa amma ba ze iya risking rayuwar ta da hankalin ta ba, su Hajiya Yayah na gida basu san me ake ciki ba, suna can da tashin hankalin rashin son ganin su da Aimah ke so, da kuma na jin ya maida ta hospital tana suma, se ganin NENE suka yi a gidan.

Bata tsaya saurarar su ba tayi wanka ta canja kaya ta wuce asibitin, a can suka hade da Masdooq ya karasa sanar da ita komai, dan a waya kadan ya fada mata, ya sanar da ita ya musu komai na tafiya a ranar.

Aikuwa su Mama sun ga bala'i, ta inda ta shiga bata nan take fita ba, a karshe tace ta karɓe

Aimahn gaba daya, kuma ta ga kafar wani mara kunya a ciki ya biyo ta, hatta da Masdooq din kuwa, a ranar suka bi Flight ita da Aimah da twins se Ethiopia......................✍️.

Vote
Comment
Share fisabilillah

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 045 [ 15/07/2024 7:35pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Ouummey
Free book!!!

Ouummey 045

PAGE 4️⃣5️⃣

BONANZA BONANZA BONANZA!!!

Ina kuke ma'abota so da kaunar littattafan ouummey?, Albishirin ku!, To ga dama ta Samu!!!.

Kamar yadda kuka sani paid books din ouummey guda uku ne,

ANJANE ₦400
RASHIN HAIHUWA ₦500
YAR DAMFARA ₦500

Dukan su sun kammala a document, sedai a maimakon ku biya ₦1,400 dan samun su, yanzu zaku biya ₦1000 ne kacal ku same su duka ukun!!!.

Wannan bonanza is valid to month ending kamar yadda masoya suka yi pleading a mayar, a hanzarta a sharbi rahusa, wannan duk kauna ce daga ouummey zuwa gare ku masoya❤️.

Ga me bukata, should chat my up through 09013101854,
Ouummey 📚✍️.

____________________Madaidaicin gidan Nene suka sauka, daki uku ne, Nene na cikin daya, dayan kuma me aikin ta se daya da ba kowa, shi ta saka a ka gyarawa Aimah, aka saka ƙatuwar katifa family, aka lailaye ta da sanin gado me kyau da daukar ido, dakin se tashin kamshi yake yi ta ko ina.

A nan aka sauke ni da yara na, kwanan mu biyu da zuwa Nene ta kira Masdooq kan sunan yaran dan ita kam ba zata iya fadin wani cutie da handsome ba, rasa sunan da ze fada yayi se kawai yace mata

"Aiman da Airah".

Daga haka Nene ta kashe wayar ta ba tare da ta bashi damar tambaya ta ko yaran ba.

Kwanan mu uku da zuwa na fara zuwa asibiti, wanda tun da na shiga dakin da aka sauke mu se yau din ne na fito, kulewa nake a daki abu na na saka yaran a gaba ina tunani, wani sa'in ni kaina ba zan iya cewa ga tunanin da nake yi ba, kawai my mind was always absent daga wajen, Nene da me aikin ta babba Aunty A'i ke kula da yaran, wani ikon Allah su bana damuwa dan sun dauke su, kawai dai in an gama gyara su a dawo min da kaya na, shikenan.

Se a kwanakin nan yaran suka samu kulawar da ta dace, wanka da ruwan zafi zuwa gashin cibi, se gashi hatta da baccin su se da ya canja, dama ga su ba rigima ba se su wuni suna bacci, ni kuma in ta sa su a gaba in yi ta kallo da tunani.

Yau muka shirya fita zuwa asibitin da Nene take ganin ya cancanta, tun muna Nigeria Dr yayi mata bayanin ina bukatar therapist, shine yau zamu je.

Tun da muka shiga mota kai na na kasa, bana kallan kowa kamar yadda tun da na zo kasar

bana magana, daga uhm se uhmuhm, har muka kai asibitin wanda drivern Nene ne ya tuko mu, muna zuwa ba bata lokaci aka yi attending mana dan muna da appointment da Nene ta karba tun jiya.

Tare muka shiga office din da Nene, tana rike da yaran duka biyu, ta tasa ni gaba ita tana bi na a baya.

Ban daga kai na kalli ko ina ba a office din balle Drn, na zauna kan kujera bayan Nene ta min izini, itama ta zauna a kusa da ni suka shiga gaisawa da likitan, ya amsa da faram faram da alama be da damuwa, daga kuma jin muryar sa ba wani babba bane.

Suka gama maganganun su sa Nene da ba wani fahimta nayi ba dan na fada tunanin da ya zame min jiki, ashe yana ta kiran sunana ban sani ba, se da Nene ta taɓa ni sannan na kalle ta, se ta nuna min shi tana fadin

"Ana miki magana".

Se lokacin na dago na kalli bangaren da Nene ta nuna min, yana zaune kan kujerar da ke motsawa da shi a hankali, matashi ne da ba ma ze kai shekarun Ya Masdooq ba, sedai be kai shi kyau ba amma yana da nasa daidai misali, daga zaune da yake zaka san ba wani dogo bane, sedai yana da fara'a sosai dake kara masa kyau.

"Kanwa ta".

Se na fara juye juye a office din dan neman kanwar sa da naji ya faɗa, ya takaita min confusion dina da fadin

"Kece kanwar ta wa ai".

Na hade fuska tsaf duk da dama ba fara'a nake yi ba, na tsuke baki tare da sunkuyar da kai, haka kawai ni be yi min ba, sam sam se na ji ma bana san ko zaman office din

"Ya sunan ki?".

Na dago na kalle shi, maimakon amsa se kawai na balla masa harara, ni kaina ban san dalilin hararar ba kawai na samu kaina da yi masa ne, ya zaro ido cikin mamaki se kuma ya yi dariya yana kallon Nene

"Hajiya kin ga irin hararar da kanwa ta tayi min?, Ko na mata laifi ne ban sani ba?".

Nene tayi dariya,

"Nu'aimah baki amsa likita ba".

Na sake tsuke baki, haka kawai yadda yake wani kikkifta ido se yayi min kama da kwarto, nace can ciki kamar me ciwon baki

"Bana son shi".

"Dama ai ba cewa aka yi ki so shi ba, ki amsa masa tambayoyin shi kawai ake bukata".

Maimakon amsawa se na mike tsaye kawai na fita daga office din, ni ban taba jin wanda bana so a tashi daya ba se wannan likitan, se kuma daga baya na gane dalilin kiyayyar, ba komai ba ne face yanayin jikin su da yayi kama da na Ibrahim, haka kuma fara'a da sakin fuskar sa, shiyasa na ji sam be min ba, bana ko kaunar ya zama likita na.

Duk yadda shi da Nene suka kada suka raya da lallashi naki sauraran su, ko kallon su ma na kiyi se hade kai da nayi da bango, kun san ni da tun da, akwai taurin kai da kafiya, to sune suka motsa yanzu.

Yake yayi daga karshe yace wa Nene

"Ina ganin kar a tursasa ta, tun da bata bukatar na duba ta ai ba wani abu bane, akwai Dr Bee'at se ta duba ta, kwararriya ce sosai da ta san kan aikin ta, tana da kwazo da jajircewa, inshallah za'a samu dacewa".

Cikin jin kunya Nene ta bashi hakuri, ya nuna babu komai kana ya saka messenger din sa ya raka mu wajen ta, ya kuma sanar da ita patient din sa ce pls ta duba ta.

Ni kam tuni na yi gaba, Nene ta biyo ni tana ta mita kamar zata ari baki, ban nuna na san ta ba ma balle ayi tunanin da ni take fadan ta har muka kai office din Dr da aka kira da Bee'at, ga shi nan kuwa baro baro jikin kofar office din an rubuta sunan ta.

Knocking messenger din yayi, se da aka bashi izini sannan ya shiga suka yi magana kana ya ce mu shigo, a darare na shiga office din ina wurga idanu, a kan ta na sauke duba na, kyakkyawar mace kamila nade da lafaya, me fara'a da sakin fuska.

Da kanta ta taso ta tare mu tare da ja mana seat, muna zama ta bude fridge din office din ta ta kwaso drinks da snacks ta aje mana duk da Nene na fada mata daga gida muke kuma babu yunwa a tare da mu.

Se da ta nutsu sannan Nene ta mata bayanin yanayi na, yanzu ma ban san an yi ba ido na kafe kan wani calendar sedai zahiri ba kalandar nake kallo ba na tafi tunani ne.

A sannu ta bubbuga pen kan table din tsakanin mu, wannan ya dawo da attention dina kan ta, na dube ta ta haske ni da murmushi, se na tsira mata ido ina tuna rabon da murmushi irin haka

ya samu gurbi kan fuska da lips dina

"Ya sunan kawar tawa?".

Ta tambaya da tatttausan harshe, se na sake bin bakin ta da kallo kamar wata mata hankali, bata yi fushi ba haka ta dinga bina a hankali, da ta lura Nene na kokarin yi min fada ma se tace ta koma kan sofa ta zauna ta bar mu kawai.

Cikin lallami ta samu na sanar da ita suna, tayi yar dariya tare da miko min yatsan hannun ta

"What a nice name, won't mind being my friend?".

Na kafe yatsan da t miko min da kallo, tsayin lokaci kafin na girgiza kai

"Bani da kawa mace, Ya Masdooq ne abokina, shi kuma ya dena so na yanzu, ya tsane ni, baya son gani na, yana kira na da bad names..., I can't be your friend, kema watarana zaki dena so na ne".

"I wonder yadda aka yi Ya Masdooq ya dena san this cute and loving friend din ta shi haka, tun da shi kadai ne friend din ki and ya dena son ki why not befriend me?".

Na girgiza kai in bitterness

"Ba laifin shi bane, ni ce na sa ya dena so na da kaina, but it was a mistake, and nayi nadama, shi kuma Ib..ibrrr...."

Duk yadda na so na yi pronouncing sunan Ibrahim baki na ya ki bani hadin kai, na tsane shi, na tsane shi tsana mafi girman muni da hatta sunan shi ko siffar shi bana kaunar me irin nashi, shiyasa na kasa yarda wancan likitan ya duba ni.
Hawaye suka shiga zuba a idanu na, zuciya ta ta matse waje guda, babu abinda ke yawo a idanu na se fuskar Ibrahim da a yau tayi bakikirin a idanu na, ji nake ina ma zan gan shi, da a lokacin babu abinda ze haka na kashe shi, ko da na san nima kisa ne hukunci na amma i wouldn't mind in har wancan bastard din ze mutu.

Lallashi Dr Bee'at ta shiga yi min, sedai na komai ta kasa kuma ji daga baki na, daga karshe da ta lura mood dina ya sake ɓaci se tayi ending session din, tace wa Nene

"Ina ganin this will be the end of our session Mah, our next appointment will be next week by 9:00am".

Nene tayi godiya muka mike, se kuma lokacin ta kula da twins, cikin kuma excitement tace

"Wow what a beautiful kids".

Ta fada tana karbar su daga hannun Nene,

"Mah ina maman su aka fito da su haka da danyen jiki, Masha Allah kyawawa da su, hope za'a bani ɗaya?"

Ta fada jokingly, dagowa nayi da sauri na kalle ta, se na matsa gabanta na mika mata hannu, Nene tayi dariya tace

"Ga maman ta su nan gaban ki tazo karbar ƴaƴan ta jin kina maganar a baki daya".

Dr Bee'at ta ware ido tana kallo na da mamaki se kuma ta yi murmushin da ya bayyana hakwaran ta

"Kai Masha Allah, amma dai kawata na da kyan jiki, ai ban yi tunanin she's married ba, kallan yar 18-19 years fa nake mata, Masha Allah, amma dai friend zaki bani ɗaya ko?".

"She's 23 years now, dake tana da kyan jiki shiyasa, aifa nan daya, ni nayi mamaki ma da ta bari kika dauka yaran dan bata yarda a dauke su".

Ni dai tura mata hannu nake baki na a tsuke, wani irin in bata daya, tabdi.

Dariya tayi ta miko min su

"Ga su nan friend, ba guduwa zan yi da su ba".

Ba kunya na karbe abu na na juya na fita, suka yi dariya ita da Nene kana suka sake tattaunawa sannan Nene ta fito bayan sun yi sallama, ni kau lokacin tuni na kai wajen motar mu.

Nenen ma kin bata yaran nayi har muka kai gida, se da kyar Nene ta samo kai na, laifin ta shine ta kai ni inda za'a kwace min yara na.

Sati nayi muka sake komawa, yau din ma dai ba wani cigaba sosai, daga nan ta kuma bamu next appointment, haka muka dinga sagarabtu, a hankali a hankali tana hillata ta da zance tana jin damuwa ta a sannu babu nuna kosawa balle jin haushi duk da kuwa ina jin kayan haushi lokacin.

Wasa wasa se da muka kwashi wata uku kafin na saki jiki da Dr Bee'at, matar nan ta taka rawa matuka a rayuwa ta da ba zan taba mantawa da ita ba, ina kuma ta mata addu'ar Alkhairin Allah da biyan bukata.

Ranar da ta san wace ni daga baki na kuwa ni da ita se aka rasa waye patient wace likitar, dan

kuka muke riris, se da tayi me isar ta sannan ta share fuska ta shiga lallashi na da tausasan kalamai, wani ikon Allah kuma kalaman ta na ratsa ni.

Dama tun a wata na hudu Nene ta daina rako ni saboda ganin na saki jiki, Aiman da Airah kuwa tuni sun wayo abin su, sedai yanayin kulafucin su da nake yi yasa suke kyuya, musamman Aiman dan baya yarda da kowa se ni, Nene da Aunty A'i, Airah ce ma take yarda da mutane sa'i da lokaci.

A wanna lokacin kuwa alhamdulillah na samu yar nutsuwa da yar na kan dan yi murmushi in an yi abin dariya, haka na kan dan jefa tsokana sa'i da lokaci musamman ga Aunty A'i da babu ruwan ta da rashin magana ta da rashin amsawa ta, tsokana ta take yi duk san da ta zo har ta sa na fara ramawa kadan kadan.

Dr Bee'at kuwa kanwa ta dauke ni ba wai patient ba, yanzu ban da session din da muke yi a asibiti har gida take zuwa sa'i da lokaci, haka kuma naji zuciya ta ta yarda da ita matuƙa.

A sannu a sannu take taka rawa wajen saita min nutsuwa ta da tunani na zuwa yadda ya kamata, yanzu wannan yawan tunanin duk babu shi, tun da ta fahimci na fara komawa nutsuwa ta ta shiga nuna min kuskure na cikin hikima da kwarewa, bata sawa na ji na tsani kai na sedai tana sawa na fahimci kuskure na, in kuma ta ga in neman ɗorawa kai na tunani da damuwa yanzun nan zata nuna min it's not my fault, haka ƙaddara ta take, and nature ne dan Adam making mistake, sedai in an fahimta se q gyara shi.

Ita ta haska min rashin laifin Ya Masdooq a duk abinda ya faru, ta kuma saka zuciya ta yi masa uzuri da cewa dole yayi fushi, ta saka nayi tunanin if I were in his shoes yadda zan ji, ranar da nayi wannan tunanin se na jinjina masa kwarai, yayi hakuri da Ni matuka tun a zaman mu na farko, a zama na biyu kuwa yayi min gwargwadon adalci, sedai ai shima da zuciya a kirjin sa, so dole ya sami hanyar fitar da zafin da na gasa masa in one way or the other, so na dauki kuskuren shi a matsayin neman hanyar fitar da zafin ran sa, so se na ji eh lallai be yi min komai ba.

Musamman da na tuno batun Abba kan yi masa uzuri a lokacin da yake gabar rasa ran sa, dan haka na watsar da duk wasu laifi da nake tunanin yayi min, sedai bana tunanin zan sake yarda in yi zaman aure da shi..............✍️.

BONANZA BONANZA BONANZA!!!

Ina kuke ma'abota so da kaunar littattafan ouummey?, Albishirin ku!, To ga dama ta Samu!!!.

Kamar yadda kuka sani paid books din ouummey guda uku ne,

ANJANE ₦400
RASHIN HAIHUWA ₦500
YAR DAMFARA ₦500

Dukan su sun kammala a document, sedai a maimakon ku biya ₦1,400 dan samun su, yanzu zaku biya ₦1000 ne kacal ku same su duka ukun!!!.

Wannan bonanza is valid to month ending kamar yadda masoya suka yi pleading a mayar, a hanzarta a sharbi rahusa, wannan duk kauna ce daga ouummey zuwa gare ku masoya❤️.

Ga me bukata, should chat my up through 09013101854,
Ouummey 📚✍️.

Vote
Comment
Share fisabilillah

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 046 [ 15/07/2024 7:36pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Ouummey
Free book!!!

Ouummey 046

Page 46

______________________Ba wai dan na dena son sa ba, ba dan bana kaunar zama da shi ba, ba kuma wai dan nayi fushi da shi ko wani abu ba, a'a.

Ba zan koma zama da shi ba saboda ina son sa ina kaunar sa, shi kuma a yanzu ba ni yake so ba, ba ni yake kauna ba, wata ce daban a rai da zuciyar sa ba Aimah ba, ni na riga nayi wasa da dama ta ta yarda ta subuce min har wata ta tsinta, dan haka zan masa sadaukarwa, irin wadda yayi min lokacin da na nace se ya sake ni na komawa wancan mugun, ya sake ni din ba dan baya so na ba, ba dan baya kaunar zama da ni ba, se dan na sami farin ciki da kwanciyar hankali, to nima irin haka zan masa.

Ban manta yace min kafin dawowa rayuwar su shi da Sa'adah Are living a happy life, full of peace, love and care, shigowa ta cikin su na neman sawa su rasa waɗannan abubuwan, ba zan yarda hakan ya kasance ba saboda ina masa fatan rayuwar farin ciki, so a will shift a little ko komai ya dawo daidai a rayuwar su, Ni kuma zan cigaba da rayuwa da yara na, su kadai sun ishe ni farin ciki, bare ma ga Nene ta, ga Dr Bee'at dina g kuma my comedian Aunty A'i, insha Allah rayuwar wouldn't be boring.

Da wannan tunanin na rufe chapter Masdooq a raina, ba wai na dena tuna shi ba, ba kuma wai na dena son shi ba, sedai ina kokarin ganin ban bari soyayyar sa ta hana ni yin rayuwa ta ta yau da gobe ba.

Yau watan mu bakwai ba kwana ɗaya da zuwa Ethiopia, ma'ana gobe zamu shiga wata na bakwai cif, tun da muka zo Masdooq na kiran waya kusan kullum, sedai Nene bata picking, lokacin nima bana san tayi picking din, daga baya da yara suka fara wayo wajen there months yana kiran vedio call a sa musu waya a fuska yayi ta ganin su, nice dai Nene ta hana.

A haka yaran suka saba da shi ɗan har yanzu suna ganin fuskar sa kullum da safe da dare, sedai ni bamu taba magana ba har yau, da Nene ke hanawa yanzu kuma a karan kai na nake gudun hakan saboda na sani ganin sa ze tada min da duk wata boyayyar soyayyar sa ne da nake hakilon binnewa, ganin sa ze tada min hankali ya yi watsi da duk wani kokari na wajen ganin na hana kai na tunanin sa, shiyasa nake dodging din sa.

A shirye na fito dan yau Laraba, sanye da dogon hijab dina ash color da yayi wa fuska ta kyau,

babu abinda na shafa ban da kohl wa ido na se lipgloss wa lips dina amma ba karamin kyau nayi ba.

Tun da na dawo hayyaci na shiga gyaran jiki na, fata ta da duk tayi min wani iri na maida hankali kan ta, skincare products kala kala na siyo na dinga gwada wa har na samu wanda ya karbe ni, kana na shiga zuwa spa duk sati biyu da nake yi a baya, shiyasa nan da nan na farfaɗo na dawo Aimah ta, musamman ga kwanciyar hankali har wata yar kiba nayi kadan bayan murjewar da nayi, in ka ganni ba zaka yarda na taba aure ba balle har da ya'ya.

Islamiyya na shiga tun last two months dan Kara sani, duk da nayi sauka amma akwai bukatar na san litattafai sosai, aikuwa na karu sosai haka kuma yanzu har aji aka bani da dalibai, in mun gama da su mu kuma ayi mana namu karatun.

Samari kuwa sedai in ban fita ba, amma sha Allahu zan dawo da biyu ko uku, kuma duk yadda nake fadar ni matar aure ce basa yarda, se kawai ma na dena fadar tun da ba amfani.

A compound na yadda twins suna wasa tare da jikar Aunty A'i da tazo dan na fada muku ba yarinya bace, yarinyar sunan ta Safar shekarun ta bakwai, twins kuwa yanzu suke seven months da sati biyu, magana a bakin su kamar sun shekara, haka kuma suna tatata duk da bata yi kwari ba, dan ma sun yi zire ne dan ba su yi rarrafe ba, ga girma tubarkallah kamar sun fi shekara, shiyasa ban fiya fita da su ba saboda baki, yanzu zaki ji ana ta tanka su se Nene tace in dinga barin su tun da ba sa rigima kuma suna cin abinci dan tun 5 months Nene ta fara basu abinci, tace ita ba ta ganewa wani goyon kawai ba da ba za'a koyawa da cin abinci ba, nima kuma se na ji dadin haka tun da rashin tsotson su ya taimaka wajen kara murmurewa ta.

Suna ganina suka dakata da wasan da suke yi, Aiman ya shiga daga min hannu yana

"Ummiii..ummiii"

Itama Airah se ta kama, da Ummi suke kira na, ban san a ina suka samo sunan ba se kawai rana daya naji Airah ta fada, daga nan kuma Aiman ya kama, shikenan suke kira na haka, na karasa na daga Aiman ina dariya, tubarkallah akwai nauyi duk da ba sosai can ba.

Airah ta shiga takowa da tafiyar ta ta yan koyo, ina ta mata dariya itama tana bangare min bakin ta me dauke da hakori biyu har ta karaso, tana zuwa na sa hannu daya itama na daga ta, itama akwai nauyi sedai bata kai Aiman ba, se suka dinga dariya wai na dauke su a tare, na dan bata lokaci wajen su kafin na sauke su na daga Safar, tana dariya da zarar ido twins na taya ta, na sauke ta ina kishi ta kuma sa dariya

"Nauyi ne da ni sosai fa Ummi, shiyasa nace kar ki daga Ni ".

"Wash hannu na sun karya ni".

Nace ina bata fuska tare da shafa hannun, duk suka kuma sa dariya, nima na saki hannun ina taya su, na shafa kan su duka ukun tare d asa musu albarka sannan na tafi suna min bye bye gaba daya.

Raina fes na ke tafe a hanyar makarantar, dake babu nisa bayan layi ne se nake tafiya da kafa, waya ta ce tayi kara, watan ta daya a hannu na, itama Dr Bee'at ce ta bani bayan ta takura min, ba yadda na iya na karba amma ni ban ga wani amfanin waya gare ni ba, ba wanda nake kira ba me kira na, ita kadai ce kuma muna magana ta wayar Nene.

Dan daburcewa nayi kafin na tuna ai na saka wayar a jaka wata yar makarantar mu itama yar babban aji Malama Sadiya zata tura min novels, da ina karantawa yanzu ne na daina Ko in ce tun da lamura suka rikice ban ma kuma tunawa akwai Novels ba a duniya.

Ina fito da wayar na ga Dr Bee'at ce, to dama in ba ita ba ba number kowa a wayar se Nene se kuma ta Aunty Luba da ke kira na, duk da ba koyaushe nake dagawa ba kuma ba wata magana mata ba, daga gaisawa shikenan amma bata yi zuciya ta daina kiran ba.

Kowa a cikin su abinda yayi min ya min zafi, amma fa na Mama, Aunty Luba da Baba yafi min zafi, ba dan komai ba se irin yadda na dauke su da babban matsayi da irin shakkar da muke da, shiyasa har yanzu na kasa sakin jiki da ita, gani nake in na saki jiki da ita zata kuma tafiya ta bar ni ne, so is better ban Kara sabon sabo da ita ba yadda in ta tafi tafiyar nata baze taba ni ba.

"Yayata ta kai na".

Nace da Dr ina murmushi, daga can ina jin dan karamin tsakin da tayi

"In na zo gidan nan ko Nene ba zata iya raba mu ba kin sani ko, wannan yayar da kike fada dan kawai ki kashe min kasuwa a dauka wata uwar mata ce, bayan ko auren fari ban yi ba".

Dariya nayi dan kamar tana gaba na take maganar ina hango yanayin fuskar ta a lokacin

"Amma dai kin san da gaske kin girme ni ko?".

"Dalla ni ba abinda na kira ki ki fada min ba kenan, ke da ba'a abin arziki dake, kina gida ne?".

"Yau fa Laraba, ina hanyar islamiyya ma yanzu haka".

"Aff na manta da ustaziya nake magana, ki shafa min kan yara na in kin koma ki kuma gaishe min da Nene ta, inshallah gobe zan shigo".

"Allah ya kawo ki lafiya, su kuma duk zan fada musu, ban da Aunty A'i da baki ambata ba, dan haka tana tambaya zan ce ba'a bani nata sakon ba ".

"Mtsww, yar hadin husuma, yau kuma saboda kiga karshe na da Aunty A'i zaki haɗa ni, to ta Allah bata ki ba ki gaishe ta itama ".

Daga haka ta yanke wayar ta, ina dariya na mayar da wayar jaka, na sani tana can tana hararar wayar, Allah ya sani ina jin Dr Bee'at a raina kamar yayata uwa daya uba daya, ina kaunar ta saboda ta nuna min kauna, yadda ta dauke ni kamar kanwar ta ko ko ince abokiyar haihuwar ta, haka ma maman ta ta dauke ni ƴa, duk da ni ban fiya zuwa gidan su ba dan so biyu kadai nake amma ita duk san da zata zo se Maman ta bada sako a kawo min, turare ne, pants, ribbon kai har da su shower gels, ba kuma ni kadai ba har da twins, wannan yasa ma Nene ke cewa wai ana mata fidda kokon asali.

Ba wai ina son Dr Bee'at sama da Aunty Luba ba ne, a cire Masdooq da bayan son yan uwan taka nake masa son soyayya, a kaf yan uwa na bani da sama da Aunty Luba a raina, daga ita kuwa se Ya Ahmad, Ya Salman sannan su ragowar, sedai itama Dr yanzu ina jin ta kamar ragowar su Ya Farooq dan itama a haka ta dauke ni.

Duk da ta ga na dawo hayyaci na da nutsuwa ta har yau bata bar ni ba, a kan su Mama kullum fada min take matsayin iyaye da ban ne a rayuwa, haka yan uwa ba'a taba fushi da su dan sune kai, kai ne su, dole ba zaka taba yi canja su ba.

Ita take ta kokarin fahimtar da ni Baba be daina so na ba, haka kuma ba wai rashin kauna ce ta sa yayi min hukuncin da yayi ba lokacin ni da Sa'adah, wanda a waje na shi kadai ne laifin sa, a gani na sam be min adalci ba, haka kuma ya nuna son kai tsakani na da yar ƴar uwar sa, sedai a cewar ta wai ba haka bane, ya yi min hukuncin da yayi ne dan ya san ya isa da ni, ya isa ya sa ni ya kuma hana ni, wai haka iyayen da suke ba sa tsayawa su saurari nasu, nice na kuskure da na tuhume shi a lokacin, sedai tace gaba daya ba laifin mu bane, kaddarar mu ce tazo a haka, rubutu ne se mun samu sabani da Sa'adah har muje gaban sa, haka rubutu ne se yayi wannan hukuncin kuma se na tanka, dan haka na daina ganin laifin sa kuma kar nayi blaming kai na.

Duk da zantukan sun shige ni amma dai har yanzu ina kan tunani ne, in yarda da hakan ko in watsar.

Da haka na karasa islamiyya, na tarar da sauran malamai yan uwa na, lokacin dalibai ba su kai ga karasowa ba dan muna riga su zuwa saboda muyi motivating din su kan earliness.

Muna gama gaisawa Malama Sadiya tace

"Malama Nu'aimah ki kuwa taho da wayar?".

Nayi murmushi nace

"Eh". Ina mika mata, ta karba tana kokarin tura min, Malama Juwairah na mata tsiya

"Ke dai Malama Sadiya kin dage se kin tura mata littattafan nan".

Bata dago da kallon wayar da take ba tace

"Saboda ina son ta karanta ne dan wallahi littattafan sun yi dadi, ga ma'ana, kuma ita tace min a baya ta karanta wasu daga ciki littattafan marubuciyar ko Malama?".

Na gyada kai ina fadin

"Na karanta guda uku kuma sun min dadi sosai shiyasa yanzu ma nake so a tura min wadannan din, duk da na kwana biyu ban yi karatun ba insha Allah xan karanta su".

Malama Nawal dake gefe tana chatting ta dan dago tace

"Wace marubuciyar ce?, Kun san akwai marubuta da yawa da suka san hannun su, akwai kuma se a hankali".

Ina kallon ta nace

"Wata marubuciya ce, duk da bana jin ta dade tana rubutu amma dai gaskiya ta iya tsara rubutu ta yadda ze kayatar, fadakar, nishadantar ya kuma ja hankalin me karatu".

"Shine nace ya sunan ta, ina so in ji ko ina karanta books din ta, in ban karanta ba se a tura min".

Fadin Nawal a kage, nace

"Sunan ta ouummey, ita tayi littafin SARAKI, HAKORIN DARIYA da KASAR MU A YAU, su kadai na karanta".

"Wallahi ka yadda da ke in har ita tayi littafin SARAKI, na dade da karanta littafin, ina jin up to a year, tun kuma lokacin nake neman number writer din amma ban samu ba".

"Aikuwa zan baki, dan littattafan ta na yanzu ma sun fi na da daɗi, shiyasa ni tuni nake following din ta a Wattpad dan haka da ta saki novel zan gani".

Inji Malama Sadiya, tana miko min waya ta, na karba tare da cewa

"Wanne da wanne kika tura min?".

"Duka litattafan ta, BA NI DA LAIFI, ABOTA CE KO SOYAYYA, ANJANE, TAWA SOYAYYAR,

RASHIN HAIHUWA, se YAR DAMFARA, amma fa Anjane, Rashin haihuwa da yar damfara na kudi ne, free pages din na tura miki, in kin karanta sun miki se ki siya paid pages din".

Nawal dake danna waya tace

"Ai ni har nayi searching din ta a Wattpad nayi following, har ma na ci karo da wani bonanza da tayi, wai gaba daya paid books din a ₦1000 instead of ₦1400, bari kiga in Maza in siya, kema Nu'aimah ki siya a bonanza din, ragin ₦400 ai ba wasa bane a wannan marrar ".

Dariya muka yi wa Nawal nace to, take kuwa nayi searching din ta nima nayi following, na kuma dauki number wayar ta da ta aje na mata sallama a watsapp, ganin bata online se na kashe data na nima na fita dan magana da ita ne dama ya kai ni.

Ganin dalibai sun fara taruwa yasa duk muka watse kowa ya nufi abin da yake koyarwa.....................✍️.

BONANZA BONANZA BONANZA!!!

Ina kuke ma'abota so da kaunar littattafan ouummey?, Albishirin ku!, To ga dama ta Samu!!!.

Kamar yadda kuka sani paid books din ouummey guda uku ne,

ANJANE ₦400
RASHIN HAIHUWA ₦500
YAR DAMFARA ₦500

Dukan su sun kammala a document, sedai a maimakon ku biya ₦1,400 dan samun su, yanzu zaku biya ₦1000 ne kacal ku same su duka ukun!!!.

Wannan bonanza is valid to month ending kamar yadda masoya suka yi pleading a mayar, a hanzarta a sharbi rahusa, wannan duk kauna ce daga ouummey zuwa gare ku masoya❤️.

Ga me bukata, should chat my up through 09013101854,
Ouummey 📚✍️.

Vote
Comment
Share fisabilillah.

Ouummey 📚 ✍️.

Ouummey 047  [ 16/07/2024 8:53pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Ouummey
Free book!!!

Ouummey 047

Page 4️⃣7️⃣

______________________Karfe biyar muke tashi a makarantar, sedai yau ganin hadari sosai ya tufke ga iska ana yi yasa dole aka sallame su da wuri saboda yan nesa, dan ruwan nan in ya balle ba'a san ranar tsayawar sa kasancewar muna karshen watan July ne.

Mu ma yau bamu zauna an mana jari na duk muka yi sallama aka watse, sauri nake yi na kai gida saboda kar ruwan ya dake ni, ina son in ga ana ruwa sosai sedai bani da damar shiga yanzu zazzaɓi ya rufe ni.

Addu'a ta bata karbu ba dan ko zagayawa ban yi ba ruwan ya kece da karfin sa, wata irin ajiyar zuciya na sauke lokacin da sanyin ruwan ya ratsa hijab dina zuwa cikin riga ta ya sauka a fata ta.

Se kawai na rage saurin da nake yi na kankame jaka ta dan kar ruwan ya shiga ya taba min litattafai, kafin in kai gida na jike sharkaf ina ta diga kamar wata kaya, ban shiga falon a haka ba dan zan lalata musu rug, se na tsaya daga kofa na shiga kwalawa Aunty A'i kira, karfin ruwan ya sa bata ji da wuri ba dan duk suna bedroom din su, da sauri ta fito tana kallo na cikin damuwa

"Me yasa zaki taho a ruwan nan bayan kin san ruwa baya miki ta dadi Aimah?".

Baki na rawa na saki murmushin karfin hali

"Wallahi a hanya ne ya tare ni Aunty A'i, ko kafin na nemi gurin fakewa na jike shiyasa kawai na karaso".

Da sauri Aunty A'i ta juya tana fadin

"Ina zuwa".

Daki na ta shiga ta dauko min kaya, doguwar rigar wani yadi ne me kauri se hula da rigar sanyi har da karin karamin bargo.

"Shiyasa nake son ki Aunty na, bari na maza na canja".

Se da na bude kayan daga nannadewar da ta musu naga har da undies, na sake sakin murmushi na shiga canja kayan a cikin corridor din, ina gamawa na lulluba bargo na na kwashi kayan zuwa daki na.

Se da na kai toilet na saka kayan cikin washing machine, undies din kuma na wanke na shanya sannan na fita zuwa kan bed na kara jan babban duvet na kara, dumin da ya shiga ratsa ni maimakon sanyin da na fito daga ciki yasa nan da nan bacci yayi gaba dani.

Ranar kwana aka yi ana ruwa, be dauke ba se karfe goma saura, mu dai muna gida mun hade cikin kayan sanyi, yau riga da wando na saka na sanyi pusha pink, twins ma na sanye da nasu se dai su baby pink ne, Nene ce bata saka ba tace ita ta saba abinta, Aunty A'i ma rigar sanyi kadai ta sa, ban biye ta ba na sawa Safar na ta irin namu, ita kuma dark pink.

Mun yi kyau sosai gwanin sha'awa, muna zaune muna karyawa a falon cikin farin ciki, hular kai na me kyau ta teddy me gashi sosai na dan tura baya kadan ina cewa

"Maganar gaskiya Aunty A'i you're a good chef, ban da Hajiya Yayah ko Mama se ta sallama miki a bangaren kitchen".

Dariya suka yi gaba daya, Nene na cigaba da tsotsar kashin hannun ta tace

"A'i sa mata waigi kar ta fadi dan santi ne take yi, to ba ma dole tayi santi ba ta ji girki me suna girki, su suna nan suna fama da feleke, taji farfesu cike da daddawa ina ba zata yi santi ba".

Murmushi nayi kawai na cigaba d acik abu na dan ba da wasa nake ba yayi min dadi, muna gama wa na mike na wanke hannu na, twins da ke gefen Nene custard ne ta ke basu se cookies, hankali kwance kuwa suke cin abin su, na zuba musu ido cike da sha'awa da jin dadin wai duka wadannan nawa ne, Allah Al Hakeem.

Seda ta gama ba su na gyara wajen dan ban bar wa Aunty A'i aiki ita kadai, muna gama wa Nene ta jawo Radio din ta ta kunna labarai, ni kuwa se na kishingida tare da ɗaukan waya ta na shiga wps, jerin litattafan da Sadiya ta tura min ne jiya, kallon su nake da son zabar wanda zan fara da shi, daga karshe dai se na fara da Ba ni da laifi dan ba ga be kai su yawa ba, haka kuma sunan ya dauki hankali na.

******

A hankali yake bin ko ina da kallo cike da wani irin yanayi da baze iya fassarawa ba, zuciyar sa matsewa take a kirjin sa cike da matsananciyar kewa, kewar ta yake yi kamar yayi hauka, san ganin ta yake yi kamar ya fita a guje, shiyasa wannan karan be tsaya sauraren kowa ba ya take dokar da aka sa masa ya fito neman ta, kuma insha Allah baze je ko ina ba se ya ganta, ba gani na normal gani haka ba, no gani irin ganin da shi kadai ya san wanne ne.

A sannu ya furzar da huci daga bakin sa, ya samu gefe kadan ya daga waya ya kira ta, sannu a hankali har ta fara ringing zuwa sanda ta dauka a sanyaye tare da gaida shi bayan ta masa sallama

"Amin waalaikumussalam warahmatullah, kin tashi lafiya?, How's my princess?".

Cike da raunin da yayi wa zuciyar ta katutu ta amsa shi can kasa

"Lafiya lau alhamdulillah ".

Se ta sake lowering voice din shi, full of care and affection yace

"Ya jikin?, Hope ba kya jin komai ".

"Babu komai hubby, se tarin so da kaunar ka tare da dimbin kewar ka dake neman hana min zaman lafiya".

Ya dan yi shiru kadan se kuma yace

"Gaba daya fa ko awa goma ba'a yi ba da rabuwar mu, har kin yi kewa ta irin haka?".

Se da tayi wani dan murmushi me cike da ma'anoni sannan tace

"Da a san raina ne ko da da na sakan daya ba zaka yi wa idanu na nisa ba Abban princess, ba zan gaji da fada maka ina maka wani irin bahagon so ba Masdooq, son da nake naka ni kai na ya na ban tsoro wallahi, kishin ka kuma har ji nake kamar zan haukace in na tuna bayan ni kana da wata matar, shi ne kuma ya tunzura ni nayi abinda nayi watannin baya da ba zan gaji da baka hakuri ba, ba hali na bane ban kuma saba ba, matsanancin kishin ka da nake yi da kuma zuga ne suka tunzura ni, dan Allah ka taimaka ka yafe min baban princess ".

Wani irin matsanancin tausayin ta ke ratsa Masdooq, yayi soyayya a baya, yana kuma cikin ta har yanzu, ko da ya so barin ta a baya ita taki barin sa, ya san yadda ake ji in aka ki mutum, ya kuma san yadda aka ji in mutum ya rasa wanda yake so, shiyasa da ya dauke mata wuta ya fita harkar ta se ga ta tazo tayi confessing duk abinda tayi wa Aimah, bata kuma rage ko daya ba.

A lokacin ya ji haushin ta matuka, ya kuma yi fushi da ita ba kadan ba, sedai be yi tunanin fushin sa ze iya fitar da ita daga hayyacin ta ba se da ya same ta cikin wani hali bayan kwanaki hudu kacal da fara fushin, dole ya aje komai ya kai ta asibiti, a can ya jiyo abinda ya gigita nutsuwa da duniyar sa, ya kuma ninka tausayin ta a ran shi ninkin ba ninkin, da farko be yadda da likitan ba, shiyasa ya dinga yawo da ita daga wannan asibitin to another.

Sedai ba yadda ze yi da rubutun ƙaddara, a duk inda suka je abinda ake tabbatar masa kenan wato Sa'adah na dauke da BLOOD CANCER!!!.

Ya sani a baya tayi fama da Cancer mahaifa, amma tun a lokacin bisa amincewar ta yasa hannu aka yi mata aiki a ka cire mahaifar dan gudun yaɗuwar ciwon, ashe dai ta baya ta rago su ka yi tun da gashi yadda abin ya kasance yanzu.

Kasa fada mata yayi, yayi ta fama da abin a ran sa, danuwar hakan ya sabbaba masa rashin nutsuwa da kwanciyar hankali, ta yadda duk wanda ya dube shi ya san da hakan, sedai kowa yana masa kallon wanda ke cikin damuwar ciwon Aimah da a lokacin na har ta fara samun sauki, eh ya damu da hakan amma fa ciwon Sa'adah sha kundum ne, ciwo ne me barazanq ga rayuwa, anytime za'a iya samun mummunan labari.

Ranar da Sa'adah ta gaji da ganin sa cikin wannan hali ne ta same shi a dakin sa after Isha, yayi zaune kan bed hannayen sa tallabe da kundin sa cikin tagumi, tsabar nisa da yayi a tunani be san ma ta zauna ba se da ta dora hannayen ta kan kafadun sa, ya juyo ya zuba mata ido cikin kallon da baya iya boye dimbin tausayin shi gare ta, ta sauke hannayen daga kafadun sa ta riko tafin hannun sa tare da sunkuyar da kai, kusan minti biyu suka yi a haka

"Ka kwantar da hankalin ka pls ya Masdooq, zuciya ta bata min dadi in na gan ka cikin damuwa, na san ina dauke da wannan ciwon tun lokacin haihuwar Aimah, rashin lafiya da yawan tarin jini da nake yi ya firgita ni, I was thinking ko nima na samu heart problem ne ban sani ba, so bayan na shiga na mata Barka se na wuce ganin Dr, hankali na ya tashi, I feel down, I feel useless and more of that jin irin cutar da nake da, nayi kuka sosai, na shiga tashin hankali, na birkice, na sani yawancin mutane will think ko haihuwar Aimah ne, kuma ba haka bane, tashin hankali na ya fi gaban haka, sedai what do I do with destiny?, I can't change it and u can't correct it, but I can accept it, so se na karbi ƙaddara ta, na godewa Allah for all the days na baya, and i asked of more a gaba, just to live with you, love you and pampered you.

Kai ma ina so ka kwarara kan ka pls hubby, accept our destiny and think of how to pass through it, ban roki Allah karin kwana dan na cigaba da ganin ka a haka ba, face dan kokarin wanzar da farin ciki a gare ka, da kuma gyara kuskure na na baya.

Masdooq na zalunci Aimah, na cutar da ita through many ways, haka kawai tana dakin ta zan bi ta na fada mata maganganu, all I want is to see her a damuwa da bacin rai, kishi ya rufe min ido bana ganin daidai, na san ka sani amma zan sake maimaita maka, wallahi ina tsananin masifar kishin Aimah, fiye da duk wata mace a rayuwar ka ko wadda zata shigo a gaba, ban san me yasa ba, sedai na bar shi as dan kana son ta, son da ya hana maka ganin nawa soyayyar gare ka, na dauki zuga na zubar da kyakkyawan hali na da ake ta min shaida da shi, Aunty Luba ta bani kyakkyawar shawara akan zuciya ta ingiza ni na tankwabar thinking of ai Aimah ta fi so so ba zata bani good advice ba.

Na bar ta da yunwa, na mata sharri dan hatta batun da ya kai mu gaban su Baba itace da gaskiya, tun farkon batun marin kitchen ma itace da gaskiya, after ta mare ni na zubar da mai ta bi ta fadi dan ta ji ciwo, and ta jin dan ina ganin yadda take dingishi, but hakan duk be sa naji sauƙin abinda nake ji a kan ta game dai kai ba, ban tashi realizing na bar hanya ba se da Dr ya sanar da ni I've limited days to live, a lokacin ne senses get into my skull, I was so mad da ba kasa gane shi da so jarraba be daga Allah kamar yadda ya jarrabe ni da son ka, dake kai kana da tunani da rabo se Allah ya baka kyakkyawan tunani, despite I not being your love and choice you accept me, kana sauke duk hakkin dake kan ka without tuna cewa ga yadda auren mu yake, se ni ce na kasa gane kowane bawa haba rayuwa ne a doron kaddarar sa, na kasa karbar kaddarar dawowar Aimah cikin rayuwar mu, na bari shaidan yayi wasa da tunani na, na biye wa san zuciya da san rai wadda na sani, ka sani, ina da cikakken yakini da Aimah ce ba zata yi hakan ba, ko da bata so na ba zata bari ka take hakkoki na ba, haka ba zata nufe ni da cutarwa kamar yadda na mata ba, a yau ni Sa'adah da har yau ban dena kishin ta ba amma hakan ba ze hana na bada shaidar gaskiya a kan ta ba cewa tana da kyakkyawar zuciya, she've a good and pure heart, ina kuma shawartar ka da kada ka bari ta kufce ma, do all d possible best of yours ka dawo da ita rayuwar ka, and know one thing, Aimah tana son ka so na gaskiya Masdooq, yarinta da shaidan suka sa ta kasa gane hakan har komai ya faru, sedai fa duk wanda ya zauna da ita a baya zaman minti biyu ze san babu wani da namiji a rai da rayuwar ta face kai, dan haka kar ka hukunta zuciyoyin ku Masdooq, fight for your love, fight for your

peace, bring her back and make her yours forever, ko ba komai uwar ƴaƴan ka ce, jinin ka da baka da sama da su"....................✍️.

Vote
Comment
Share fisabilillah

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 048  [ 16/07/2024 8:56pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Ouummey
Free book!!!

Ouummey 048

Page 4️⃣8️⃣

__________________Tun da ta fara maganar yake sauraren ta da dukkan nutsuwa da zuciyar sa, abin ya dake shi matuka, blood cancer fa ga Sa'adah, and after that wai her days q limited, a lokacin da likitan ke sanar da shi haka ya ga Bala'i dan kuwa masifa ya shiga zubawa yaba fadin in shine da ran ta ya kashe ta yanzu mana, haka kuma yaki tsayawa ya saurari ragowar bayanin likitan dan in ya fadi wasu adadin ranaku ga Sa'adah din zuciyar sa na iya bugawa.

A hankali ya matse hannayen ta cikin nasa

"Me yasa kike cire princess daga jerin ƴaƴa na bayan ita ce babba a cikin su?".

"Kar mu yaudara junan mu Masdooq, na sani dole princess ta amsa sunan ƴa gare ka tun dai ai kai baban ta ne, amma fa ba mahaifi ba".

Da sauri ya dago idanun sa da suka rine na damuwa, rashin bacci da rashin kwanciyar hankali

"Kar ki fara haka Sa'adah, ni dake kadai muka san wannan, me yasa ba zamu binne ba kamar yadda muka yi planning years back?".

"Ba ze boyu ba Masdooq, zancen duniya ba ya taba buya, ko da kuwa ace cikin kasa muka shiga muka yi maganar muka birne tabbas watarana wani ze hako. Ni da kai mun sani princess ba yar cikin mu bace, ba ma ni da mahaifar da zan yi conceiving balle na haihu, mun karbe ta ne a asibiti a India after mutuwar iyayen ta wanda suka kasance Africans aka kuma nemi dangin su aka rasa, hakan ba ze tava canja wa ba Masdooq, princess will forever be our daughter but not biological daughter, ina kuma shawartar ka da mu sanar da magabatan mu ko dan abinda ka iya zuwa yazo nan gaba, babban abin farin ciki na shine na shayar da ita, na dandana motherly feeling, Allah ya Ara min wannan damar, and ya bani wata ta yi mata tarbiyya, duk da ban sani ba ko tafiyar mu zata yi nisa tare amma ki ba komai hakan ma I'm grateful, forever grateful ya Allah, and you Masdooq, bana tunanin rayuwa would have been beautiful with another Man not you, and ina godiya ga Allah for this also".

Kasa ma sake ce mata komai yayi a lokacin, se kawai ya janyo ta jikin sa ya rungume yana sakin ajiyar zuciya a kai a kai, itama ta rungume shi tana hawaye, babu worst feeling kamar sanin kana dauke da deadly cuta, and the worstest kuma sanin kwanakin ka a irge su ke, ban da karfin imani, tawakalli da komawa ga Allah babu abinda ya hana zuciyar Sa'adah bugawa , amma kamar yadda ta fada ne ta godewa Allah ta kuma karbi ƙaddara, fatan ta in ta tashi tafiya Allah ya bata me sauki ya kuma sa ta cika da imani.

Kamar kuma kar a san da ciwon, shikenan se jiki ya rikice, bata taɓa wuni lafiya kalau, ban da tarin magungunan da take sha kullum, ga karin jini da a tsukin se da aka mata so biyu, ba komai ne ya rikita jikin ba se fargaba da damuwa da suka mata yawa, daga karshe dai dole ya dauke ta suka bar kasar da sunan ya tafi yin wani aiki.

Princess a gidan Hajiya Yayah ya bar ta dan can Mama ta koma da zama saboda gudun barin ta ita kadai a gida damuwa yayi mata illa dan ba kadan ba ta saka lamarin Aimah a ran ta.

Sun yi yawo sosai, farko India suka je ta ga Dr, aka yi the needful aka sallame ta bayan ta kwanta a asibitin for two months, daga nan suka wuce Dubai suka yi a month, Japan suka yi two weeks, France suka yi two months, Russia suka yi one week se a karshe suka wuce Saudiyya suka yi umara, basu dawo ba se ana saura sati daya sallah dan a can suka yi azumin su gaba daya.

Alhamdulillah lafiya ta samu yadda ma ba su yi zato ba, haka kuma da suka je Saudiyya ta gan ta gaban ka'abah se ya saki duk wani abu dake ranta a lokacin, tayi kuka sosai a jikin ka'abah na duk wani damuwar ta, ta godewa Allah duka ni'imomin sa gare ta kana ta nemi yafiyar zunubai da kura kuran ta, daga nan ta ji sauki sosai a ranta, haka kuma ta kudure neman yafiyar Aimah bisa zaluncin da ta mata, in har ta yafe mata bata jin tana da sauran damuwa,

dan ban da Aimah zata iya rantse wa bata taɓa cutar da wani tana sane ba, da gaske tana da sanyin hali, nutsuwa da fahimta, sedai kishi yasa ta bari shaidan yayi wasa da hankalin ta wanda Allah ya fargar da ita da wuri.

Dawowar su aka yi sallah, kowa a cikin su Hajiya Yayah da su Ya Salman yake kawai suke, Aimah ce tsaye a rayukan su, sedai Nene ta kafa ta tsare dan Allah ya isa ta yi wa su Hajiya Yayah kan duk suka bari munafukan ƴaƴan su suka zo mata wajen Aimah, Masdooq kadai ta cire amma shima tace bata amince ya zo yanzu ba, da kan ta zata neme shi in lokaci yayi.

Wannan yasa babu wanda yayi yunkurin bin su Ethiopia, sedai kira fa kan kamar zasu fasa wayar Nene, su suke karar mata da caji saboda kiraye kirayennsu, da suka addabe ta se kawai ta sa ka aka mata blocking din su gaba daya, har su Hajiya Yayahn, daga lokacin kuma ta daura dambar dena daukan New number ko daga ina ne in dai number Nigeria ne.

Satin su biyu da dawowa yana shirye shiryen tafiya wajen Aimah bisa shawarar Sa'adah se kuma urgent tafiya ya kama shi daga wajen aikin sa, ko sallama be yi wa Sa'adah ba se a waya ya wuce, ba kuma su samu kan su ba se after two weeks, a jigace ma ya dawo sedai duk hankalin sa na kan su ita da yaran su, duk da yana ganin yaran daily safe da rana amma ai ita bata bari ya gan ta, hakan kuma na cikin abinda ke kara masa damuwa day by day, ga kuma kewar ta da ke addabar zuciya da ruhin shi.

A yau da yake tsaye a airport din babban birnin kasar Ethiopia ji yake kamar yayi fiffike ya gan shi a gidan, zuciyar sa na matsewa da yanayin da shi kan sa ba ze iya fassarawa ba, ita kadai yake bukatar gani a lokacin, ita kadai ba da kowa ba.

Ya mayar da wayar sa aljihu bayan sun yi sallama da Sa'adah, hannayen sa zube cikin aljihun wandon jikin sa ya shiga takawa zuwa inda ze sami abin hawa, with each takun da yake yi zuciyar sa na sake cika ne da begen ta.

A gaban gidan keke napep ya sauke shi, ya bashi kudin sa ya wuce amma ya kasa karasawa gate din gidan, yayi tsaye yana karewa gidan kallo bugun zuciyar sa na hauhawa, tuntuni ya gane Allah ya jarrabe shi da jarrabawa me zafi dan kuwa so da kaunar Aimah be shige shi da wasa ba, a ko ina na jiki, jini da zuciyar sa yake jin ta, ba ze iya fasalta irin girman so da kaunar ta a ran sa ba, amma ze iya cewa be taba ganin wani da ke son wata irin soyayyar da shi Masdooq ke wa Nu'aimah ba!.

Yafi karfin minti talatin q tsaye kafin ya shiga daga kafar sa da ta masa nauyi ya shiga kusantar gidan, be ankara ba se ganin shi yayi gaban gate din karami me kyau, yasa hannu da niyyar kwankwasawa se kuma kofar ta motsa alamun a bude take, ya daga hannun sa ya kalli lokaci, karfe sha daya da rabi na safiyar ranar Alhamis ne.

A hankali ya tura karamar kofar jikin gate din, tana budewa kuma ya saka kafar sa cikin compound lamarin da ya haddasa masa matsanancyar faduwar gaba.

Se da ya tsaya ya karanta addu'o'i sosai sannan cike da karfin hali da san nuna jarunta ya shiga takawa zuwa kofar falon.

Yana zuwa itama ya kai hannu ya tura se ta bude, da sallama kasa kasa ya sa kai cikin falon, sedai da alamun masu gidan sam ba su ji shi ba.
Ya kalli Nene da ta ba wa Radion ta amanna idanun ta a rufe tana saurare, se kuma ya mayar da duban sa ragowar kusurwar dakin dan ganin ta ina ze hango ta ko ƴaƴan sa.

Idanun sa na fadawa kan ta zuciyar sa ta wani harba har seda ya dage kirjin sa dan ji yayi kamar zuciyar zata fado ne, ya lumshe idanun sa cike da farin cikin ganin ta, a sannu cikin sanda ya karasa inda take, gaba daya hankalin ta ya dauku ga abinda take yi a waya da be san mene ba.

A sadade ya kai bakin sa daidai kunnen ta bayan ya gama kare mata da kallo da jiran ko zata ji zuwan sa sedai shiru, cikin sassa yan sauti me tafe da bege, kauna da tarin kewa yace

"Baaaarbieeeeee".

******

Karatu na nake yi cike da nishadi, gaba daya na bada hankali na ga wayar, tausayin Badar da irin kaddarar ta ya cika min zuciya ta, wato ita dai ƙaddara kowa da irin tasa, ita kuma tata kaddarar ta aure aure ce, rabuwar kuma batare da wani sanadi ba, ga shi al'umma da iyaye sun mata wata fahimtar ta daban, wanda ta sani ba zasu kai ta jin radadin mutuwar auren ba, ni ko da Ni na nemi saki da kaina amma naji zafi da dacin sa balle ita da bata san hawa ba balle sauka, a kanann shekaru kaddarar aure aure ta same ta, lallai Badar ta ga rayuwa, kuma ina so naji yadda labarin nata ze karke, se kuma naji wai dama nima na bada labari na a rubutu kamar dai yadda Badar tayi da alama, amma dai bari na gama karatun, kowane tunani yazo daga baya.

Ban ankara ba, ban lura ba se jin wani sassanyan sauti nayi a kunne na, cikin kira na da sunan da mutum daya ne ya rada min, shi kuma kadai ke fadar abin sa, sunan da akalla na shafe shekaru biyar ban ji shi cikin kunne na ba.

"Baaaarbieeeeee".

Sunan ya ratsa cikin kunne na ya anya cikin jini na ya zagaye kana ya wuce zuciya ta, daga nan kuma ya zarce ƙwaƙwalwa ta, ya tilasta min lumshe ido batare da na shirya ba, kewar sunan da me fadar sunan ba bijiro min.

"My Honeybun".

Na sake jin shigar dayan mattatarar sauti na, a yanzu kuwa zuciya ta ce ta doka, irin dukan nan me karfin gaske, gudun jini na ya karu, na shiga bude idanu na a hankali cike da tsoron me zan tarar, to ko dai Nene ke tsokana ta?

Amma ai bama irin wannan wasan da ita, hasali ma Muryar nan bata ta bace, ta shi ce shi ruhi na, mahadin rayuwa ya, uban ƴaƴana, mijina kuma yayana.

_'to ko dai Dr Bee'at ke neman tsokana ta tun da dama tace zata zo?_.

Duk da zuciya ta ta san wannan tunanin karya ne a kuma hagunce amma haka na tilasta zuciyar tawa yadda dan wanda nake tunanin sam babu abinda ze kawo shi nan, yana ganin ƴaƴan sa a sanda duk yaso, yana tare da matar sa da yake so, ga kuma iyaye da yan uwan sa, to zuwan me ze yi gare ni bayan ya riga ya rufe babi na?.

Se na bude ido na juyo saitin da naji mutum a tsaye ina cewa cikin sanyin murya

"Amma dai kin san kin tsora ta ni ko Dr, tukuna ma a ina kika san wannan sunan da a sani na mutum daya ke......".

Magana ta ta katse lokacin da muka yi locking eyes, ido cikin ido muka yi dan shi dama tuni duban sa na kai na, in disbelief na lumshe ido dan na san ganin ido ne kawai, ina bude ido zan ga babu shi ya baje, sedai ko da na bude idon se na sake cin karo da fuskar sa me yalwar kwarjini da haiba, drunken eyes din sa a shanye a kai na baya ko kiftawa, Ni se nayi blinking ido na na sake yi har so uku amma duk ina ganin sa, na ambaci sunan sa da yardarwa kai na na fara haukace wa tun da har na fara gane gane ido biyu

"Yaaa Masdoooogq".

"Uhmmmm Barbie".

Yace cikin wani irin sauti, ai da sauri na hantsilo daga kan seat din har ina buge goshi na, shima se ya mike tsaye sosai, Ni kuwa ina mikewa na shiga ja da baya baki na na rawa na shiga nuna shi

"Wwwaaii....da..dda..dagaske...kkkkk..aine??".

Maganar ta fita daga baki na a rarrabe, maimakon amsa se ya shiga takowa zuwa inda nake, ni kuma ina ja baya jiki na na bari dan firhicij ganin sa, mamaki da kuma rudewa, ban san na kai kofar dakin ba se ji nayi kawai kofar tayi baya na shige dakin, kafin na gama daidaita kai na daga kokarin faduwar da nayi har ya shigo, abin da ya sake ruda ni be wuce ganin ya sakawa kofar lock ba...................✍️.

Vote
Comment
Share fisabilillah

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 049 [ 17/07/2024 7:26pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Ouummey
Free book!!!

Ouummey 049

Page 4️⃣9️⃣

______________________Har na bude baki zan yi magana se kuma na fasa, internally nake fadawa kaina _'ke Aiman, daidaita kan ki da nutsuwar ki mana, kin manta waye a gaban ki ne?, Me kike tunanin ze miki da zaki rude haka?, Wa ya sani ma ko maganar yara ze miki ke kuma kika tafi wani tunanin da da zai ji se ya kwasa miki mari_'.

Se na shiga daidaita kai na, na haxihe firgici na da rudewar ganin sa, kana na danne tsallen murna da zumudin ganin sa da zuciya ta ke yi na gyara tsayuwa ta tare da nema bakin bed na zauna

"Ina kwana baban princess?".

Na gaida shi can kasa fuska ta ba yabo ba fallasa, be amsa ba se da ya tako shima ya zauna gefe na har kafafun mu na gugar na juna, na dago na dan kalle shi kana na mai da kai kasa kamar wadda ta ke gaban suruki.

Gaba daya ji nake kamar ina tare da stranger ne ba wai Ya Masdooq sweetheart dina ba, ya kafe ni da ido yana nazari na, ganin ba shi da niyyar tafiya se nace

"Nenen na falo, twins kuma na wajen Aunty A'i a daya dakin ".

A sannan ne ya ka da baki yace

"Na ga Nene sanda na shigo amma ba wajen ta na zo ba, twins ma ba wajen su na zo ba shiyasa ban neme su ba, I'm here to see my wife, hug her and kiss her, am here to Express how badly I miss my wife".

Cikin mamaki na dago ina bin shi da kallo, matar sa fa yace yazo gani, to ko dai sun yi da Sa'adahn zata zo nan ne shine ya biyo daga wata tafiyar?, Amma kuma ta zo nan tayi me?.

Take wata zuciyar ta bani amsa da _'Kakar mijin ta ce fa, maybe zata zo gaishe ta ne'_.

Da wannan tunanin na dago kai na dube shi cikin tabbatarwa

"Amma kuma ai bata zo ba, maybe kun yi sabani ko se zuwa anjima zata karaso".

Na bashi amsa zuciya ta na min daci, sedai ban bar abin ya dore ba na kore shi sanin ai nima na ce ba zan koma masa ba, then kishin na meye.

Ya Masdooq ya kalle ni tare da sakin tattausan murmushi yana rayawa a ran shi wato dai wautar autanci ba ze taba barin Aimah ba.

Ban ankara ba se ji nayi yasa hannu ya fizgo ni jikin sa, na ware idanu na akan fuskar shi shima se ya ware min nasa, ya subhanallah ai da sauri na rufe nawa kirji na na dokawa, ya sunkuyo da fuskar sa kan tawa ya hade goshin mu waje daya, haka dogon hancin sa na gogar nawa

"Wace matar ce muka yi sabani bayan ta gaba na, watan ta bakwai fa a kasar nan yanzu, to ina ta je da zan jira ta har ta karaso?".

Duk yadda kasalalliyar muryar sa ta kassara min jiki haka na bude baki nace

"Wai kana nufin ni?, Ko dai wata matar gare ka ban sani ba?".

Cikin sigar rada ya rage Muryar sa

"Babu mace da zata yadda ta auri mijin tace, dan haka ke din dai nake nufi Barbie".

A raunacen da ya kashe min laka na janye jiki na na ja baya na zubawa fuskar sa ido, yayi mulmul abin sa ya kara kyau, kwarjini da haiba, ga sajen shi da ya zagaye kyakkyawar fuskar sa da yana cikin abinda nake so a tare da shi

"Abin mamaki, ko da dai ba lallai ya zama na mamaki ba, ban taba zaton after all that happened zaka dube ni a matsayin kanwa ba, sedai yau ka karya ta hasashe na, na gode sosai".

Da rashin fahimta ya kalle ni se kuma ya furta da bakin sa

"Ban fahimci zancen ki ba".

Se da na sake kwarara kai na sannan na iya cewa

"Ina nufin kenan kana so kace har yanzu kana so na a matsayin kanwar ka?".

"Ko a da ban taba kin ki ba, haka matsayin ki be sauya ba, sedai na baki space ne dan ki samu cikar burin ki".

Na sunkuyar da kai cikin jin dacin tuno baya, se kuma na dago idanuwa na taf da hawaye

"A baya ban samu wannan damar ba, amma a yanzu ina amfani da wannan ina rokon yafiya da afuwar ka, dan Allah kayi hakuri ka yafe min Ya Masdooq ".

Da sauri ya riko ni tare da sa hannu ya dauke hawaye da suka fara sintiri kan kunci na

"Komai da ya faru a baya ina so mu bar shi a bayan, dan Allah ki cire komai a ran ki kamar yadda na cire, kowane bawa yana tafiya ne aka tafarkin kaddarar shi, so mu wannan ne kaddarar mu kin ji wifee".

Se na gyada kai na dauke hannun shi daga jiki na na ja baya

"Sister.. kanwa not wife Ya ".

"Kamar yaya?".

Na koma na zauna dan bana san tsayuwa

"I mean ni kanwar ka ce, ba mata ba, mata daya gare ka wato Sa'adah, so kar ma ka fada a gaban ta balle ta hana ka abinci ".

Na karashe jokingly, na dan gifta shi da nufin bude kofar dan fita nace

"Ko zamu je ka ga yaran?".

Hannu na ya riko ya dawo dani gaban sa

"Yaushe aka raba aure tsakanin mu ban sani ba?".

Cikin gabuntar autanci na da kan taso sa'i da lokaci nace

"A'a ba'a raba ba amma ai za'a raba din ne, maybe ma yanzu ka fin ka tafi?".

Na karashe da sigar tambaya, se naga ya canja yanayin kallon sa gare ni fuskar sa dauke da wani miskilallen murmushi

"Nene ce tayi wannan decision din kowa?".

"No ba ita bace, nice and it's for your own good not mine".

"Uhm so kece, kuma fa hakan yayi".

Na dago na kalle shi, wato rashin son har ya kai haka kenan, se kawai na hadiye na gyada kai na sake juya wa dan tafiya, wannan karon ma janyo ni yayi yace

"Rufe idon ki ga wani abu nan zan cire miki".

Cikin yarda da shi na rufe din, a hankali kuma naji saukar hannun sa kan fatar ido na, na sauke ajiyar zuciya a boye shi kuma tasa ta fito fili.

"An gama".

Yace, se na bude idon na sauke kan nashi se kuma na janye da kudirin barin wajen dan yadda zuciya ta ke bugu ina son kebancewa dan daidaita kai na, ware ido nayi ko nace zare su jiki bakon al'amarin da ke wakana tsakani na da Ya Masdooq a karo na farko cikin zaman mu na biyu da shi, bakin mu ne ya hade waje daya yana kissing kuma idanun sa a bude tar cikin nawa, da sauri na janye nawa na shiga kici kicin kwace wa amma ya tsaurara rikon.

Daga karshe ma se ya sake min kugu ya juya dani jikin bango Ya matse hannun sa kuma tallabe da both cheeks dina ya na sauya salon sumbar.

Gaba daya jiki na yayi sanyi, kafafu na suka kwashi rawa, na shiga kokarin zubewa amma se ya tallafe ni da jikin sa ya hana hakan, kissing dina yake yi yana shafa fuska ta da tusa hannun sa

cikin gashi na, se kawai na fara hawaye dan kukan ma babu bakin yi.

Kusan minti uku muka yi a haka kafin ya zare bakin sa daga nawa amma be raba fuskar mu ba, ni kam se na sulale kasa ina fashewa da kuka da sautin sa ke fita kasa kasa.

Me yasa ze min haka, me yasa?, Be san yadda nake fighting kai na bane akan shi? Ko be san yadda son s d kaunar sa suka min illa ba.

Shi kam daga tsayen yake kallo na, sedai ganin kukan nawa ba me karewa bane se ya tsugunna gaba na ya tallabe habar da hannu daya, dayan kuma yasa ya lakato hawaye na

"Why the tears? Kukan na menene Barbie?".

"Na abinda ka min ne bayan ni da kai rabuwa zamu yi".

Nace cikin crying voice, se ya matso jiki na sosai ya tallafo ni zuwa kan kafafun sa kana ya saka hannu ya dago haba ta ya rike idanu na cikin nasa

"Har abada...har abada babu rabuwa tsakanin mu Barbie, ni da ke are meant to be, together we will see today, tomorrow and forever, kar ki sake ce min zamu rabu, dan you're my girl and you'll forever be, tashi muje ki raka ni wajen yaran".

Na dago na kalle shi seeing how serious he's, sedai be san irin shirin da nayi bane, in a shirye yake nima haka, duk da alkawari nayi wa Abba kan yafe masa duk laifin sa tun kafin yayi min, shiyasa ma ban rike shin ba na watsar da komai, ina kuma tuna yadda Abba yace burin sam zama mata da miji na har abada sedai bana tunanin hakan ze samu.

Na dandana zaman rashin so na tsayin shekara ba wata daya, illar hakan ba se na fada muku ba dan ban da Allah ya kubutar da ni da tuni ina can ina gararamba akan bola na haukace, so ko da na yafe masa komai bana jin har abada zan kuma zaman rashin so, sedai ko ƙaddara.

Ban amsa shi ba dan bana san jan zance bayan muna rufe ne a daki mu biyu, se kawai na bude kofar saboda mukullin na jiki, na fita ya biyo bayana, na kalli Nene da har lokacin Radio din ta na kusan ta, sedai da alama bacci ne yayi gaba da ita ba wai saurare take ba.

Gaban dakin Aunty A'i na tsaya nayi knocking, daga ciki tace a shigo, se na bude kofar na ja gefe ina bashi hanya, cikin karamin sauti nace

"Baban twins ne yazo ganin su Aunty".

Se kuwa Aunty A'i ta zabura ta gyara zama tana saurin fadin

"Lale marhaban da Musaddiqu, sannu da zuwa sannu da zuwa".

Cikin sakewar da nake mamakin yaushe suka san juna haka ya shiga dakin yana fadin

"Yauwa Aunty A'i, fatan mun same ku lafiya".

"Wallahi alhamdulillah dan albarka, ya wajen su hajiyan?".

"Suna nan lafiya Aunty".

"Masha Allah, bari a kawo maka ruwa da abinci ka kwaso tafiya, sannu".

Daga haka Aunty A'i ta yunkura ta fita, ban tsaya ba na bita kitchen dan ina bukatar clarification akan confusing dina da suka yi.

A can na tadda ta ta na jera abinci kan babban tray, ga fruit da alama yankawa zata yi, na karasa kusa da ita na dauki wuka na shiga yanka fruits din bayan na wanke

"Ni kam a ina kika iya Hausa ne Aunty, na dade dama ina so na tambaye ki se dai na share, yau kuma jin kina lale marhaban irin na tsofaffin Hausawa yasa na kasa jurewa se da na tambaya".

Batare da ta bar abinda take yi ba ta shiga bani amsa

"Mun yi zaman Nigeria sosai saboda kasuwanci da ya kai baban mu can, and again wannan arean da muke gaba daya hausawa ne, yawancin wanda aiki ko kasuwanci yake kawo su kasar nan a nan suke zama, shiyasa ma se kiyi zaton a Nigeria kike in ba kin shiga cikin gari sosai ba, a gefen unguwar nan har kasuwa ce da mu ne suna kasuwar hausa wadda duk hausawa ne ke sana'a a cikin ta, duk wani abu da kike tunani da ya danganci hausawa zaki same shi a nan inshallah ".

Gyada kai nayi cike da fahimta, muka karasa haɗawa sannan muka dauka, bata shiga ba ni ta bawa na shiga na kai na dawo na karbi dayan.

Babu Fulako ya nannade kafa ya shiga cin abincin, ko da yake shi da gidan kakarsa fulakon me ze yi, mu kam waje muka bashi shi da yaran shi, yana cin abinci suna ta masa ihu da haye masa jiki dan ko da na so dauke su se yace na bar su kawai.

Se da ya gama sannan ya fito dauke da ƴaƴan sa, Safar kuma ta kwashi kayan plates din zuwa kitchen.

Shi ya tashi Nene da kan sa, tana ganin sa ta hade rai ta yi kicin kicin, ko gaisuwar sa bata amsa ba ta jefa masa tambaya

"Lafiya kai kuma, me ya kawo ka bayan nace kar kazo se na kira ka?".

Dan langwabe kai yayi, yayi kalar tausayi kamar wani Maraya

"Na kasa jure kewar jikar Nene ne, kullum zan ga yara amma ban da ita, hankali na ya kwasa kwanciya shiyasa nazo".

Se Nene ta dan saki fuska dan taji dadin yadda ya nuna damuwa da jikar ta

"Shiyasa ka take doka ta kenan?".

"Sam ba haka bane kakata me so na, son jikar ki ke naman hauka ta ni, wallahi ji nake zan iya zaucewa in ban gan ta ba a tsukin nan".

Cike da kunya Nene ta dauke kai bata kuma cewa komai ba, se shi ne yace

"Hajiya Yayah da Mamana na gaishe ki".

Ya faɗa a saibance yana lura da ita a kaikaice dan ganin reaction din ta, tabe baki tayi tare da dauke kai gefe kamar ba zata ce komai ba se kuma tace "uhm".

Se ya kama kan sa jin yadda tayi, sedai abin na damun sa a rai dan baya son ganin iyayen sa cikin damuwa, cikin lallashi da lallaba yace

"Dukkan mu a rayuwa masu kuskure ne Nene, amma abinda ke saukaka zafin wannan kuskuren shine nadama, in mutum ya fahimci kuskuren sa se ya gyara, shiyasa in har muna son daidaiton rayuwa se mun zama masu afuwa da ba wa mutane second chance, in ba haka ba zamu yi ta holding grudges against each other, hakan kuma ba abinda ze amfane mu da shi face hana mu kin dadi da kwanciyar hankali, irin haka ne kuma kuskuren da su Mama suka yi da a yanzu suke nadama, ina rokon ki da ki basu dama Nene in ba haka ba lamarin ba ze taba gyaruwa ba, wallahi sun yi nadama sun gane kuren su, Mama tana can cikin tashin hankali, da alama itama depression din ke neman kama ta dan jiya da naje ganin su kafin na tafi ita kadai na ga ta zurawa bango ido tana kallo tana ta magana"..................✍️.

Comments din ku yayi kasa sosai fa, haka votes din ku, ban sani ba ko littafin ya dena muku dadi ne, ko yanzu bakwa enjoying ne, in kuma ba haka ba pls do pamper me with your votes and comment, pls.

Vote
Comment
Share fisabilillah

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 050  [ 17/07/2024 7:27pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Ouummey
Free book!!!

Ouummey 050

Page 5️⃣0️⃣

_____________________Zancen ya shigi Nene sosai amma se ta danne bata nuna ba, se ma ta dauko Radio din ta ta Murda ta canja tasha tana sauraren wakokin garin su na da da ake yi, Masdooq ya zuba mata ido, wato dai itama ta iya kafiya da taurin kai, Allah ma yasa ba ita daga Mama har Aimah suka gado ba.

Haka suka cigaba da zama , shi yana wasa da ƴaƴan sa ita kuma tana jin radio din ta, ni kuwa ina daga bedroom kan bed ina karatun littafi na abi na.

Ban ji kiran sallah ba saboda speaker din masallacin kusa da mu ya lalace, se kawai ji nayi an fisge min waya ta, na zabura na mike zaune daga kwance da nake, na dube shi yana rike da wayar yana duba abinda ke kan screen din, se ya dago ta kalle ni

"Kema kina bata lokacin ki wajen karanta wadannan karairayin kenan?".

"Ba na karanta karairayi se litattafan da suke da ma'ana masu ilmantar wa".

"A tashi haka lokacin sallah yayi".

Na karbi wayar daga hannun shi na aje, ya riga ni shiga toilet din dan haka na zauna jiran shi ya fito, yana fitowa na shiga nayi alwala na fito se na tadda shi kan sallaya, da hannu yayi min nuni da muyi jam'i, ban ki ba ya ja mu sallah.

Muna idar wa na yi azkhars dina da tasbih kana na gaida shi, abinda ya zame min dabi'a kenan duk in na yi sallah.

Tashi nayi zan koma kan bed ya riko hannu na ya dawo dani gaban sa ya zaunar, na zuba masa ido dan jin dalilin hakan, se yayi gyaran murya yana kallan fuska ta

"After duk abubuwan da suka faru months back na zo baki hakuri Aimah, duk da wasu abubuwan babu laifi na a ciki amma na dauki komai da komai, so batare da wani bude zance ba ko maganganu ina me baki hakuri tare da neman alfarmar ki yafe min duk wani bacin rai da damuwar da na saka ki, with or without my consent kin ji ".

Na dan kai da kai gefe ina hadiye yawu tuno wahalhalun da na sha watannin baya, sedai kamar yadda na fada muku na riga na yafe mishi na kuma masa uzuri, in yana da laifi a abinda ya faru be fi kashi 10 cikin dari ba, dan haka basu kai in ce zan rike shi da su ba.

"Na dade da yafe maka Yaya, ban rike ka ba tun farko dan na yi wa Abba alkawarin yi maka uzuri da kuma yafiya gare ka akan laifin da zaka min tun kafin kayi, so komai ya wuce a gare ni insha Allah".

Jawo ni yayi ya rungume kam kam yana fadi kasa kasa

"Na gode sosai wify, na gode my wife Allah ya miki albarka".

"Ameen ". Nace ina zame wa, se ya kada baki yace

"And again, ina nemawa Sa'adah alfarma, ki yi hakuri itama ki yafe mata, ba halin ta bane wallahi, zuga ce da sharrin shaidan kuma ta tuba, Please ki yafe mata".

Na tsare shi da ido ina masa wani kallo me kaifi, tsayin lokaci ban janye ido na ba har se da ya tsargu, ganin yadda ya shiga kame kame se kawai nayi murmushi na haye bed ban amsa shi ba.

Taya ka, taya ma ze yi wannan tunanin?, Yafiyar ma shi ze nema mata?, Duk abinda tayi min ta fi karfin kira ko ko dan iska text ta nemi gafara se shi ze nema mata?, Bayan tana cikin yan gaba gaba wajen jefa ni halin da na samu kai na a baya, ko da yake hakan ba komai bane, ai

inda soyayya ba abinda ba za'a yi ba.

Gaba daya se naji karatun ma na daina ganewa bana kuma fahimta, raina ya daina min dadi, se kawai na kashe wayar na kwanta sosai tare da rufe ido na.

Bude kofa aka yi, na zata ma shine ta fita se naji Muryar Nene na fadin

"Wai kana nufin q gidan nan zaka kwana ba hotel ba?".

"Wane irin hotel kuma ana zaune kalau Nene, ga ni da gidan kaka da kuma dakin mata, haba dai".

Nene ta karkace kai tana masa wani duba, se kuma ta girgida kai ta kalle ni

"Ke tashi muje".

Kamar me jira na diro daga gadon da sauri, waya ta ma ban iya na dauka ba na yi gaba, Nene ta masa tsaki sannan ta fito.

*******

Galala haka Masdooq ya raka bayan su da kallo cikin mamaki, me je hakan kenan?, Tsaya ma, me suke nufi da shi ne.

Ya tako kafa ya kafa dan ya gan ta har wata ƙasa amma a tafi a bar masa daki, shi in sun kwantar da hankalin su ai ba wani abu yace ze mata ba ko, shi kawai dai ya dinga ganin ta a kusa dashi, shikenan fa, amma shine za'a wani tafi a bar masa daki, irin ga shi nan an tura masa aniyar sa ya ci kan sa da kan sa ko.

Shi fa kamar ma ya lura Aimah wani ja baya take dashi duk da tace masa ta yafe masa shima kuma yace ya yafe mata, to me yasa in har hakan ne har ranta ba zata bashi dama su tafiyar da auren su to another level ba.

Me yasa ba zata bashi ya gwada mata irin tsantsan soyayyar sa gare ta ba, me yasa ba zata bari ya nuna mata irin girman matsayin ta a rai da rayuwar sa ba, a'a se ta biye wa Nene ta tafi ta bar shi, shi fa har sauri na ya ga tana yi, irin ya ishe tan nan.

Se ya tura baki kamar karamin yaro ya harari kofar ya haye bed din ta yana yin kwafa, a nan ya ga wayar ta da take karatun wannan karyar na su dazu, se ya dauka ya na farin cikin ze samu number din ta, at least hakan ze kara dawo da shakuwar su ta baya.

Se kuma ya danna da fargabar Allah ya sa ba lock, se kuwa yana dannawa ta kawo kyakkyawan hoton ta da ya cika screen din, sanye take da sky blue kaak sanyi da hular su da

kuma takalmin su, hannun ta rike da ƙatuwar teddy da ta rungume, ta dan yi tsalle haka kuma tana dariya, gashin ta da be gama shigewa hular ba ya watsu a iska, tayi kyau matuka sosai, a idanun sa kuwa abin har ba'a ma magana.

Se ya shiga gallery, can ya dinga cin karo da photos din ta kala kala cikin mabanbantan yanayi, wasu ma bata san an mata ba, kuma duk babu na yarwa, se ya janyo wayar sa ya shiga loda su a ciki, shi da baya ajiyar pics dan ko nasa ba su fi biyar ba, amma na Aimah yanzu ya tura fin hamsin.

Se kuma ya saka number din sa a wayar tata ya kira, tana shiga ya katse ya dauki wayar sa yayi saving number, a wayar ta kuma ya goge history din kiran.

Haka ya dinga nata shige shige sedai ban da pics din ta, number Luba, Nene da wata da aka saka Dr babu wani number kuma daban, se kuma wakoki.

Har ya gama abinda ze yi da wayar ya aje se kuma tunanin sunan Dr da ya gani ya fado masa, to me take yi da number wani Dr a wayar ta, as a married woman ai be kamata ace ta aje number gardi a wayar ta ba, take se yaji wani nashi ya soki kirjin sa, wato har sun yi shakuwa har haka da zata aje phone number sa, wato shiyasa ma take ta wani fada masa yanzu ita kanwa ce, waye zasu rabu meye saboda maza na biyo ta ko, lallai zata ga shirme kuwa dan ze gwada mata ya fita danyen kai.

Da wannan ya goge number Dr Bee'at daga wayar bayan ya gama zage ta tsaf a ran sa da fili a matsayin namiji, se da ya goge se kuma ya ciji yatsa da tunanin me yasa ya fara gogewa ba tare da yayi blocking ba.

********

Kan gadon Nene na haye na kwanta tare da juya mata baya dan bana san duk wata magana yanzu, itama bata ce komai ba ta yar da katifar dake tsaye ta sa mata bedsheet tayi kwanciyar ta, gaba daya ban san mene damu na ba amma jin rai na nake ba dadi, haushi nake ji amma na rasa na wa, gaba daya na kasa bacci se juye juye da nake ta yi.

Can kamar an tsikare ni na mike na saka bedroom slippers dina na nufi kofa, waya ta zan dauko na kira Dr, tace min zata zo kuma bata zo ba, ina so in ji idan lafiya.

Har na kai bakin kofa Nene da ashe bata yi bacci ba tace

"Ina kuma zaki?".

Kamar daga sama haka naji maganar ta, se na tsaya tare da dan juyowa

"Zan je in dauko waya ta a daki na ne".

"Uhm wato waya...". Nene ta fada da wani yanayi a Muryar ta irin na karki mai da ni shashasha din nan, Ni kam da ban san gatse ba nace

"Eh zan kira Dr ne, tace zata zo kuma bata zo ba, ina so in ji in lafiya".

"Yo da bata zo ba ai ga wani likitan can ya zo ko, to koma ki kwanta ba inda zaki".

Kafa na shiga bugawa idanu na na tara hawaye dan dama a gaba nake

"Haba Nene haba Nene, na fa fada miki waya ta zan dauko ko?".

"Ni kuma na fada miki ba zaki je ba ko?".

Ta fada tana mikewa zaune daga kwancen da take, se na tura baki hawayen na zubowa

"Ni wallahi bana san ana min irin haka, kawai se a hana mutum zuwa dakin sa, kin ce na taso na taso kuma yanzu waya ta ma ba zaki bari na dauka ba".

Nene da ta saki baki taba kallo na cikin mamaki tace

"Lallai ban yi mamaki ba, wai ni zaki raina wa wayo, kina so ki tafi can wajen shi shine zaki wani fake da dauko waya?, To yaushe ita ta Rabi'ahr ta kira ki balle ki mata sharrin wai tace zata zo?, Kin ga Nu'aimah ki fita daga idanu na na rufe, bar ganin kin yi ya'ya biyu, in ban zane ki ba kice ba Amina nake ba, yarinya mara hankali ana neman kwatar miki yanci kina hauka, an fada Miki ana yi wa namiji haka?".

Takaici, tsoro, mamaki da tunanin me zan wa tsohuwar nan na huce suka hana ni yin magana se idanu da na zuba mata, wai me take nufi, tana so tace me wai ina son zuwa wajen Ya Masdooq ne?, To akan me zata yi wannan tunanin?, Bata ganin yadda tana cewa na taso na taso ba ko waiwaye, shine har zata ce haka?.

Se kawai na fashe da kuka na koma na fada kan bed din ta ina yin abu na, hawaye bibbiyu kamar wadda aka duka, to dama abin ka da me jiran kirsi, ni kaina na san ba maganganun ta ne suka saka ni kuka ba, kawai na fake da hakan ne nayi abi na.

Cikin tsoro da takaici Nene ke kallo ba, ta fadi wani magana da kamar karin magana ne da yaren su, se kuma ta gyada kai tace da Hausa

"Lallai kina da sauran aiki a gaban ki Nu'aimah, kuma wallahi ko kukan jini zaki yi ba zan bar ki ki fita kije wajen wancan katon kawai din ba, bari ma ki gani".

Se kawai ta tashi taje ta sawa kofar key ta zare abin ta ta tusa cikin fatarin ta, Ni kam lamarin

Nene yau se ya zame min wani iri, na bita da kallo baki sake ta koma ta kwanta abinta tana mitoci da kananan maganganu, se kawai na gyara kwanciya ta ina addu'a dan na hakura da dauko wayar, yo to ma in ba fatarin nata zan je na dauko key din ba ta ina zan fita.

Haka muka kwana abin mu ko amsa sai da safe da na mata bata yi ba, Nima kuma ban maimaita ba na tura baki ina fadi a raina

_'ba hakurin da zan baki in ma shi kike jira, haka kawai daga zuwan sa mata se ki bi ki saka ni a gaba, se kace ni na kira shi, shi baki takura masa ba kawai ni kizo ki addabe ni'_.

Da haka na juya mata baya sosai ina sake sake a raina, tunani nake ta wace hanya zan biyo muyi rabuwar lafiya lafiya da baban yaran can, bana san duk abinda ze sa a ga ban kyauta ba, amma dai koma yaya ne dole ya sau ni.
Ita kuma Sa'adah wallahi ba zan taba yafe mata ba in har bata nemi yafiyar ta da kan ta ba, in da Allah ya taimaka se ya sa ba ni na cuce ta ba, ita ce ya cuce ni.

Da wannan tuna in bacci kwashe ni, ban farka ba se da can dare da Nene ta shiga daddaba ni, matar nan akwai ibada, tun zuwa na gidan ta na lura da bata da yawan bacci da dare, da karfe uku tayi take tashi ta shiga sallah, daga nan se ta zauna lazume lazumen ta, ba zata tashi ba se an kira sallah, se tayi raka'atanul fajr kana ta gabatar da sallar asuba, shima bata kwanta ba se gari yayi haske, shiyasa in ta koma kuma bata gamsu da wuri, se ta kai 11 na safe.

Nima zuwa na ta na sake gogewa da sallar dare, duk da ni bana irin tata, in na tashi 3am zan yi nafilfilu da lazumi har a kira Sallah, daga nan in nayi raka'atanul fajr se in yi sallar asuba, daga nan kuma zan koma in kwanta abina se kuma sanda na farka dan kai na, dan haka ban da sahihin lokacin tashi daga bacci.

Yau ma haka muka yi, sedai muna cikin sallah se ga knocking din sa , se da nayi gyaran murya sannan ya wuce, ina jin shi yana bugawa Aunty A'i kofa ita ma, daga nan na ji fitar shi zuwa Masallaci...........✍️.

Vote
Comment
Share fisabilillah

Ouummey 📚✍️

Ouummey 051  [ 18/07/2024 7:56pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Ouummey
Free book!!!

Ouummey 051

Page 5️⃣1️⃣

_____________________Ina kitchen ina hada breakfast ya dawo daga masallaci kamar yadda na san shi tun ainahi, in aka yi subh baya tahowa se gari yayi haske sosai, Aunty A'i na daki na bar mata shirya twins, dama haka muke yi, in zata yi girki zan shirya su, in kuma ni zan shirya su ita kuma zata yi girki.

Ina gamawa na shiga fita da su zuwa tsakiyar falon dan a nan muke cin abinci, na kai na koma dan kwaso wasu se ganin sa naji tsaye kofar kitchen din ya harde hannuwa a kirji yana bi na da wannan kallon nasa me kashe min jiki tun a da can.

Na dauke kai ina gaishe shi, ko ya amsa to ni dai ban ji ba se hannu da ya mika min, na kalli hannun na kalle shi

"Zan taya ki ne".

Ajiyar zuciya nayi tare da mika masa team flask din hannu na dan bana san jan magana da safiyar nan, shi kuwa na ga kamar ba Ya Masdooq din da na sani ba mata yawan magana yanzu duk waccan matar ta sa ta bata shi da surutu.

Tunanin nan da nayi se ya dawo min da zancen mu na jiya, wai yana nema mata yafiya, kai jama'a!!

Na dauki warmer daya da ta saura dq oat fin twins tare da kokarin daukan cups sedai kayan sun wa hannu na yawa, haka na fita da wadannan da tunanin na kai na dawo, ina komawa na samu ya dauko se na juya zuwa falon ya biyo bayana.

"Bari naje nayi wanka, na je?"

Ya fadi yana kallon na, wani yanayi na can shekarun baya ya dawo min, a lokacin duk abinda ze fada min se ya faɗa da sigar tambaya, har na taba ce masa me yasa yake haka, amsar da ya bani a lokacin itace wai saboda hankalin sa na kwanciya da yin koma me ne in ya san da amincewa ta.

A hankali na dube shi, idanun sa na kai na se na wa da suke taf da hawaye suka fada cikin nasa, ya langwabar da kai yadda ya saba min a da in yana lallashi na, se kawai hawayen nan suka shiga zuba kamar an koro su, dan sanabe se ga shi har da shessheka, shima na sa idanun sun kada, da alama shima bayan ya tuna, ya kama hannaye na ya rike cikin nasa tare da ja na jikin sa ya rungume yana cewa cikin raunananniyar murya

"I miss my Barbie, I miss my Honeybun, her cute smile, her magic eyes, her melodious voice, her...her...her everything, I miss you AIMAAAAHHHHH".

Nima hannu na saka na rungume shi kam kam, Ina jin na fi shi wannan kewar da yake fadi, kewar Ya Masdooq dina, my sweetheart, my sweet tooth, my friend, my besty and my other half, a yanzu ba batu ne ake yi na miji da mata ba, batu ne ake yi na wancan lokacin da muke Abokai, aminai kuma mafi shakuwar yan uwa, shiyasa na aje komai na tarye shi ɗan nima ina bukatar jin shi cikin jiki na.

"I missed you more, so...Soo...very bad sweetheart, life has been very dull, blank, empty and baadd without you and your care, please don't ever leave me sweetheart, don't pleassssseeee".

Na karasa Please din ina sake fashewa da kuka, se ya zaro ni daga jikin sa ya haɗa fuskokin mu tare da cupping face na, yace cikin irin wancan muryar ta sweetheart dina, tone din da shi kadai yake amfani da shi a gare ni, haka shima wani kadai yake wa magana da shi yace cikin whispering muryar sa very cool

"I won't Barbie, I promise you I won't, and am sorry for leaving you at that time, am sorry and forever will be, I missed you beyond your expectations, beyond words can  explain, don't leave me too Barbie, never please".

Gyada mai kai na shiga yi har lokacin hawaye na basu tsaya ba kamar an bude famfo, ya sa hannu ya lakato ya kalla se kuma ya lumshe ido yace

"Close your eyes".

Ko a da da ban fahimci feelings dina toward him ba bana masa musu balle yanzu dan haka na ja idanu na na rufe, ban san abinda ze yi ba kenan da ban rufe din ba, ga shi kamar aikin asiri na kasa motsa ko da yatsun hannu na ne balle kafafu na balle jiki na gaba daya.

Ajiyar zuciya ce ta shiga kwace min cikin wani yanayi jin yadda yake wiping away my tears da harshen sa, na kasa motsi kamar wadda aka dasa har se da ya janye dan kansa bayan hawayen sun tsayar da kan su da kan su, se lokacin kuma kuzari na ya dawo nima na dawo duniyar mutane, da sauri na sunkuyar da kai na gaba na na dukan uku uku, a gaggauce na juya masa baya da nufin barin wajen, se kuwa idanu na cikin na Nene dake tsaye jikin kofar dakin ta, da alama tsoron Allah ne ya kashe ta a wajen har ta kasa magana.

Ni kuwa kunya, takaici da tashin dadi ne suka rufe ni, yanzu fa Nene se tayi mana wata fassarar bayan ba abun da take tunani bane, ko ba aure ai dai shi din yaya na ne ko.

Na kikkifta ido kusan so uku kafin an fara murza yatsun hannu na cikin na juna, se kuma na matsa kusa da ita da sauri ina cewa

"Uhm....uhm..uhm..ne..nennn..ee ba fa abinda kike tun....".

Daga min hannu tayi cikin katse ni, bata ce komai ba ta juya zuwa dakin ta, ni kuma na bi bayan ta da sauri dan mata bayani.

*******

Suna shigewa ya saki wani irin tattausan murmushi yana shafa kwantaccen gashin kan sa zuciyar sa fes haka kuma cike da farin ciki, ko da ace har yanzu Aimah bata son shi ze iya koya mata hakan tun da har ba kowa a zuciyar ta, haka kuma har yanzu tana missing wannan bond din na tsakanin su, dan haka ze yi amfani da shi ya juya manufar alakar su a ranta zuwa soyayya.
Da wannan tunanin ya wuce zuwa daki, cikin farin ciki da annashuwa yayi wanka abin sa.

Ko da ya tsaya gaban wardrobe se ya shiga tunanin wane kalar kaya ne ma a jikin ta, Pakistan ne masu kyau da suka mata cif cif ta saka kalar lemon green, s kuwa shima ya ciro kananan kaya, lemon green color shirt da aka white trouser, ya gyara jikin sa da kan sa nan da nan, se da ya gama komai sannan ya zubawa mirror ido dan ganin ya ya.

Tabbas yayi, shi kan sa ya san wankan ya fita shiyasa ya dauki turare ya karawa jikin sa kana ya xura Safar sa ta zaman gida ya fita falon.

*******

"Please Nene ki saurare ni, ba abinda kike tunani bane ba fa, let me explain mana".

"Akan me kike magana kenan Nu'aimah?".

Wani irin sototo nayi ina dubab ta cikin rashin fahimta, ta fa san me nake magana amma shine

zata wani basar, nima se na basar din na ce

"Na ganin mu tare da Ya Masdooq dazu.a...aa...a.a.uhm".

"To ai ban ce komai ba ko, bayan haka ai dai shi din mijin ki ne".

"Nene Please".

Memakon ta saurare ni din se ta canja maganar

"Ki fadowa su A'i su zo mu karya, kun san ban jure yunwa".

Kallon Nene nake yi kamar zan rusa ihu amma bata nuna ta gani ba, dole haka na fita zuwa kiran su Auntyn, Nene ta bi baya na da ido a ranta tana cewa

_'har ni zaku kawowa farillan iya shige tsakar falo, ban da Allah ya sa ba yara a gidan da me zasu kalle ku?, Hmmm zan yi maganun ku ne gaba daya'_.

Ashe har ma ya kira su Auntyn dan a falon na tadda su, na juya na koma na fadawa Nene hadu sun fito sannan ta taso, fuska a sake kamar ba abinda ya faru ta amsa gaisuwar Ya Masdooq, ni kuwa duk a darare nake, abincin ma ba wani ci nake sosai ba, se na bige da bawa Aiman oat, Anty A'i ce ta lura ba na cin wani abin kirki

"Ya ba kya cin abin cin Ummi?".

Dake ta kan kira ni Ummi sa'i da lokaci yadda yaran ke kira na, na yake mata haƙora

"Na ci fa Aunty, na koshi ne".

"Ba abinda ta ci Aunty, ki ce mata taci fa kar na mata dura".

Na kowane fuska ina duban sa, to Allah ya sani ni na manta Nene na wajen

"Ni za'a wa dura kamar wata Airah?".

"Airah ma ta fiki girma a idanu na, ko baki san you're my Baby bane?".

Aunty A'i s ta dauke kai kamar bata ji ba, ita kuwa Nene ita kadai ta san me take sakawa cikin ran ta

"Nice Airah ta girma?".

Na tambaya ina tabe baki kamar wata yarinya, shi kuwa se ya kashe min ido daya yana kai

kofin tea bakin sa, kasa kasa yace

"Wai yaushe na dena miki wanka ne eye, ko da yake da gaske kin girma tun da har kin iya dauka na, ga nan su Aiman sakamako na yawo ko ina".

Wallahi ban taba tunanin ze fadi haka ba, kai ko kusa da haka, balle kuma Nene da ke kusa da ni da duk yadda ya rage murya se da taji, tsohuwar nan akwai ji kamar me kunnen maciji, Ni dai tsabar kunya, nauyi da mamakin shi ban ma iya tankawa ba se kawai na maida hankali kan Aiman, ina jin idanun sa kai na amma ban dago ba, ina gamawa na gyara masa bakin sa dan Airah na hannun Aunty tana bata.

Mikewa nayi na shige daki tare da saka lock, wanka nayi hankali kwance dan na san in dai na bar kofar nan a bude se ya shigo, ina fitowa na zauna nayi shafe shafe na da na saba, gyara nan gyara can har kusan awa sannan na gama na zura doguwar riga irin ta mutan kasar, Pakistan din dama kawai na saka ne amma ban yi wanka ba dan Nene bata bari a mata amfani da toilet, na tsaya na karewa kai na kallo, tubarkallah Masha Allah, ni kaina na san nayi kyau, natural kyau dan babu ko digon powder a fuska ta, ko kohl din ma yau ban saka ba.

Turare kawai na saka na zura slippers dina na fita, tun da na fito ya zuba min Mayun idanun san nan dake shanye, gaba daya yasa na ji na daburce har ina kokarin sarkewa, ganin ba shi da niyyar janye se na shiga buga kafafu

"Ni wallahi bana so".

Duka suka dago suka dube ni, Aunty A'i tace

"Meye bakya so autar Mama?".

"Aunty ki ce masa ya dena kallo na haka, so yake na fadi ne?".

Yar dariya tayi ta kalli Ya Masdooq da ya lumshe idanun sa

"To ai ni ban ga yana kallon ki ba yar Nene, hala dai rigimar ce ta motsa ko".

Na tura baki na dauke kai na daga kan su shi da Aunty A'in na karasa gefen Nene na zauna, tsohuwar nan kuwa se ta mike kamar ta ga dodo, ta dauki Radio din ta ta fama ta wuce daki, na bita da kallo baki sake kana na juya kan Aunty A'i dake dariya

"Nayi mata wani abu ne?".

"Sam sam Ummi".

"To amma na ga tana ta wani basarwa da shan kamshi?".

Aunty A'i tayi kasa da murya tana kallon dakin Nene

"Kyale ta, kin san fa itama ta iya rigima".

Yadda Aunty A'in tayi ne ya ban dariya, na kuwa dara, Airah dake hannun ta itama se ta shiga dariyar, na tashin na karbe ta na shiga jefa wa sama ina cabewa ina mata waka muna ta dariya abin mu, Aiman dake kan laps din Daddyn sa ya shiga zillo da miko hannu yana kiran

"Ummiii..... ummiii...ummiii".

Se na dakata tare da miko masa hannu, da sauri kuwa ya zame daga kan baban yayo waje na, se na aje Airah a gefe kadan shima na shiga jefa shi, sedai kasancewar ya fita nauyi nan da nan na jigata, na aje shi ina maida numfashi su kuwa se dariya suke shi da yar uwar sa, Ni kuma ganin su a haka na sa ni farin ciki ina ta sakin murmushi.

Daga gefe shima ya zuba mana ido cikin godiya ga Allah, wai wannan matar sa ce, wadannan kuma ƴaƴan sa, kai alhamdulillah.

Karar waya ta ce ta sa na mike zuwa bedroom, ina dauka na ga number Dr Bee'at sedai babu suna kamar an goge saving din, na shanye mamaki na na dauka muka gaida ina mata ciwon bakin rashin zuwan ta jiya

"Wallahi baki muka yi yan uwan Abeey, shiyasa ban samu zuwa ba, amma insha Allah gobe zan shigo".

"Fatan sun zo lafiya, a musu Barka da zuwa pls, tom se kin zo amma fa ki zo da wuri akwai labari, a gaida Mama na".

Ina fada na kashe da sauri ina dariya, na san da ban kashe ba ta na nan tana lallaba ni na fada mata kawai tun yanzu dan ita bata san jan rai.

Ina juyawa dan fita na gan shi tsaye jikin kofa ya jingina idanun sa kamar a rufe amma fa ni na san ba'a rufen suke ba, kuma kallo na yake.

Na tura baki gaba ina bata rai, se kawai ya juya yana fadin

"Ki shirya yaran mu fita, jibi nake son komawa".

Jin zancen komawa se na ji raina ya ɓaci, yaushe ma yazo da har yake fadar komawa, wata bakwai be taba zuwa ba yanzu yazo amma ko sati ba ze yi ba ze ce ze tafi, kamar na yi masa magana se kuma na hadiye, akan me zan ce ya zauna bayan matar son shi na can na jiran shi, maybe ita tace ya dawo din, ai ko da na gan shi a kasar nan na san ba waje na yazo ba, yaran

sa ya zo gani, ya kuma gani, to me ze zauna yayi min................✍️.

Vote
Comment
Share fisabilillah

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 052  [ 18/07/2024 7:57pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Ouummey
Free book!!!

Ouummey 052

Page 52

______________________Ban canja kaya na ba dan babu bukatar hakan, yaran kawai na canja wa zuwa wasu daban, shima ya canja shigar da zuwa Ethiopian male attire, in kuka gan shi ba zaku taba cewa he belongs to Nigeria ba, yayi kyau matuka sosai.

Har daki naje nayi wa Nene sallama, na zata zata hana ko tayi ta tuhume tuhume se kuma naji tace se mun dawo, na sha jinin jiki na daga ganin yadda take cin goron ta hankali kwance, ba ko yaushe take ci ba shiyasa ba wanda ze gane ma se ya gan ta tana ci din.

Jiki a sanyaye na juya zuwa dakin Aunty A'i itama na mata se mun dawo, ita har bakin kofar falo ta rako mu tana a dawo lafiya sannan ta koma.

Motar Nene ce ya dauka, ni ban ma san sanda ya sa a ka wanke masa ita ba dan a aje take, da alama ya shirya wa fitar tun jiya.

Safar na baya, ni ina gaba kusa da shi rike da Airah, shi yake driving yana rike da Aiman.

Shiru babu wata hira tsakanin mu dan ni gari nake kallo ta window, shi kuma yana bin wakar "baby calm down" da ya kunna take tashi a motar kasa kasa, da hannu daya yake tuki dan dayan na rike da Aiman da tun farko na ce ya kawo na rike su gaba daya yaki, sa'i da lokaci yana dagowa ya kalle ni da ban ma san yana yi ba.

Tunani kawai nake yi na me ze faru in muka rabu?, Ze kwashi yarana ya kai wa matar sa, ni kuma a bar ni gaban Nene in cigaba da zama, ko kuwa ze bar min su.

A haka muka kai wani katon wajen shakatawa da ni ban ma taba sanin akwai shi ba, yayi parking a parking lot sannan ya dube ni yadda nake Len gurin ta window

"Zamu iya shiga?".

Na juyo na kalle shi se na gyada kai na bude door din side dina na fita, hannu na daya dauke da Airah, dayan kuma karamar handbag dina, Safar ma ta fito haka shima yayi locking motar sannan ya zagayo inda nake, hannu ya kai ze karbi handbag din na dube shi da tunanin me ze yi, se ya dage min gira yana sake neman karba, se na sake masa kawai, ya karba tare da gyara mata riko sannan ya nuna min hanya da ido.

Zuciya ta ba dadi na fara takawa zuwa cikin wajen, a jere muke haka ya daidaita takun sa daidai da nawa, duk da ma shi ba shi da sauri a tafiya balle garaje, komai na sa a nutse yake yin sa, Safar kuma na gaban mu.

Lokacin da muka shiga cikin park din sosai na bude ido ina kallo, gurin ya tsari matuka gaya, yayi kyau beyond tunani na, kayan wasa na yara ga sunan birjik, kai har ma da na manyan, ga kuma can gefe wani hadadden garden me cike da niima, kai hatta kamshin wajen na daban ne, a sanyaye kuma me kwantar da hankali, kamshin tsirrai na sake kara masa dadin shaka.

Wajen wasan yaran muka nufa, ya kira daya daga cikin masu kula da yaran suka yi magana, ban taba sanin ya iya Yaren su ba se ranar, suna gama magana ya karbi Airah daga hannu na yana mata wasa, ya kira wata mace me sanye da uniform irin nasa ta karbi Aiman, suka fito da wani karamin na'ura Ya Masdooq yayi scanning hannun sa a kai nima nayi suma suka yi se kuma suka bashi karamin plastic card, kana suka wuce da yaran har da Safar.

"Muje".

Wani kallon rashin fahimta na masa

"Muje ina?, Ina kuma zasu kai min yara na?".

"Nutsu mana, kin san dai ai ba zan cutar da su ba ko?".

Shiru na masa ina kallon sa a kage, so kawai na ke ya yi min bayanin ma'anar bada yara na da yayi

"Su ne masu kula da yaran a wajen wasan su, haka kuma in iyaye na da wani excuse din zasu basu yaran su kula musu da su zuwa mean time din da zasu zama available, za'a yi scanning fingerprint din su saboda tsaro haka kuma cameras na nan lungu da sako ta ko ina a wajen da ake iya ganin kome ke faruwa, su wadannan din in mutum ze bar yara a hannun su yana yin requesting tun kafin yazo kamar yadda nayi, company din su ke assigning din su ga duk wanda yayi requesting, so ki kwantar da hankalin ki, yaran ki ba bata zasu yi ba kuma ba abinda ze same su, now let's go ".

Dan ajiyar zuciya na sauke, duk da haka ni dai hankali na be gama kwanciya ba, na juya muka nufi garden din se dai ina tafiya ina waigen yara na har na kusa faduwa, ya riko ni jikin sa yana fadin

"Careful ".

Be sake ni ba kuma har muka shiga garden din, nan ne ne sake ware ido ina kallo, can wani bangare muka yi zuwa wata karamar mat me laushi, gefe da gefe tsuntsaye ne ke shawagi kala kala, su dawisu ne, jimina ne, wasu kalan kananan tsuntsaye masu kyan kala, green, blue, yellow... different colors suna ta yawo abin su.

A hankali na zame takalmin kafa ta Black heel me kyau na zauna, taushin mat fin har yafi na yadda ido ke gani, shima ya zauna, irin zaman da nayi na tankwashe kafa haka shima yayi har gwiwar mu na gugar juna.

Na kalle shi idanun sa na kai na, na janye na maida nawa kan tsuntsayen nan dake burge ni, dawisun nan na wani irin girgiza kana ya bude kyawawan fuka fukan sa, lallai fatabarakallah Ahsanul khaliqeen.

"Nu'aimah".

Na maida duba na gare shi batare da na iya amsawa ba

"Na fahimci kwata kwata baki fahimci maganar da muka yi a gidan Nene ba, shiyasa na kawo ku ban dan na samu kebe wa da ke ta yadda zamu tattauna a nutse".

Nan ma ban ce komai ba se zuba masa ido da nayi ina kuma sauraren sa

"Yaushe kika shirya komawa Nigeria?".

Kallon da nake masa ne ya sauya, ban gane in koma Nigeria ba, to in je in yi me?, Kamar

yasan abinda nake tunani se ya dora da

"I mean yaushe zaki koma gidan ki, gidan auren ki Aimah?".

Dan sauke ajiyar zuciya nayi, me yasa baze fahimta ba?, Me yasa baze gane ba, ya fi son muyi ta maimaita zance daya ne?.

"Ai mun gama magana ko sweetheart, ba mun yi sealing maganar da zaka sake ni ba?".

Wani kallo yayi min, more of harara, da alama zance na ya bata masa rai dan har se da fuskar sa ta canja, ya zuba min ido kana yace kasa kasa cikin kaushin murya

"Har yanzu?, Har yanzu zuciyar ki bata aminta da ni ba?, Har yanzu baki ji zaki iya rayuwar dindindin da ni ba?".

Na kau da kai gefe kirji na na bugu, be sani bane, da ya san irin tarin kaunar sa da ke dankare a kirji na da be fadi haka ba

"Se yaushe ne zaki buɗe idanun ki ki kalli gaskiya Barbie?, Kina tunanin zaki iya samun wanda ze fini kaunar ki ne Aimah?, Me yasa ba zaki buɗe kirjin ki da zuciyar ki ki bani dama ba?".

Na sunkuyar da kai, bana doubting kaunar sa gare ni matsayin yar uwa, sedai ina doubting soyayyar sa gare ni matsayin abokiyar rayuwa, a baya ina da tabbacin babu wani da namiji da ya kai shi so da kauna ta, sedai a yanzu ta ko ina shi da kan sa yake nuna min matar sa ce a rai da zuciyar sa.

"Ba zan takura da se kin koma yanzu ba, xan miki adalcin baki lokaci kiyi tunanin sosai, amma ki sani wannan karon babu gudu babu ja da baya Aimah, ba zan taba gajiyawa ba har se na ga abinda ya turewa buzu nadi".

Da haka ya zame ya kwanta a wajen tare da yin pillow da tausasan tumtum din dake jere a gefen mu, ni dai gaba daya na rasa me ke min dadi, kaina ya cunkushe da tunanin irin zaman da zan yi da shi da matar sa in na yadda na koma, haka kuma ina tuna makomar yara na in naki komawar, se kuma uwa uba yadda ganin sa cikin damuwa ya dame ni.

Ya kwanta ya rufe fuskar sa da tafukan hannayen sa duka ta yadda bana iya ganin fuskar tasa.

Haka muka zauna har kusan awa daya kafin ya tashi yace min yana zuwa, na raka bayan sa da kallo har ya bace min kana na sauke ajiyar zuciya cikin rashin sanin abin yi.

Be dade ba ya dawo bayan sa ma'aikacin wurin ne yana rike da madaidaiciya tray me kyau, yana zuwa ya zauna shi kuma yaron matashi ya aje tray din ya juya ya koma.

"Ga shi nan ki ci".

Dan zuba masa ido nayi ganin yana neman komawa ya kwanta, se na riko hannayen sa, ya fasa kwanciyar tare da zuba min ido, nan da nan se idanuwa na suka cika da hawaye

"Kai fa, ba zaka ci ba?".

Murya a cushe yace "na koshi".

"Kaji haushi ne?, Fushi kayi da ni?".

Na tambaya da karyayyiyar murya, bece komai ba se kallo na da yake yi kawai,

"Kayi hakuri Please ".

Na fada hawayen na zubowa,
"Kaji".

Nace ganin ba shi da niyyar amsawa, ya sauke ajiyar zuciya tare da kau da kai ya furzar da huci, se ya juyo tare da bude min baki alamun haaaa, yasa hannu kuma ya share min hawayen.

Da sauri na gutsuro meatpie karami na sa masa abaki, ya lumshe ido yana taunawa kana ya bude a kai na da na zuba masa ido, dage min gira yayi tare da kashe ido guda se kuma ya tauna meatpie din cikin wani salo alamun yayi dadi, se na yi murmushi na gutsura nima na kai baki na, haka na dinga ciyar da mu duka, se incident din ya tuna min rayuwar mu ta baya a gidan Mama, haka nake ciyar da shi mafi yawan lokuta.

Ba mu ankara ba se gani mukai wayam babu mun cinye, na kalle shi ya kalle ni, se kawai muka fashe da dariya, na zuba drink na bashi ya sha kana na shanye sauran sa.

Se kuma muka yi shiru daga nan, se aukin kallon juna da muke, in muka hada ido kuma muyi wa juna murmushi, daga karshe se ya sake zame wa ya kwanta, wannan karon akan laps dina ya dora kan shi, ban yi wata wata ba na tura yatsu na cikin tatttausan gashin kan sa bakikirin ya sha gyara da mayuka tare da turaren kai, na shiga yawo da yatsuna a kan sa kamar me yin susa, shi kuwa yayi luf kamar me bacci saboda dadin da hakan ke masa, ni dai tunani na cigaba da yi kan abinda ya kamata na yanke na makomar rayuwa ta, daga karshe na bar shi kan yin shawara da Dr Bee'at da kuma Aunty A'i, tun da ita Nene na lura jujun ta ya motsa kwana biyu.

Muna haka bamu ankara ba se kiran sallar zuhr muka ji, ga mamaki na da na duba waya ta wai har sha biyu da rabi da minti biyar tayi, na aje wayar tare da dan dukowa dan na ga ko ya tashi daga baccin, se kuwa jin unexpected kiss nayi kan lips dina, na ja baya da sauri ina ware ido, shima se ya mike zaune yana sakin silent smile tare da dage gira, da sauri na kau da kai na

tare da mikewa tsaye ina fadin

"Lokacin sallah ya gabato, mu je gida ko?".

Nace a tausashe, se ya gyada min kai, na kuwa sa takalmi na shima haka muka bar wajen, wajen yaran muka yi nan muka gan su suna ta wasan su, masu kula da su na tare da su akan kayan wasan, Ya Masdooq yayi musu magana kan zamu wuce se suka bashi wannan na'urar yayi scanning fingerprint din sa nima haka, suma suka yi kana suka amshi karamin card din su daga wajen sa, aka sauko su Airah daga kan digital horse din da suke, na karbi Aiman ya karbi Airah kana na rike wa Safar hannu shi kuma ya rike min handbag dina muka nufi fita daga wajen.

Ban san wane irin kyau muka yi ba da har muke daukan attention din jama'a dan duk inda muka yi haka zaka ji ana wow, Masha Allah, beautiful, tabarakallah...and so on, ni dai A'uzubikalmatillah nayi na shafawa Aiman da Safar nima na shafa kana na sa Ya Masdooq yi musu shi da Airah, da haka muka shiga mota muka bar wajen, bamu koma gida ba se da muka shiga supermarket ya dibgo mahaukaciyar siyayya gare ni da su twins, ni da na gani ma kasa magana nayi dan hana ni shiga yayi, shi kadai ya shiga ya siyo komai.

Ban iya masa godiya ba har muka kai gida, na fada daki da sauri na yi alwala na tada sallah, shima masallaci ya wuce dan kusan karfe biyu ma ta gota lokacin.

Ina fitowa na tarar Nene ta baje ledojin da ya shigo da su suna gani ita da Aunty, kayan yara ne su twins masu kyau, kowa se da ya siyo masa kala sha biyar biyar, se Safar me kala goma, se kuma ni da ya jibgowa dogayen riguna, abayas da na irin kasar zuwa English gowns guda ashirin, se kuma riga da skirts zuwa da jeans guda sha biyar, se kuma hijabai biyar, se undies da suka sani jin matukar kunyar sa da ta su Aunty A'i dake dagawa, se kayan bacci goma, gaba daya dai siyayyar kusan tawa ce.

Muna zaune gaban kayan ya shigo, tun da ya zauna nake bin sa da wani irin kallon kauna da ni kaina ban san ina masa ba, Hajiya Nene ikon Allah da duk motsin mu idanun ta na kai tana sake yadda da hukuncin da ta yanke a ran ta, dan ba zata zuba ido tana zaune azo ana mata fitsara a gida ba.

Ban samu yi masa godiya ba se da daddare, ko da na fara godiyar se kawai ya hade bakin mu waje guda, na lumshe ido kawai ban yi yunkurin kwace wa ba se da naji yana niyyar canja salo dan hannayen sa sun fara neman yin barna, na zame na juya na fita da sauri ina fadin na gode.

Washegari yana gama karyawa ya fita zuwa gidan yan uwan Nene, duk da ma daya ne ne Kawu Humed, gidan sa shima ba nisa da na Nene haka matar sa me kirki wadda ya kara aura dan ta farkon ya mutu, ina yawan zuwa gidan sedai dake basu da yara se gidan be cika dadi ba.

Ni kuma a gida be dade da fita ba Dr Bee'at tazo, nan muka kule a daka bayan ta gaida da su Nene, yaran ma Aunty A'i na tarkatawa dan na samu nutsuwar yin magana da ita.

Bayan ya gama jin komai da na fada ta gyara zama tace..................✍️.

Vote
Comment
Share fisabilillah

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 053 [ 19/07/2024 8:28pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Ouummey
Free book!!!

Ouummey 053

Page 5️⃣3️⃣

_________________________"Shawara kike so ko kuma goyon baya kike so?".

Na dubi Dr da mamaki, in ba shawara nake so ba har na zauna na bude nata ciki na haka?

"In har shawara kike so to ni dai cewa zan yi ki koma gidan mijin ki, in kuma goyon baya kike so se in yi backing din ki".

"Dr kar ki bata min rai pls, in ba shawara nake nema ba ai se in yi gaban kai na kawai ko?".

"Shine nace in dai ita kike nema to ki komawa mijin ki".

Hararar ta nayi ina kokarin mikewa dan da gaske na fara jin haushin wannan wulakancin da ta tsiro yau, ta maza ta riko ni tana dariya

"Dalla ina zaki?, Allah se kin zauna kin saurare ni tun da nima na saurare ki da farko".

Zama nayi ina tura baki gaba, na kau da kai gefe na ki yarda na kalle ta, itama baya damu ba ta shiga cewa

"Akwai dalilai da dama da ze sa ace ki komawa Masdooq, ba kuma iya ni zan fada miki haka ba, duk wanda ya san ku haka ze fada miki, kema kuma kin san wasu, one of which is yaran ku. Kin san dai ko da kuke jini daya Masdooq ba za bar miki yaran sa ba alhalin kin ki shi ba tare da wani kwakkwaran dalili ba?, Ze karbe su ne yaje ya kai wa matar sa me son sa, wannan dai da ta azabtar dake uwar su, to ina ha su kuma.
Na biyu, shin kina tunanin in kika rabu da Masdooq zumunci zaku cigaba da yi kamar yadda wautar ki ta gwada miki?, Bayan yana yi miki so me girma? Ko kina tunanin ba ze yi kishin ki ba? To bari kiji, daga lokacin da kika rabu da Masdooq kin raba zumunci tsakanin ku, ba da shi kadai ba har da iyayen sa da ma wasu cikin yan uwan sa, kin ga kuwa kin bata goma daya bata gyaru ba.
Na uku, Aimah kina tunanin zaki samu namijin da ze so ki ya kaunace ki a rayuwa kamar baban twins?, Bana jin zaki samu nan kusa, ban ce Miki babu ba amma wallahi wahala suke, namijin da ze so ki y kaunace ki a karan kan ki da dukkan flaws din ki, alhalin yawancin maza yanzu material love suke yi, a so ki dan kyan ki, surar ki ko kudin gidan ku, wanda wannan komai me iya karewa ne, amma namijin da ze so ki a ke kan ki shine namiji, wanda soyayyar sa is unconditional, dama ba dan wani abu ya so ki ba balle in ya kare ya bar ki, kalle ni dai, me na rasa? Ina da kyau, ina da ilimi haka gwargwado familyn mu na da rufin asiri, amma aure har yau ya gagara as my age of twenty eight, saboda me?, Duk mazan da ke zuwa waje na wani abu na tare da ni suka yi biyu ba ni karan kai na ba, ke kin samu kina neman yi wa kan ki sakiyar da ba ruwa Aimah?.
And lastly, in kin rabu da shi yaya zaki yi da soyayyar sa da kaunar sa da kike yi, ko an ce Miki kuna rabuwa zaki dena jin komai ne?, In haka kika dauka to maza ki aje, ko kun rabu da Masdooq ba zaki taba dena son sa ba, kuma duk namijin da kika aura da son wani a ran ki kin cuce shi dan ba zaki taba sauke hakkin sa yadda ya kamata ba, musamman dake ga zuri'a a tsakanin ku da dole se kun dinga haduwa, balle kuma ga zumunci, ina tabbatar Miki zaki jefa kan ki da kan ki halaka, kina auren wani namiji kina kaunar wani.
Kin ga wannan bayanin, bana tunanin duk inda kike je za'a fada miki akasin sa dan iya gaskiya na fada miki a matsayin kanwa ta kuma kawata".

"Hmmm". Na sauke numfashi, tun bayan tafiyar Dr ta bar ni da aikin tunani, se dai har yanzu da ake kiran sallar magrib na kasa gano nakasun shawarar ta, da farko ban aminta ba se da nayi consulting Aunty A'i, ba wai dan ban yadda ba se dan ina son jin ita kuma me zata ce, menene view din ta a kai, kamar kuwa hadin baki se ga shi ta maimaita maganganun Dr, har na ta kara akai, hakan ya sa jiki na yin sanyi na ji na aminta da shawarar su, sedai amma ina kara yin tunani ne dan jin ko zan hango wata baraka a shawarar na su.

Na sak sauke ajiyar zuciya a karo na ba adadi na mike zuwa daki, alwala nayi na gabatar da sallar magrib di ta, ina idarwa na yi tasbih din da na saba, se kuma na tashi zuwa dakin Nene, wunin yau ban gane mata ba, duk muka hada ido se in ga tana yi min kallon zan yi maganin ki, ko kuma zaki gane kuren ki, dan haka gwara naje muyi ta ta kare ni da ita, ba zan iya ba, ta bar ni naji da damuwar da ke damuna mana.

Na shiga da sallama, bata amsa ba ta daga min hannu ta cigaba da amsa wayar da take yi, tana ajewa ta dube ni sa'ilin da nake kokarin yin magana

"Tashi kije ki cewa A'i a sa abincin daren da yawa, in kuma ta gama ki kama mata ku yi sabo, muna da baki zuwa anjima".

Na kalle ta sosai da mamaki,

"Baki kuma Nene?, Dama kina da wasu dangin bayan Kawu Humed da har zasu kawo miki ziyara?".

"A'a Nu'aimah, ai ni da shi daga sama muka fado, kin ga ai ba zamu yi dangi ba".

Na turo baki cikin jin haushi dan na fahimci magana ce ta fada min

"Wai ni Nene me na miki ne da yau wuni guda kike ta nema na da fada, ehe tsakani da Allah ni dai na san ban miki komai ba".

"Ai nice dage Sarkin fada, kin ga kuwa ina zan jira se an min wani abu kafin nayi halin nawa?".

Na fa lura tsohuwar nan magana take nema da ni, so take in kula ta ta rikice, to ba dani ba, se na tashi ina cewa

"Ni dai Allah ya huci zuciyar ki, bari na je na fadawa Auntyn".

Na samu na gudu, ko da na sanar da Aunty babu jinkiri muka shiga hada sabon abinci dan har ta gama mana tuwon shinkafa miyar kuka ashe, muna aikin kuna hira, ta na cigaba da bani tips din zama da kishiya, tana sake kuma tausa ta akan Masdooq.

A haka na ji sallamar sa da shigowar sa, muka amsa daga kitchen din, be shigo ba ya mana sannu da aiki ya baje gaban yaran sa dake wasa, Safar dazu aka zo aka tafi da ita gida saboda makaranta, muna daga kitchen din muna jiyo su, yadda suke wasa yana biye musu kamar shima yaro ne abin gwanin sha'awa.

Se da aka kira Isha ya tashi ya fita bayan ya leko ya sake mana sannu da aiki, ganin mun hada komai saura kawai saukewa se nace wa Aunty A'i bari na je nayi sallah, ta min sannu da aiki na fita ina dariya dan fiye da rabin aikin ita tayi, ni wanda na yi be taka kara ya karya ba.

Wanka na fara yi dan zubda maiko da kamshin abinci da na kwaso, na fito daure da guntun towel dina ina tafe ina yarfe ruwan da ya taba min gashi, na zauna kan stool a gaban mirror ina sake tsane kan, se da na goge sosai sannan na sake shi yayi baya, na shiga shafe jiki na da mayuka na masu tsada da basa toning, ina gamawa na dau deodorant shima na goga kana na dauki man palms dina shima na shafa se kuma na kafa, na gama shafe shafe na da gyaran kai na tashi dan dauko kayan da zan sa, a lokacin ne nayi ido hudu da shi zaune kan bakin bed dina idanun sa da duk wani attention din sa a kai na, firgita nayi da farko dan ban ji bude kofa ba balle shigowar sa, na ja baya da sauri ina damke towel dina, gaba daya na rikice musamman da ganin irin kallon da yake min idanun sa sun sake shanyewa haka har wani ruwa ruwa ne suka kwanta ciki, da azama na afka toilet tare da locking kofar, na jingina jikin ta ina maida numfashi.

A sannu naji takun sa na yowa wajen kofar, har na ji shi jikin ta shima ya jingina kamar yadda nayi, wannan cool deep voice din nasa ya sake deepening, can kasan makoshi ya ce

"Ki in ji Nene".

Na dan dubi kofar kamar shi nake gani
"Nene kuma?".

Ina iya jin sautin fitar huci me zafi daga bakin sa kafin yace

"Zaku gaisa da bakin ta".

"Oh, har sun karaso kenan, okay bari na saka kayan se in zo".

Na fadi haka wai da nufin ya tafi ya bani space in shirya, amma se na ji shiru babu takun sa, nayi kasa da murya cikin tabara nace

"Please sweetheart mana, kaje zan saka kaya ne fa".

Se kuwa naji takun sa yana barin wajen, can kuma naji bude kofa tare da rufewa, hakan ya shaida min ya tafi, na bude kofar toilet din na fito ina sakin ajiyar zuciya, ni ina zan iya da rigimar sweetheart, gaskiya ya koyi tabara da shagwaba kamar ba shi ba, mtsww, nayi tsaki a

raina ina cewa ai duk wannan matar tasa ce ta bata shi.

Ban ankara ba se jin an min wani wawan runguma nayi har towel dina na neman faduwa, na firgita matuka musamman da na gane shi ne dan kamshin turaren sa da kuma warmness din da a jikin sa kadai nake jin sa, na shiga kici kicin kwace wa ina cewa cikin rawar murya

"Kaya fa zan saka sweetheart, kuma ka san Nene na jira na, Please ka sake ni".

"I...wanntt..only..your warmness, ba abinda zan miki, ki nutsu".

Duk d ban gama yarda ba haka na nutsun kamar yadda yace, ya kara kwakume ni yana tura kan sa cikin wuya na, jikina ya dauki rawa amma ban janye ba, kusan minti goma a haka kafin ya janye jikin sa ya shige toilet dina, na saki wata bahaguwar ajiyar zuciya ina rufe ido, se kuma na maza na bude na shiga saka kaya na da sauri gudun kar ya fito ban gama ba.

Silver English gown na saka cikin wanda ya siyo min jiya, ta min cif cif kuwa kamar an gwada ni, tana da kyau sosai an yi mata ado da beads, na dau dan karamin scarf din da suka sa da be wuce in kama gashi da shi ba, haka kuwa ma nayi nayi, ina gama packing kan na saka scarf din na daure da shi, na kitse jelar kana na zagaye parking din da ita.

Fuska ta na wadata ido na da kohl, baki na kuma da wet lips, shikenan ban Kara komai ba, na zura bakin bedroom slippers dina na nufi fita falon, se naji tattausan hannun sa ya ratsa damtse na ya dawo dani baya, idanun sa akan lips dina dake shining, kawai ya rufe idon sa ya nufo fuska ta da tasa, gane me ze yi yasa na sa hannu na tare fuskar sa da sauri, ya bude min idanun sa tar gaba daya a kai na, ya subhanallah, ai ban san sanda na saki fuskar tasa ba dan wani irin mashi masu tsananin kaifi na ji suna fitowa daga idanun sa zuwa nawa, karin abin wani tattausan murmushi da ya sake min kana ya karasa ya hade fuskar mu waje daya ya shigar da lips dina cikin nasa.

Yana gama shanye wet lips din ya cika ni ya ja baya yana bin fuskar tawa da kallo, da alama so yake ya tabbatar ya shanye gaba daya kafin ya sake ni, aikuwa yana gani babu se ya cika ni tare da nuna min hanya, da sauri na fita ya rufa min baya.

Turus nayi a falon ganin wadanda ban taba zata ba, Guess who?!.

Su Hajiya Yayah ne, Baba, Mama, Ya Salman, Ya Najeeb, Ya Farooq, Aunty Luba, Ya Ahmad se matayen su, Aunty lateefa da Aunty Siddiqa se kuma ƴaƴan su.

Mutuwar tsaye nayi dan ko kafa ta ba kasa motsawa, bin su kawai nake da kallo daya bayan daya abubuwan da suka faru a baya na dawo min daki daki, hawaye suka shiga tsere a kumatu na, jiki na kuma ya kwashi rawa, da sauri na juya zan koma daki ya riko ni, na juyo da sauri se na sauke idanu na kan sa, ya girgiza min kai nima se na shiga girgiza nawa, ba zan iya abinda yake so ba, ba zan iya tsayawa gaban mutanen nan ba, zuciya ta a karye take da iya ganin su,

kaunar su da kewar su ta cika min rai, sedai su kuma na san ba abinda ya kawo su ba kenan, maybe ma sun zo su saka Nene itama ta kore ni ne.

Yin wannan tunanin se na fincike na koma dakin da gudu, ya rufa min baya a sukwane, ya dago ni daga jinginar da nayi da garu ina kuka ya rungume, nima na saka hannu na sake kankame shi, kukan da nake yi yana tafiya da duk wani zafi da haushin su da nake ji a raina, so, kauna, da kewar su na maye gurbin su
Da kyar da lallashi da ban baki Ya samu na daina kukan kana ya shawo kai na da kyar na fita falon, can gefe na je na zauna se shima yq biyo ni ya zauna kusa da ni tare da riko hannu na, da idanun sa ya ce min "I'm here with you". Na sunkuyar da kai na kafin gently na gaishe su irin general din nan, kamar masu jira suka shiga amsawa baki na rawa.

Nasiha sosai Nene ta yi a wajen, kana ta gwadawa kowa laifin sa, musamman Mama da su Ya Salman, Baba kam shi ba'a ba shi laifin komai ba dan tace bai da shi, itama abinda yayi na hukunci ta dauke shi as daidai a matsayin sa na wanda ya isa dani, dan haka a wajen ni ta bawa laifi, Hajiya Yayah ma laifin ta kadan be, na kasa zuwa ta duba ni bayan ta kai ni gidan Masdooq, ban da haka bata da wani laifi, Aunty Luba ma an wanke ta tas haka nima a idanu na ta fita dan uzurin ta me girma ne, mijin ta ne ya mata tsakani da ni, ta kuma yi masa biyayya, Ya Ahmad ma laifin sa kadan ne, duk da ba mazauni ne bane ya kama ta ace in ya shigo yazo ya ga a wane hali nake ciki kuma a gaisa, Mama, Ya Salman, Ya Najeeb da Ya Farooq sune ainahin masu laifi, fada sosai Nene ta musu, kana ta dawo nasiha, daga karshe tace a yafi juna, duk suka bani hakuri wanda ina kuka nake amsawa, ban da ma da karfafa gwiwar gwarzona bana jin zan iya zama a wajen, amma hannun sa dake cikin nawa su suka bani confidence din fuskantar kowa, suna bani hakuri ina basu, haka aka yayyafi juna aka manta komai, sedai na kasa sakin jiki da su gaba daya, har gwara Aunty Luba.

Ba'a tashi a wajen ba Hajiya Nene ikon Allah ta zartar da hukuncin ta na komawa ta gidana jibi tare da miji na, tace ya hakura da komawa gobe ya jira jibi mu tafi gaba daya har su Hajiya Yayah, Nene fa bata ko ji ta baki na ba ta yanke hukuncin ta, Allah ma yasa nima na yarda da komawar da Yasin se mata bore.

Ya Masdooq kuwa ba wanda ya kai shi murna da farin ciki, bini bini da mun hada ido ze min winking, ga wani smirk da yake saki, ni kuwa na bi na hade fuska kamar wadda aka turowa sakon mutuwa, a cikin raina kuwa zulumi ne da fargaba tari guda....................✍️.

*KAR KU MANTA BONANZA IS YET TO END, JUST 1K AND READ 3 AMAZING NOVELS, YAR DAMFARA, RASHIN HAIHUWA AND ANJANE, KAR KU BARI A BAKU LABARI*

Vote
Comment
Share fisabilillah

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 054  [ 19/07/2024 8:31pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Ouummey
Free book!!!

*KAR KU MANTA BONANZA IS YET TO END, JUST 1K AND READ 3 AMAZING NOVELS, YAR DAMFARA, RASHIN HAIHUWA AND ANJANE, KAR KU BARI A BAKU LABARI*

Ouummey 054

Page 5️⃣4️⃣

________________________Jiya muka sauka a Nigeria, mun baro mutanen Ethiopia cike da kewa da begen juna, Dr Bee'at kuwa mun sha kuka ni da ita kamar ba za'a sake haduwa ba washegarin zuwan su Hajiya Yayah na kira ta na sanar mata da komai, se kuwa gata har da Maman ta, muka bar su tare su manyan bayan ta gaishe su, mu kuma muka kule daka ni da ita da Aunty Luba, Aunty Luba ce ta sake maimaita mata labarin mu har zuwa jiya, se gashi kamar an dade da juna, ita da Aunty Luba kamar da ma can sun saba, sune har da musayen number waya.

Lokacin da muka fito dan raka ni makarantar islamiyya in musu sallama ne su kuma mazan suka shigo, suma duk suka gaisa ina introducing din ta, itama ina fada mata wannan ne Ya wane, har aka zo kan Ya Ahmad, irin kallon da yake bin Dr yasa ni da Aunty Luba kallon juna cikin mamaki dan Ya Ahmad ba ruwan sa da mata, ko aiki be fiya so ya hada shi da mace ba, se gashi ya shagala da kallon Dr har ma be iya jin gaisuwar da ta masa ba se da na maimaita masa, cikin borin kunya ya amsa tare da wucewa da sauri, se hakan ya bamu dariya muka shiga kyakyatawa kuwa.

Ko bayan mun dawo daga islamiyya an zauna cik abincin rana haka ya dinga satar kallon ta har se da itama ta gane, se gashi an koma yar satar kallon juna, mu dai muna daga gefe ni da Aunty Luba muna kallon ikon Allah.

Cikin hukuncin Ubangiji a ranar da zamu taho Ya Ahmad yayi proposing soyayyar sa wa Dr, bata wani ja ba tayi accepting, aikuwa ba karamin faranta min hakan yayi ba, babu wanda ya kai ni murna dan Ya Ahmad na auro ta shikenan mun sake hadewa abin mu.

A gidan Hajiya Yayah na sauka haka ma Mama, nan suka sake neman yafiya ta har abin na bani kunya, basu dena ba se da na fashe musu da kuka ina tabbatar musu su iyaye ne gare ni Ni ban rike su ba.

Gida na daban Ya Masdooq yasa aka gyara min a cikin gidajen sa, dake tun ainahi he's not the polygamous type, duka gidajen sa tsarin zaman mace daye ne da su, se gashi Allah ya jarrabe shi da auren mata biyu.

Tun kan muzo gidan an gama gyarawa amma dai Hajiya Yayah tace na sauka gidan ta na kara hutawa kafin na shiga.

Washegarin dawowar mu ni da Aunty Luba tazo muka tafi wajen gyaran jiki, gyara ne aka min me suna gyara in and out duk da cewa ina gyara na a can amma wannan daban ne, a wuni guda se gashi na canja matuka, hatta gashi na da bana wasa da gyara shi yau gyaran da yasha na daban ne, kamshi kuwa kamar an ciro ni daga cikin turare, kayan gyaran jiki tun ina can Nene ta dinga bani, a lokacin ban gane ba cewa take dauri ne saboda yara na, se da dazu kafin fitowar mu Hajiya Yayah ta min hadin gumba sannan na gane wato Nene rufe ni tai baibai, amma ko ba komai dai na gode.

Aunty Luba tace ta aje min wasu amma ba yanzu ba , tafi so in zan yi amfani da su ya zama su kadai ne zan yi dan in gane ingancin su da kyan su, k da muka koma gida Hajiya Yayah se yaba wa take, ita dai Mama bata magana se murmushi da bina da kallo, duk wani shiri da ya kamata ayi an yi, kaya na na hade waje daya tsaf, har na gidan Mama Aunty Luba taje sun hado min ita da mama ladi, sun kuma kai gidana sun jera min, Baba uba nagari me so da kauna ta shi yayi min kayan daki, tun daga kan furnitures har zuwa kan kujeru, kayan gado set uku adadin bedrooms dake gidan, daya a kasa biyu a sama se falo biyu, sama da kasa, se kuma kitchen

din girki dake kasa da kuma mini kitchen da ba'a girki a sama.

Komai da aka zuba a gidan nan unique ne, sam babu gama garin kaya, duk da ban je na gani ba amma a hoto kadai da Aunty Luba ta nuna min se da na kasa cewa komai.

Ado blue-black aka yi da milk, karshen haduwa gidan ya hadu, abin da ya kara dadada min har da garden da nake masifar so, kai gida fa yayi iya yi.

Ranar da zamu tare ni da shi kadai muka tafi ban da yara, Hajiya Yayah tace mu bar su a wajen su tukuna suma su saba da su, bayan mun sha nasiha me ratsa jini da jiki a wajen Baba da Hajiya Yayah, Mama kam albarka kadai ta saka mana, muka shiga gidan mu bisa rakiyar yayye na gaba daya da yar uwa daya tamkar da dubu Aunty Luba, godiya kam har na rasa kalar wadda xan mata dan ita tayi tsaye kan duk wani abu da za'a siya a sa min a gidan, da kuma tsarin da aka yi jeren, bata zauna ba se da ta ga komai da komai yayi yadda ya kamata.

Karfe goma duka yayye na suka min sallama suka tafi bayan sun saka min kudade masu kauri a account, kowanne da irin tasa bajintar dan ya Farooq bayan kudin ya dau nauyin renovating shago na na kwalliya da gyaran jiki, Ya Salman kuma yace ze bude min na snacks, shi kam ya Najeeb mota ya bani karama me kyau irin ta mata, Ya Ahmad sarkar gold da dan kunnen ta ya bani, na rasa ma godiyar da zan musu se kawai na fashe musu da kuka, da kyar Ya Masdooq ya bambaro ni daga jikin Aunty Luba suka samu suka tafi.

Ya rufo gidan bayan sun tafi dan ba megadi tukuna, sun dai yi magana da Ya Farooq kan a samo masa me gaskiya da rikon amana.

A falon sama muka zauna,

"Ina zuwa Barbie".

Yace yana nufar mini kitchen din dake Wani corridor, ban jira shi ba na tashi na shiga zagaye gidan ina godiya ga Allah da kuma Baba at the same time, se na dinga jin sam ban kyauta ba a baya da na zargi Baba da son kai, dattijon ya fi karfin haka ya kuma wuce wannan karantar.

Ina tsaye cikin main kitchen din mu na kasa ina kallon irin dukiyar da aka narka ya shigo, sanyin hannun sa cikin nawa ya shaida min tsayuwar sa a tare da ni, ya rungumo ni ta baya kai na a kirjin sa shi kuma ya dora kan sa a kai na yake cewa

"Shi ne kika gudu kika bar ni ko?".

Da murmushin yadda yayi maganar a shagwabe na bashi amsa da

"I just can't wait na ga gida na ne".

"Uhm to wa kika fi so?".

"Tsakanin wa da wa kenan?".

"Ni da gidan naki mana".

Yar dariya nayi ina lumshe ido jin yadda yake goga min kan sa a kai na hannun sa na shafa wuya na

"Taya ma zaka hada kan ka da gida na, wannan fa gida na ne ni kadai, kai kuma mijin mu ne mu biyu ni da Sa'adah, to zan fi so, na mu na mu biyu ko nawa na ni kadai?".

Juyo da ni yayi gaba daya yana bin lips dina da wani tsumammen kallo

"Kina so kice dai kin fi son gidan ki ko?".

"To ni dai ban ce ba".

Na fada ina karya wuya murmushi na escaping lips dina, be yi wata wata ba ya hade fuskar mu ya cafke lips dina ya shiga kissing, ban ki ba na saka hannu na zagaye wuyan sa ina dage nima ina taya shi.

Ban san yaushe ya dauke ni ba dan hankali na yayi gaba se da ya janye na gan mu a falon sama gaban plates din da ya dauko ya aje gefen ledojin da muka taho da su.

A hankali na sauke ajiyar zuciya ina saisaita kai na, kunya ta kama ni ganin yadda ya zuba min ido, muna hada ido a karo na barkatai na masa hararar wasa se ya fashe da dariya, kayan ledar ya shiga zuba mana cikin plate din,  chicken cottage ne, se potato salad, gefe kuma fresh milk da kefir ne.

A nutse ya matso dap plate din kusa da ni, kana ya dau spoon ya debo ya nufi baki na yana dage min gira, a hankali na bude ya saka min, na lumshe ido taste din potato salad din na ratsa ni, na taso ina mai sign din ina zuwa.

Kitchen din sama na shiga na wanke hannu na sannan na koma, Bismillah nayi na sa hannu na debo na nufi bakin sa, bude wa yayi na sa masa, har da hannu na ya haɗa ya side kamar ze cinye sannan ya saki, ni kuwa duk jiki na ya saki saboda abinda yake min, a haka muka gama ci ina bashi ina bawa kai na dan na ki karbar na hannun sa dan ni ban ga cin wadannan abubuwan da spoon ba.
Ni na kwashe kayan na nufi kitchen shi kuma yana take min baya , ban aje ba se da na wanke yana nanike a baya na kamar wani baby.

Daki muka shiga, wai ashe daki daya zamu zauna shi ba ya san mu raba daki, gaba daya am

not comfortable, fahimtar hakan yasa ya fita yace bari yazo, da wannan damar nayi amfani na yi wanka na canja kaya har ma na haye bed na kwanta tare da lulluba.

Se da nayi minti kusan biyar sannan ya shigo, ya shiga wanka ya fito ya hau shirya wa, nidai na rufe ido abina, yana gama shirya wa ya je yayi locking kofar ya dawo ya zauna gefen bed, addu'a yayi ya shafa nima ya tambaye ni nayi, gyada masa kai kawai nayi, se ya kashe wutar ya hawo gadon gaba daya.

Kirji na ya shiga dukan uku uku na abinda ke iya faruwa a daren, duk da ba shi ne karo na farko ba balle na biyu ban dena fargaba, na farko ta karfi ne yayi min, na biyu ma kusan haka shiyasa tsoron lamarin ya shige ni, ban kuma san wani dadi ko wani abu ba dan ba zan iya karar da komai ba.

Gaba na ya yanke ya fadi lokacin da ya jawo ni jikin sa ya rungume, fargaba ta sake cika ni, shiru shiru ina jiran jin wani abu amma babu, da aka dan dau lokaci ma se na ji sauyin fitar numfashin sa alamun yayi bacci, se lokacin hankali na ya kwanta nima na rufe ido, not long bacci yayi gaba da ni.

Washegari ya tashe ni sallar asuba shi kuma ya tafi masallaci, ina idar da sallah ban koma ba na gyara  gadon da ya dan yamutse kadan, na fesa turare kana na jona burner na saka na wuta.

Mintina goma na bashi ya yi yadda nake so na zare socket din kana na daga curtains din window dana kofa kamshin ya fita ya zama saura me sanyin dadi, nai wanka na fito, a gurguje nayi shafe shafe na ganin gari ya fara haske, atamfa na saka baka me ratsin golden color, ɗinkin fitted gown ne cikin kaya na na gida, sawa daya na mata se wannan na biyu, tana min kyau nima na sani, na kafa daurin da ya fito da gashi na ta baya, ya karkace ta gefe, yau kam kwalliya na yi me kyau, casual sassauka nayi na yi wankan turare kamar yadda na saba, na fita falo na cakare, ban dade da zama ba ya shigo, kasa karasowa cikin falon yayi ya kame waje daya yana bina da kallo kamar wadda ya fara gani yau, ganin ya kasa shigowa ni se na tashi na shiga takawa gare shi, cikin taku na me daukan hankali ina rausaya kamar wani reshen bishiya wnada naturally haka tafiya ba yake, mutane da yawa kuma na ganin ai iya yi ne.

Ban yi wata wata ba na fada jikin sa na rungume shi, se lokacin shima ya sauke nannauyan numfashi ya saka hannayen sa dake rawa ya sake jana cikin jikin sa yana zura kan sa ko ina a jiki na ciki shaƙar daddadan kamshin da nake yi.

A sannu na shiga tafiya ina cikin jikin sa shima yana bina with each step da nake yi backward, a haka muka kai cikin falon, na zame baya da sauri shi kuma ya fada zaune cikin kujera cikin rashin kwarin jiki, nima se na koma wata na zauna, se da na bari ya dawo nutsuwar sa sannan na sulale kasa a gaban sa nace

"Ina kwana?".

Zuba min ido yayi

"Wa yace miki haka ake gaida miji?".

Na dago na zuba masa lulu eyes dina ina kada su

"To yaya ake yi?".

"Come on, zo na nuna miki".

Na kalli farin tafin hannun sa tas kamar ba na namiji ba, in a slow motion coke da jan aji na dora nawa a kai, ya kama ni na tashi kana ya dora ni kan laps din sa, yayo kasa da fuskar sa ya hade goshin mu da tsinin hancin mu, muka zubawa juna ido cike da bege da matsananciyar kauna, zan rufe ido ganin yana karkata kan sa,

"No Please, kar ki rufe idon, kalle ni".

Da kyar na iya sake ware idanu na da suke neman lumshewa da kan su na watsa cikin nasa, a haka ya karkata kan sa ya daidaita bakin sa da nawa, idanun sa cikin nawa ya kai bakin sa kan nawa ya kama ya shiga kissing roughly, gashi ya rike idanun sa cikin nawa ya hana ni janye wa.

A sannu ya sa hannu ya ture dankwalin dake kai na ya shiga yamutsa gyararren gashi na dake kwance luf, hannun sa ya shiga yawo a sassan jiki na, ban hana ba dan ban da niyyar hakan se shine ya takawa kan sa da kan sa burki ya janye ya koma ya zauna ya zaunar da ni kan laps din sa, a haka har mukai regaining nutsuwar mu.

Hannun sa ya saka a kan fatar bayana da ke bude yana shafawa

"Kin ga yadda ake gaida miji".

Na juya na saka hannu na shafa sajen sa dake kwance luf luf na kai baki nau'i kissing idanun sa ban ce komai ba na koma na sake lafewa cikin jikin sa.
Bacci muka koma, bamu tashi ba se after ten, da kyar Ya hakura ya bar ni na hada mana breakfast bayan na kira Hajiya Yayah na ce kar a kawo mana abinci.

Haka muka karashe kwanа dayan mu ba abinda ya haɗa mu wani daban ban da shafe shafe da kissing, ranar da ya koma wa Sa'adah kuwa na sha kuka abina na kewar sa da kishin sa, sedai ya na iya, tsarin Allah ne.

Inda na ji sauki tun da ya fita office muke kan waya, be bar ni ba se da yaji na saki, da ya tashi office kuwa nan ya fara zuwa, though a gurguje muka gaisa ya tafi, wannan ya sake bata min rai, kai da mijin ka ace wai a tsaitsaye zaku gaisa, haka dai har ya karasa kwanan sa na can ya

dawo min.

Tarba na shirya masa ta gani ta fada, yana zuwa muka fadawa junan mu kamar wasu mayu, kafin na sake shi ya tafi wanka, yana fitowa na gabatar masa da daddadan abinci na cika masa tumbin sa, daga nan muka cigaba da soyayyar mu abin mu.

Kamar wasa ina ganin ya bar ni ne in huta har abin ya soma damu na, gani nan dai in ci me kyau in sha me kyau, duk sanda baya tare da ni a gida muna tare a kan waya, soyayya ruwa ruwa yake gwada min nima ina kokarin ganin na maida masa, sedai abin na sosa min zuciya yadda duk yake nuna kwadayin sa a kai na be taba tsallake romancing ba, ko da wasa be gwada wucewa ba, da yaga ma yana neman missing control ze sake ni ya fita daga dakin ko kuwa ya juya min baya.

Ina so in sanar da Aunty Luba amma na kasa, gani nake zan tona asirin aure na ne, Dr Bee'at kuwa bata ma da aure balle na fara sanar da ita, to yaya zan yi ne!!!..............✍️.

*KAR KU MANTA BONANZA IS YET TO END, JUST 1K AND READ 3 AMAZING NOVELS, YAR DAMFARA, RASHIN HAIHUWA AND ANJANE, KAR KU BARI A BAKU LABARI*

Vote
Comment
Share fisabilillah.

Ouummey 📚✍️.

Ouummey 055 [ 20/07/2024 8:35pm ]

BA KOWANE SO BANE...
(yake zama samu)

✍️ Ouummey
Free book!!!

Last page

____________________Iya dubawa ta na rasa wa zan nufa da wannan batun dan haka na hakura na kawo ido na saka masa, sedai na fara janye masa, ba kamar baya da in ya taba nu nake biye masa ba, yanzu da ya kawo hannu nake gocewa, in kuwa ya rike ni na dinga neman zame wa kenan.

To tsakani da Allah kan zan cigaba da yadda yana gwama min lissafi yana bari na cikin wani hali, saboda shi ya san yana da wata matar da ze iya zuwa ta magance masa damuwar sa, to ni ma kam na dena yarda.

Wannan janye masan da na fara yana damun sa, duk da be fito fili ya nuna ba amma in na kwace daga jikin sa fuskar sa na nuna damuwa, ban kuma taba nuna na gani ba, so nake yi ya gaji ya magantu da kan sa, daga nan ni kuma se in amayar da abinda ke raina.

Kun san lamari irin na shaidan, wannan halin da Ya Masdooq ke gwada min se yake tunzura zuciya ta, yana sa min sake sake cewa ai dama Ya Masdooq baya so na yanzu, tausayi na da neman ganin ya farantawa iyayen mu yasa ya dage ya dawo dani, ba wai dan kauna ba.

So daya dai matar sa yake yi wa, ita yake kauna shiyasa a idanu na har rawar jiki yake yi in ze koma mata, ranar da nayi wannan tunanin wuni nayi ina kuka, kuma dake ranar ya bar gida na se ban samu me rarrashi ba, na yi kuka iya kuka har idanu na suka kumbura, zazzaɓi ya rufe ni me hade da ciwon kai, na kwana da shi na tashi, be sake ni ba se da rana da na daure na sha maganin da na tsana.

Wannan ɗan zazzabin da kuka banzan tunanin da na kakabawa raina yasa har faɗawa nayi a kwanakin.

Ranar da ya dawo gida na kuwa ba wani tarba ta daban, ba wannan murna da rawar jikin da nake yi, duk gaba daya se ya sha jinin jikin sa, damuwar yanayi na yasa fara'ar da ya shigo da ita ta bace.

Na dago na kalle shi lokacin da yake tambaya ta me ke damuna, ban san me zance masa ba, damuwar yadda ka ɗauke ni ba mace ba zan ce ko kuwa cewa zan yi damuwar rashin soyayyar ka gare ni?, Se kawai na kada kai nace ba komai.

"Kin ga yadda kika rame kuwa a kwanaki biyu kadai Barbie? Kuma kice min ba abinda yake damun ki kiyi tunanin zan yarda?".

Bana san ya matsa min da tambayoyi se nace

"Nayi zazzaɓi da ciwon kai ne jiya da shekaranjiya, seda na sha magani sannan na samu sauki".

Ya na kokarin rungume ni a jikin sa yace

"An so very sorry, kin yi rashin lafiya har kin tashi ban sani ba, kiyi hakuri, but please ba fata nake ba amma duk sanda kika ji ki ba daidai ba ki sanar min ko da kuwa ba a gidan nan nake ba, lafiyar ki sama yake da komai kin ji ko?".

Zame wa na shiga yi dan bana san wannan nanike min din da yake, tun da baya buƙata ta a matsayin mayar sa then why the teasing

"Insha Allah, ban kira ka bane kar na katse muku nutsuwar ku ko na shiga lokacin ku".

Irin yadda words din suka min ɗaci a harshe Allah ne kaɗai ya sani, amma ya zan yi tun da wanda nake yi dan shi be san ina yi ba.

Ranar duka ban bari ya taba ni da wani niyya ba, kissing ɗin da ya maida kamar wani farilla na ki yarda, hatta rungumar da yake min in zamu yi bacci yau duk na hana hakan, yana sake miko hannu a karo na uku dan ja na jikin sa na ture hannun nace

"Pleaaaasseee".

Ban san me ya gani ba da ya kyale ni sedai ya matso dab dani har muna shakar numfashi juna, hakan kuma yana affecting dina, se na juya masa baya a hankali kuma na matsa can ɗaya edge din gadon, ina jin idanun sa a jiki na shaidar kallo na ne yake yi, sai dai ya zan yi, be bar ni da wani zabin ba bayan wannan.

A haka muka kwana, da safe na tashi da wuri na hada masa breakfast kamar yadda na saba, na hada masa ruwan wanka a toilet sannan na tashe shi, yana shiga wanka na fitar masa da kayan da ze saka na feshe su da turare kana na aje masa kan bed na fita.
Dining na kuma na zauna ina jiran fitowar sa, na zuba tagumi hannu bibbiyu na lula cikin tunani, nayi nisa da har ban san fitowar sa ba se da ya sa hannu ya janye min tagumin ya zauna gefe na cikin rashin daɗin rai.

Nayi firgigit na kalle shi se kuma na maida kai kasa saboda dan uban kyan da ya zuba, bana san na fiya kallan sa dan zuciya ta raunana zata sake yi, se kawai na janyo plate na shiga zuba masa abinci, dake ya fi son abinci me dan nauyi da safe, ina gama zubawa na saka spoon a ciki

na tura masa gaban sa ina fadin

"Na kwanta kan hannu na yana min zafi, please help me and feed yourself".

Da sauri ya miko hannun sa dan kama nawa se nayi azamar mai da shi baya, karya nayi ba wani kwanta wa da nayi kan hannun, kawai ciyar da shi din ne yau bana jin yi dan bana cikin dadin rai kwata kwata, kuma ba zan iya pretending ba.

"In ga hannun?".

Na girgiza kai ina faking smile

"No ai ba wani serious issue bane, ze bari zuwa anjima insha Allah".

Insisting yayi nima kuma na ki bayarwa dan babu abinda hannun yayi, yana gani ze gane karya nake, kiran wayar sa da aka yi ne ya cece ni, daga wajen aikin su ne ana bukatar shi urgently, wannan ya sa ya bar maganar ba wai dan ta mutu ba, ya ci abincin da sauri kuma sama sama kana ya mike dan tafiya.

A maimakon compound da nake raka shi har gaban mota, yau a bakin falo na tsaya na masa addu'a, na karashe da fadin

"Zan yi aiki ne a ciki, ban gyara kitchen din da nayi girki ba".

Ya gyada min kai kawai tare da pecking goshi na ya juya da sauri ya fice.
Baki ne ke jiran sa, nan suka shiga gabatar da abinda ya kawo su har zuwa lokacin da ya gama da su suka tafi, a lokacin ne kuma ya samu nutsuwar yin tunanin abinda ya addabe shi.

Gaba daya Barbie ta canja masa, ba ze iya cewa ga ta inda ta canja ba tun da bata dena masa duk wani hidima da ta saba ba, sedai ta janye kusancin da ke tsakanin su, kwata kwata kamar ba ita ce suke tare last month cikin farin ciki ba, abu daya ya sani, dole ya titsiye ta ya ji keke faruwa.

Kalli fa jiya kwata kwata taki ya rabe ta, ba hug ba kiss, hatta a bed se ta juya masa baya, to me yayi mata haka?, Ko bata san da wannan kananun abubuwan yake samu ya rage zafi bane? Ko kuwa bata san irin karfin halin da yake yi wajen ganin be forcing kan shi a gare ta ba?, Ta san kuwa yadda take birkita shi? Yo van da Allah ma yana shiga lamarin ta ya ya ze iya dinga controlling kan sa a kan ta bayan ya kasance Burin zuciyar sa.

Ba ya so ne ya takura ta a wannan fannin, baya son ya tursasa mata abinda bata so ko bata shirya ba, shiyasa yake janye wa har zuwa lokacin da a nasa tunanin zata yadda da cakuduwar rayuwar su waje daya, ba wai shi ya tursasa mata hakan ba, yana so n ko me ze faru ya kasance da san ran ta, da kuma soyayyar sa a zuciyar ta, ba wai a yi rayuwa tana hakuri da shi

a ran ta ba alhalin bata son shi.

Wannan shine view din shi, da zuciyar sa ta yadda da hakan tunanin sa ma kuma ya daidaita a kai.....!.

Na sauke ajiyar zuciya bayan tafiyar sa, na koma dining din da niyyar karyawa sedai na kasa taba komai se tagumi da nayi, har yau zuciya ta ta kasa aminta da na sanar da wani matsala ta, se nake ganin ban zama mace me iya sirranta damuwar gidan auren ta ba, shiyasa na zabi zama da matsalar batare da na sanar an bani shawara ko maganin ta ba.

Da kyar na iya three spoon na ake, abinci baya min dadi a baki, se kawai na tattara na kai kitchen na saka a fridge, na debo kayan fruits na yayyanka na dauka zuwa falon sama na kunna TV na aje abina ina sha ina kallo, karfi da yaji na kore damuwar da ke raina saboda gudun komawa yar gidan jiya, bana so lafiya ta ta sake tabuwa akan abinda be taka kara ya karya ba, musamman  na san ba so na yake ba, to kuwa be cancanci in cutar da kai na saboda shi ba.

Da wannan na samu saukin halin da nake ciki, na wuni cikin sanyin rai daidai gwargwado, da na gaji da kallon na kira Dr muka sha firar mu, se gashi har ina dariya dan akwai ta da barkwanci.

Da yamma na hada masa abinci yadda ba saba, na jere kan dining na shiga daki na canja wanka na sauya kaya zuwa marasa nauyi, doguwar rigar wani cotton material ne me taushi kuma ba nauyi, rigar ta tsaya min kan kauri na, ta sama kuma gajeran hannu ne da ita iya armpit, bata da fadi amma kuma bata kama ni tsam ba, ta min kyau sosai haka kuma se bin jiki na take yi tana kwantawa saboda rashin nauyin yadin.

Na fesa turare tare da kana gashi na cikin ribbon kana na sake shi yana reto a baya na, idanu na sun sha kohl baki na kuma lipgloss, bayan su ban Kara komai ba se mascara da na sa na taje gashin idanu na.

Ban dade da zama a falon ba ya dawo, ya dinga bi na da ido duk inda nayi dan kiri kiri na zame daga rungumar da yaso yi min, dole ya shiga wankan da nake fadin na hada masa ruwa, yana futyya canja kaya ya dau key din mota ya tafi duba Sa'adah.

Wannan na ɗaya daga cikin abinda ke tabbatar min da itace yake so, ni kawai alfarma yayi min ta zama cikin rayuwar sa, in dai a gida na yake yana dawowa daga aiki yayi wanka to ze tafi duba ta ne, ni kuma in yana gidan ta da safe yake zuwa duba ni in ya fito tafiya aiki, kullum a gurguje muke gaisawa saboda kar ya makara, daga nan se wata safiyar, ita kuwa bayan ya dawo saboda su samu lokacin juna sosai da sosai, nayi murmushin takaici kawai.

Be dawo ba se bayan sallar magrib kamar yadda ya saba, na gaishe shi kawai na cigaba da kallon da ya samu ina yi, ya dade yana kallo na kafin ya dawo kan two sitter da nake zaune ya kira sunana a tausashe, kallon ne kawai nake yi amma ba abinda nake ganewa dan ƙwaƙwalwa

ta tafi tunani a kan makomar rayuwa ta har ban ji kiran da ya min ba seda sanyin hannun sa ya ratsa nawa tafin hannun.

Na dago da idanu na da suka canja kala saboda kukan da yake ci na na dube shi, ya zuba min ido shima cikin tashi damuwar

"Tunanin me kike yi haka har nake kiran ki baki ji ba?, In ni ne ai gani a kusa dake ko?".

Ya faɗa da yar tsokana dan ya dan yi cheering dina, na kau da kai gefe nace a sanyaye

"Yi hakuri, ban ji ka bane".

Wannan karon ba wasa ya juyo da ni saitin sa ya kuma kashe kallon ta yadda zamu saurari juna sosai

"A kwanakin nan sam na kasa gane miki Aimah, kin canja sosai ta ɓangarori da dama, ga damuwa da nake gani kusan kullum tattare da ke, kuma in na tambaye ki se kice min babu komai, shin baki yarda da ni bane ko kuwa ban kai na ji damuwar ki bane?".

"Ba abinda yake dd......".

Tun ban kai karshe ba ya katse ni da sauri

"Kar ki ce min babu abinda yake damun ki dan ko duka jiki na kunne ne ba zan taba yarda ba, na san ki tun kan ki san kan ki dan haka na san kina da damuwa, ki wa Allah da Annabi ki sanar da ni ko menene, kar ki ja zawa kan ki wani ciwon da wannan yawan tunanin, in haja ya faru ban san me zan cewa iyayen mu ba, ba kuma zan yafe wa kai na ba".

Na tsira masa ido ina kallo, zuciya ta na tunzura ni nayi masa maganar da ke cin raina kusan kullum, dan haka na dube shi

"Ka yi min alkawarin tsakanin ka da Allah ko me na tambaye ka zaka fada min gaskiya?".

Da sauri ya shiga gyada kai

"I promise you zan fada miki Barbie in har na sani".

Seda na runtse ido sannan na iya yin kundumbalar fadin tambayar da nake bukatar amsar ta, daga amsar ne kuma zan gane irin gurbin da Masdooq yayi min a rayuwar sa

"Shin kana tausayi na ne? Kana tausayin rayuwar da nayi shekara biyar baya da shekarar da ta wuce shida kenan, shi yasa kake nuna min kulawa da bani lokacin ka?".

Tambayar ta zo wa Masdooq a hagunce, ya zuba min ido dan be gane me nake nufi ba, nima kuma na ja baki na tsuke se bin shi da kallo da nake yi zuciya ta na dokawa da irin amsar da zan yi samu daga gare shi.

A cikin ran sa yayi wa maganganu na fassarar da abinda yake gani shi nake nufi dan haka ya gyara zama

"Ina tausayin ki matuka Aimah, fiye da duk yadda zaki yi tunani ko hasashe, soyayyar ki da tausayin ki yasa kike da gurbi me girma a rayuwa ta, kuma su suka sabbaba min baki kulawa da lokaci na, dan fanshe miki damuwar da ina cikin wadanda suka sa ki ciki, ke abar tausayi ce gare ni Aimah dan mace kike me rauni, mata ta, uwar yarana, haka kuma yarinya karama da ta shiga wa i hali a cikin kananan Shekaru ".

Daga haka ya zuba min ido yana min duban 'na amsa tambayar ki'.

A gare ni kuwa nan da nan na samu amsar da dama na san ita zan samu, tausayi na yake ba so ba, a matsayin kanwar sa, matar sa, uwar ƴaƴan sa kuma yarinya karama yasa yake tausaya min, tausayin ne kuma ya sa ya kawo ni cikin rayuwar sa ba wai soyayya ba, shiyasa yake min duk abinda yake min, ita matar sa da soyayya ce tsakanin su ai ina ganin banbanci a fili na matsayi da kulawa.

"Me yasa kika tambaye ni?".

"Saboda na san matsayi na a rai da rayuwar ka, kuma alhamdulillah na sani, na gode sosai".

Yana niyyar bude baki yayi magana se ga tashin ikama na sallar Isha, wanda bama mu ji kiran ba, se ya hadiye maganar da ze yi ya tashi ya tafi masallaci.

Ni kam ina salla ina kuka, ina godiya ga Allah na wannan jarrabawa tasa gare ni, da kuma fatan in cinye ta.

Ko da na idar se kawai na nemi waje kan bed nayi kwanciya ta, da na ji shigowar sa ma ban tashi ba na ja abin rufa kawai na rufe kai na gaba daya, har ya shigo dakin ina a haka, ya zauna bakin gado yace

"Tashi muyi magana Nu'aimah".

"Bacci nake ji, ka bari next time in ka dawo daga daya gidan mayi".

"Ki tashi muyi magana nace".

Ban ko motsa ba nace

"Nace ka bari next time".

"Ki tashi nace muyi magana Nu'aimah Bashir, kar ki bari na yi loosing control a kan ki".

Ya fadi cikin kaushin murya da bacin rai, ai ban san sanda na tashi ba se gani na nayi zaune tunkurkur.

Ya zuba min jajayen idanun sa da ban san me yasa suka canja launi ba yace

"Me kike nufi da tambayar da kika min dazu?, Har ma da bakin sauye sauyen da kika kawo tsakanin mu?".

Take idanu na suka ciko da ruwa

"Saboda na san matsayin da ka aje ni a rai da rayuwar ka, kuma ka fada min dazu na ji, yanzu na sani, na san hurumi na da iyaka ta, kaga sai na dena wahalar da kai na da zuciya ta akan ka, na tsaya iya matsayi na wanda ka aje ni.

Sauyi kuma ni ban kawo sauyin komai ba, kawai nayi maka abinda kake so ne da ka kasa faɗa".

Ban sani ba, yanayin kallon fuskar sa na mamaki ne, confusion ne ko kuwa bacin rai ne ba zan iya cewa ba, abinda na sani kawai da kyar Ya bude baki yace

"Wane matsayi ne kika fahimci na aje ki a rayuwar tawa, ina bukatar jin sa.
Shima abinda nake so na kasa fada din da kika yi min, ina son sanin sh yanzu ".

A lokacin ji nayi it's high time na amayar da abinda ke cikin ciki na yana damu na yana kuma hana min nutsuwa, ko zuciya ta zata zauna waje daya daga kai kawo tunanin da take yi

"Matsayin kanwar ka abar tausayi, matar da tausayi yasa ka dawo da ita cikin rayuwar ka ba wai dan kana so ba, uwar ƴaƴan ka da ka rufawa asiri ja tausayawa ka dawo da ita cikin gidan ka dan ta rayu da ƴaƴan ta, wannan shine matsayin da ka bani a cikin rayuwar ka Masdooq da na dade ina neman sani, ka kuma taimaka sanar dani dazu.
Abinda kake so kuma ka kasa faɗa shine yin nesa da ni, rashin son kusanci tsakanin mu, baka son zama da ni kana tursasa kan ka ne, ko ba haka bane".

Jan da idanun sa suka yi a yanzu kuwa duk yadda na kai ga kokarin dakewa seda na tsorata da watsa min su, yana bani wani kakkausan kallo yace

"Ban san me nayi ko na aikata ba daidai ba da Allah ya jarrabe ni akan SOYAYYAR KI NU'AIMAH, ban san ko munin laifi na ne Allah yasa na fada hannun ki ba, a farko nayi tunanin komai ya kare ya wuce ashe ba haka bane jarrabawa ta yanzu ta fara.

A farko na wahala da soyayyar ki da tunanin kina so na, na aure ki da tunanin zama dake na har abada se kika nuna min ke wani ne a ran ki ba ni ba, na rabu dake a lokacin da nake cikin tsakiyar a kogin son ki, ba dan na dena son ki ba se dan sama miki farin ciki, babu zato babu tsammani Allah ya sake dawo dake cikin rayuwa ta a karo na biyu, tsoron ki da fargabar ayyuka da kalaman da zasu iya fitowa daga bakin ki zuwa gare ni sanin yadda bakya so da kauna ta yasa na nisanta kai na da ke, na kuma ke yin abinda ya ke kona zuciya ta a gare ki duk sanda wani abu ya kusan ta mu wato hantarar ki, daga baya na gane ina cutuwa fiye da ke akan hakan dan ko digo na kaunar ki be bar raina da zuciya ta sun huta ba face ninkuwa da yake yi a koyaushe, na dena se dai na kasa rabar kusa dake dan kiyaye furucin rashin kauna daga bakin ki, zuwa lokacin da na gane hakan kuskure ne na aikata babba, na kuma sauka daga kan turbar koyarwar addinin mu, na nemi yafiyar ki kika yafe min, sakin fuska da kuma yafiyar ki gare ni yasa naji kamar komai daya faru mara dadi ya wuce, yanzu lokaci ne nayin farin ciki da samun martanin so da kauna daga gare ki, ashe nayi kuskure Aimah?, Ashe har abada ba zaki taba barin zuciya ta da gangar jiki na su huta ba?, Yau ke kike questioning so da kauna ta gare ki har kina kwatanta shi da mere tausayi, tausayi dai tausayi?, You've hurt me by downgrading my feelings toward you, you have hurt my feelings Aimah, You've hurt me, kin cutar da ni Aimah, kin zagi soyayyar da nake miki, Ya Rabb ".

Abin da ban taba tunani ko zato ba, hawaye ne suka shiga bin kuncin jarumi na a lokacin, hawayen da suka rikito da dukkan wani tashin hankali na duniya da lahira a gare ni, na give na dimauce, me yasa na kasa fahimtar sa, me ya sa na kasa gane soyayyar sa a gare ni, me yasa ko wace cutarwa me taba zuciyar sa daga gare ni take fitowa, wane irin tunani ne da ni, wace irin zuciya gare ni mara adalci, ya hayyu ya qayyum na shiga uku.

Se kawai na rushe da kuka, irin me karfin nan da ke hana bawa iya magana, tausayin Ya Masdooq da soyayyar sa na sake ambaliya a zuciya ta, ina jin na tsani kai na da jefa shi cikin wannan hali.

Ya sa hannu ya share hawayen da suka zubo masa kana ya mike cikin nauyin jiki dan fita daga dakin, ba ze iya tsayawa yana sauraren kukan ta ba, hakan tada mai hankali yake, shi ya rasa wace irin zuciya gare shi da a cikin kowane hali bata fasa so da kaunar Aimah, ya rasa wane irin kulafuci ne haka na zuciyar sa da ta kama Aimah ta kankame, sedai ya sani hakan jarabawar sa ce daga ubangiji, ze kuma yi kokarin ya cinye ta insha Allah.

Da wani irin karfi na afka ma bayan sa, na sa hannuwa na na rukunkume shi kam, cikin azababben kuka na nake cewa

"Ban taba kin ka ba wallahi, ban taba tsabar ko ba ko da na sakan daya ne, shirme, shiririta, yarinta da kuma sharrin shaidan suka sa a wancan lokacin na kasa gane kai kadai ne wanda nake so da kauna, kai kadai ne namijin da na mallakawa soyayya ta, ban farga ba har se da nayi wa kai na sakiyar da ba ruwa na raba kai na da kai, a wancan lokacin halin da na shiga bana ko san tunawa, a kuma lokacin ne na farga da kaunar ka da ta mamaye min ko ina na zuciya ta, duk namijin da na gani se in ga ai be kai ka ba, ta kowane fanni a zuciya da idanu na

gaba kake da daukacin maza, sedai ya zan yi bayan na riga na bar kari tun ran tubani, na sani a lokacin ka riga ka rufe babi na, ka aje littafi na a gefe tun da har kayi aure kana da mata, tuna sunan kana da mata kadai is killing me Masdooq, Ian tsananin son ka da kishin ka shiyasa hatta gidan Hajiya Yayah na kaurace masa dan bana san ganin matar ka ko kai, ganin ka a matsayin na wata ba nawa ba ze iya sawa na hadiye zuciya na mutu.
Kaddarar da ta sake hada mu a karo na biyu baya zo min da sauki ba, na shigo gidan ka kirji na cike da soyayya gare ka, sedai ka nuna min kiri kiri babu wata mai suna Aimah a littafin rayuwar ka, matar ka ta fada min ni ba kowa nace gare ki a lokacin face matar cushe, nima kuma na sani haka din ne, kunya da tarin nadama suka hana ni bayyana soyayya ta gare ka, se kuma kai ma ka nuna min baka bukatar duk wani kusanci tsakanin mu, ka nuna min ni din nayi katsaladan ne ga rayuwar farin ciki da kaunar ku, wannan yasa na hadiye duk wani so da nayi burin bayyanawa, na sawa raina for once zan maka adalcin barin ka da matar da kake so, shiyasa na takure rayuwa ta a waje daya, komai da ya faru daga nan in dai daga gare ka ne ina daukar shi ne a rashin kauna da so, na yafe maka ne dan ba zan iya fushi da rai daya da zuciya take wahala akan shi ba, na kuma roki taka yafiyar da neman mu dawo kamar da dakai dan in dinga samun relief ko da da ganin ka ne, ko kuwa da kulawar ka gare ni ko da kuwa ba ta sigar soyayya bane.
Na so barin rayuwar ka gaba daya, duk da na san xan cutu matuka amma a tunanin na barin ka da matar ka da kake so shine sakayya mafi kyau da zan maka wadda zata tabbatar da kaunar da nake maka, sedai Dr ta nunain hakan kuskure ne, ta nuna min ai kana so na, ni kuma na kasa yarda da kalamanta sanin tuni ka samu madadi na, ta tabbatar min da zancen ya da fadin in yadda in dawo gare ka zan samu tabbacin daga bakin ka ko ayyukan ka, sedai maimakon tabbacin soyayya se na samu akasin haka, Ya Masdooq tsayin watan mu daya da rabi da shigowa gidan nan matsayin ma'aurata baka nemi komai daga gare ni ba kamar yadda kowane namiji yake nema daga matar auren sa da yake so, banda romance babu abinda ke shiga tsakani na da kai, a farko na zata ka bar ni ne na huta ko kuwa mu kuma samun kusanci tsakanin mu, se daga baya na fahimci ba haka bane, Ni din ce baka bukata, saboda dalilin da ban sani ba, shiyasa zuciya ta ta bar min as saboda baka so na ne, namiji na tara wa da macen da yake so ne kaɗai, dan haka kayi min a zaman mu kafin haihuwar twins, bayan haka abubuwa da dama dake faruwa na yadda kake daukar Sa'adah da muhimmanci fiye da ni ya sake tabbatar min da hakan, shiyasa na tambaye ka da tunanin zan iya jin akasin sakar zuciya ta, amma se ka tabbatar min hasashe na daidai ne akan ka, kana zaune ne da ni bisa doron tausayi ba SOYAYYA ba, fada min Ya Masdooq yaya kake so nayi?, Yaya kake so nayi reacting? Ya kake tunanin zuciya me rauni da ta kwallafa rai ga soyayyar wani ɗa namiji tilo zata ji lokacin da ta tabbatar babu makamancin wani abu wai shi so a tasa zuciyar a kan ta???".

Na karashe ina sake rushewa da kuka, irin wanda zan iya rantse wa ko lokacin da nake cikin wancan halin na kaka na kayi ban yi shi ba.

In a slow motion, kamar wanda ba shi da laka a jiki ya juyo da ni muna fuskantar juna, idanun sa har lokacin jan da sukai be ragu ba, ya sa hannayen sa duka biyu ya kama each damtse na, yace cikin raunatacciyar Muryar da ban taba jin shi da ita ba

"Ban taba daina son ki ba, ba kuma zan daina ba har abada, kamar yadda na fada miki tsoron furucin ki da aikin ki yasa na nisanta kai na dake.

A yanzu kuma ban ki kusantar ki ko neman hakki na na miji a kan ki dan rashin so ba, na yi ne dan baki lokaci ki saki jiki da ni, ki aminta da ni a matsayin miji, ki kuma yarda zaki yi spending ragowar rayuwar ki dani, wannan shine dalili na, wanda Allah ne shahidi ba karamin kokari nake ba wajen danne duk wani sha'awar ki Wada soyayyar ki ke sake rurawa wuta cikin jini na, ban taba tunanin zaki fahimci hakan ta wani siga ba, da ban fara ba, da kuma nayi magana dake baki da baki akan haka, amma yanzu kin ji dalili na, ina kuma neman yafiya da afuwar ki akan haka, ina kuma fatan zaki goge wancan gurguwar fahimtar da kika min a ran ki".

Na tura baki gaba, fuska jage jage da yawa, kwallin idanu na duk ya zazzago saboda kuka nace

"To su kuma sauran abubuwan fa, kalla fa ni da safe kake zuwa min in kana gidan ta, a tsaitsaye muke gaisawa saboda kada ka makara, amma ita a ranar girki na da yamma kake zuwa mata kuma baka dawowa se bayan magrib ".

Be amsa ba da farko se kallo na da yake, a ran sa yana ayyana tabbas Barbie ta fi Sa'adah kishi, rashin dama da bata sami ba ne ya danne hakan, sedai insha Allah ze yi iyayin sa daga yanzu ya ga be yi abinda ya motsa wannan zazzafan kishin nata ba.

"Saboda hanyar gidan ta hanya daya ne da nasu Hajiya Yayah, shiyasa nake zuwa da yamma mu gaisa daga nan na wuce can na gaida su Mama, a wajen su nake yin magrib tare da Baba kana na dawo nan, dan in nace da safe zan je zan makara kafin na kai office, kin yarda da bayani na?".

Da sauri na gyada kai, sam da kishi ya rufe min ido kwata kwata ban kawo haka ba, kunya ta kama ni na sada kai na kasa, shi kuma yayi yar dariya kadan, ya ja ni cikin jikin sa ya rungume, dukan mu se da muka sauke ajiyar zuciya saboda kewar kuna da muka yi dan na hana mu kin dumin juna saboda wani banzan tunani na, na lafe a jikin sa kamar wata yar mage, shi kuma yana ta shafa bayana kan sa akan gashi na idanun sa a lumshe.

Mun dade a haka kafin ya kai bakin sa wajen kunne na

"Ango nake yau ko Barbie?".

Da sauri na sake kankame shi kunyar kai na da kai na na kama ni, se lokacin na shiga tambayar kai na shin me na aikata ni Nu'aimah, wai da gaske ashe kamar yadda ake fada ina da wautar autanci? Lallai yau na yarda.

Dariya yayi min ya ja ni toilet, duk yadda na so xillewa be bar ni ba se da muka yi wankan tare, ya nado ni cikin towel ya dauko ni kamar wata jaririya, da hannu daya ya kashe hasken dakin kana ya kwantar dani kan bed shima ya bini.

Soyayya iya soyayya Ya Masdooq ya gwada min ita a wannan daren, duk wani damuwa, shakka, tsoro da fargaba se da ya tabbatar ya kau min da su daga zuciya ta, ya shayar da ni madarar soyayya ziryan babu sirki, be bar ni ba se da ya cika min zuciya da dimbin farin ciki da alfaharin samun sa a matsayin miji, abokin rayuwa kuma uban ya'ya gare ni.

Washegari tattalin da yake nuna min da kulawa har kunya suke bani, soyayya kuwa kamar ze haukata ni, ririta ni yake kamar kwai akan cokali, har se da ya koma yana bani tausayi, lallai na yarda na amince soyayyar Masdooq gare ni is unconditional and unfadable, itace cikakkiyar ma'anar true love.

Na tabbata matukar son da Masdooq ke min, ya ninninka nawa, nawan banza! Duk wani motsi idan na yi zai ce ya ya?, In kuwa yana office se na gaji na tura masa text din ya maida hankali kan aikin sa na kashe waya ta kafin yake nutsuwa, soyayya ce da ya dade a cikin ta yake kuma shan wahalar ta, tashi daya se wahalar nan ta juye zuwa zakin da yafi zuma gamsarwa, shiyasa gaba daya se ya nemi rikice wa.

A kwanaki ƙalilan muka yi shar da mu, mun kara murjewa da haske kamar wanda aka ciro daga inji, Aunty Luba da tazo ta dinga santin yadda na koma, haka ma su Aunty Siddiqa, Hajiya Yayah kan su murnar su bata buya ba da naje gaishe su, hatta Baba se da yace

"Tubarkallah ƴata hankali ya kwanta, Allah ya kara muku zaman lafiya da hakuri da juna".

Mama kuwa duk in da nayi haka take bina da ido, ya Masdooq kam ta sake kama shi ta rike kam, dan tace shine ɗan ta, ni kam ta Hajiya Yayah ce.

So daya naje gidan Sa'adah, lokacin ta yi wani rashin lafiya naje duba ta, ina ganin yadda take bina da ido, sa'i da lokaci kuma ta kan share hawaye, ni dai a raina nace ohon miki, sharri ne kika yi kuma kin ga karshen shi, dan a gaban ta Ya Masdooq be iya ya boye so da kulawar sa gare ni ba, shi ya bani ruwa ya zubo min abinci, da na ce bana jin yunwa kuwa yayi ta lallashi na na daure na ci baya sa zama da yunwar da na koya yanzu, a lokacin juya mana baya tayi, se kuma ta bani tausayi, tabbas da ciwo ace kana son namiji shi kuma soyayya, kulawa da hankalin sa na kan wata, dan haka na taka masa burki ta hanyar nuna mqsa ita da girgiza kai, shima da ya fahimta se kawai ya bar mana gidan.

Tun daga ranar ban kuma zuwa ba, se lokacin da ita tazo, a cewar ta tazo neman yafiya ta, ban ja da nisa ba na yafe mata, to meye amfanin rikon ba yan ta ko ina Allah ya gama min komai, princess kuwa tana zuwa min weekend dan ni kadai ce a gidan kamar mata, twins Mama da Hajiya Yayah sun kwace mana su, shine yake tsokana ta wai na yi zuciya na haifo mana namu, nace kuwa ba yanzu ba.

Daga baya se na koma zuwa wajen sana'a ta da tuni aka gama gyarawa har an debi sabbin ma'aikata sun fara aiki, a sati so biyu nake zuwa, se kuma wajen snacks dina da shima aka gina

min mafaidaicin waje, shima tashi ɗaya nace a samin #Asaimah bakery, lokacin ne Ya Masdooq ko ince sweetheart dina ya nemi jin ma'anar sunan, ko da na sanar masa kuwa irin godiyar ya min ta hanyar soyayyar da ya gwada min ranar ba abin da zan manta kwana kusa bane.

Aunty Luba ta kawo min kayan gyaran da ta siya min wajen SURAYYA HALIN YAU, yadda na ga kyan su da ingancin su yasa na zama customer ta sosai ga matar, ga kirki ga fara'a ga kuma haba haba da jama'a.

Ta ko ina rayuwa ta yi min daidai alhamdulillah, a ko da yaushe godiya kawai nake ga Allah da ya Ara min dama ta biyu dan gyara kuskure na, be bar ni da iyawa ta ba kuma ya tsaya min, alhamdulillah ya Rabb.

******TWO YEARS LATER*****

Ina jin shi yadda ya lafe a baya na kamar wani Maraya, ko da yake ai marayan ne, wanda ya rasa mata ai a kira shi Maraya in dai da kara.

Yau kwana hamsin da biyu da rasuwar Sa'adah Allah ya jikan rai, sanadin ciwon ta na Cancer da duk ba mu san da shi ba se ana saura kwana biyu ta rasu, Aunty Hauwa maman ta ta sha kuka lokacin da taji deadly cutar da ƴar ta ke dauke da, nima na tausaya mata matuka dan wallahi yadda na sha kuka kunce yar uwa ta ce ba kishiya, gaba daya na manta da abinda ya faru a baya, tausayin ta kawai nake yi, addu'a ba kalar wadda ban mata ba, sedai shi ciwo in na tafiya ne se hakuri.

A kasar India ta rasu sun tafi da ita ganin yadda jikin ya rikice, sedai a nan aka mata sutura aka binne ta, tun bayan rasuwar kuma ya canja min, baya min magana, ko me zan ce se dai uhm da uhm uhm.

Na masa uzuri a lokacin dan tabbas yana cikin tashin hankali, sedai har aka yi arba'in be canja ba, ni kuma na gaji da halin sa, abinci ze ci, amma ba magana, in muka zo kwanciya se ya juya min baya, haba jama'a, kamar ni ce na kashe masa mata, se na fita harkar sa, lallashin da nake masa kamar wani jariri na dena, duk a jiya kenan fa, da dare na kwanta kawai na ga ya juya min baya, nima da zuciya ta ciyo ni se na sauka na bar masa dakin na koma dayan, ina shiga kuma na saka key.

Ina jin sa yazo yana bugu da kiran suna na na mai banza, ince dai space yake so, to na bashi, ni da na kashe Sa'adah da baya san gani to na bar masa dakin.

Ban bude ba se da zan fito dora breakfast wato yanzu, shine ya biyo ni kitchen din ya lafe min a baya, hannayen sa kan matashin ciki na dan wata hudu, ban kula shi ba na cigaba da aiki na, se da na gama komai na dauka a tray xan kai dining ya karbe tray din ya aje, kawai ya hade fuskar mu ya shiga sumbatar duk inda bakin sa ya kai dan na datse baki na denying him the

access to my mouth.

Kuka na fashe masa da shi, nan da na kuwa ya rude ya hau furta kalmar sorry kamar ze ari baki.

Na shiga bubbuga kafa a kasa ina cewa cikin kukan da ya fi kama da na shagwaba shagwaba gaskiya gaskiya

"To ni me nayi maka, kawai ka dena min magana, ka dena kula ni, a bed se ka juya min baya irin ki ci kan ki din nan, in ba ka so na ne yanzu se in yi addu'a nima kawai in mutu in huta".

Aikuwa na karasa rikita bawan Allah, wane irin mutuwa a na zaune kalau, murya na rawa yace

"Kul, kar ki kara, bana so ko da wasa ki kuma kiran wai ki mutu, in kika mutu ni kuma fa, wallahi kika mutu nima se na biki mun mutu tare".

Dariya ya bani yadda yayi maganar, ganin dariya ta se ya sake rungume ni dan ya san maganar kuma ta mutu, na sauko daga fushin, dama ni ban da riko balle kullaci.

Mun dade a haka kafin yace

"Ina tausayawa Sa'adah matuka ne Aimah, ta sha wahala akan soyayya ta yayinda ni kuma kece a raina, ta same ni kuma ya zama ciwo yayi mata cika, ko kin san princess ba yar Sa'adah bace saboda an cire mata mahaifa dalilin Cancer?, Ta mutu bata taɓa haihuwa ba, bata bar baya ba, bata bar me yi mata addu'a ba, wannan ne yake taba ni in na tuna, ina sake tabbatar Miki wallahi Sa'adah has a good heart, all that happened a baya sharrin shaidan ne, kishi da kuma zuga, dan Allah ki yafe mata Barbie ".

"Ta fada min, ta sanar da ni yadda kuka samu princess tun kan ta rasu, ban fada maka bane jin baka sanar min ba, kuma ka daina cewa bata bar baya ba, twins ƴaƴan ta ne, haka ma duk abinda zan haifa a gaba, zamu sanar da su suna da wata Mamy da ta rasu me kirki, zamu dora su kan turbar yi mata addu'a, insha Allah ta dace a inda take, Ni kuma tuni na manta da komai da ya faru, Allah shaida na dade da goge komai a raina tun bayan da na yafe mata".

Sweetheart ya kankame ni cike da farin ciki kalamai na, wanda ni da gaske har zuciya ta haka nayi su, yayi min godiya ta hanyar da yafi kwarewa akai, nima na amsa shi ta irin martanin da yafi so.

Rayuwar mu tayi kyau, kamar kuma yadda nayi alkawari haka na sa Mama ta dinga sanar da twins yi wa Mamyn su addu'a, Hajiya Yayah ma na fada mata, se gashi hakan be musu wuyar rikewa ba.

Watan ciki na biyar sweetheart ya dauki hutun wata biyu muka tafi SEOUL babban birnin

KOREA, mun huta sosai a can na sati biyu kafin muka wuce honey mooning kasar England, birnin Chesterfield muka yada zango. Daganan sai Derby da Reading-Berkshire.

Hutun amarci ne da ya buɗe sabon shafi a tarihin soyayyar mu. Kuma cikin kundin shafukan da ba zamu taba mance wa ba ko su goge daga kundin tarihin rayuwar mu.

Dawowar mu da wata uku na haife ciki na, muka samu baby girl kyakkyawa kamar yan uwan ga, wannan karon ma ni ta kwaso, sweetheart na ta zumbura bakin wai ba'a masa adalci ba, ni kuwa dariya kawai na ke masa, Mama na ta lallaba shi wai next da zan haifa dole ma ya zama replica din shi, a ranar da na haihu aka sallame ni dan ni da baby na muna cikin koshin lafiya, gidan Hajiya Yayah aka sauke ni, kullum kuma gidan baya rabo da yan uwana da ke zuwa safe da dare, matan su kuwa a nan suke wuni, Aunty Luba da Dr Bee'at da aka yi auren su da Ya Ahmad two years back har ma ta haifi babyn ta namiji me sunan Abba, sune tsaye akai na da duk wani abu da ya shafi baby, ga kuma uwa uba me gayya me aiki da ya tattaro shima ya dawo gidan Hajiya Yayah, tayi fadan ya gaji yace ba inda za shi alhalin matar sa da yar sa na nan, in ana so ya tafi a bashi abin sa, Mama ma kuma ta goya masa baya dan haka Hajiya Yayah ta fita batun su, kwana ana biyar da haihuwa Nene da Aunty A'i suka dira kasar, ko ta ina ina cikin gata da rahamar ubangiji, shiyasa bana taba gajiya da gode masa.

Ranar suna yarinya taci sunan SA'ADAH bisa zabin da aka bani, babu wanda be yi farin ciki da wannan halin dattaku nawa ba, Aunty Hauwa mahiafiyar Sa'adah me rasuwa da kuka da komai take gode min har se da ta sani kuka, akwati biyu tayi min tayi wa baby uku, dan tace wannan haihuwa ita aka yi wa.

Baba yayi ta wa min albarka, farin ciki na be wuce na ganin na farantawa ran da kullum ke hakilon faranta min ba, na rasa Abba na amma baba be bar ni nayi kukan maraici ba.

Saboda tsabar rashin ta idon da Ya Masdooq ke tsulawa a gidan nan yasa sati na uku Hajiya Yayah ta tarkata ni ta maida, Nene kuwa dama sati biyu tayi ta tai bayan ta hado min kayan gyara na su na gargajiya me inganci, Aunty Luba ma ta bangaren ta bata yi sanya ba haka ma Hajiya Yayah, ita dai Mama yar kallo da murmushi ce, sedai farin cikin ta a bayyane yake.

Muna komawa gida kuwa muka dora daga inda muka tsaya, soyayya da kauna mara algus make gwadawa juna, a duk sanda na kalli mijina ji nake yi kamar nafi kowace mace Sa'a, shiyasa ina addu'a yan matan mu da zawarawan mu Allah ya aurar da ku ga mazaje nagari, masu kaunar ku da gaskiya, wadanda zasu so ku a duk yadda kuke, sedai fa kwalelen ku, babu wadda zata taba samun miji irin MASDOOQ ƊIN AIMAH!!!!!!

TAMMMAT BIHAMDILLAH, ALHAMDULILLAHIL LAZIY BINIIMATIHI TATIMMUS SALIHAT.

Anan na kawo karshen littafin ba kowane so bane.....alkhairan da na rubuta a ciki Allah ya bani

lada, kuskure na kuma ina neman Allah ya yafe min.

Gare ku fans din ba kowane so bane, kwarai da gaske kun nuna min madarar kauna cikin tafiyar wannan littafi, ina addu'ar Allah ya saka muku da Alkhairi baki daya ya haɗa mu cikin alkhairan da ke cikin wannan rayuwa ya kuma tsare mu daga fitintinun ta.

Kaunar da nake muku ce tasa nayi muku bonanza na littattafai na na kuɗi, wanda dab take da karewa, gata kamar haka:

*KAR KU MANTA BONANZA IS YET TO END, JUST 1K AND READ 3 AMAZING NOVELS, YAR DAMFARA, RASHIN HAIHUWA AND ANJANE, KAR KU BARI A BAKU LABARI*

Ga duk masu bukata suna iya tuntubata a wannan lambar
09013101854

Nagode Nagode, se mun sake haduwa a cikin wata tafiyar, in har da rai da lafiya.
Bissalam, ouummey 📚✍️.